Fina-Finan Hausa Na 2000-2017: Nazarin Yanayinsu da Sigoginsu

Na

Ahmad Salihu BELLO

B. A, (1995) B.U.K , M. A, (2006) B.U.K , P.G.D.E, (2007) N.T.I

P16ARAL9054

A Thesis Submitted to the School of Postgraduate Studies,

Ahmadu Bello University, Zaria, in Partial Fulfilment of the Requirement for the Award of

Doctorate Degree in African Literature (Hausa), Department of African Languages

And Cultures, Faculty of Arts, Ahmadu Bello University, Zaria.

Nigeria

2018

Sadaukarwa

Na Sadaukar da wannan aiki ga Mahaifina Marigayi Malam Salihu Bello Wudil, wakilin Dagacingarin Garindau, Kano, tare da duk wani Malami da ya koyar da ni karatu na ilimi, da kuma iyalaina.

Declaration

I hereby declare that the work in this thesis titled “Fina-Finan Hausa Na 2000-2017: Nazarin Yanayinsu da Sigoginsu” (Hausa Films of 2000-2017: An Analysis of Their Forms And Features)was performed by me in the Department of African Languages and Cultures, under the supervision of Dr B.S.Y.Al-Hassan, Professor Magaji Yakawada Tsoho and Dr Haruna Aminu. The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. No part of this work has been presented for another degree or diploma at any institution.

Ahmad Salihu Bello Sign…….. Date…….

Certification

This thesis titled "Fina-Finan Hausa Na 2000-2017: Nazarin Yanayinsu da Sigoginsu"(Hausa Films of 2000-2017: An Analysis of Their Forms And Features) meets the regulations governing the award of the degree of Doctor of Philosophy of the Ahmadu Bello University, and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

Dr. B. S.Y. Al-Hassan, Signature……
Date……..

(Chairman, Supervisory Committee)

Professor Magaji Yakawada Tsoho, Signature…….. Date……
(Member, Supervisory Committee)

Dr Haruna Aminu, Signature …… Date……
(Member, Supervisory Committee)

Dr Salisu Garba Kargi,Signature…….. Date……
(Head of Department)

Professor Sadiq Z. Abubakar, Signature……. Date……
(Dean, School of Postgraduate Studies)

Godiya

Godiya ta tabbata ga Allah maxaukakin Sarki, mai kowa mai komai, Allah wanda babu wani abin bautawa da gaskiya sai shi. Tsira da aminci su tabbata ga Annabi Muhammad Sallallahu alaihi wasallam.

Malamaina dake Jami'ar Ahmadu Bello Zariya ba ni da wani abu da zan ce illa Allah ya biya muku dukkanin buqatunku duniya da lahira musamman: Farfesa Xalhatu Muhammad, Allah ya qara masa lafiya da Dr B. S.Y Al-Hassan da Farfesa Magaji Yakawada Tsoho da Dr Haruna Aminu Na gode a bisa jagoranci da kuma haqurida kuka yi da ni lokacin gudanar da wannan aiki. Farfesa Muhammad Lawal Amin da Dr Salisu Garba (H.O.D) da Farfesa Balarabe Abdullahi, sun ba da gagarumar gudunmowa ta musamman wajen an samu mafitar da ta kai shi ga gacci. A gaskiya ba abin da zan ce da su, illa, Allah ya raya zuri'arku ya biya muku dukkan buqatunku duniya da lahira.

Ba zan manta da Dr Shu'aibu Hassan ba, jami'in da ke kai kawo a kan harkokin karatunmu na wannan sashen (P.G Co-ordinator), ina godiya a bisa yadda ya yi ta ba ni shawarwari musamman wajen tsara tambayoyin bincike na wannan aiki da kuma shawarwari daban-dabanmasu amfani. Jinjinata ga Dr Hauwa Bugaje; ta cancanci yabo da kuma godiya ta musamman, haqiqa mukan zauna da ita a lokuta da dama domin tattaunawa a kan yadda za a tsara wannan aiki, takan ba da shawarwari bakin gwargwado. Hakazalika, abokan karatuna a matakin digirin qoli ya kamata in gode musu musamman, Dr Aliyu Isa Sulaiman, shugaban Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya na

Jami'ar Jihar Kaduna, wadda ya taimaka min qwarai da aron littattafai da kuma ba ni shawarwari. Kazalika, godiya ga sauran abokan karatuna irin su Dr Tahir Rabi'u na Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello Zariya da Malam Sama'ila Jibrin na Kwalejin Ilimi ta Akwanga. Ina godiya ga Dr Sambo Aminu na (Institute of Education, A.B.U Zaria) da kuma Malam Sarki Muhammad na sashen Harsunan Afrika da Al'adu, Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya, haqiqasun taimaka min wajen ba da shawarwari da kuma qwarin gwiwa a kan wannan aiki don ganin ya hau turbar da ta dace.

Godiyata ga mahaifina da ya ba ni tarbiyyar neman ilimi na addini da na boko, tare da ba ni duk wani goyan baya domin ya ga na cimma wannan buri na kammala wannan karatu, addu'o'insa a kaina sun yi tasiri qwarai da gaske. Sai dai kuma Allah bai nufa zai shaida sakamakon wannan aiki ba, Allah ya jiqan sa da rahama.

Har a kullum, nakan yi alfahari da malamaina da suka koyar da ni karatu tun daga matakin Firamare har zuwa Jami'a.Ina mai yi muku jinjina da godiya ta musamman a bisa koyar da ni da kuka yi, tare da sa ni a hanyar ilimi, har Allah ya sa na kai inda na kai a yau, a mastayina na magajinku. A firamaren Wudil *Special School* inagodiya ga Hedimastanmu Malam Hassan Biu da malamina na musamman a aji Malam Nasiru Muhammad Wudil. Godiya ga abokinaInjiniya Aminu Aliyu Wudil, wadda a yanzu kwamishina nena ayyuka da gidaje da sufuri na Jihar Kano, wanda shi ma ya yi ta ba ni shawara da qwarin gwiwa don na yi wannan karatu na digirin qoli. A sakandare godiya ga shugaban makarantarmu kuma babana Malam Tijjani Adamu Dirimin Iya, wato Kwalejin Horar da Malamai da ke garin Haxejia da Malam Muhammadu Yaro Musa da

Malam Bello Ballama Birniwa da Mr Cosmos Nzegbule. A matakin Jami'ar Bayero, Kano, godiya ga malamaina da suka koyar da ni a matakin digirin farko da na biyu su ne: babana Farfesa Sammani Sani, godiya ta musamman ga Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau da Farfesa Lawal Xanladi Yalwa da Farfesa Muktar A. Yusuf da Dr Ahmad Magaji da Farfesa Aliyu Mu'azu duka a Jami'ar Bayero, Kano.Kafin in kammala, ina miqa godiya ta musamman ga malaman sashen koyar da Hausa, na Kwalejin Ilimi ta Tarayya da ke nan Zariya da sauran ma'aikatan (sashen non-teaching staff) da kuma mai gayya mai aiki shugaban Kwalejin Dr A.A. Ladan da mataimakinsa Dr. Sulaiman Balarabe sun yi ta jan hankalina a kan in maida hankali wajen binciken nan domin sun taimaka min da addu'o'insuda kuma ba da shawarwari a matakai daban-daban. Abokai nagarinmu Wudil, ina godiya da qwarin gwiwa da suka ba ni, musamman Abdullahi Maikano da Ahmad Guda da Kabiru Ali Garindau da sauransu.Ba zan manta da aminina Abdullahi Salisu Kademi ba, shi ma ya cancanci yabo, kullum burinsa ya ji na kammala wannan karatu, to ga shi Allah ya amsa mana. Ina miqa godiya ga Malam Galadima na Kwalejin Ilimi ta Tarayya da ake Zariya, kusan kodayaushe in muka haxu zai ce ya batun karatu, a yi maza a mayar da hankali, Allah ya ba da sa'a. Godiya ta musamman ga Malam Haruna Abbas shugaban Sashen Hausa FCE Zaria, da sauran malamaida lokaci ba zai ba ni damar lissafa su ba. Abubakar Sulaiman Abubakar da Umar Nuhu Samaru waxanda aka yi ta qoqarin buga wannan aiki tare da su, Allah ya sakamusu da Alheri.

Na gode

A. S. Bello

Abstract

The Hausa films do face a lot of challenges from scholars, clerics and parents with regard to their theme, plot, costume, language, characters and characterizations. Whereas, some viewers argue that the films do not portray the customs, norms and values of Hausa society they claim to belong. While some of the producers and characters argue that there is nothing wrong in the films, because to them, they are putting in their best to educate, and entertain the society. As a result of the above argument, this research entitled "Hausa Films of 2000-2017:An Analysis of Their Forms And Features" attempts to study Hausa films with the view of passing an academic judgment. The research thereforeselected ten films from various perspectives and analysed them. Ethnography theory is the theoretical framework for the analysis of the data. The methodology used employsdescriptive method. Data for the research were gathered from thequestionnairesadministered and oral interviewswere conducted with the stakeholders and some scholars in the academia, alarge number of questionnaires were administered, those retrieved were used for analysing the data. The analysis of the data was based on the five basic features in studying films, which are adopted from Haruna (2012). The research was able to discover that some Hausa films lack originality in the storyline(plot), because they are an imitation of European or Indian cultures. Furthermore, some of the films portray other non-Hausa cultures within the Nigerian society. The research also identified that, what the producers are after is the monetary gains not the representation of Hausa norms and values. It was also discovered that a substantial percentage of the characters are non-Hausa natives and therefore most of the foreign cultures infused into Hausa films might have emanated from them. While a number of producers' only concern themselves with the monetary proceeds realized from the films.

Tsakure

Fina-finan Hausa na shekarar 2000 zuwa 2017 suna fuskantar suka daga wajen malaman addinin Musulunci da na boko har ma da iyaye bisa yadda ake aiwatar da su, ba sa bisa tsari na wakiltar al'adu da xabi'un Hausawa balle uwa uba addini wanda aka san Bahaushe yakan yi riqo da shi kodayaushe a cikin rayuwarsa. Kodayake wasu daga cikin masu sana'ar fim xin suna ganin babu wani abin qi a cikin fina-finan nasu, sun ce su dai suna ilimantar da al'umma kuma suna nishaxantar. Kash! Sai dai ba a nan gizo ke saqa ba, domin waxanda aka yin fim xin domin su har yau qorafe-qorafe suke yi a kan masu samar da fim xin da kuma masu taka rawa a cikin fim. Don haka, wannan bincike ya yi qoqari ya shigo tsakiya domin nazarin wasu fina-finan don a ware tsakuwa daga cikin aya. Hanyoyin da aka bi wajen yin bincike sun haxa da ginshiqan hanyoyi; inda aka tattauna da masana da masu ruwa da tsaki a harkarsamar da fina-finai irin su furodusoshi da daraktoci da jarumai har ma da 'yan kallo. Sannan akwai sauran hanyoyi da aka bi na raba bugaggun tambayoyin bincike ga masana, tambayoyin da aka karvo sun kai aqalla kashi 72% na duka tambayoyin da aka raba, an kumayi sharhinsu. An xora sharhin fina-finan da aka yi nazarin su a kan tsarin nazarin fina-finai na jigo fim da tsarin fim da harshen 'yan wasa da tufafin'yan wasa da halayyar 'yan wasa kamar yadda aka xauko a cikin Haruna (2012). Binciken ya gano yawanci fina-finan Hausa ba su da asali, wato wanki da xauraya ya mamaye kusan duka qullin labarin fim. Sannan sun fi mai da hankali wajen kwaikwayo fina-finan Turawa da na Indiyawa, har ma da na wasu qabilu maqwabtan Hausawa. Binciken ya gano da dama daga cikin masu aiwatar da fim xin asalin su ba Hausawa ba ne, don haka ba lallai ne su damu da kare martabar al'adar Bahaushe ba. Sa'annan da dama daga cikin masu samarda fina-finan Hausa wato furodusoshi sun fi mai da hankali wurin neman kuxi, ba kare tadar Hausawaba.

QUMSHIYA

Title Page……i

Sadaukarwa……ii

Declaration……iii

Certification……iv

Godiya……v

Abstract……vii

Tsakure……viii

Qumshiya……ix

BABI NA DAYA: SHIMFIDA

1.0 Gabatarwa…….....1

1.1 Manufar Bincike…….....4

1.2 Dalilin Bincike…….....4

1.3 Hasashen Bincike……5

1.4 Farfajiyar Bincike…….....6

1.5 Dalilin Zaven Fina-finan ……6

1.6 Muhimmancin Bincike……7

1.7 Kammalawa …….....8

BABI NA BIYU: WAIWAYE

2.0 Gabatarwa…….....10

2.1 Adabi…….....10

2.2 Al'ada……..…….....11

2.2.1 Nau'o'in Al'ada……...13

2.3 Qasar Hausa da IyakokintaJiya da Yau……..15

2.4 Sajewa Da Nashewar Al'adu……22

2.5 Fasalin Al'adun Hausawa……23

2.5.1 Addini…….....24

2.5.2 Tufafin Hausawa Na Gargajiya……26

2.5.3 Ire-Iren Tufafin Hausawa na gargajiya:……27

2.5.4 Aure a Qasar Hausa…….....27

2.5.4.1 Ire-Iren Aure…….....32

2.5.5 Haihuwa a Al'adar Bahaushe……...33

2.6 Fim …….....37

2.6.1 Rabe Raben Fina-finan Hausa…….……38

2.6.2 Samuwar Fina-finan Hausa……..39

2.6.2 Muhummancin Fim Ga Al'umma…….45

2.6.3 Dangantakar da ke Tsakanin Fim da Al'ada ……46

2.6.4 Fim A Afirka…….……47

2.6.5 Yadda Ake Shirya Fina-finan Hausa……47

2.6.6 Hanyoyin Nazarin Fina-finan Hausa ……50

2.6.6.1 Jigo …….....50

2.6.6.2 Tsari…….....50

2.6.6.3 ‘Yan Fim (‘Yan Wasa) ……51

2.6.6.4 Harshen ‘Yan Fim ……52

2.6.6.5 Tufafin ‘Yan Fim …….52

2.6.6.6 Kayayyakin Fim ……..54

2.6.6.7 Kwalliya ……54

2.6.6.8 Sauti ……..…….....55

2.7 Bambancin Da Ke Tsakanin Fim da Hausa da Kuma Fim Cikin Hausa…….…….55

2.8 Siffofin Fim Da Hausa ……..….57

2.9 Siffofin Fim Cikin Hausa …….58

2.10 Fim a Matsayin Wasan Kwaikwayo ……59

2.11 Bambancin Fim da Wasan Kwaikwayo …….……..61

2.12 Fim A Matsayin Adabi……..63

2.13 Adabi A Matsayin Taska …..…….……..65

2.13.1 Taskar Harshe…….....67

2.13.2 Taskar Al’ada…….…….....69

2.14 Zamantakewa A Al'adar Bahaushe……..74

2.15 Alaqar Fina-finan Hausa Da Habarce…….……..…….…..……..80

2.16 Fina-finan Hausaa Mahangar Qwararru…….……85

2.16.1 Addini…….....88

2.16.2 Al'ada…….....88

2.16.3 Waqa a Fina-finan Hausa……..……....……..91

2.16.4 Tasirin Baqin Al'adu a Cikin Fina-finan Hausa…….…..……92

2.16.5 Gudunmuwar Mata a Fina-finan Hausa……...102

2.17 Kammalawa …….....106

BABI NA UKU: HANYOYIN BINCIKE

3.0 Gabatarwa…….....108

3.1 Hanyoyin Tattara Bayanai ……..108

3.2 Ginshiqan Hanyoyi……...108

3.2.1 Ziyarar Garuruwan Qasar Hausa……..119

3.2.2 Rubutattun Tambayoyi Da Dabarun Tsattsafe su……..110

3.2.3 Tattaunawa Da Masana…….....111

3.2.4 Ganawa da Ma'abota Fim……...……113

3.2.4.1 Hira Da Furodusoshi…….…….120

3.2.4.2 Hira da Daraktoci…….…….....121

3.2.4.3 Hira da ‘Yan Fim Ko Jarumai……..123

3.2.4.4 Hira da Masu Kallon Fina-finan Hausa……..125

3.3.1 Sauran Hanyoyi…….…….....126

3.3.1.1. Xakunan Karatu …….....126

3.3.1.2 Kundayen Bincike da Muqalolin Qara wa Juna Ilmi……127

3.3.1.3 Ziyarar Kafafen Yaxa Labarai……..127

3.3.1.4 Kallon Fina-finan Hausa.……127

3.3.1.5 Ra’in Bincike……..…….....128

3.4 Hanyoyin Tace Bayanai……..……..130

3.4.1 Sharhin Tambayoyin Bincike…….....130

3.4.2 Sauran Hanyoyin Tace Bayanai……145

3.4.2.1 Qirqira…….....146

3.4.2.2. Asali…….....147

3.4.2.3 Wanki Da Xauraya…….……....149

3.4.2.4 Fassara…….....150

3.4.2.5 Kwaskwarima……..……150

3.4.2.6 Baddalawa…….....152

3.3 Tace Fina-finan Hausa Ta Bayan Fage …….…….153

3.3.1 Qirqirar Labari …….....154

3.3.2 Tushen Labari a Fina-finan Hausa……155

3.3.3 Marubucin Labari…….……....155

3.3.4 Furodusan Fim…….....156

3.3.5 Daraktan Fim……....156

3.4 Tace Fina-finai A Cikin Fage……..……157

3.4.1 Tarihi da Halayyar ‘Yan Fim……..…….158

3.4.2 Harshen ‘Yan Fim…….…….159

3.4.3 Kwalliyar ‘Yan fim…….161

3.4.4 Suturar ‘Yan Fim……163

3.4.5 Kayan Wasa.…….....165

3.4.6 Rawa da Waqa…….....167

3.7 Kammalawa…….....169

BABI NA HUXU: YANAYI DA SIGOGIN FINA-FINAN HAUSA

4.0 Gabatarwa…….....170

4.1 Tsokaci A Kan Fina-finan Hausa……171

4.1.1 *Bori*……..171

4.1.2 *Juyin Sarauta*……..……..172

4.1.3 *Qafar Ungulu*……173

4.1.4 *Na Hauwa*……173

4.1.5 *Malam Zalimu*…….…….175

4.2 Tsokaci Kan Fina-finai Da Hausa (Ba Al'adar Hausa Ba)……176

4.2.1 *Gwaska*……..177

4.2.2 *Ibro Hotiho*……178

4.2.3 *Qara'i*…….……180

4.2.4 *Su Ma Mata Ne*…….……..181

4.2.5 *Doya da Manja*…….……..182

4.3 Fina-finai Cikin Hausa A Mizanin Nazari……184

4.3.1 Zubin Fina-finai Cikin Hausa……184

4.3.1.1 *Bori*……..…….184

4.3.1.2 *Juyin Sarauta*…….……187

4.3.1.3 *Qafar Ungulu*…….189

4.3.1.4 *Malam Zalimu*…….……..190

4.3.1.5 *Na Hauwa*……..…191

4.3.2 Jigo A Fina-finai Cikin Hausa……193

4.3.2.1 *Bori* …….…….193

4.3.2.2 *Juyin Sarauta*…….……193

4.3.2.3 *Na Hauwa*…….…….194

4.3.2.4 *Malam Zalimu*…….194

4.3.2.5 *Qafar Ungulu*……..……..……195

4.4.3 Harshe ‘Yan Wasa A Fina-finai Cikin Hausa……195

4.4.3.1 Xin *Bori*……..196

4.4.3.2 *Juyin Sarauta*……197

4.4.3.3 *Malam Zalimu*……199

4.4.3.4 *Na Hauwa*……199

4.4.3.5 *Qafar Angulu*……201

4.5.4.1 Tufafin ‘Yan Wasa AFina-finan Hausa……...204

4.5.4.1 Xin *Bori*……204

4.5.4.2 *Juyin Sarauta* ……206

4.5.4.3 *Qafar Angulu*…… ...,207

4.5.4.4 *Na Hauwa*……207

4.5.4.5 *Malam Zalimu*……208

4.6.5 Halayyar ‘Yan Wasa a Cikin Fina-finan Hausa……..209

4.6.5.1 Xin *Bori*…. 209

4.6.5.2 Juyin Sarauta …….. 212

4.6.5.3 *Qafar Ungulu*…… 214

4.6.5.5 *Na Hauwa*…….. …215

4.6.5.5 *Malam Zalimu*……..…….. …218

4.7 Fina-finai Da Hausa A Mizanin Nazari……219

4.7.1 *Gwaska*…… 220

4.7.2 Xin *Ibro Hotiho*……..……221

4.7.3 *Qara'i* ……..……..…..…… 224

4.7.4 *Su Ma Mata Ne*…….……..…..…….. 226

4.7.5 *Doya da Manja*…….…….…… 229

4.8 Jigon Fina-finai da Hausa……...…..…….231

4.8.1 Q*ara'i*.…….…….……. 231

4.8.2 *Ibro Hotiho*…….…….……232

4.8.3 *Su Ma Mata Ne*……..…….233

4.8.4 *Gwaska*……..…….…… 234

4.8.5 *Doya da Manja*……....…….235

4.9 Harshen 'Yan Wasa A Fina-finai da Hausa…….…… 236

4.9.1 *Ibro Hotiho*…….……..236

4.9.2 *Qara'i*……..……...239

4.9.3 *Gwaska*…….…… 240

4.9.4 *Su Ma Mata Ne*…… …..242

4.9.5 *Doya da Manja*…….. ….243

4.10 Tufafin ‘Yan Fim A Cikin Fina-finai Da Hausa…… …245

4.10.1 *Qara’i.*…… …245

4.10.2 *Hotiho*…….. …247

4.10.3 *Gwaska*…….. ...248

4.10.4 *Su Ma Mata Ne*…… ..248

4.10.5. *Doya Da Manja*…… ..249

4.11 Halayyar ‘Yan Wasa A Fina-finai Da Hausa……. 250

4.11.1. *Hotiho*……. 251

4.11.2 *Qara’i*…….251

4.11.3 *Su Ma Mata Ne*……..……252

4.11.4 *Gwaska*……..…….....252

4.11.5 *Doya Da Manja*……..……..253

4.12 Kammalawa……..... 257

BABI NA BIYAR: KAMMALAWA

5.0 Gabatarwa…….....261

5.1 Naxewa…….....261

5.2 Kammalawa…….....263

5.3 Shawara……..... 270

Manazarta……..... 279

Rataye Na 1: Fina-finan Da Aka Nazarta Tare Da Sunan Kamfani..……..…..289

Rataye Na 11: Samfurin Bugaggun Tambayoyi.....…….292

Rataye Na 111: Taswirar Qasar Hausa…….293

BABI NA DAYA

SHIMFIDA

2.0 Gabatarwa

Adabi madubi ne da yake haskaka rayuwar al'umma. Adabi shi ne faifai da ake amfani da shi domin a baje kolin fasahar al'umma, wato gwanintarta a fagen harshe da al'adunta in ji Umar, (1987:5). Qarqashin adabin ne ake tantance yadda al'umma takan aiwatar da al'amuran rayuwarta na azancin magana da waqe-waqe da wasanni da kuma labaru, duk waxannan fagage ne da suke qunshe cikin rayuwar al'umma kama daga haihuwa da aure da kuma mutuwa.

Cudanyar Hausawa da baqin al'ummomi ta sa an sami bunqasar adabin Hausa a zamanance musamman a fannin karatu da rubutu irin na ajami da na boko. Bayan samuwar karatu da rubutun boko, sai aka assasa ci-gaban adabin rubutun zube da rubutattun waqoqi da wasan kwaikwayo na zamani. Fim na xaya daga cikin nau'o'in adabin zamani da yake fito da al'adu da dabi'u da kuma fasahar al'umma (Sulaiman, 2015:3-4). Adabi shi ne yake taskace yadda al'amuran rayuwar al'umma ke gudana a rubuce ko a zahiri ta hanyar wasan kwaikwayo ko sauraro a rediyo ko a talabijin. Ita kuwa al'ada, a ganin Umar (1998) sababbiyar hanyar rayuwa ce, wadda akasarin jama'a na cikin al'umma suka amince da ita. Ya ce waxannan zavavvun abubuwa waxanda aka saba da su, sukan haxe kowane fanni na rayuwar Xan Adam, kamar dangogin ibada da harshe da abinci da sutura da muhalli da sana'o'i da mulki da aqida da tsarin zaman tare. A taqaice ire-iren waxannan amintattun abubuwa da mutanen nan suka amince masu, suka saba da yin su, su ne al'adunsu, in ji Umar, (1998: 4).

Shi kuwa fim yana xaya daga cikin hanyoyin sadarwa na zamani da ake shiryawa don isar da saqo da kuma wayar da kai ko juyar da tunanin xan Adam. Haka kuma akan yi amfani da fim domin yaxa wata manufa mai kyau ko kishiyar haka ta hanyar amfani da na'urar xaukar hoto mai motsi, daga bisani bayan an tace sai a sarrafa shi zuwa faifai na Bidiyo ko *CD* (Umma, 2008:61). Wannan bincike yana goyan bayan wacan ra'i na Umma a kan cewa fim abu ne wanda yake haska adabin al'umma. Kamar yadda ake nazarin wasan kwaikwayo, ya Allah rubutacce ko na talabijin ko na rediyo ko kuma na majigi/silima, to, haka shi ma fim yake wani nau'i na adabi ne da akan yi nazarinsa ta fuskoki daban-daban. Don haka, a turbar adabin fina-finai za a yi nazarin al'adun wata al'umma da ta yi naso a cikin wata, da nazarin harshe har ma da tunanin al'umma, kamar yadda muka gani ayyukan Ahmad, (2016) da Rabi (2016) da sauran lamura da suka jivanci zamantakewar al'umma. Wataqila wannan bai rasa nasaba da daxaxxiyar alaqa da ta wanzu a tsakanin al'ummar Hausawa da wasu baqin al'ummomi maqwabtan Hausawa, a wata riwayarsu Mahadi (1979) da Sani (1978) sun ce wannan dangantaka, an qulla ta ne tun a wasu lokuta masu tsawo da suka shuxe, kuma shi ma Ajayi (1970) da Smith (1983) da Jaja (2008) da Muhammed, (2011) sun tabbatar da hakan a ayyukansu.

Irin wannan dangantaka ba ta tsaya nan ba, sai da ta yi naso har ta kai ga adabin fina-finan Hausa. fina-finan Hausa suna taka rawar fito da adabi da al'adun Hausawa na gargajiya da na zamani, kodayake ana samun qorafe-qorafe a kan yadda ake aiwatar da harkokin fim xin a wannan zamani a qasar Hausa a kan ba sa tafiya bisa tsari. A wannan bincike an yi nazarin al'adu da xabi'un Hausawa a matsayin wani mataki na tantance fina-finan Hausa da kuma

fina-finai da Hausa. Misali a da can baya, a tsakanin 1980 har zuwa farkon 2000 akan gina fina-finai Hausa a bisa al'adun Hausawa kawai masu nuna ainihin tsarin rayuwar Hausawa da yanayin zamantakewarsu. Misali, fim xin *"Daskin da Rixi"* an xauko shi ne daga adabin tatsuniyar Hausawa, aka juya shi ya koma fim. An nuna al'adar rayuwar Bahaushe tsagwaronta tun daga muhalli da halayya da zubi da sutura da sha'anin mulki (sarauta) da cimakar gargajiya da biyayya a gargajiyance da kuma amfani da daidaitacciyar Hausa. Haka kuma a fagen adabin zamani sai aka xauko labarin Sarki Jatau daga littafin *Magana Jari ce* aka shirya fim mai suna "*Sarki Jatau*". Fim xin ya nuna yadda ake aiwatar da wasu bukukuwan gargajiyar Hausawa da mulki da kaxe-kaxe da girmamawa da kara da kawaici da kunya. Don haka, abin ya ci gaba har ta kai fina-finan Hausa a yanzu suna sauya kamanni ko siffa da fasalin aron al'adu da harshe da xabi'u daga labarun qasashen waje da kuma aro daga fina-finan Turawa da Indiyawa da Sinawa da Larabawa a juyar da su zuwa fim na Hausa, hakan ya haifar da kutsen baqin al'adu da xabi'u na nesa a cikin fina-finan Hausa. A riwayar su Adamu (2004) da Lakin (2004) da Umma (2008) da Inuwa (2009) da Chamo (2012), fina-finan Hausa suna kwaikwayon al'adun maqwabtan Hausawa kamar Yarbawa da Inyamurai da Nufawa da Gwari da Kanuri.

Saboda haka, wannan nazari mai suna fina-finai Na Shekarar 2000-2017: Yanayinsu da Sigoginsu, ya ginu ne a kan nazarin tasirin baqin al'adu a fina-finan Hausa, sai dai kuma kafin a fito da baqin al'adun an fara da nazarin fina-finai na Hausa tsantsa, ta hanyar nazarin fim, wato kawo xan sharhi game da kowane fimda kuma bayanin a kan zubi da harshe da tufafi da halayya tare da jigon kowane fim. Har ila yau, an kawo bayani kan fina-finai da aka

yi su da Hausa, amma suke cike da baqin al'adu, su ma an bi matakan nazari wajen tantance su da nufin cim ma manufar wannan bincike.

3.1 **Manufar Bincike**

Duk da cewa ba sabon abu ba ne a sami aro na al'ada ko na harshe a cikin adabi, sai dai akan yi wannan aro ne ta hanyar hikimar nan ta hankaka mai da xan wani naka. An yi haka da dama a sassa na adabi musamman a qagaggun labarai. Shi ma fim ba a bar shi a bayaba wajen irin wannan aron, sai dai daga shekarun 2000…, an lura cewa irin wannan aron ya wuce gona da iri, har ta kai ga tasirin aron ya sa masu kallo sun gane cewa ba aro ba ne wanki da xauraye ne kawai.Manufa da muradin wannan aiki su ne:

i Nazartar fina-finan Hausa na shekarar 2000-2017.

ii Fito da tasiri ko illar waxannan fina-finai ga bunqasar adabi da al'adun Hausawa tare da tantance matsayin fim a cikin adabin Hausa. Da dalilan da suka haifar da wannan matsalar.

iiiAmfani da hanyoyin nazarin fim a matsayin mizanin auna fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa.

ivFayyace tasirin baqin al'adu da ake samu a fina-finan Hausa ga rayuwar Hausawa a wannan zamani, ta yadda za a tantance fina-finai da aka yi da Hausa, da waxanda aka yi su cikinHausa.

vDomin a yi nazarin yanayi da sigogin fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa.

1.2 Dalilin Bincike

Nazari a kan fim musamman na Hausa ba baqon abu ba ne. An gudanar da ayyuka da dama kama daga nazarin jigo da salo har ma da tasirin baqin al'adu a cikin fim,kamar ayyukan su Inuwa (2009) da Abbas (2008) da Aminu (2012) da Chamo (2015) da Sulaiman (2016) da sauransu. Sai dai har yanzu da sauran rina a kaba, domin galibin waxannan ayyuka ba su tavo inda ke ci wa al'umma tuwo a qwarya ba. Ma'ana qorafin da masu kallo da sauran al'umma suke yi cewa fina-finan Hausa ba sa wakiltar al'adu da xabi'un Hausawa shi ya asassa wannan bincike, amma duk da haka ana son kallon su domin suna nuna wasu abubuwa waxanda al'ummar Hausawa sun tasirintasu da su, a sakamakon tarayya ko tasirin baqin al'adu a cikin rayuwar Hausawa, kamar Indiyawa da Turuwa.Domin ko ayyukan da aka yi kan tasirin baqin al'adu a fina-finan Hausa, ya tsaya ga nazarin al'adun na nesa ne kawai, kuma ba a yi qoqarin tantance fina-finai na Hausa da kuma fina-finai da Hausa ba. Bisa wannan dalili ne wannan bincike ya yi hovassa da niyar cike wannan givi.

1.3 Hasashen Bincike

Kamar yadda masana irin su Adamu (2004) da Lakin (2004) da Aminu (2012) Chamo (2015) da Sulaiman (2015) suka tabbatar cewa fina-finan Hausa wani muhimmin vangare ne na adabin Hausawa wanda zamani ya zo da shi kuma ya yi mutuqar tasiri a kan sa. A wannan bincike ana hasashen cewa:

i Har yanzu akwai fina-finai na Hausa waxanda ake shirya su bisa al'adun Hausawa zalla duk kuwa da yanayi na dunqulewar duniya da ake ciki.

iiAna hasashen cewa baqin al'adu sun yi mutuqar tasiri a fina-finan Hausa, domin ko al'umma na raxe-raxin cewa wasu fina-finan Hausa ba sa wakiltar Hausawa.

iii Har ila yau, a wannan bincike anahasashen ganin gudunmowar da masu shirya fina-finai suka ba da wanda ya yi saandiyar shigowar wasu baqin al'adu.

Don haka, sakamakon wannan bincike ya tabbatar da mafi yawan hasashen wannan aiki kamar yadda aka gabatar a cikin aikin.

1.4 Farfajiyar Bincike

Babu shakka an yi ayyuka da nazarce-nazarce bakin gwargawado a kan fina-finan Hausa, kodayake waxanda suka yi bincike a kan fina-finan Hausa a matakin digirin qoli za iya qirga su da yatsu. Aduka ayyukan nasu, ba a ci karo da wanda ya yi nazarin fina-finan Hausa a qarqashin wani mashigi da za a iya tantance fina-finan Hausa ko kuma fina-finai da Hausa ba. An taqaita wannan aikin ne a kan nazarin wani vangare na tadodin Hausawa a cikin wasu fina-finain Hausa. An zavo fina-finai talatin (32) na shekarar 2000-2017. An kuma xauki samfurin wasu daga cikinsu aka nazarci guda 10. Domin haka, an fito da sigogi da yanayin fina-finan musamman a bisa tsari na zubin 'yan fim da harshen 'yan fim da tufafin 'yan fim da jigon fim da halayar 'yan fim wato dacewar xabi'ar xan wasa a tunanin Bahaushe ko rashin dacewa.

1.4.1 Dalilin Zaven Fina-finan

An zavo fina-finan ta la'akari da shekarun da aka samar da su, tun daga lokacin da siffofi da yanayinfina-finan Hausa suka fara sauya kamanninsu a fagen aiwatarwa, alokacin da suka fara bijirewa tafarkin shirya fina-finai a bisa al'adun Hausawa. Wato daga shekarar 2000 zuwa 20017a inda are-aren labarai daga wasu fina-finan qetare suka dinga tasiri a cikin masana'antar fina-finan Hausa, wato an yi fatali da qirqirar labari bisa adabi ko kuma al'adar

Hausawa kamar yadda aka fara a da can baya, ma’ana ba a cika mayar da hankali wajen qirqira ba. (Alkanawy, 2004, da 2005).

Don haka fina–finan ba sudamu da nuna al’adar Bahaushe ba, wasu masu shirya fina-finai da dama ba Hausawa ba ne, wasu lokutan ma labarin da akan gina fim a kansa ba Bahaushen labari ba ne, idan kuwa har labarin fim ba Bahaushen labari ba ne, ta yaya zai wakilci al’adu ko kuma tadodin Hausawa?Ke nan tana iya kasancewa a yayin shirya fim xin yanayin labarin yana iya tasirin a kan fim, fim xin ya kasance mai nuni da kyawawan al’adu ko kuma munanan al’adu wanxanda al’ummar Hausawa ba ta so, musamman a qoqarin aiwatarwa sai a yi ta samun tasgaron shigar giza-gizan sauye-sauyen xabi’u da yanaye-yanaye da suka savawa halayyar Bahaushe. Don haka, shi ya sa aka zavo samfur na waxannan fina-finai domin a ware aya daga cikin tsakuwa, domin kuma a kaucewa shaci faxi. Wannan shi zai tabbartar da cewar waxane fina-finai ne na Hausa, sannan waxane ne kumafina-finaida Hausa.

Wani ma’aunin da aka yi amfani da shi wajen zaven fina-finan shi ne, zavo fina-finan daga wasu garuruwan qasar Hausa, saboda su wakilci sauran garuruwan qasar Hausa. An zavo su daga kamfanoni daban-daban waxanda suke shirya fina-finan Hausa. Garuruwan da akazavo domin wakilci qasar Hausa, su ne Kano da Zariya da Katsina. An zavo fina-finai masu xauke da halayya da wasu xabi’u al’ummar Hausawa, inda aka yi amfani da su a matsayin tsani na fito da hanyoyin tantance fina-finan Hausa ko kuma fina-finai da Hausa.

Ganin cewar an samar da xaruruwan fina-finai daga shekarar 2000-2017, ba za a iya cewa dole sai an yi nazarin su gaba xaya ba, don haka aka zavo guda talatin da biyu a matsayin wakilai, a cikin talatin da biyu xin aka sake xauko guda goma a matsayin samfuran na gaba xaya don su wakilci sauran fina-finai.

1.5 Muhimmancin Bincike

Muhimmancin wannan bincike shi ne tabbatar da cewa masana fina-finan Hausa da manazarta wannan fage sun bar wata kafa wadda wannan bincike yake so ya toshe ta. Wato batun dai shi ne babu wani bincike da ya fito da wani mashigi da za a iya bi domin tantance fina-finan Hausa, ta yadda za a iya dinga yanke masu hukuncin shin fina-finan Hausa ne, ko kuma fina-finai ne da Hausa? Masana da manazarta sun daxe suna ta tattaunawa a kan wannan batu, amma ba a sami wani manazarci da ya qwanqwance wannan batu ba zuwa cikin kundin bincike mai kama da wannan.

Ana sa rai wannan bincike zai ilmantar da al'umma domin su fahimtu da wata sabuwar fasahar sanin makamar iya tantance fina-finai na Hausa da kuma fina-fina da Hausa.Binciken zai zama qari a kan waxanda aka yi a baya, domin alfanun masu bincike a fagen nazarin fina-finai, a ajiye su a xakunan karatu da ke a jami'o'i da kwaleji-kwaleji a matsayin kundin nazari ga 'yan baya.

Ana fatar wannan aikin ya kasance wata taska ce ta adana waxannan muhimman ayyukan fasaha, na yanayin zamantakewar al'umma a cikin fina-finan Hausa, tare da fata an tattara wa manazarta ilimin walwalar xan Adam taskar da za su iya amfani da ita wajen nazartar wasu xab'iun Hausawa a fagen nazarin fina-finan Hausa.

Kamar yadda aka bayyana cewa adabi, musamman na fina-finai, madubi ne na rayuwar al'umma, ana fata binciken ya zamo taska mai amfani ga manazarta walwalar xan Adam, wajen fahimtar halayyar zamantakewar Hausawa a cikin fina-finai na Hausa.

Haka kuma ana fatar aikin ya zama mai alfanu ba kawai ga xaliban da suke nazarin adabi ko fina-finan Hausa ba, a'a, har ma ga masu nazartar fim da wasannin dandamali a wasu Harsunan Nijeriya.

Ana kuma fatar aikin ya kasance taska na nazartar salo, wajen samun kayan nazari, musamman salon harshen da 'yan wasa da zubin 'yan wasa da halayyarsu da tufafinsu da jigon cikin fina-finan Hausa.

Haka ma masu bincike kan adabi za su amfana da wannan bincike domin ya buxa fagen da ba a zurfafa nazari a kansa ba. Ana fata aikin ya haskaka wa manazarta wasan kwaikwayo da fina-finai yadda za su iya gane ire-iren fina-finai ta fahimtar yanayinsu da sigarsu.

Ana fata wannan nazari zai taimaka wa masu rubuta labarin fim da masu tsara shi da zaven `yan wasa da su yadda za su iya kakkave kura-kurai da gazawar da ake ganin ta yi wa fannin fim katutu.

Haka kuma ana fata hukumomin da suke kula da wannan fasaha da tace fina-finan za su amfana da wannan binciken don zai taimaka wa tsare-tsarensu, su san kifi na ganin ka mai jar koma.

1.6 Kammalawa

A taqaice, wannan babin sharar fage ne na shimfixar aikin, tare da nuna inda bincike ya dosa. An fara kawo manufar bincike da dalilin bincike da kuma hasashen bincike. An kuma qarqare babin a inda aka kawo kadadar bincike da muhimmancin binciken a fagen ilimi. Babin da ke biye da wannan babin, shi ne babin da ya waiwayi ayyukan da suka gabata masu nasaba da wannan aikin.

BABI NA BIYU

BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

4.0 Gabatarwa

Wannan babin ya yi bitar ayyukan masana da suka gabata. An fara da kawo ma'anar adabi da ma'anar al'ada da nau'o'in al'ada da sajewar al'adu ko kuma a ce nashewar al'adu. An yi bitar batutuwa daban-daban a kan binciken da masana ko qwararru suka yi a kanfina-finai, kamar tasirin baqin al'adu a cikin fina-finan Hausa da aikin fassara da zamantakewa da matsayin mata a fina-finan Hausa. Daga bisani aka bi tarihin Hausawa da fasalin al'adunsu domin bincike an yi shi ne kan Hausawa da kuma farfajiyar qasar Hausa. Babin ya fitar da ma'anar fim da rabe-rabensa da kuma yin sharhi a kan yadda ake shirya fim na Hausa da sigoginsa a taqaice, an kuma yi bitar yadda fim ya shigo qasar Hausa da bunqasarsa. Daga bisani aka tsunduma cikin kawo waxannan matanoni da suke da alaqa da wannan aiki na kusa da na nesa, musamman bitar ayyukan Umma Abbas, (2008) da Umma Inuwa,(2009) da Mu'azu, (2006) da Chamo, (2001) saboda mutuqar muhimmancin su ga wannan bincike.

2.1 Adabi

Masana da manazarta sun bayyana asalin kalmar adabi ma'anarta daban-daban. Daga cikin waxannan masana akwai Dangambo (2008) ya bayyana asalin kalmar ‘’adab’’ ta Larabci ce,

wadda ta sami juye- juyen ma'ana dangane da sauyawar zamantakewar jama'a kafin ta xauki siffar da take da ita yanzu. Lokacin jahiliyyar Larabawa, kalmar tana nufin walima ko liyafa. Wato, kiran jama'a zuwa ga wani abinci da aka shirya don a ci. Amma bayan shigowar Musulunci, sai ma'anar adabi ta juya ga dukkan wasu hanyoyi na gyaran halaye, ko kuma abubuwa masu kyau, kamar ladabin cin abinci da ladabin zance, da sauransu. Da tafiya ta yi tafiya, sai ma'anar kalmar ta faxaxa, ta qunshi wasu dangogin ilimi kamar labarai da tarihi da waqoqin baka da harshe da sauransu.(Isa, 2013:435).

A lokacin da Musulunci ya shigo qasar Hausa tare da harshen Larabci, sai Bahaushe ya xauki kalmar ya sanya ta cikin harshen Hausa ya sake mata siga ta zama adabi wadda ma'anarta take nufin dukkan wani abu na fasaha da Bahaushe ya yi musamman don nuna wata hikima wadda ke bayyana rayuwarrsa. Umar (1987) ya ce adabin Hausa shi ne sarrafaffen harshen Hausa mai qunshe da hikima ta musamman. Ana iya samun wannan ta baka a sigar tatsuniya, ko karin magana, ko waqa, ko almara, ko wasannin kakkarya-harshe, ko gagara-gwari, ko ka cici-ka cici ko sauran nau'o'in zantuka hikima da suka fito daga bakin Bahaushe. Wannan shi Umar ya kira da adabin baka, ya ce ana iya samun sarrafaffen harshen Hausa da aka rubuta cikin Ajami ko Boko a tsarin waqa ko zube, ko wasan kwaikwayo. Wannan shi ne rubutaccen adabi.

Masana irin su Xangambo (2008) sun bayyana cewa, adabi ya rabu biyu. Adabin gargajiya (adabin baka) da adabin zamani (rubutaccen adabi). Haka kuma ya qunshi nau'o'in da suka

haxa da zube da waqa da wasan kwaikwayo, Umar (1987) kuwa cewa ya yi ana iya samun adabin ‘na da’ da na ‘zamani’.

2.2 Al’ada

Wani masanin zamantakewar al’umma Haralambos (2013) ya ba da ma’anar al’ada da cewa haxaka ce da qwarewar fito da fasahar wata al’umma. Ya ce za a iya samun al’adar al’umma a cikin wasannin gargajiya da zane-zane da cikin rayuwar al’umma ta zahiri. Sai ya ce a dunqule, al’ada hanyar rayuwar al’umma ce gaba xaya. Musamman tsarin zamantakewa da xabi’unta; waxanda suka haxa da tunaninta da xabi’unta, kuma akan iya sadar da ita daga wani qarni zuwa qarni. Don haka, a cikin al’adar al’umma ne za a iya tantance nau’o’in waqoqinta da kaxe-kaxe da adabinta.

Kalmar al’ada kamar yadda Bunza (2006) ya nuna na nufin dukkanin rayuwar Xan-Adam tun daga haihuwarsa har zuwa kabarinsa. Sani (1982) yana mai ba da waxannan sigogin al’ada kamar haka, al’ada tana nufin haila watau irin jinin nan da mata suke yi wata-wata. Tana kuma nufin bin wata hanya don yin maganin gargajiya misali yin karatu; ko tofi, ko turare, ko zubar da jinni da sauran su. Don haka, da Sani (1982) da Muhammad (2004) da Bunza (2006) duka suna ganin al’ada tana xauke da abubuwan da suka shafi yanayin rayuwar al’umma, da harkokin da suke yi na zaman duniya. Emmitt da Pollock (1997) sun bayyana ma’anar al’ada da dabaru daban-daban a fili ko a voye waxanda suke wanzuwa tare da

jama'a tun da daxewa. Xabi'u sukan shiryar da mutanen da suka mallake su wajen zaman duniyarsu. Al'ada takan shafi dukkan al'amuran da suka qunshi rayuwar mutanen da ta shafa. Domin al'adu kan shafi tunanin mutane da rayuwarsu da zammantawarsu, ta zama kamar wani danqo ne da yake haxa kan mutane a wuri guda. Abdulmumin (2004) ya ce kalmar al'ada tana nufin hanyar rayuwa da ta zamo karvavviya ga mafi yawan jama'a.

Don haka a taqaice, wannan ma'ana ta qarshe ta shafi yanayin rayuwar al'umma, da harkokin da suke yi don zaman duniya. Shi ake nufi a wannan bincike, tun da yake al'ada tana nufin hanyar rayuwa. Kuma al'ada ga rayuwar Bahaushe wani qaton kogi ne, wanda sai dai ka ga iyakar ganinka ka bar sauran. Don haka, al'ada a tafiye take ga dukkanin harkoki da mu'amala ta rayuwar Bahaushe. Domin ta haxa da muhallinsa da tarbiyyarsa da tufafinsa da auratayyarsa da abincinsa da sauransu.

2.2.1 Nau'o'in Al'ada

Wani masanin zamantakewar al'umma Haralambos (2013) ya raba al'ada zuwa kaso shida a dangane da tsarin yanayin zamantakewar al'umma:

a. Al'ada mafi daraja (*High Culture*) kayan al'adu da masana 'yan boko sukan gano wa al'umma musamman ire-iren fasahar al'adunsu.

b. Al’adun yanki (*Folk Culture)* al’adun da aka san jama’ar wata nahiya da suna yi. Kuma aka alaqanta su da ita su kaxai, kamar su tatsuniyarsu da waqoqinsu da labarun gargajiya tun daga wani zamani dadaxxe da ya shuxe ake aiwatarwa.

c. Al’adu na bai xaya (*Mass Culture)* : wannannau’in al’ada ce wadda akan sadar da ita ta hanyar yaxa halayyar xabi’u da tunani da darajoji wadda aka samar da su daga tunanin haxakar al’umma, a kuma same su a taskar labarai da waqoqi.

d. Al’adun masu kwaranya (*Popular Culture*): duk wata al’ada ko halayya da tunani da hotuna da yanayin zamantakewa da suka kwaranyo zuwa cikin wata al’ada, musamman a dubi yadda al’adun mutanen yamma a tsakiyar qarni na ashirin ya kwaranyo har zuwa farkon qarni na ashirin da xaya.

e. Haxakar Al’adu a duniya (*Global Culture*): wannan na nufin al’adun wata al’ummar nahiyar tana iya yin tasiri a kan wata a dalilin qaurace-qaurace kamar yadda ‘yan Afrika suka zama Amerikawa baqaqe.

Ya kamata a sani, waxannan nau’o’in al’adu waxanda Haralambos ya kawo, wannan bincike ya fassara su ne da taimakon Bargery (1934) da kuma Hausa *Metalanguage* (1990) da kuma*Qamusun Hausa*, (2006). Bayan an fito da yadda masana suka ba da ma’anar al’ada dangane da fahimtar da suka yi mata, sai aka ga ya kamata a fito da rabe-raben al’adar, yin hakan zai nuna ma mai karatu cewar al’adar ta kasu kashi-kashi da kuma sanin irin kason da ya shafi wannan aikin. Sannan yana ganin za a iya raba al’ada zuwa kaso kamar haka: al’ada da xabi’a

Bayyananniyar al’ada ita ce, wadda mutum kan iya ganin su quru-quru da idanunsa har ma ya tava su da hannu ko wani sashe na jikinsa. Misali al’adar sanya sutura da yanayin muhalli da kasuwanci da kayan amfanin gida kamar qorrai da tukwane na gargajiya, kowacce al’umma tana irin da tata fasahar a bisa yadda take sarrafa su. Ko kuma a ce ire-iren kayan dafa abinci kamar su rariya da tukunya da dai sauran su. Wannan duk kayayyakin amfanin gida na gargajiya da suka fito qarqashin al’ada bayyananniya, kowacce al’umma tana da irin nata. Xabi’a dai ita ce halayen mutum da kuma yanayin xabi’ar zamantakewarsa da jama’arsa takan nuna daga cikin halayensa, takan nuna shi a fili, sannan hankali ya xauka ko kuma ya qyamace shi. Shi ma wannan ya kasu kashi biyu: kyakkyawar xabi’a da mummuna. Wani masanin al’adun Hausa Magaji (1999) ya ce daga cikin kyawawan xabi’u akwai mutuntaka da kyautayi da girmamawa. Munanan xabi’u su ne sata, da tumasanci da gulma da roqo da raraka da bara. Amma masana irin su Mahdi (1979) Yahaya (1983) da Xangambo (1984) suna ganin al’ada ta kasu kashi biyu, wato al’adun da aka gada daga kakanni, kuma aka san al’umma da ita. Za a iya yi wa wannan al’ada da laqabi da tsohuwar al’ada. Misali yafa gwado ko kuma tafiyar mil goma a qafa da goya amarya a gadon baya in za a kai ta gidan miji da cin abinci a cikin akushi da sauransu. Al’adun zamani kuwa na nufin baquwar al’ada da ta sami wurin zama a cikin al’adun wata al’umma bayan sun yi cuxanya da wasu al’ummu da suka shiga cikin su, misali, al’adun Turawa a cikin na Hausawa ko al’adun Larabawa. Ana iya kiran waxanan al’adu da al’adun sauyi. Wai saboda wayewa ya sa an canja daga al’adun asali na al’umma zuwa na wata a bisa dalilai na yaqi da qaura da cinikayya da Jihadi da addini da zamantakewa, sai ake ganin a duk lokacin da wata al’aumma ta xauki al’adun wata al’umma ta yafa ana cewa ta xauki baquwar al’ada ko a ce na zamani ne.

2.3 Qasar Hausa da Iyakokinta Jiya da Yau

Kafin bayani ya yi nisa a kan iyakokin qasar Hausa, ya kamata a san wane ne Bahaushe? Adamu (1978:4) ya bayyana Hausawa da cewa su ne waxanda a tarihance aka haife su ko kuma kakaninsu a qasar Hausa ta vangaren iyaye maza, ko kuma waxanda suke da nasaba ta qut-da-qut da al'adar Hausawa, ta hanyar zaven harshen Hausa, da al'adunsa da kuma addini. Shi kuwa Adam (1997:16) ya bayyana Hausawa cewa mutane ne masu tsananin riqon al'adunsu na gargajiya, musamman wajen tufafi da abincinsu da al'amuran da suka shafi aure da haihuwa da sha'anin mu'amala tsakanin dangin da abokai da shugabanci da al'amuran sana'a ko kasuwanci ko neman ilimi da sauransu. A nan dai idan aka lura da waxannann bayanai na masana, za a ga cewar muhimmin abu, kuma jigo da yake bayyana Bahaushe a gane shi, ita ce al'ada. Don haka, a iya cewa Bahaushe shi ne wanda ga asali Hausa ta haife shi, kuma ya yi riqo da harshensa da kuma al'adunsa.

A vangaren iyakar qasar Hausawa kuwa, a ra'ayin Adamu (1997) yana gani qasar Hausa tana da girma qwarai da gaske, tana da yanayi kamar na damina da kaka da bazara da sanyi. A nan yana da muhimmanci a san ko ina ne qasar Hausa, ina ne iyakokinta, su wane ne makwabtanta. Wannan shi zai taimaka mana wajen qara fahimtar yadda yanayin qasar Hausa take da kuma yadda yanayinta yake kasancewa a cikin shekara. Adamu, (1997), ya ba da iyakokin qasar Hausa ta amfani da taswirar qwallon duniya, aka yi amfani da layuka da aka zana domin qara sauqaqa gano wurare a bisa qwallon duniya kamar haka:

> ….za a sami qasar Hausa a tsakanin layi na goma sha biyar (150N) zuwa na goma sha takwas (18^0N) na arewa da ikwaita; kuma tana tsakanin layi na takwas (8^0E) da na goma sha biyu (12^0E) a gabas da layin Greenwic

Masu nazari a fannin lamurran qasa (*Geography*) sun ce, wannan hanya ita ce mafi karvuwa wajen fayyace kowane muhalli da ainihin mazauninsa a bisa doron qasa. An kasa kwallon duniya zuwa gida-gida ta amfani da wasu layuka guda biyu, wato layin *longtitude* wanda ya faro daga arewa zuwa kudu a kan qwallon duniya; sai kuma layin *latitude* wanda ya faro tun daga gabas zuwa yamma a kan kwallon duniya.

Adamu (2011) ya bayyana inda ake kira qasar Hausa a wata maqala da ya gabatar sai aka fassara kamar yadda yake cewa:

> Qasar Hausa ta faro ne tun daga Abzin a tsaunuka shiyyar arewa (a qasar Nijar ta yau) zuwa wasu kilomitoci kudu da Kufena da Turunku a Zazzau (a qasar Nijeriya ta yau) *daga sashen kudu ke nan; ta kuma soma daga tsakanin kwarin Neja a shiyyar yamma har zuwa iyakokin Nijeriya da Nijar a gabas*

Wannan bayani na Adamu (2011), ya ba mu haske a kan farfajiyar da qasar Hausa take a doron qasa, domin ya kawo mana mahallin da ita kanta qasar Hausar take, ta yadda idan mutum ya xauki littafin taswirar kwallon duniya (atlas) zai iya hasashen ko ina ne qasar Hausa. Adamu (1997) ya qara da cewa:

> Kasar Hausa a yau tana cikin Afirka ta Yamma a arewacin Nijeriya. Kuma a kwance ta tavo har cikin qasar Nijar wajen su Maraxi da wasu ‘yan garuruwa, haka kuma daga Gabas ta yi iyaka da wani yanki na

> Jamhuriyar Binin a gabar da kogin Kwara, daga wajen kudu kuma ta yi iyaka da qabilun Gwari da kuma qabilun kudancin Zariya da na kudancin Bauci.

To idan muka kalli waxannan bayanai da suka gabata, kallo irin na fahimta, ana iya kammalawa da cewa, yanzu kam mun fitar da muhalli ko farfajiya da ake kira qasar Hausa a fannin tarihi da fannin kimiyyar lamurran qasa (Geography). Idan kuma aka haxa waxannan bayani, za a ga haqiqannin inda ita wannan qasa ta Hausa take a cikin farfajiyar Afirka.

A duk bayanan da aka gabatar, kowane xaya daga cikin su ya ba da muhallin da farfajiyar qasar Hausa take, ma'ana babu inda wani daga cikinsu ya yi takin saka da wani a wurin fayyace ta. Duk sun ba da bayani waxanda suka yi canjaras da juna.

Masana ilimin labarin qasa, sun bayyana qasar Hausa da cewa wuri ne da ke da shimfixaxxiyar qasa a mafi yawanta, ana kuma samun wasu wurare masu tudu da kwari, akwai manyan duwatsu da tsaunuka. Daga arewacin qasar inda ake kira Sahara, nan ne ake samun itatuwa marasa inuwa sosai. Sai kuma daga kudanci, wurin da ya fi yawan itatuwa masu duhu, wato sashen kurmi.

Gusau, (2003) yana mai faxaxa wannan batu da cewa a Arewacin qasar akwai wurare masu dausayi a sanadiyyar kusanci da tafkuna ko rafuka ko kuma xaya daga cikin gulaben da suka samu a sanadiyyar rarrabuwar igiyoyin manyan koguna da suka ratsa qasar wato; kogin Haxeja wanda ya faro daga Kano, ya yi gabas har zuwa tafkin Chadi. Akwai kuma kogin Rima wanda ya faro daga Zamfara ya gangara Arewa zuwa Nijar sannan ya karkato Kudu ya

yi Yamma da Sakkwato ya haxe da kogin Kwara. Shi kuwa kogin Kwara ya yi iyaka ne da qasar Hausa daga sashen Yamma.

Adamu, (1997) ya yi bayani a kan yanayin qasar Hausa na shekara-shekara a inda yake cewa:

> Qasar Hausa, tana da yanayin shekara-shekara iri biyu ne, lokacin damina da na rani. A lokacin damina ne wato tsakanin watan Mayu-Satumba ake samun ruwan sama, yawan ruwan da ake samu kima ne amma duk da haka yakan biya buqata wajen aikin gona. Lokacin rani yana farawa daga Oktoba zuwa Afrilu, rani ya kasu biyu; lokacin xari ko hunturu da lokacin zafi wato bazara. Bazara lokaci ne da rana take yin tsananin zafi iska takan tsaya cik. Sai dai kuma wani lokaci guguwa takan tashi daga wani wuri zuwa wancan.

Qasar Hausa ta kasance mai yanayi iri biyu wato damina da rani saboda irin halin da qasar take da shi, wato a wani vagare qasar tana da manyan itatuwa masu duhu kamar yankin qasar Zariya, sannan wani vangaren qasar tana da gajerun itatuwa kamar irin yankin qasar Sakkwato. Kasancewar hakan shi ya sa qasar Hausa take da yanayin shekara iri biyu. Bugu da qari, qasar Hausa wuri ne da ke da ma'adinai daban-daban a qarqashin qasa, kamar su kanwa da qarfe (jan karfe da bakin karfe da azurfa da sauransu), akwai kuma yumbu (qasa) wadda ake tubali na gini da kuma ginin tukwane da dai sauransu da ita.

Wannan bincike yana ganin idan aka yi la'akari da bayanin waxannan malamai, ana iya cewa da qamshin gaskiya a ra'ayoyinsu domin sun nuna cewa Hausawa dai mutane ne da suke zaune a qasar Hausa tun farkonta. Domin su Ibrahim da wasu (1982) suna da ra'ayin cewa, daxewar harshen Hausa a duniya ya dogara ne ga daxewar Hausawa. Wato, ke nan, tun a

lokacin da mutane suka karkasu zuwa jinsi-jinsi, a nan ne aka sami qabilar Hausawa masu magana da Hausa. Wannan bincike ya yarda da wannan ra'ayin. Bugu da qari wasu na da ra'ayi a kan Bayajidda (Abu Yazid) sun ce ya zo Daura ya tarar da mutane har da magajiyarsu a Daura. Abin nufi a nan dai, Hausawa suna da kafaffiyar daula. To a nan tambaya ita ce, kafin zuwan Bayajida da wane harshe suke amfani? Haka kuma, mutum zai iya tambaya yadda zance ya gudana tsakanin tsohuwar da Bayajida ya sauka a gidanta, wanda ya roqi ruwa a wurinta domin ya ba dokinsa. Ta kuma gaya masa cewa ba ta da ruwa, ta kuma labarta masa labarin Sarki macijiya, sannan ya nemi ta ara masa guga ya samo ruwa. Amsa a nan idan wannan batu haka yake, to Bayajida ya samu Hausa da Hausawa a mazauninsu, wato ba shi ne asalin Hausawa ba. Ashe ba abin mamaki ba ne idan an ce Bayajida ya koyi Hausa kafin ya iso Daura ko kuma bayan ya zo Daura. Wannan bincike yana ganin batun bayajidda yana buqatar a sake bincike a kan tarihin alaqarsa da Hausa da kuma Hausawa.

Shi kuma Smith (1959) ya nuna rashin amincewarsa da bayanin dangane da asalin Hausawa musamman ma cewa wai shekara dubu da suka wuce babu Hausawa. Shi yana ganin cewa kasa rarrabewa aka yi tsakanin asalin Hausawa da kuma asalin daular Hausawa da aka kafa a dalilin rashin fahimtar juna. Kazalika, Malamin bai amince da cewa Hausawa sun samo asali a sakamakon auratayya tsakanin Berber (Buzaye) da kuma Tukururu da suka same su a wurin ba. Don haka ra'ayinsa ya karkata ko ya fi danganta Hausawa da harsuna 'yan gidan Chadi, irin su Margi da Bolawa da Ngizim da Buduma da Kotoko da jukun da Angas da Sayawa da sauransu. Haka nan yana ganin cewa Hausa ta raba hanya da waxannan harsuna shekaru dubbai da suka wuce. Masanin ya qara da cewa mai yiwuwa akwai dangantaka tsakanin

harshen Berber da na Chadi, amma tun kafin sahara ta zama Hamada. Ya kara da cewa, babu shakka ba abu ne mai karvuwa ba a ce shekarau 960 da suka wuce babu Hausawa.

Shi kuma Adamu (1979), a ra'ayinsa, Hausawa dai su ne daxaxxun mutane mazauna qasar Hausa da suke amfani da al'adun Hausawa kuma suna riqo da harshe Hausa. Wannan ra'ayi na Adamu ya so ya yi dai-dai da na Amfani, (2011) kan cewa, an tabbatar da cewa a can cikin tarihi akwai wani lokaci da mutane suka yi ta yin qaurace-qaurace daga yankin Tafkin Chadi suna yin Yamma. Babban dalili yin waxannan qaurace-qaurace shi ne qeqashewar tafkin Chadi. Gulbin Kebbi da Tafkin Chadi akwai nisa qwarai kuma akwai makekiyar qasa. A lokacin qaurace-qauracen, waxansu mutane sun qarasa har gulbin Kebbi, waxansu kuwa iyakarsu tsaunukan Borno. Waxannan mutanen sun dade qwarai a wannan makekiyar qasa yadda har ma ba a san lokacin da suka zo ba. Ba a san su sosai ba sai a qarni na sha biyar. Mutanen qabilu ne daban-daban, Hausawa da Bolawa da Ngizim da Manga da Margi da Buduma da Kotoko su ne manyan kabilun a ciki, yawanci waxannan qabili suna zaune a jihohin Borno da Yobe da Jigawa ne a yanzu. Hausawa sun fi yawa kuma sun fi warwatsuwa cikin wannan makekiyar qasa. Amma su Alhassan, da wasu, (1982) sun ce ainihin qasar Hausa ta asali tana Afirka ta yamma ne, a farfajiyar nan da ke tsakanin hamadar Sahara da dazuzzukan da suka doshi gavar tekun Atlantika daga kudu. Kuma ana kiran qasar da sunan Sudan ta yamma, wato tsakanin Tafkin Cadi da gwiwar Kogin Kwara a can yamma. Idan muka duba bayanan su Alhassan za a ga lallai hakan yanayin qasar Hausa take dangane da iyakarta ko a yanzu ma.

A bisa bayanan waxannan masana za a iya cewa qasar Hausa ta asali ta faro ne tun daga Asodu, can arewa maso gabas da Agades. Daga nan ne Gobirawa suka taso, da kaxan-kaxan har suka zo inda suke a yau a Nijeriya. A yanzu kuma, Hausa tana yaxuwa ne, tana qoqarin komawa har zuwa gidanta na jiya. Qarshen iyakar qasar Hausa a kudu kuwa shi ne, Yawuri da Zariya da inda Bauchi ta yi iyaka da Kano da Garun Gabas (watau Birom) ita ce iyakar qasar Hausa daga gabas. A yamma kuwa bakinta Filinge. A duba rataye na biyu za a ga tasawirar qasar Hausa da iyakokinta.

A bayanin nasu sun ce qasar Hausa ita ce inda ba a buqatar naxa Sarkin Hausawa. Wato wannan bayani ya ware duk wasu zango-zango, inda ake magana da Hausa. Amma idan ana maganar inda harshen ya yaxu ne, ya zama harshe na xaya ko na biyu a bakin mutane, to wuraren da aka ambata a nan ba su fi rabin qasar Hausa ba.

Qasar Hausa galibinta shimfixaxxiya ce, mai yawan sarari. Akwai ta da tsaunuka da tuddai jifa-jifa. Kuma duk yawan wannan qasa, manyan koguna biyu ne suka ratsa ta cikinta, da kogin Rima da Kogin Haxejiya. Kogin Kwara ya zama kamar iyaka ne daga yammacin qasar. Kogin Rima shi ne ya taso daga qasar Zamfara, ya gangara ya yi arewa zuwa Nijar, sa’annan ya karkata kudu, ya bi ta yamma da Sakkwato, ya je ya faxa cikin kogin Kwara. Shi kuma kogin Haxejiya, masominsa a qasar Kano ne. daga nan ne ya gangara gabas, ya bi ta Gashuwa ta Gaidam, ya ke ya faxa a Tafkin Cadi.

Daji a qasar Hausa iri biyu ne. irin dajin da ake kira Sahel shi ne daga arewa. Daji ne mai qarancin bishiyoyi, gajeru kuma jifa-jifa. Kusan duk bishiyoyin da ke wannan wuri suna kaxewa qarqaf da rani, har ka yi tsammanin sun bushe. In damuna ta kusa kuma sai duk su fara ganye. Ciyawa kuwa tuni dabbobi sun cinye rabinta, kuma suna tattake rabi. Amma da zarar an yi ruwan farko na damuna, sai ka ga ko'ina duniyar ta zama koriya shar.

Daga Sahel idan ka yi kudu, dajin zai riqa qara kauri, bishiyoyi na qara tsawo da kusanci da juna, da kuma wasu ganyaye da ciyayi da ke shekara da korensu. Ciyawar kuma ta fi ta Sahel tsawo. To wannan shi ne dajin Sabana.

A qasar Hausa, yanayin shekara iri biyu ne; lokacin damuna da na rani. A lokacin damuna ne (watau tsakanin watan Mayu zuwa Satumba) ake samun ruwan sama. Yawan ruwan da ake samu kima ne, amma a duk da haka yakan biya buqata wajen aikin gona. Lokacin rani shi ne daga Oktoba zuwa Afrilu. Rani ya kasu biyu; lokacin xari ko hunturu, da lokacin zafi watau bazaar. Bazaar lokaci ne da rana takanyi tsananin zafi. Iska takan tsaya cik. Sai dai kuma, wani lokaci guguwa takan tashi daga wannan wuri zuwa wancan. Takan kwashi ura da haki, ta riqa hajijiya da su, sai duk inda ta lafa ta sauye su (Alhasan da wasu, 1982:1-3).

Dangane da bayanan masana da aka kawo a sama, wannan bincike ya lura cewa qasar Hausa qasa ce mai faxi da yalwa. A halin da ake ciki, tana da al'ummomi daban-daban, kodayake dai Hausawa su ne mafi akasari a ciki. Qasar tana da yanayin rani bayan xaukewar ruwan sama,

lokacin qasar ke bushewa. Akwai kuma yanayin damina, lokacin da ake samun ruwan sama, ake kuma gudanar da noman damina.

2.4 Sajewa Da Nashewar Al'adu

Wani masanin zamantakewar al'ummomi Haramlambos, (2013) ya nuna yadda al'adun al'ummomin duniya sukan yi tasiri a kan junata dalilin zamantakewa irin ta yau da gobe. Babban dirka da ke assasa tasirin al'adu ita ce qaurar al'adu (*Culture Migration)* ; takan tabbata ne a sanadiyyar tashin wata al'umma daga qasarta ta asali zuwa wata qasar da nufin koyon harshe ko sha'awar harshen wata nahiya ko don qaunar al'adarta. Wato mutane ne masu tushen al'adu mabambanta sukan taso zuwa wata nahiya su sauka a qasar, saukarsu ke da wuya da xan wani lokaci sai su jingine tasu al'adar su xauki ta nahiyar da suka baqunta. A dalilin haka sai ake samun hayayyafar al'adar hankakanci, (*Cultural Adaptation)* wato al'adar mai da xan wani naka. Idan zama ya yi zama, baqin da suka baqunce su, sukan iya yafa ko xaukar wasu al'adun garuruwan da suka je bayan an yi cuxanya da juna har ma baqin sun zama 'yan gari domin duk wata al'adar garin suma sun iya har ta zama tasu. Misali: takari a qasar Makka da zaman Hausawa a qasar Yarbawa ko kuma zaman Yarbawa da Gwarawa da Kanuri da Nufuwa a qasar Hausa.

Sajewar al'adu , (*Cultural Assimilation*): a nan qananan al'adu mutanen gari ne sukan saje da manyan al'adu, misali sajewar al'adun Asiyawa a cikin ta Turai ta Kanada, wanda yanzu da wuya ka iya bambamce su.

Tasirin al'adu, (*Cultural Influence*) : wannan yakan tabbata bayan wata al'umma ta yi cuxanya da wata babba, wanda a dalilin haka al'adun babbar al'umma sai ta yi tasiri a kan qaramar tun daga kan harshe da tsarin bukukuwa da addini har magungunan gargajiya.

Al'adar cin gashin kai (Cultural *Plurality) :* Tsari ne da qananan qabilu masu al'adu iri guda sukan tafiyar da al'adunsu da xabi'unsu a cikin wata babbar al'umma ba tare da tsangwama daga babbar al'ummar ba. Ma'ana wani yanayi ne da qananan al'ummomi sukan zauna a bisa tsarin zamantakewar cin gashin kansu ba tare da wani ya tsangwami wani ba. A irin wannan zama kowa yana da damar ya yi zama irin ta al'adarsa, komai yawan al'ummomin da suke cikin qasar ko nahiyar. Misali kamar qasarmu Nijeriya.

Sauyin Al'ada *(Cultural Change*): Shi ma wani nau'i ne na tasirin al'adu a tsakanin al'ummomin duniya. A nan akan yi amfani da iko ne na gwamnati ko hukuma ko mulki domin a tilasta sauya al'adun mutanen wuri don a cim ma wata manufa a kaikaice ta yadda wannan rayayyen al'ada za a shigo da shi da qarfin tsiya, ko kuma sannu a hankali da dabaru. Wannan bincike yana mai ra'ayin cewa lallai waxannan bayanai na Haralambos nau'o'in al'adu ne waxanda ake cin karo da su kuma suna faruwa a cikin rayuwar Hausawa ta zahiri. Domin wasu daga cikin tasirance-tasirance al'adu da ake samu a cikin wannan zamani a qasar Hausa ya sanya al'adun Hausawa na dauri sun sami koma baya a dalilin sauyin juyin zamani da kuma are-aren al'adun qetare da Hausawa suka dinga yi.

2.5 Fasalin Al'adun Hausawa

A nan an xauki wasu daga cikin al'adun Hausawa na gargajiya da ake ganin sun fi kusa da manufar binciken aka yi bitar su, wato al'adun haihuwa da sutura da aure da al'adun mutuwa da addini gargajiya da tarbiyya da tadojinsa. An yi bayanin su kamar yadda aka san Bahaushe da su, a rayuwarsa ta yau da kullum a gargajiyance.

2.5.1 Addini

Muhammad (2004:12) da Adamu (2007) sun yi ittifaqi a kan addinin Hausawa a yau shi ne Musulunci, sannan wanda a yau kusan kashi 95 cikin xari na al'ummar Hausawa Musulmai ne in ji su. Sun ci gaba da cewa qalilan ne a cikin al'ummar Hausawa waxanda ba Musulmai ba, qalilan xin su ne waxanda har a yau suke bin addinin gargajiya (maguzawa), sai dai Allah da ikonsa su ma kullum rayuwarsu tana sauyawa a inda suke shiga addinin musuluncin.

A nan idan muka xauki addinin gargajiya, to, ana nufin maguzanci, idan kuma aka ambaci addininMusulunci ana nufin, addinin Manzon Allah Annabi Muhammadu (S.A.W.). Addinin Gargajiya: Addini ne mai daxaxxen tarihi, al'umma daban-daban sun yi bauta iri iri a lokuta daban daban a duniya. Bauta kuwa hanya ce da akan bi domin samun biyan buqata. Misali al'ummomin duniya a da can baya kafin su karvi addinin Musulunci, sun bauta wa abubuwa da dama, Misali:- Adamu (2007) ya kawo su kamar haka:

a. Masar sun bauta wa Osiris wanda suka danganta abin bautar da kogin Nilu. Girkawa kuwa sun bauta wa Diogolos.
b. Larabawa sun bauta wa gumaka irin su Waddu da Suwa'a da Yagusu da sauransu. Har bayan bayyanar addinin Musulunci sukan bauta wa gumaka fiye da (360) manya daga cikin akwai su Lata da Uzza da Manata.

c. A Afirka ta yamma kuwa, mutanen Ashanti sun bauta wa Abosoni. Dahomi sun bauta wa Vondu.

d. Dangane da Hausawa kuwa ba su yi sassake-sassake ba, kamar yadda wasu daga cikin waxanda aka lissafa a baya suka yi na gumaka a siffar tsuntsaye ko mutane ko dabbobi da sauransu a matsayin abin bauta, sai dai sun bauta wa iskoki iri daban-daban. Muhammad (2004:12) da Adamu (2007)

Masana irin su Adamu (1979)da Sani (1983) da Bunza, (2006) sun ce addinin Hausawa na gargajiya kafin zuwan Musulunci, shi ne tsafi ta hanyar bauta wa iskokai. Bahaushe ya yi imani cewa, ba shi kaxai yake ba, akwai wasu halittu a voye waxanda sun fi yawa kuma sun fi shi qarfi, idan aka cuce shi, ba zai iya ramawa ba, kuma suna da xabi'a irin ta mutum. Misali, idan aka faranta masa za a ga sakamako mai kyau, haka idan aka baqanta masa za a ga sakamako maras kyau, wannan shi ya sa suke qoqarin faranta musu, kuma suke guje wa duk wani abu da zai vata musu rai. Mudi Sipikin ya kawo abubuwa guda uku waxanda su ne ginshiqan bautar Hausawa a cikin waqarsa ta "Gadar Zare": tsafi da bori da camfi. Har yanzu kuwa akwai virvishinsu a wasu wurare na qasar Hausa ga kaxan daga cikin baitukan:

Shi ne nake son mu taru mu gane
Camfi da qage rashin ilimi ne
Tasfi su bori rashin hankali ne
Aminci da su ko haqiqar vata ne
Da wauta da shirme da sharholiya

Ku gane mutane fa ba wata Inna
Da ke shanye hannu, qafa a ina?
Rashin lafiya ne kawai ku shina

Wajen likitoci akwai magana

Ku zan tambaya don sanin gaskiya

Wallahi Tallahi babu Nakada
Kar ma ku ce za ku nan wata shaida
Matsafa kawai ne suke farfaganda
……..
Sun ce a bori akwai Alhaji (Mudu Sipikin, Waqar Gadar Zare)

Haka nan kuma sukan sami duk wani labari ne ta hanyar mai kula da Iskoki. Misali, shiga wajen dodo ba tare da an ba shi abin da yake so ba, mutum zai iya mutuwa, wannan shi ya yi sanadiyar tsafin da ake yi. Sannan kuma sun yi imanin wuraren zamansu ko' ina ne, amma sun fi zama a kogon itatuwa da mararrabar hanya, da kan tsauni, da juji, kuma suna yawo kowane lokaci amma sun fi yawo da tsakar rana. Hausawa sun yi ban gaskiyaIskoki na iya rikixa zuwa komai, misali, mutum ko tsuntsu ko maciji ko guguwa ko kare ko mage da sauransu. Duk irin waxannan su ne Hausawa suke ta qoqarin bauta masu domin cim ma buqatunsu na yau da kullum. A taqaice, Hausawa sun yi imanin cewa Iskoki sun fi qarfinsu shi ya sa suke bauta musu. (Bunza, 2006).

Hausawa na da imanin cewa akwai misalin bori 150 waxanda ake hawa borinsu, kuma sun kasu zuwa kashi biyu wato farare da kuma baqaqe, aqidarsu ita ce farare ba su cutar kowa, kuma sukan taimaka masu ta fuskar buqatunsu, yayin da baqaqe kuwa muguntarsu ta yi yawa, yawancin taimakansu ta cutarwa ce (Bunza.2006:21-56)

Wannan shi ya sa a wannan lokacin suke cikin bauta musu kullum ta hanyar sadaukar musu da jinin dabbar da suke buqata. Buqatar iskokan shi ne shan jinin dabbar da take ta fita daban daga cikin sauran dabbobi irin ta. Daga cikin fararen iskoki, akwai sarkin fararen aljanu wato Sarkin Rafi ko Ibrahim, ko Sharu ko Zugu. Sannan akwai kuturun iska. Sai kuma Bafulatana wato inna uwa, akwai kuma xan Galadima wadda ya gwannance a caca ko kuma duk wata harkar shashanci.

A baqaqe kuwa akwai kure wanda yakan yi halayya irin na kura/kure. Idan kuma aka tava shi yakan sa wa mutum ciwon kai ko havo. Sai kuma gajimare, iska ce wanda ta fi zama a gidan tururuwa ko tsohuwar rijiya. Duk irin waxannan halaye nasu shi ya sa Hausawa suke bauta musu.

2.5.2 Tufafin Hausawa Na Gargajiya

Tun da aka halicci Annabi Adam, ya riqa amfani da ganye wajen kare jikinsa. Daga baya ne dan Adam ya fara amfani da fatar dabbobi domin kare tsiraicinsa, sai bayan da aka fara noman auduga wanda ya yi sanadin samar da tufafi. Kuma ta hanyar tufafi ne za a iya bambance tsakanin wannan qabila da waccan a gargajiyance, Misali a ga mutum da sanye da riga riqe da kwagiri da zani a xaura kuma sanye da hular sanyi, wannan yana nuna shi daga qabilar Inyamurai yake koda yake akwai kwaikwayon al’adu yanzu.

Kasancewar qasar Hausa tana da rairayi da kuma itatuwa ko bishiyoyi, a lokacin sanyi akwai tsananin sanyi haka ma a lokacin zafi ana tsananin zafi, wannan shi ya sa Hausawa suke da tufafi masu yalwa ko wadata, yawancin tufafi Hausawa akan yi masu aiki, a kuma rina wasu.

2.5.3 Ire-Iren Tufafin Hausawa na gargajiya:

Marubuta kamar su Funtua (2011) da Muhammed (2004) da Garba (1984) sun ce za a iya kasa tufafin Hausawa na gargajiya zuwa gida biyu, na maza da na mata, wanxanda Hausawa suke amfani da su a gargajiyance. Tufafin maza: Babbar riga, ita ta fi muhimmanci, Hausawa suna amfani da babbar riga a harkokinsu na yau da kullum, musamman abin da ya shafi biki kamar suna, da aure da bikin Sallah ko kuma wani biki na naxin sarauta.

Muhimmai daga cikin manyan rigunan Hausawa guda huxu su ne, gare da sace da shakwara.Waxannan su ne manyan tufafin maza na gargajiya, sai dai aiki ko ado shi yakan sanya su sami wasu sunaye daban-daban. Ta haka aka sami, wundiya da tsamiya aska tara da aska biyu da girken Nufe. Bayan waxannan akwai falmara da zubo/zubuni da alkyabba da abaya da jabba waxanda zuwan Musulunci ne ya sa Hausawa suka same su a sanadiyyar zaman su da Larabawa.

Huluna: Hausawa na da hulunansu na gargajiya tun kafin zuwan baqi, amma zuwan baqin ya sa suna qaru da wasu hulunan da dama daga cikin hulunan Hausawa na gargajiya akwai bakwala da dankwara da havar kada da zita da sauransu. Tufafin Mata: Zani shi ne muhimmi

daga cikin tufafin mata. Akwai zannuwa iri daban-daban waxannan zannuwa sun haxa da: Bakurxe da bubu da saqi da tsamiya da mudukare. Rigunan Mata: Dangane da rigunan mata kuwa, ga al'ada ba su da yawa kusan guda biyu ne, kawai daga rigar madukare, sai riga mai hannu. Bayan waxannnan tufafin matan da muka yi bayaninsu, irin su, fatari ko xan tofi da kallabi da saro da kuma xan irali. (Muhammad, 2004:16).

2.5.4 Aure a Qasar Hausa

Masana irin su Alhassan da Usman da Zarruq (1982) da Sani (1983) da Furniss (1996) da Adamu (1998) da Muhammed (2004) da Ali (2008) sun yi tarayya a kan maganar al'adun aure da ire-irensa a qasar Hausa. Sun ce aure babban al'amari ne ga xan Adam, domin shi ne sanadin haihuwa, ga Hausawa ba a lissafa wanda ba shi da aure a cikin dattawa. Saboda muhummancin aure har al'ada ta yarda a yi wa marar aure waqa a watan azumi. Al'adun aure a qasar Hausa sun bambanta daga wannan gari zuwa wancan. Bambancin kuma ya dogara a kan al'adun biki da na nema, amma akwai abubuwa da yawa waxanda yadda ake yin sa ya zama xaya a ko'ina. Musulunci yana buqatar sadaki da yardar waliyyan amarya da waliyyin ango, sannan kuma wajibi ne a sami jama'a da suka shaida. Ga sharhi a kan yadda ake gudanar da aure da tsarabe-tsarabensa:

Auren fari: Ga al'ada idan saurayi ya ga yarinya yana son ta da aure, ba zai tunkari uwarta ko mahaifinta ba, sai dai labari ya je kunnensu ta wata hanya daban. Mai 'ya mace zai riqa ganin samari suna ziyartar gidansa da zarar 'yarsa ta fara tasawa. Samari suna yi wa 'yan mata kyauta gwargwadon iyawa, su kuma 'yan mata suna kai kyautar da aka yi masu gida wurin

iyayensu mata ko kishiyoyinsu, ta haka ne iyaye maza suke jin labarin maneman ya'yansu mata. Idan manemi ya amince ga alama budurwa tana sonsa sai ya sanar da iyayensa. Ga al'ada saurayi ko yarinyar ba za su yi wa iyayensa magana kai tsaye ba, sai dai ta hanyar wani. Da zarar iyayen saurayi sun sami labarin yarinyar da yake nema, kuma idan ya zamanto suna da shirin su yi masa auren sai su aika da mutane don nema a wajen iyayen yarinyar. Galibi akan tafi da kyauta (mun gani muna so) gwargwadon qarfi.

A wannan zuwan iyayen yarinya ba za su yi wani jawabi ba, sai dai nuna farin cikinsu, tare da muna cewa za su yi shawara. Iyayen yarinya kan binciki halayen yaron da yake neman 'yarsu da kuma wasu bayanai daban da sauransu. Daga nan, sai su aika wa iyayen yaron da cewa sun amsa. Yaro ya ci gaba da nema bisa wannan izini ne yaron da budurwa za su ci gaba da ganawa wato zance.

Zance a gargajiyance: Wannan wani mataki ne na neman aure kuma wata hanya ce ta koyar da tarbiyya a tsakanin al'ummar Hausawa, wato alkunya.Yayin da saurayi da budurwa suka ga juna suna so kuma iyaye suka amince da ya ci gaba da nema, saurayi kan je wajen budurwar da abokinsa domin zance, ita budurwa takan fito ne tare da 'yar rakiya, yarinya qarama, sukan fito ne tare da wata shimfixa a soro, inda kowa zai zauna a gefe, saurayin da abokinsa a gefe xaya, ita kuma budurwa da qawayenta a gefe xaya, galibi irin hirarrakin da ke gudana kan faru ne a tsakanin abokanan saurayi da qawayen budurwar. Su kuma [saurayi da budurwa] alkunya ta hana su sakewa, haka za a yi ta ci gaba har wani lokaci mai tsawo kafin su yi sallamar sai da safe haka wannan zance zai ta gudana har zuwa lokacin biki.

Lefe: Wanda aka yarda za a xaura aure da shi zai kawo dukiyar aure tare da lefe, waxansu kuma sukan ba da dukiyar aure tun kafin a sa ranar aure. Ana ba da kayan tufafi na amarya wato zannuwa, kalluba, da takalma, taguwoyi da kayan kwalliya, da su man shafawa da turare da hoda da sauran tarkace. Yawan abin da za a sanya a kayan lefe ya danganta da qarfin mai aure da kuma al'adan gari.

Kayan Xaki: Iyayen yarinya hakkinsu ne su shirya wa 'yarsu kayan xaki, za su yi tanadin gado da shimfixa da kayan girki wato tukwane da murhu da kwanuka, da turmi da tavarya. Ban da waxannan kuma suna aika wa ango da kayan abinci kamar su gero da dawa, da shinkafa da kayan miya da kuxi qalilan don cefane.

Qunshi: Idan ya rage kamar kwana uku zuwa ranar xaurin aure ana kama yarinya a sa ta a lalle, ga al'ada amarya da qawayenta za su gudu su vuya a wani wuri. Qawayenta tare da wata kakarta za su gano ta, su kama ta da qarfi. Daga nan ne sai wata tsohuwa ta shafa mata lalle, ta bar dandali ke nan, sai ka ji amarya da qawayenta sun fashe da kuka. Ita kuma tsohuwar sai ta yi ta guxa tana cewa; wayyo kaico, su wance an girma.

Daga nan sai a kai amarya gidan wani uba ko xan uwa wanda aka daidaita shi zai yi mata qunshi na farko, daga wannan gidan sai a tafi wani gidan. A ko ina sai an yini an kwana biyu a wajen, sannan ta dawo gida a rana ta uku wadda a wannan maraicen ne za a kai ta gidan

miji.Wasu kuma ba su zuwa gidajen dangi, wasu iyayen kuma sukan hana yarinya gudu, kuma a hana ta fita, sai qawayenta za su rinqa shigowa.

Xaurin Aure: Ana qare qunshi a ranar xaura aure, wasu suna xaura aure da asuba wasu kuma da azahar, iyaye ko wakilan ango su za su kawo goro mai yawa yadda za a xiba a ba dangin amarya a kuma ba dangin ango a sami mai yawa yadda za a rabawa jama'ar da suka taru, daga nan sai wakilan ango da na amarya su zo gaban liman a tsaida sigar aure kowa na nan.Liman zai ce ''Ina waliyyan amarya da na ango? ''sai waliyyan su zo su zauna a gaban liman daga nan sai ya tambayi sunayen masu aure, misali sai waliyyan su ce ''Bello da Zainab'', bayan haka sai Liman ya nuna masu yadda za su yi, sai jama'a su ji waliyyin amarya ya ce''na ba da 'yata Zainab aure ga Bello a bisa sadaki kaza…''sai kuma a ji waliyyin ango ya ce''na karva masa''. Bayan an yi wannan ne liman zai yi addu'a wanda a cikinta zai ambaci Bello da Zainab da sadakin duk jama'a su shafa.Daga baya kuma sai a yi addu'ar fatan alhairi gare su da sauran jama'an gari masurai da waxanda suka rasu.

Tarewa: Idan maraice ya yi sai a shiga shirin tarewar amarya, a al'ada akan jira dangin ango kafin a kai ta. 'Yan xaukar amarya sun kasu kashi biyu, akwai akwai dattawa mata da za a turo su zo cikin lumana su gai da iyayen amarya su nemi a ba su amarya, iyayen amarya za su yi maraba da su, sannan su lulluvo amarya a zo a kai ta wurin ubanta ko waliyinta ya yi mata gargaxi tare da addu'a, in ya gama sai amarya da 'yan rakiya da kuma waxanda suka zo xauka daga wajen ango a tafi a kai amarya xakinta ba tare da wata hayaniya ba. Kashi na biyu shi ne na yara maza da 'yan mata waxanda za su zo da kwaramniya, kaxe-kaxe wai sun

zo xaukar amarya. Idan sun zo su ma za a yi masu maraba sai kuma a lullave wata yarinya a ba su a ce “ga amarya nan” ita wannan ita ce amaryar boko, wato amaryar gangan: ita wannan yarinyar ake xora wa a doki ko kuma yanzu mota, a yi yawo cikin gari ana waqar abokin ango ya yi sa’a har a isa gidan ango.

Qunshin Ango, Ango zai koma gidan abokansa a ranar da amaryarsa ta tare a gidansu. A nan zai jira har yini uku za a raka shi gida a daren yini na uku. Al’adu sun bambanta a qasar Hausa a bisa abubuwa da ake yi wa ango a wajen qunshi. A inda ake qunshi sosai, wata dangin uwar ango za ta zo ta shafa masa lalle. Sannan a bi da qunshi sosai, wasu ba su yin qunshi sai dai a yi zaman hira kawai. Amma wannan irin na zamani ne kuma ba al’adar Hausawa ba ce. A wasu wurare akan aro wa ango alkyabba daga wajen limanin gari ya yafa a lokacin da yake angonci.

Sayen Baki: A lokacin da ango yake can wajen angwancin, iyayen amarya za su ci gaba da shirya mata xakinta. A daren yini na uku sai abokan ango su raka shi gida, za su iske amarya da qawayenta. Abokin ango zai yi sallama, ‘yan mata za su amsa, amma ita amarya ba za ta yi magana ba, za ta yi lulluvi ta koma gefe guda shi ma ango zai shigo amma ba a gaba yake ba. Samari da ‘yan mata za su ci gaba da hira har wani lokaci za su zare jiki a hankali su fita, sai a bar amarya da babbar qawarta (qawar rana) da ango da abokinsa, da ma duk hirar da ake yi amarya ba ta tankawa kowa. Idan sauran samari da ‘yan mata sun fita sai abokin ango ya taqalo amarya da magana amma sai ta qyale, sai qawar ta ce ita ma da take maganar bakinta ya fara yami, gara ta yi shiru. Sai abokin ango ya ce “Amarya ba ki mana magana ne saboda

yamin baki? To bari mu ba ku goro" sai ya xauko xan guntun goro ya miqa wa qawar, sai ta qi karva ta ce ya yi kaxan, sai ango ya ce, ni bani ga wani nan guda a wurina sai ya miqa wa qawar sai ta karva, sai abokin ango ya ce da ci min bakin naku ba na goro ba ne".

Da haka dai za a cigaba da hira har a kai ga roqon amarya ta yi magana. abokiyarta ke magana, daga nan sai a shiga cinikin baki daga mafi qanqantar kuxi har zuwa kuxi masu xan dama, da turare da 'yan tarkace.

Shagulgulan Biki: A kusan mako guda ake yinin biki aure, ana yin wasu abubuwa na nuna farin cikin masu biki ana kaxe- kaxe da raye-raye, a wasu lokuta ma har ana kaxa kixan al'ada na sana'ar masu aurenta na gado, idan maqera ne akwai kixan da ake yi wa maqera suna kixa da waqa wasu kuma suna roqon baki. Bayan wannan kuma akwai waxanda karatun Alkur'ani suke yi.

Kamar yadda aka riga aka ambata akwai 'yan bambance bambance a wajan al'adun aure daga waccan nahiya ta qasar Hausa zuwa wancan. Wasu daga cikin abubuwan da suka bambanta, sun haxa da walima, buxar kai, budurcin amarya, kifin murhu da sauransu.

2.5.4.1 Ire-Iren Aure

Bayan auren fari akwai wasu nau'o'i na aure da ake yi a qasar Hausa;

1. Auren Sadaka

2. Auren Jawara/Bazawara

3. Auren Je-ka-da-kwarinka

4. Auren Yada Lada

Auren Sadaka: Kowa yana nema wa jininsa albarka, saboda wannan dalili ne wasu mutane suke ba da ‘ya’yansu mata a aure sadaka, ko da an karvi kayan samari, ba za a tava ba, sai a jiye uba zai yi shawara da matarsa, ya shaida ma matar niyyarsa ta ba da xiyarsu aure sadaka, In uwa ta amince, sai uba ya sa a maida wa kowa kayansu a kuma shaida ma jama’a cewa za a yi sadaka da yarinya.

Daga nan ne kuma sai samari su sake salon kyauta. Duk abin da za a kawo sai kimanta masu kawo kyauta suna kiran wannan qoqon bara, to da iyaye sun daidaita shawara ba a daxewa sai xaura aure da wanda yarinya ta zava a cikin masu neman ta.

Auren Bazawara: Jawara ko bazawara ita ce mace wadda ta tava aure, amma sai suka rabu da mijinta saboda rashin jituwa, ko kuma mutuwar shi mijin.

Galibi auren bazawara ba shi da tsada kamar na buduwa, a wasu lokuta akan sami inda masu zarafi suke kashe kuxi da yawa in bazawarar da zai aura yarinya ce, ko kuma iyayenta suna da wata martaba. A auren zawara babu kauce-kauce da yawa da jawo iyaye daga farko har karshe. A nan mai nema yana magana da ita matar kai tsaye, sai sun daidaita da junansu sannan ake kiran waliyyai su zartar da xaurin aure.

Je ka da Kwarinka: Wannan aure ne na dattawa galibi ita wadda aka aura ba za ta iya barin gidan da take ta tare a gidan miji ba, sai shi mijin ya riqa zuwa wajen matar ya kwana kuma

da safe ya koma nasa gidan. A irin haka wataqila matar tana da iyali daga auren baya, ba ta buqatar ta bar gidan ya bar iyalin da gidan a hannu wani.

Auren Yada Laya: Jefi-jefi akan iske wasu mazajen masu yawan husuma. Wannan lokaci har vatawa ta kawo mutuwar aure. Da an xan rabu kuma sai a yi wa juna haquri a riqa marmarin komawa daga baya kuma sai a mai da auren.

2.5.5 Haihuwa a Al'adar Bahaushe

Manazarta al'adu kamar CNHN (1981) da Gabi (2006) da Kulumbu (2006) da Sarkin Sudan (2008) sun yi tarayya a kan cewa al'adun haihuwa sun bambanta daga wannan wuri zuwa wancan, kamar yadda al'dun aure suka bambanta. Daga lokacin da mace ta sami cikin farko babu wata al'ada da ake yi muhimmaya sai bayan cikin ya yi wata bakwai. A nan al'ada ta kasu kashi biyu, wasu iyaye sukan fi son xiyarsu ta koma gida ta haihu a gabansu, irin wannan komawa gida saboda haihuwa ita ake kira goyon ciki. Wasu kuma sukan bar xiyarsu ta haihu a xakinta. Amma duk da haka akan yi wani xan biki da ake yi wato xaurin kirji.

Idan mijin yarinyar saurayi ne, iyayensa da iyayen matar za su daidaita ranar da za a yi xaurin qirji. Wajen maza za su ba da zani domin wannan biki, in ranar ta zo sai a taru a yi abinci, a ci a kuma rabawa dangi domin sanarwa, ita mai ciki za a sanyata ta yi wanka, kuma daga wannan wankan sai ta ajiye tufafin da ta saba sanyawa,ta xaura sabon zanen da aka kawo ta rufe qirjinta da shi kuma ta yi xammara.

Ga al’ada a zamanin da can, akan sa magunguna na sassaqe da saiwoyi a cikin ruwan da za a yi wa mai ciki wanka,kuma iyayen yarinyar ne za su yi mata wanka,ba ita za a bari ta yi ba. A waccan lokacin matan Hausawa ba su sanya tare mama ko xan tofi, duk cikar yarinya za ta yi za ta bar qirjinta a buxe sai ta sami ciki an yi wannan bikin sannan za ta fara xaura zane a kan qirjinta. (Muhammed, 2004:16).

In kuma ba ta sami ciki ba, sai qirjinta ya qwanta da kansa tukun, sannan za ta fara xaura zani a qirji. Da wadda aka yi wa xaurin qirji da kuma wadda ta tafi goyon ciki akan taimaka masu da magunguna na sassaqe.

Idan haihuwa ta zo akan sami wata tsohuwa a kusa da mai haihuwa wadda za ta taimake ta, ta kuma taimaki jinjirin da aka haifa, wannan ita ce ungozoma, kuma takan zama ‘yar uwar mai haihuwa, amma a wasu wuraren akan sami tsofaffi waxanda suke wannan irin aikin kamar sana’a.

Ungozoma: Ita ce wacce take taimaka wa mai haihuwa da kuma jinjirin da aka haifa. Ga al’adan aikin ungowanzoma shi ne yanke cibiya da zaran mai haihuwa ta sauka, bayan wannan kuma sai ta xauki xawainiyar dafa ruwan zafi wanda mai jego za ta yi wanka da shi ta kuma a riqa wankan jariri.Ana buqatar mai haihuwa ta rinqa gasa qarqashita da ruwan zafi har zuwa mako guda bayan ta haihu, in yarinya ce iyayenta ko unguwanzoma,su suke

taimaka mata,wadda ta saba kuma ita take yi da kanta. Bayan wanka da ruwan zafi, safe da maraice har kwana arbain mai jego za ta riqa shan ruwan xumi, kuma duk abincinta ko kununta za a sa yaji.

Yadda Ake Raxa Suna: Za a raxa ma yaro kiran salla a kunansa na dama, a kunnasa na hagu kuma a yi masa iqama, sanan kuma a raxa masa sunansa misali Ibrahim ko Abdullahi ko Muhammad da sauransu. Irin waxannan sunaye su ake kira sunan yanka. A rana ta bakwai sai ‘yan uwan mijin mai haihuwa su zo da rago musu raxin (zanen) suna. Bayan jama’a suka taru a safiyar rana ta bakwai sai iyayen na wajen maza su shida wa malami sunan jaririn, shi kuma malam sai ya je wurin da aka shirya za a yanka rago, yayi addu’a ya yanka ragon da sunan da aka sa wa jaririn. Bayan wannan sai addu’o da kuma nema wa jaririn tabarruki, sannan sai a bar maroqa da sauran masu mutane ci gaba da shagalin suna. Ana aika wa dangi na kusa da naman suna, ga al’ada naman suna a rabe yake, ana soya kayan ciki a rarraba wa jama’a duka na kusa.cinyar dama ana ba dangin matar da ta haihu, ta hagu kuwa sai a ba dangin miji. Gadon baya na mai haihuwa ne, wanzami kuma nasa wuya ne, Malami zai sami buzu, ita kuwa ungozoma sai a ba ta kai da qafafu. Amma wannan bayanin ba a ko’ina a qasar Hausa ake bin sa ba.

Sunayen Yanka Da Laqabi: Suna kalma ce da ake amfani da ita domin rarrabewa tsakanin wannan da wancan, haka kuma ta suna ne, akan danganta mutum da al’ummar da ya fito daga cikinta, wato kusan kowace al’umma tana da irin nata sunayen, sai dai ko addini ya haxa, misali idan aka ce, Abdullahi, ko Ahmad, ko Ibrahim to da wuya a iya bambance

kowace qabila ce. Amma in aka kira mutum da shekarau za a gane Bahaushe ne, sannan Adebayo daga qabilar Yarabawa yake, Nwachukwu kuwa daga qabilar Igbo ko Inyamurai yake.

Kafin Hausawa su amshi kiran addinin Musulunci, sukan dubi lokaci ko halin da aka yi haihuwa su sanya wa wanda aka haifa sunan da za a rinqa kiran sa misali sammako, Na-hantsi, Damina, Marke, Shekarau, Ci-wake, Talle, Ajuji, Tanko, Barau, Cindo, Kande, da sauransu, duk sunaye ne da Hausawa suke sa wa'ya'yansu kafin addinin Musulunci. Sunaye irin su Mati/Mato da kuma Tanko, sunaye ne da ake sa wa yara maza waxanda mata suka gabace su. Sunaye irin su Talle, Audi, akan sa wa waxanda aka haifa bayan rasuwar mahaifinsa ko mahaifiyarsa.Yarinya qanwar maza ita ce kande. Magaji ko Magajiya akan sanya sunan ne ga wani babba da ya rasu a gidan domin a dinga tunawa da shi.

Matar da 'ya'yanta suke yawan mutuwa tun suna qanan tana kiransu da sunan da yake nuna wai kiran su da sunan da ba ta damu da xan ba, tun da zai mutu da garaje ne, waxannan sunaye su ne kamar haka; Toka, Angulu, Jibji, Ajuji, Barau, Barman. Bayan Hausawasun karvi addinin Musulunci, amma duk da haka sun sabunta wasu na kafin Musulunci, misali irin su Ajuji zuwa Barman ko Barau, da Azumi, da Labaran, da Sallau da sauransu.

Sanadiyyar zuwan addinin Musulunci, ya taimakawa Hausawa wajen samun sababbin sunaye waxanda suka danganci rana, wato Ladi, Danladi, Ladidi, wato waxanda aka haifa ranar Lahadi. Liti, Danliti, Altine, Tani a ranar Litinin:Talatu, Dantala a ranar talata. Balaraba,

Balarabiya, Bala, Larai a ranar Laraba. Lami, Danlami, Na- Lami a ranar Alhamis. Danjuma, Jummai, Jummalo a ranar Jumma'a. Asabe da DanAsabe da Assibi a ranar Asabar. Bayan samun irin waxannan sunayen akwai irin su Abdullahi, Abdulkarim, Abdulmajid da sauransu, akwai kuma sunaye na sahabbai ko Annabawa, misalin Aliyu, Abubakar,Muhammad , Ishaq, Idris, da sauransu.

Bayan wannan a kan xauki xaya daga cikin halittun ubangiji a haxa su da addini, irin waxannan sunaye sun haxa da ShamsuddIn, Kamaluddin, Saifullah, da sauransu. Dangane da 'ya'ya mata kuwa, Hausawa kan sa sunayen fittatun mata, waxanda suke a tarihin Musulunci akwai irin su, Hauwa'u, Hadiza, Maryam, Aisha, Amina, Rabi'a.

Akwai kuma sunaye irin su Alhaji, Hajiya waxanda ake sa wa yaran da aka haife su da babbar Sallah, kafin lokaci ko bayan Sallah da kwana uku. Sunaye irin su Yawale ko Yabi, akan sa wa yaro ko yarinya, idan aka haife su a Makka ko Madina ko kuma samun cikin su a can. Akwai rukunin sunaye waxanda malamai ke sanyawa 'ya'yansu da suka haifa sun haxa da Lantana, da Makana, da Shakunu, da Izawaqa, da Adiya, da Ara'aita da Yasin da sauransu.

2.7 Ma'anar Fim

Fim dai yana xaya daga cikin nau'o'in hanyoyin sadarwa zamani don isar da saqo da wayar da kai ga rayuwa mai kyau ko cusa wata manufa mai kyau ko kishiyar haka ta hanyar amfani da na'urar xaukar hoto, sannan a sarrafa shi zuwa fai-fai na bidiyo ko CD (Umma,2008:61).

Shi ko Xakin-gari, (2004) cewa ya yi fina-finan Hausa sun samo tushe ne daga rubutaccen wasan kwaikwayo wanda Hausawa ba su san da shi ba sai bayan zuwan Turawan mulkin mallaka, waxanda suka kafa makarantun boko da hukumomin fassara da na talifi da dai sauransu, waxannan su suka taimaka wajen samuwar marubuta da kuma litattafai.

2.7.1 Rabe Raben Fina-finan Hausa

Manazarta sun rarraba fina-finan Hausa zuwa kaso daban-daban, a ra'ayin Umma A. Inuwa (2009) tana ganin an raba fina-finan Hausa ne a bisa yadda aka samar da su daga na'urar xaukan hoto. Wato an raba fim na Hausa zuwa gida uku. Na Bidiyo da *CD* da *DVD*.Fina-finan bidiyo su ne na farko da aka riqa kalla domin a lokacin da aka fara harkokin samar da fina-finan Hausa, ba da na'urar *CD* ko *DVD*ba ne.

Dangane da *CD da DVD* kuwa, sababbin abubuwa ne a wurin Hausawa domin ba a fara amfani da su ba sai a wajen shekara 2007 inda abin ya fara zama ruwan dare. Kuma kusan duk fina-finan da aka yi a baya a yanzu an saka su a *CD da DVD* ne (Inuwa, 2009:70).

Ita kuma Abbas (2008), ta raba nau'o'in fim dangane da jigon da ake gina fim xin kan sa misali fina-finan soyayya (*love*) da na ban dariya (*comedy*) da wahalhalu da sarqaqiyar rayuwa (adventure) da na ban tsoro (Horror) da na ban tausayin vacin rai (*tragedy*) sai na qarshe fim xin tarihi (*documentary*). Amma shi Chamo, (2005) gani yake za a iya raba fina-finan Hausa zuwa manya-manyan kaso guda biyu waxanda suka haxa da fina-finan zamani da kuma na gargajiya.

Fina-finan zamani su ne waxanda jigoginsu da kuma yadda aka shirya su, suna nusantarwa ne a kan harkokin zamani, kayayyakin da ake amfani da su ma na zamani ne, misali tufafi da gidaje da yanayin zamantakewa. Bayan haka a qarqashin wannan kaso za a samu waxanda suke jigonsu na faxakarwa ko ban-dariya ko soyyaya ko siyasa, waxanda suke su ne manyan jigogin fina-finan Hausa. Kuma kashi tamanin daga cikin xari na fina-finan Hausa sun faxo cikin wannan kaso. Misali fina-finai kamar su *Rana da Sutura da Biki da Badali da Babban Gida da Wasila da Aisha da Xan Adam da So da Ibro Xan Daudu da Mujadala da Kumbo da* sauransu.

Fina-finan gargajiya kuwa su ne waxanda aka yi amfani da kayayyakin gargajiya wajen shirya su. Sannan aka yi amfani da kyawawan al'adu da xabi'un Hausawa wajen aiwaar da fim xin, misali kulawa da irin su kunya da kara da kawaici da kuma sanin ya kamata yayin aiwatarwa.

2.7.2 Samuwar Fina-finan Hausa

Marubuciya Nafisa (2002) ta ce idan aka yi maganar shigowar fim Nijeriya, to bai wuce qarni na ashirin ba. Turawan mulkin mallaka ne suka shigo da shi. Bayan samun 'yancin kai, sai aka samu kafuwar gidajen Talabijin kamar a Ibadan wanda kuma shi ne ya kasance na farko a Afirka a shekarar 1959 wato *Western Nigeria Television Service,*WNTS Nafisa (2002) ta qara da cewa daga nan kuma sai Arewa ta karva ta yi nata 1962 wato,*Broadcasting Corporation of Northern Nigeria,*BCNN a Kaduna.

Bayan kafa waxannan manyan gidajen Talabijin, sai aka fara samar da fina-finai waxanda ake amfani da na'urar "*celluloid*" wajen xaukarsu. "*celluloid"* na'ura ce da ake xaukar fim da ita ake kallo mai dodo da ake kira "negative" kuma ana amfani da harshen Hausa wajen yin fina-finan . Fim na farko da aka yi aka kuma xauke shi da na'urar "*Celluloid*" cikin Harshen Hausa shi ne "Baban Larai" na wani xan Arewa mai suna Alhaji Adamu Halilu a 1968. Sai kuma a 1976 aka yi "Shaihu Umar" (Nafisa Adamu, 2002:8).

A wata lacca da muka yi a matsayinmu na xalibai masu karatun digiri na biyu a shekarar 2001 da Malam T.M 'Yaradua a kwas mai suna (Hausa Drama) Hau 8219, Jami'ar Bayero, Kano mun yi wani bincike na haxaka inda aka gano cewar farkon samuwar fina-finan Hausa abu ne da ya faru a qarshen qarni na 20, tubalin samuwar fina-finai shi ne wasan kwaikwayo. Shi kuwa wasan kwaikwayo ya samu bayan Turawan mulki sun zo, sun kafu tare da shimfixa tsare-tsarensu da suka shafi mulki da ilimi da sauransu. Wasan kwaikwayo ya kasance xaya

daga cikin manyan rabe-raben adabin zamani guda uku. Sauran su ne waqa da kuma rubutun zube.

Tun kafin shigowar adabin zamani, wato kafin zuwan manyan al'umma guda biyu, wato Larabawa da Turawa, Hausawa suna da wasannin gargajiya masu tarin yawa da suke qunshe cikin rayuwarsu, kamar wasan bori da kalankuwa da shan kabewa da wasan tashe da sauran suUmar, (1987:19). A tarihance an fara samun kamara a yammacin Turai a 1932, an yi wani Bature xan qasar (*Belguim)* wanda ya qirqiri na'urar xaukar hoto, kuma hoton zai yi wani motsi, ita wannan na'urar sunanta*Phenakistoscope* wannan na'ura ita ce ta farko ta xaukar fim, to, daga baya ne sai wani baturen Amerika mai suna "*Excel*" ya qara daraja na'urar '*Phenakistoscope'* zuwa '*kinstoscope'*. An qara samun ci gaba a fannin daga wannan na'ura zuwa na majigi tare da taimakon *Joseph Platan* da *Nieppe Ilis* don nuna hoto da fina-finai. ('Yar'adua, 2001).

'Yar'adua (2007) ya qara jaddada cewa haqiqa duk wani ci-gaba da aka samu duk ya hau ko ya bi ta bisa kan nasu qoqarin, wanda yin haka ya haifar da sababbin na'urorin xaukar hoto na zamani da Hausawa suke amfani da su a yanzu wajen shiryawa da kuma gabatar da fina-finan Hausa a yau. Wato na'urar xaukar hoto ta bidiyo da kuma talbijin.

Halima Xangambo, (1999) ta qara jaddada cewa wasan kwaikwayo na farko da aka samu shi ne aka rubuta shi cikin tsohuwar Hausa mai suna "Wasan Muhammadu Agigi" a shekarar 1902. Wanda ya rubuta shi, shi ne wani xan kasuwar Kano da ake kira Haji Ahmad

Masukwani Kano, savanin da, da ake cewa wasan kwaikwayo na farko shi ne Six Hausa plays na Dr. R.M East. Wasan Muhammadu Agigi wani Bajamushe ne mai suna Dr. R. Prietze ya rubuta shi da harshen Jamusanci. Sannan Sisela Steden Stickre Brickey ya fassara shi zuwa turanci shi kuma Farfesa U.B Ahmad na Jami'ar Ahmadu Bello ya farauto shi a can Jamus.

Wasa na biyu shi ne *Six Hausa plays* Dr. R.M East a shekarar 1930 kuma ya samu a sandiyyar kafa hukumar fassara wato *Translation Bureau* da aka kafa a shekarar 1929 a qarqashin Mr. C.E.J Whitting (Yahaya, 1988). Ta haka aka samar da littafi wasan kwaikwayo da dama cikin harshen Hausa waxanda suka haxa da littafan wasan kwaikwayo irin su "*Wasan Marafa*" na Abubakar Tunau da "*Malam Inkuntum*" na A.A. Dogondaji da "*Zamanin Nan Namu*" na Sha'aibu Maqarfi da sauransu da yawa. An yi ta ci gaba da samarwa da kuma aiwatar da wasan kwaikwayo rubutattun da wanzar da wasannin zuwa majigi da silima ko a talabijin da rediyo da sauran kafafe makamantansu.

Bayan haka, akwai wasu hanyoyi da suka taimaka wajen samar da fina-finan su ne, akwai qungiyoyin wasan kwaikwayo na musamman waxanda aka kafa domin yin wasannin kwaikwayo a dandamali da kafa gidajen rediyo da talabijin a jihohin Arewa da kamfanoni masu zaman kansu da sauransu.

A nan Nijeriya za a iya alaqanta samuwar fim da gudummawar da hukumomin suka ba da na "*Native Authority*" take yi na wayarwa da mutane kai na sanin sababbin dabaru na koyon aikin gona na zamani, inda aka yi amfani da fim wajen wannan harka. Misali an shirya fim

don bunqasa noman gyaxa da auduga. Wannan shi ya haddasa samar da fim xin “Baban Larai”.

Kamfanin “*Nigerian Tibacco Company*” yana daga cikin kamfanin farko da ya shirya fina-finan majigi na Hausa. Kuma Hausawa ne ke fitowa don jan hankalin manoman taba da mashayanta su qara qaimi. An dai shirya fim xin ne a shekarar 1970 wanda jigonsa shi ne koyar da shan taba da kuma yaxa ta. Suna kuma yin wasu tallar taba mai dagi da taba mai zobe da kuma taba Target (Adamu, 2001:9)

Kamfanin sukari mai iyali wato mai suna da Turanci “*Tate Family Sugar*” shi ma yakan yi amfani da nuna hotunan majigi, sai dai su, sukan yi tallan ne, suna kuma nuna majigin don jawo hankalin jama’a (‘Yar’adua, 2007:31) dukkan wannan sun qara ba da haske wajen samar da fina-finai.

Samuwar gidajen rediyo da talabijin a jihohin Arewa, shi ma ya taimaka wajen samar da fina-finan Hausa. A da duk wata manufa ko tsari na gwamnati da ake so Jama’a su sani, to, ana yin amfani da waxannan kafafe don a yaxa. Wannan sai ya ba da haske wajen shirya wasannin kwaikwayo don faxakar da al’umma ko nishaxantarwa. A gidan rediyon Kaduna mallakar gwamnatin Arewa da aka kafa a shekarar 1961, Marigayi Qasimu Yaro ya shirya wasan kwaikwayo da aka dinga gabatarwa a gidan rediyon a shekarar 1965. An sami ci gaba da wanzuwar wasannin gidan rediyo shekarar 1971 zuwa jihoyin Arewa, ko da yake tun kafin nan an gabatar da wasan zamanin namu da zaman duniya iya wa ne a rediyo Kaduna. Daga

baya a shekarar 1972 aka shigo da wasan Samanja mazan fama, bayan an kammala yaqin basasar qasar nan wasan ya ci gaba har yau, kuma akan watsa a gidajen Talabijin. Daga cikin wasannin gidan talabijin na jihohi akwai:

Gidan Talabijin	**Sunan Wasa**	**Sunan Wanda ya Rubuta**
N.T.A Kano (Danhaki)	Taskira Asirin mai xaki	Mustapha Muhd
N.T.A Kano	Karo da Goma	Sharu Lawal Adam
N.T.A Kano	Xan Kurma	Garba Ilu
N.T.A Kano	Ba'are	Danlami Dauda
N.T.A Kaduna	Quliya Manta Sabo	Dauda Ahmad
N.T.A Kaduna	Magana Jari ce	Abubakar Imam
N.T.A Kaduna	Shaihu Umar	Sir Abubakar Tafawa Balewa
C.T.V Kano	Na dakama	Usman Abdullahi
C.T.V Kano	Bakan gizo	A.A Kurawa
C.T.V Kano	Hadarin Qasa	Malam Abdu
K.T.R.T.V. Katsina	Ramin Kura	Armaya'u Liti

Yawancin masu shirya wasannin gidajen talabijin da na rediyo sukan karvi goron gayyata zuwa wuraren biki ko taruka ko lokutan bukukuwan Sallah da ire-irensu don gabatar da wasa. Wannan sashen akwai mutane irin su Danhaki da Alhaji Buguzum da Samanja da Qasimu Yaro da Xankurma da Golovo da sauransu. A 'yan wasan wannan zamani kuwa, akwai irin su Rabilu Musa (Ibro) da Ali Nuhu da Sani Danja da Nafisa Abdullahi da sauransu da dama.

Ta fannin qungiyoyi kuwa, akwai irin su Tumbin Giwa wanda Auwalu Isma'il Marshall shi ne shugabanta, sannan akwai su "Janzaki *motion pictures*", qarqashin Muhammad Balarabe.

Misali fim xin *Gimbiya Fatima* 1-4 an yi a shekarar 1994. *Munkar* 1995 da Mandawari *Enterprising* da Iyantama *Multimedia* da *Tsoron Allah Garkuwa*. Waxannan qungigoyi na daga cikin jiga-jigan havakar fina-finan Hausa.

Wani muhimmin abu da ya taimaka wajen samar da fina-finan shi ne tasirin fina-finan qasashen waje irin su Indiya da Sin da Turawan yamma, don akan xauki wani salon na fina-finai wajen a sanya cikin na Hausa domin Fim xin Hausa ya yi armashi don neman ci-gaban fina-finan Hausa.

Adabin zamani har ila yau ya taka rawa wajen samar da fina-finan Hausa. Bayan hovvasan da aka yi na kakkafa hukomomin irin su hukumar fassara da hukumar Talifi da Hukumar NORLA da NNPC maxaba'ar buga littafai ta Arewa da kamfanin Gaskiya wanda hakan ya yi sanadiyyar samun qaruwar littafai da dama a labarai da na wasan kwaikwayo, kamar su *Shaihu Umar* naSir Abubakar Tafawa Balewa da *Magana Jari Ce* na Alhaji Abubakar Imam da *Kulva Na Varna* na Umar Xanjuma Katsina, daga baya aka mayar da su fina-finai (Adam, 2002:10).

Sauran abubuwan da suka taimaka wajen samar da fina-finan kamar yadda Inuwa, (2002) da Abdullahi, (1988) da Rabi'u (1981) da Nasiru (1992) suka zayyano, sun haxa da wadatar na'urai xaukar hoto da kafa hukumonin adana kayan tarihi da al'adu da sha'awar 'yan wasa wajen samar da gogaggun 'yan wasa da masu shirya fina-finan Hausa. A nan idan aka yi la'akari da manyan jiga-jigan masu shirya fina-finan Hausa za ka tarar yawancin su marubuta

litattafai ne na labarai wanda daga baya suka rikixa zuwa harkar fina-finai kaxan daga cikinsu akwai; "*Mandawari Enterprises*" da "*Gidan Dabino Entertainmentand Publishing*". Sai masu shirya Fim irin su Bala Anas Babinlata wanda shi ya wallafa littafan; *Amintacciyar soyayya 1-2 da Idan Ungulu ta Biya Buqata da Idan Vera da Sata* , daga baya aka maida labaran littafa zuwa fim wato *Hali da Saudatu da Rikicin Duniya da Bakandamiyar*. Ado Ahmed Gidan Dabino shi ma ya rubuta littafai kamar *In da So Da Qauna* da irin su *Wani Hani ga Allah* da sauransu. Kuma ya ci nasarar mayar da wasu fina-finai, wasu kuma ba littafai ba ne, kawai fina-finai ne ya shirya su musamman. To a dalilin xaukar nauyin shiryawa da kuma yin fim xin, sai aka samu havaka da ci gaba wajen samun fina-finan Hausa fiye da yadda ake zato.

Daga lokacin da aka fara shirya fina-finai na Hausa, wato misalin shekaru kamar ashirin da bakwai da suka wuce zuwa yau, zai yi wuya mutum ya yi gaggawar faxar adadin fina-finai da aka shirya. Abin lura a nan shi ne kusan duk manyan garuruwan da ke a arewacin Nijeriya, za a sami kamfanunnukan shiryawa fim da furodusa aqalla guda. Ga wasu daga cikin masu shirya fina-finan; Sarauniya *Production* da Iyan Tama *Multimedia* da Ibrahimawa *Production* da Tumbin Giwa *Production* da Gidan Dabino Video*Production* da MJ Video*Production* da sauransu.

2.7.3 Muhummancin Fim Ga Al'umma

Masana fim irin su Adamu da wasu (2004) da Gidan Dabino da wani (2004) suna masu cewar fim tantagaryar kimiyya da fasaha ce, kuma rayuwar xan Adam ce ake nunawa. Fim yana

xauke da tarihi da xabi'un jama'a da muhallinsu da abincinsu da kuma suturarsu, musamman bisa harshensu da tsarinsu na rayuwa da hanyoyin tunaninsu da kuma falsafar rayuwar mutanen da ake yin fim xin don su. Har ila yau, fim hanya ce ta sadarwa da ilimantarwa da jan hankali da nishaxantarwa da faxakarwa da yaxa manufa da tallatawa. A dunqule-kafa ce daga cikin kafafen yaxa labarai. Sannan kuma hanya ce ta kasuwanci da samar da aiki yi ga jama'a.

A taqaice, manazarta adabin suna ganin ana yin fim ne domin a samar da abubuwa kamar : tsoratarwa da yaxa wata manufa da ilimantarwa da wayar da kai da sanarwa da nishaxantarwa da tallatarwa. Amma masana irin su Yakub (2003) da Muhammad (2002) daNwogu (2007) da Adam (2012) sun nuna yadda fina-finai suke taka rawa wajen fito da matsayi da darajar da Allah ya yi wa mutum a cikin al'umma ta hayar haska harkokin rayuwarsa a cikin al'umma. Misali, wasu na ganin ta harkar fim ne za a iya qwato wa mata haqqinsu da hana cin zarafin yara. Wasu kuma na ganin ai ta hanyar fim ne za a iya haxa kan al'umma a zauna lafiya.

Daga xan abin da waxannan masana suka faxa a kan fina-finai, za a iya tambaya a ce to wane fim ne na Hausa? Idan aka dubi yadda ake aiwatar da fina-finan Hausa a cikin wannan qarni da muke ciki, shin suna amsa sunan su a matsayin fina-finan Hausa? Ko kuwa za mu ce fim ne da ake aiwatar da shi da harshen Hausa amma ba na Hausa ba ne. A gaskiyar al'amari, a duk yayin da aka ce wannan fim yana amsa sunan al'ummar Hausa, to, abin da ake sa rai a gani shi ne, a fito da duk wasu sigogi da yanaye-yanaye na al'ummar Hausa a cikin fim xin. Kamar amfani harshe da sutura da muhalli da tsarin zaman iyali da zamatakewarta da duk wasu ababe da za su nusar da xan kallo, tare da gamsar da shi cewa wannan fim da nake kallo na al'ummar Hausawa ne, koda ba a faxa masa ba, tunaninsa da fahimta da basirar da Allah ya huwace wa xan Adam zai iya sa shi yanke hukunci da kansa cewar fim xin yana tallatar da

al’adu da kyawawan xabi’un Hausa. A wata tattaunawa da na yi da Ahmad Al-Kanawy da Falalu Xorayi sun ce kashi 75 cikin xari na fina-finan Hausa sun kauce hanyar raya da havaka al’adu da xabi’un Hausa. Ba lalle ba ne don an shirya fim da harshen Hausa sannan ya amsa sunan fim na Hausa. Abu da zai sa a ce fim ya amsa sunansa na Hausa, shi ne sai dai in duka kayan cikin fim da kuma aiwatar ‘yan fim sun dinga nuna al’ada da xabi’un Hausa tun daga farko har qarshe, kamar yadda aka gani a fina-finan farko irin su Sarki Jatau.

2.7.4 Dangantakar da ke Tsakanin Fim da Al’ada

Wasu masana a harkar nazarin fina-finai irin su Gamache (2008) da Onuzulike (2010) sun nuna cewa fim adabi ne da yake haskaka al’amura da suke wakana a cikin al’umma, amma al’ada ita sha kundum ce na yadda al’umma take aiwatar da rayuwarta a bisa yadda ta yi imani da ita, don haka fim wani sashe ne da yake haskaka al’adar al’umma. Gamache (2008) ta qara da cewa ana iya duba tarayyar fim da al’ada ta nazarin yadda fina-finan sukan taka rawa wajen nuna al’adar al’umma (t*eXtual analysis*), misali za a iya nazarin fim don a fito da jigon kyauta da mutuntaka da zalunci da addini da bukukuwa da sauransu.

2.7.5 Fim a Afirka ta Yamma

Masana ilimin fim a Afirka irin su Chukumah da Amalah (2009) da Ori (2009) da Adejunmobi (2009) da Aveh (2009) sun yi tarayya kan kyakkyawar alaqar da take tsakanin

fim da adabin mutanen Afirka, sannan sun nuna yadda al'adun sukan sarqe a cikin adabi. Shi ma Onuzulike (2010) da Diawara (1992) da Oyewo (2008) suna ganin fim a matsayin fage ne da yake yaxa adabi da al'adun al'ummar Afirka da kuma yadda fina-finan suke yin tasirin a kan al'adu da tarihin Afirka, musamman na qasashen Nijeriya da Gana da Kamaru da Kenya. Masana irin su Oni da Oladitan, da Ibitola da Dipio, da Isola (2008) sun kalli ci gaba da aka samu a fanin fim a zamanance a Afirka, musamman wajen shiryawa da samar da fina-finan a fagen yadda ake amfani da sababbin na'urar xaukar hoto da kuma sautuka masu inganci.

2.6.7 **Yadda Ake Shirya Fina-finan Hausa**

Wani manazarci Chamo (2003) yana mai cewa fina-finan Hausa suna da wasu qa'idoji da ake bi kafin a kai ga shirya su, da farko yin rajista da jiha da kuma qasa. Dangane da yadda ake shirya fim, kuwa an bayyana waxansu matakai da ake fara la'akari da su kafin samar da kowanne fim na Hausa matakan kuwa sun haxa da:

Labari

Samun kuxin yin aiki

Yadda za a samar da kayan aiki da ma'aikata

Samar da wuraren da za a yi aikin

Labari shi ne qashin bayan kowanne fim, idan labari ya tsaru to fim xin zai yi ma'ana kuma zai samu karvuwa a wajen al'umma, domin shi ne ake sarrafa shi ya zuwa abin kallo.

Sannan ana samun labari ta hanyoyi da dama waxanda suka haxa da qirqira da la'akari da wani abu da ya faru a cikin al'umma a yi rubutu a kai wato (*true life story*) da kuma amfani da tatsuniyar. Misali kamar fim xin *Ruwan Bagaja* da *Daskin da Ririxi* . Wata hanya da ake samun labari wajen aiwatar da fina-finan Hausa kuma ita ce kwaikwayo daga littattafan da aka rubuta na labarai ko wasan kwaikwayo ko kuma fina-finan wasu al'ummomim kamar Indiyawa da Turawa da Igbo ko *Nigerian film Yoruba da Igbo*; wanda wannan hanyar ce a yanzu ta fi mamaye labaran fina-finai Hausa. (Hira Da Falalu Dorayi da Chamo)

Samun kuxin yin aiki da kasafinsa: Ba wai kawai a fina-finai Hausa ba har ma da sauran harkoki na rayuwa kuxi yana taka muhimmiyar rawa wajen kai wa ga samun nasarar harka. Saboda haka, dole ne duk wani mai son shirya wani fim ya yi tanadin kuxin da zai ishe shi wajen gudanar da wannan fim domin idan ba shi da isassun kuxin ana iya samu matsaloli masu yawa waxanda za su iya kai wa ga rashin samun nasara.

Bayan an samu kuxin, to, dole ne mutum ya tsara yadda za a yi amfani da su ta hanyar biyan ma'aikata da sauran waxansu abubuwa da za su taso a lokacin gudanar da wannan fim. Kamar dai kayan aiki da ma'aikata. Kayan aiki a fina-finai Hausa, sun haxa da na'urar xaukar hoto da samar da haske da tufafi da abinci da kayan kwalliya da sauransu. Sauran ma'aikata sun ne darakta da mataimakinsa da kuma mai xaukar nauyin fim wato furodusa.

Daga nan sai 'yan wasa waxanda suka haxa da mata da maza, manya da qanana, waxanda suke fitowa a matsayin mutanen da aka rubuta labari a kansu, kuma haqqin mai bayar da

umarni ne ya zavi ‘yan wasa da suka dace da labari ba amfani da son zuciya ba. Sai kuma sauran ma’aikata da suke taimakawa wajen samun nasarar shiri waxanda suka haxa da masu na’urar xaukar hoto da masu kwalliya da masu abinci da sauransuwanda dole ne furodusa ya yi tanadinsu wajen samun nasarar fim xin da yake ta qoqarin yi.

Samar da wuraren da za a yi shiri: Yana da muhimmancin gaske ga duk wani furodusa bayan ya bayar da labarinsa ga darakta ya tsara wuraren da ya kamata a xauka shi ma. Ya yi qoqarin samun su, ko dai a qauye ne ko birni domin yanayin ya dace da labarin, wanda rashin bin irin wannan umarni na darakta ne yakan kawo savani a fina-finai Hausa domin za a ga ana fim a kan qauye maimakon zuwa qauye sai a ga birni. Sannan duk wani yanayi da ake son a samu na wani gida ko ofis ko mota dole ne furodusa ya samar kamar yadda ake buqata.

A taqaice, shirya fim ya shafi duk waxannan abubuwa da aka yi bayani a sama, bayan an sami labari ko ta wacce hanya ce sai a gyara shi a kai ga Darakta wato mai bayar da umarni wadda shi ne zai sarrafa sigogin labari zuwa abin kallo, walau na baka ne ko na zube (*script to screen*) idan aka gama haxa labari aka tsara shi, akan rarraba shi zuwa kashi, wato fitowa-fitawo. A kowace fitowa akan rubuta irin maganganun da za a faxa da kuma yanayin da ake buqatar xan wasa ya kasance Darakta yakan tarbiyyartar da ‘yan wasa a kan halaye da xabi’u da kuma ire-iren maganganun da ya kamata su kwaikwaya, sannan su aiwatar.

2.6.8 **Hanyoyin Nazarin Fina-finan Hausa**

Aminu (2012) ya kawo wasu hanyoyi da za a iya bi domin a yi nazarin fim, waxanda kuma rashinsu ko rashin waninsu ke rusa fim gaba xayansa ko kuma ya dusashe armashinsa. Ga bayaninsu daki-daki kamar haka:

2.6.8.1 **Jigo**

Masana da dama sun bayar da gudummuwarsu wajen bayyana ma'anar jigo a cikin ayyukan adabi, kaxan daga cikin su sun haxa da Chamo (2012) da Abbas (2008) da Yahaya da wasu (1992) suka bayyana jigo yana nufin abin da ake magana a kansa ne ko kuma wani saqo da wani aikin adabi ke son isarwa ko kuma wata manufa ta musamman da marubuci ya bayyana ta ko dai kai tsaye ko kuma a fakaice.

Su kuwa Xangambo (1993) da Yahaya (1997) da Gusau (2003) da Mukhtar (2004) bayyana jigo suka yi da shi ne saqo ko manufa ko bayani ko kuma ruhin da waqa ta qunsa wanda shi ne haqiqanin abin da mawaqin ke son isarwa ga jama'a.

2.6.8.2 **Tsari**

Zubi a matsayinsa na xaya daga cikin sifofin fim masana da dama tun daga 'yan mazan jiya har na yau, sun tofa albarkacin bakinsu game da ma'ana da matsayinsa a cikin fim. Aminu (2012) ya bayyana ana buqatar zubin fim ya kasance yana da farko da tsakiya da qarshe kuma ya kasance a xinke. Watau, ya zama akwai jituwa a tsakanin sassa daban- daban na wasan, waxanda suka haxa da aiki da wuri da kuma lokaci. Sannan kuma ya kasance suna xamfare da juna ta yadda a duk lokacin da aka cire xaya, to sauran na iya rugujewa.

Ya qara da bayyana zubin fim a matsayin wani abu ne da yake gine bisa sanannen tsarin farkon fim da tsakiyarsa da qarshensa. Masanin ya qara da cewa, shi farkon fim yakan qunshi gabatar da matsalar da ke cikin fim ne wanda yawanci yakan sa ‘yan kallo zaquwar ganin yadda za a warware wannan qiqi-qaqa. Tsakiya kuwa, watau qololuwa, kan qunshi wurin da abubuwa suke rikicewa ko rincave ne a cikin fim. Sai kuma qarshen fim inda ake samun warware matsalolin wasan wanda zai kai ga qarewa cikin nishaxi ko akasin haka, watau cikin ban tausayi.

A qarshe za a iya cewa, shi dai zubi a fim tamkar gishiri ne a cikin miya, ta yadda idan ya yi daidai, to wasa zai yi armashi. Idan kuma ya yi yawa ko ya yi kaxan, to fim ba yakan cin ma burinsa ba.

2.6.8.3 **‘Yan Fim (‘Yan Wasa)**

Aminu (2012) ya bayyana a duk lokacin da aka waiwayi batun ‘yan wasa, to dole ne a yi la’akari da abubuwa guda huxu: Na farko, su kasance sun cancanta, ta yadda duk abin da za su faxi ko kuma suka aikata a cikin fim ya zamana zai iya fito da saqon da ake son isarwa ne a fim. Na biyu, ana son a sanya su ko kuma su fito a wurin da ya dace, alal misali, wurin da ya kamata mace ta fito bai kamata a ga namiji a wurin ba, ko kuma wurin da ya kamata dattijo ya fito sai a ga yaro. Na uku, dole ne xan fim ya kasance ya mallaki irin xabi’ar duk wanda zai kwaikwaya a zahiri, ba wai ya yi wa xabi’ar haye ba. Misali, wanda zai kwaikwayi liman dole ya zamanto yana da kamala da kuma cikakken ilmin da aka san limamai da su. Na huxu, dole

ne a sami dogewar xabi'a, watau idan a miqe za a tafi, to ya zarce har qarshen fim. Idan kuma za a waske ko kuma za a sami sauyin xabi'un, to dole shi ma ya doge har qarshen fim.

Har wa yau Aminu (2012) hanyar da ake bi wajen zave ko shirya 'yan fim, ita ce ta hanyar lura da dukkan abin da yake furtawa ko yake aiwatarwa. Domin kuwa, waxannan su ne ma'aunan da 'yan kallo suke hukunci da su a kan kowane xan fim. Amma, duk da haka, alqalanci a kan halin xan fim, yana dogara ne a kan xabi'unsa da kuma kalamansa a cikin fim wanda xan kallo shi ne zai yi masa hukunci da ya dace.

2.6.8.4 **Harshen 'Yan Fim**

Aminu (2012) ya ce, abubuwan lura game da harshen 'yan fim sun haxa da; dole harshensu ya dace da irin rawar da suke takawa. Haka kuma a iya bambancewa tsakanin kalaman umurni da na buqata, da kuma sassauqar magana da ta barazana, sannan kuma da kalamin tambaya da na amsa, da dai sauransu. Masanin ya qara da cewa, kyakkyawan harshe ga xan fim shi ne tun farko ya zamanto a fayyace yake, ba a sarqe ba. Shi kuwa fayyataccen kalami, yakan qunshi sauqaqan kalmomi ne irin na yau da kullum ba masu zurfin ma'ana irin na adon harshe ba. Domin kuwa, rashin amfani da fayyataccen harshe yakan mayar da kalami tamkar zaurance ne ko kuma bauxaxxen harshe. Zance yakan zama zaurance ne idan an yi amfani da adon harshe kamar irin su kwalliya da tamka da jinsantarwa da kambamar zulaqe da dai

sauransu. Idan kuwa an yi amafani da baqin kalmomi ne, to sai ya zama bauxaxxen harshe, domin kuwa yana iya rikitarwa kuma ya hana fahimtar manufar fim.

2.6.6.9 Tufafin ‘Yan Fim

Wani masani Aminu (2012) cewa ya yi, tufafin ‘yan fim abu ne mai daxaxxen tarihi a fagen shirya fim kuma mai muhimmanci, domin ya rigayi abubuwa irin su tsare-tsare da shirye-shiryen dandamali. Har ya qara da cewa, za a iya aiwatar da fim ko ba a dandamali ba, amma ba zai yiwu a aiwatar da fim ba tare da tufafin fim ba, saboda a cewarsa, maqasudin wasan kwaikwayo shi ne koyi da halayen mutane ko xabi’unsu. Idan kuwa za a yi koyi da xabi’u ko halaye, to dole a sauya kama. Watau a sanya tufafin wasan da ya dace. Masanin ya qara da cewa, su dai tufafin wasa suna sauyawa ne gwargwadon matsayin da xan fim zai fito kuma suna iya kasancewa masu tsada ko masu sauqi, ya dai danganta da wanda za a yi koyi da shi.

Su kuwa, Wilson da Goldfarb (2002) bayan sun bayyana muhimmancin tufafi a rayuwar xan Adam da yadda tufafi ke taka muhimmiyar rawa a rayuwar xan Adam, sai kuma suka danganta shi da tufafin ‘yan wasa a fim, inda suka ce, kamar yadda tufafi suke da muhimmanci da kuma tasiri a rayuwar xan Adam ta yau da kullum, haka suke ga ‘yan wasa fim. Bambanci kawai shi ne, tufafi a wajen fim dole ne ya zamanto yana da quduri kamar haka:

- Taimakawa wajen tsari da salon fim

- Taimakawa a wajen tarihi da muhallin da aka tsara fim
- Taimakawa wajen fiddo da xabi'un 'yan fim a cikin fim. Watau ta hanyar bayyanar da matsayinsu a rayuwa da irin aikin da suke yi ko kuma tsantsar halayensu.
- Taimakawa wajen tantancewa tsakanin taurari a fim da kuma bi-yarima da kuma bambancewa tsakanin wannan rukunin jama'a da wancan.
- Taimakawa wajen biyan buqatun kowane xan fim, ta yadda kowane xan fim zai ji daxin watayawa a yayin aiwatarwa da tufafinsa da ke jikinsa ba tare da matsala ba. Misali xan fim da zai yi rawa ko wuji-wuji, to tufafinsa kada su zamanto xamammu ko matsattsu, ta yadda za su takura masa yayin gudanar da fim.
- Taimakawa wajen dagewa da irin tsarin fim gaba xayansa. Watau idan fim na talakawa ne, to a ga haka har qarshensa.

Waxannan masana sun ci gaba da cewa, su kansu tufafin 'yan fim suna da mataimaka waxanda suke kyautata aikin tufafin fim a cikin fim. Waxannan mataimaka sun haxa da waxanda ake riqewa ko sanyawa kamar su takobi da sandar girma da kuma bel da malfa da ma'aunin likita da dai sauransu. Sai kuma na shafe-shafe kamar su hoda da kuma fenti. Daga nan, dodon fuska wanda ake sanya shi domin vad da kama ko shigar burtu.

2.6.6.10 Kayayyakin Fim (*Properties)*

Waxannan su ne duk wasu kaya na dandamali da aka yi amfani da su a yayin shirin fim, waxanda za a iya tava su ko a gansu domin su samar da qaye da armashi na muhallin wuri. Misali, shimfixa darduma a fadar Sarki ko ajiye tum-tum ko maficin xawisu. Misali a yayin

da aka ce an nuna maqeri a maqera, za so a samar masa da murhu da zuga-zugi da fartanya ko garma da ya qera. Idan kuma ana qauye ne, sai mu ga tarkace irin su zana da qorai da wasu tarkace na mutanen qauye da za su nuna sahihancin muhallin fim. Da zarar xan kallo ya ga yanayin kayan komatsai da aka hasko a cikin fim, koda ba a ce qala ba, tunaninsa zai faxa masa inda ake. (Adamu, 2017 da Iyanama, 2011).

2.6.6.11 Kwalliya (*Make-up*)

Iyantama (2011) ya ce kwalliya wani muhimmin jigo ne a yayin shirin fim, a nan, ana nufin qawa ko sauya wasa kammani ta yadda zai ta hau matsayin da aka bas hi ya hau a fim dai-dai da surarsa. Kwalliya muhimmin lamari ne a harkar shiryawa da samar da sina-sinai a fim, domin abu ne wanda in an yi shi yadda ya kamata xan kallo zai ga armashin fim ya kuma qayatar da shi. Akan xauki wani jami'i da ya qware a wannan fage na kwalliya domin ya dinga cika aikinsa a kan 'yan wasa. Mai nazarin fim zai iya kallon kwalliyar da aka yi wa xan fim tare da alaqanta shi da rawar da ya taka kan shin ya dace ko bai dace ba? (Adamu,2017)

2.6.6.12 Sauti (*Sound*)

Ana nufin murya ko qara, Fim dai kamar yadda masana suka tantance shi, yana daga cikin rukunan wasannin kwaikwayon na'ura ne, ba rubutacce ba ne balle a ce na dandamali. Don haka, a lokacin samar da shi da kuma harhaxa shi za a so a ci darajar sautin ya fita tangaras tare amo da mai zaqi. A wasu lokotan akan samu akasin haka, don haka ya wajaba da mai nazari da qimanta darajar sauti na fim, wato ya yi armashi ko kuwa dai babu laifi ko kuma

dama-dama ne? A nan sai nuna kura-kurai da wuraren ake ganin ya kamata a inganta saboda gaba. (Iyantama, 2016)

2.7 Bambancin Da Ke Tsakanin Fim da Hausa da Kuma Fim Cikin Hausa

Masana sun ta kai kawo wajen tofa albarkacin bakunansu a kan bambancin da ke tsakanin fim da Hausa da kuma fim cikin Hausa. Wasu suna ganin shigar baqin al'adu a cikin fina-finan Hausa a qarni na ashirin ya taimaka wajen asassa wannan bambanci, za a iya cewa kwaikwayon al'adu da kaxe-kaxe da raye-raye na indiyawa zuwa cikin fina-finan Hausa yana daga cikin dalilan da ba za a iya kiran fina-finan Hausa na Hausa ba. (Gandu, 2006: 74-78). Masana irin su Adamu (2004) da Malumfashi (2009) sun nuna cewa babban abin da zai iya bambanta fim da Hausa da fim cikin Hausa shi ne aiwatarwa, a duk lokacin da aka ga fim xin Hausa ya fito da siffar kwaikwayon wani abu daga wata al'ummar qetare ta daban zuwa cikin fim xin Hausa, wato shigo da wani baqon a tsarin zamantakewar Hausawa cikin fim xin Hausa. Idan aka dubi yadda ake gina fina-finan Hausa, za a ga suna baddala fina-finan Indiyawa ne a mai da su na Hausa. Ka ga ke nan dole a ga bambancin qarara domin fim xin Hausa da yake da tushen Bahaushen labari, tabbas zubinsa da salonsa da harshensa da tsarin tufafinsa da muhallinsa da 'yan wasan (halayyarsu) zai fita daban da fim xin da asalin labarinsa an xauko shi ne daga labarin Indiya ko Amerika aka mayar da shi na Hausa, domin masu iya magana sun ce *tsintaccen mage ba ta mage*. Idan kuma an wanko fim xin ne, to, lallai za a samu tasirin ko kutsen ararriyar xabi'a ko al'adar waccan baquwar al'ummar cikin fim xin da aka kwaikwaya a cikin na Hausa. Don haka, shi fim irin wannan ba zai amsa sunansa da fim cikin Hausa ba, sai dai a ce da shi fim ne da aka yi da Hausa.

Suleiman (2017) ya nuna cewa akwai ra'ayoyi da bayanai na mutane waxanda suke gabatarwa domin nuna cewa akwai bambancin fim da Hausa da kuma fim cikin Hausa. Wasu daga ciki na ganin ba wani abu ya bambanta fina-finan Hausa da fina-finai cikin Hausa ba face yadda wasu daga cikin fina-finan suke xauke da tsari irin na gargajiya, ga wasu kuwa fina-finan da ake samu tun farkon vullar fim a qasar Hausa su suka fi cancanta da a kira fina-finai cikin Hausa. Sulaiman (2017) ya ce bambancin fina-fanai da Hausa da fim cikin Hausa shi ne: su fina-finan da Hausa; su ne ire-iren fina-finan da aka yi su da harshen Hausa, kuma Hausawa ko ba Hausawa suka aiwatar da wannan fim ba, ko kuma an yi amfani da Harshen Hausa ne kurum a matsayin harshen sadarwa, amma ba sa nuna sanannen tsarin rayuwar Bahaushe. Wannan tsarin rayuwa ya haxa tun daga al'adu da tsarin zamantakewa da tattalin arziqi da shugabanci da sauransu. Amma idan ana magana a kan fina-finai cikin Hausa ko na Hausa, ana nufin fina-finan da aka gina su a bisa tushensu na adabin Bahaushe da hikimarsa da fasaharsa a cikin al'umma tasa. Waxannan fina-finai su ne waxanda aka qirqira, sa'annan aka adana a rubuce. Sannan aka wanzar da su a aikace. Fasihai waxanda Allah ya ba su baiwar qirqirar abubuwan adabi sukan kasance sun tasirantu da wasu abubuwa na rayuwa waxanda suke tafiya ko kuma suke faruwa a wannan lokaci ko kuma ake hasashen faruwarsu nan gaba, waxannan ababai suke fitowa a ayyukan adabin fim. Idan an samu fim wanda ya kasance tsarin labarinsa qirqira aka yi, wanda ba shi da nasaba da aro ko fassara ko makamancin haka a qagaggen labari na zube ko tatsuniya aka mayar da shi Fim na Hausa, za a iya kiransa da fim mai adabi tsantsa na Hausa.

2.8 Siffofin Fim Da Hausa

Qamusun Hausa (2006) ya bayyana ma'anar siffa da hanyar bayyana kamannin abu. Sifoffi kuwa na nuni da jam'i na siffa. A nan za a dubi kamannin ne na fina-finai na Hausa da kuma fina-finai da Hausa. Kaso na farko su ne siffar fina-finai waxanda suke iqirarin na Hausa ne, alhalin daga kallon yanayin zubinsu da salonsu da jigonsu za a san ba su cancanci a kira su da fina-finan Hausar ba. Hujja a nan ita ce: ko ya zamanto fina-finan ne waxanda tushensu an wanko su ne, an kuma xauraye su ne daga wani tushen labari wanda bai da alaqa da Hausa a maida da shi fim xin Hausa, ko kuma fassara ce aka yi daga wani harshe zuwa na Hausar. Amma fa duk da haka, masu iya magana sun ce "kama da wane ba ta wane". Don haka fina-finan Hausa da aka gina su, aka tsara su, aka aiwatar da su, bisa waxannan hanyoyi, za a tarar sifoffinsu guda ne, wato ba su wakiltar asali da fasahar qirqira da adabi da al'adu da xabi'u irin na Hausawa. Alal misali "Wanki da Xauraya" a fina-finan Hausa na nufin "satar fasaha" daga wani fim zuwa wani. Ma'ana a nan ita ce yadda ake wanko kuma a xauraye wani fim na wata al'umma ta daban don a samar da wani fim na Hausa ba tare da an bar komai ba. Shi ma wannan, ana yinsa ta fuskoki biyu. Fuska ta farko, kan kasance gaba xaya fim ake wankewa kamar yadda aka gani a wasu fina-finan Indiya zuwa na Hausa, misali, *Indon qauye* da *Har da Mijina* wanki ne daga fina-finan Turai. Fanni na biyu, shi ne wanda za a wanko wani fanni na tsarin labari, daga wani fim zuwa na Hausa (Sulaiman: 2017:4). Kamar yadda aka gani a fim xin *Gwaska* an xauko daga fina-finan Indiya da Amerika aka gwama, sannan aka tayar da fim da Hausa. Duka fina-finai 'yan wanki da xauraya da fassara suffofinsu guda ne.

2.9 **Siffofin Fim Cikin Hausa**

A nan ana batun wasu nau'o'infina- finai ne masu wakiltar al'adu da xabi'u da fasahar Bahaushe. Sukan zo da sifoffi kamar haka: qirqiran labari na asali da baddalawa da kuma nashewa. Misali idan aka samu fim wanda ya kasance tsarin labarinsa qirqira ne, wanda ba shi da wata nasaba da aro, ko fassarawa. Don haka, dalilin qirqirar labarin da aka yi na fim a kai, shi ne almuhim a wannan yanayi. Misali fina-finai irin su "*Ruwan Bagaja" da "Daskin da Rixi*" an san tushensu daga adabin zube ne na Hausa don haka ba makawa za su iya xaukar siffar yanaye-yanaye na al'adu da xabi'un Hausawa. Haka zalika, baddalawa shi ma, wani nau'in adabi ne, zuwa cikin wani adabin ne, ta dabarar mayar da sassan adabin baka zuwa rubutacciyar adabi, wato qagaggen labari da rubutaccen wasan kwaikwayo. Idan an samu wannan baddalawa a fina-finan Hausawa, dole ta kasance ba ta sava da sanannen tsarin tunani da xabi'u da tsarin zamantakewar Bahaushe ba. Ana iya samun sauyi wajen tufafi da abinci da gine-gine da sadarwa, da kuma harshe, a sake masu kama, su zama na Hausawa, ta yadda mai kallo zai xauka dama can a qasar Hausa aka tayar da ainihin labarin. Misali fim xin *Ciki da Alakum*. Shi kuwa nashewa, ana nufin hankakanci (Sulaiman, 2017:9). Wato mayar da abu naka ta yadda mai shi ba ya iya sanin abin daga gare shi yake. Ana samun wasu fina-finan da wannan siffar. A iya cewa Hausawa 'yan fim, sun bi tsarin xaukar baquwar al'ada da sauya ta don ta dace da al'ummar da aka yi dominta. Misali kamar yadda mawaqan Bandari suka kwaikwayon waqoqin Indiya aka mayar da su waqoqin yabo na manzon Allah da Hausa.

Fina-finan Hausa sun ci moriyar yin amfani da waxanda baqin abubuwa, wajen aro daga fina-finan Ibo da Yarbawa da littattafansu na soyayya a sauya musu siffa da kamanni su shiga

cikin tsarin al'adu da koyarwar addinin Hausawa ta yadda za a xauka daman tun asali nasu ne tunda daman akwai mazahabar da take nuna cewar ana iya samun *cultural assimilation* kamar yadda Haram Lumbos ya nuna.

2.10 Fim a Matsayin Wasan Kwaikwayo

A ra'ayin Ahmed (1985) wasan kwaikwayo shi ne duk wata matsalar wasa da ta qunshi abu biyu:

i. Na farko dai ta zama wasa ne, ko kuma abu ne wanda yake ba gaskiya ba ne lokacin da ake abin.

ii. Na biyu shi ne, wasan ya zama maqasudinsa na sake-kama ne. Ya ba da misalin wasannin irin su 'yankamanci da na kalankuwa. A zamanance Ahmed, (1987) ya nuna akwai wasannin da Ahmad Kano da Radolf Prietz suka yi guda biyu tun 1902 da ajami aka yi su. Ya ce qila ma tun qarni na sha takwas aka fara rubuta wasan kwaikwayon Hausa. Malumfashi, (2015). Don haka, Ahmadu Kano da Rudolf Prietz sun rubuta wasannin kwaikwayo har guda shida, kuma dukkan waxannan wasannin babu wanda aka rubuta bayan 1930. Ga tsarin shekarun da aka rubuta su:

    1. *Turbar Qudus, 1989*
    2. *'Yan matan gaya, 1900*
    3. *Tarihin Rabeh, 1902*
    4. *Turbar Tarabulus, 1902*
    5. *Wasan Gizo da qoqi 1910*

6. Wasan Boka da Majinyaci, 1910

Malumfashi, (2015) ya ce binciken Ahmad ya tabbatar da ra'ayin "Ummariyya" mai cewa qila a samu wasannin kwaikwayo tun kafin 1902. An samu 1900 da kuma 1898. Kuma ya rusa tunanin da ke cewa ba za a yi amfani da ajami "tunda ya zo ne tare da addini" a rubuta wasan kwaikwayo ba. Sai dai a yayin da wasu ke ganin gasa ce ta fara haifar da rubutaccen zube, daga baya kuma aka samu rubutaccen wasan kwaikwayo mai suna *Six Hausa Plays* (1930) na R.M East da Abubakar Imam (Malumfashi, 2015:1). Daga baya an gano cewa duk da yake gasa ta bayar da irin tata gudunmuwa, to amma ba ita ce mabuxi ba. Tun kafin gasa aka fara rubuta wasan kwaikwayo in ji Ahmed (1987) da Malumfashi (2015).

Hanya ta farko wadda ta tabbatar da kasancewar wasan fina-finai a matsayin wasan kwaikwayo ita ce ana samun kwaikwayo na abubuwa waxanda yake sun faru ko kuma qirqirarsu kawai aka yi. A yayin kwaikwayon waxannan abubuwa duk 'yan wasa da aka yi amfani da su da kayayyaki da tsarin labarin da aka yi amfani da su a wannan lokaci ba da gaske ba ne. Saboda haka kamar yadda yake a wasannin dandamali ko rubutacce wanda ke nuna abubuwan da ke ciki ba da gaske ba ne, haka ma yake a wasannin fina-finai.

Kasancewar wasan kwaikwayo ba ya cika sai da 'yan wasa, wannan ya gwada cewa waxannan fina-finan suna da dangantaka ta fuskar 'yan wasa da wasannin dandamali. Kamar yadda ake zaven 'yan wasa da tantance su da kula da lafiyarsu da kuma irin gwanintar da suke da ita duk matakai ne waxanda wasan dandali da rubutattun suke da su, haka ma wasannin fina-finan Hausa.

Wani abu da zai burge mai karatu shi ne fahimtar cewa kamar yadda wasannin kwaikwayo suke da nau'o'in ban tausayi da raha ko tir-madalla ko kuma wasu nau'o'i na wasan jaruntaka, haka ma wasannin fina-finan na da wannan nau'o'in. Ana kuma iya samun na raha da ban tausayi da tir-madalla da na ban tsoro da wanda yake nuna jaruntaka ne ko mai xauke da soyayya ko motsa zuciya.

Akwai amfani da harshe wajen aiwatar da waxannan wasannin. Ana amfani da zavavvun kalmomi waxanda ke bayyana tunani da tsarin zamantakewar al'umma a cikin wasannin dandamali ko rubutattu, haka ma a wasan fina-finan . Harshe da ake amfani da shi zantuttuka ne masu bayyana matsayin 'yan wasa, da irin dangantakar da ke tsakanin xan wasa da wani xan wasa. Hakanan kuma, zantuttukan 'yan wasan kan nuna matsayin wasan na kasancewarsa na raha ne ko kuma na ban tausayi.

Batun isar da saqo ko manufa kuwa, batu ne wanda ke tabbatar da kasancewar wasannin fina-finai a matsayin wasannin kwaikwayo, domin kuwa ana shirya su ne domin faxakar ko ilmantar ko kuma a nishaxantar da al'umma. Wannan ma haka yake ga wasan kwaikwayo ko na dandamali, ko rubutacce, ko na rediyo ko kuma na talabijin (Sulaiman, 2015:11-12).

2.11 Bambancin Fim da Wasan Kwaikwayo

Sulaiman (2015) yana ganin akwai wasu abubuwa waxanda suka bambanta fim da wasan kwaikwayo. Wasan kwaikwayo daman a kan rubuta shi ne domin aiwatarwa a gaban masu kallo. Shi kuwa fim tsari ne wanda aka yi amfani da na'urar xaukar hoto mai samar da haske mai motsi. Kamara ce takan xaukar hoto, wannan shi ne abu na xaya daga cikin abubuwan da suka bambanta wasan kwaikwayon fina-finan da rubutacce ko wanda ake aiwatarwa a dandamali. Ana iya sarrafa wannan na'ura da xaukar hoto domin samar da wasannin fina-finai da kuma samun sauqin wurare ko sauyin yanayin da duk yadda ake buqata a cikin wasa, a sauran ire-iren wasannin kwaikwayo kuwa, sai dai a bayyana ko a rubuce ko kuma ta hanyar mai shela, ko kuma aiwatar a zahiran nan take a kan dandamali.

Wani bambancin da ke tsakanin wasan kwaikwayon Hausa da na fina-fina shi ne akwai dangatakar da ke qulluwa a tsakanin masu aiwatar da wasan dandamali da masu kallo. Wannan kuwa yana samuwa ne a sanadiyyar cuxanya da juna a lokacin da ake gudanar da wasannin dandamali. Wannan dangantaka da zumuncin da ke tsakanin 'yan kallo da masu gudanar da wasa, da kuma wadda ke tsakanin 'yan kallo da wasu 'yan kallon babu a wasannin fina-finai, saboda babu wata cuxanya ko hulxa wadda take haxa 'yan kallo da masu shirya wasa, haka nan a tsakanin masu kallo. Don haka, idan dai ana aiwatar da wasan kwaikwayon dandamali don jama'a ne, to shi kuwa wasannin fina-finai kan iya kasancewa don mutum guda ne.

Wasannin kwaikwayo na (dandamali ko rubutacce ko na rediyo ko na talabijin) galibi sun fi bayyana haqiqanin hoton rayuwar al'umma waxanda suka shafi gwagwarmaya a tsakanin

masu mulki da marasa galihu, ko gwagwarmaya tsakanin baquwar al'ada da 'yar gida ko hanyoyin bunqasa zamantakewar al'umma wanda kan kai ga qwato haqqin da 'yancin al'umma. fina-finai kuwa ba su cika nuna waxannan abubuwa ba.

Batun sauya wa wurare tsari ko kayayyakin da ake amfani da su na sutura ko wuri a yayin da ake gudanar da wasannin dandamali na xaya daga cikin hanyoyin da suka bambanta shi da na fina-finai. Wasannin fina-finai sun fi amfani da kayayyaki da shirye-shirye mai xaukar tsawon lokaci kafin harhaxa shi.

Akwai kuma wani bambanci na irin kayayyakin da ake amfani da su a wasan kwaikwayon dandamali irin su fitilu da suke haskaka wuri da kuma sauran kayayyaki da wurare. fina-finai sun fi amfani da waxannan fitullun da sauran na'urori kamar su motoci da lambuna da sauran qere-qere a yayin xaukar shirye-shirye da suke yi kafin a samar da wasa guda na fim ba kamar yadda yake a wasan kwaikwayon dandamali ba.

Akwai kuma bambancin yawa da qwarewar amfani da 'yan wasa, a wasan kwaikwayon dandamali, ba a buqatar 'yan wasa masu yawa kamar yadda ake buqatarsu a wasannin fina-finai. Duk da yake a kowane nau'in wasannin qwarewa ta zama dole, a mafi yawan lokuta na dandamali sun fi kusantar rayuwa ta zahiri cikin qwarewa da bajinta.

Fim yakan xauki lokaci mai tsaro kafin a shirya shi, har ya kai ga shiga kasuwa, amma na wasan kwaikwayo shi take yanke ake shirya shi a kuma gabatar da shi ga ‘yan kallo. Fim yakan yi amfani da nau’o’i kala-kala wajen sauya yanayin hoto mai motsi zuwa wata siffa ta daban ko sarrafa xan wasa kamanni wato “*Special Effect*” wanda babu hakan a fagen wasan kwaikwayo. Bugu da qari, wasan kwaikwayo za a iya gabatar da shi cikin xan qanqanin lokaci a qalla wasanni biyu zuwa uku, amma fim kuwa abin da kamar wuya, dole sai a dinga yawo daga wuri zuwa wuri da xauka a na’ura, sannan a kai wurin edita yana harhaxawa zuwa fim guda bayan an kammala tace zaqin sauti da kalar hoto mai motsi da kwalliya da sauransu.

2.12 Fim A Matsayin Adabi

Sulaiman (2015:2-3) rubuce-rubuce da nazarce-nazarcen da aka yi a kan wasannin fina-finan Hausa sun fi mayar da hankali a kan wasu fannoni na nazari waxanda suka haxa na asali ko samuwar waxannan wasanin fina-finan . Wasu kuwa sun duba irin tasirin da adabin baka ya yi a waxannan finafinan, ko kuma irin adon harshe ko ingausar da ke cikinsu. Kaxan ne suka nazarci wasannin ta hanyar xora su bisa sannannun hanyoyin nazarin wasan kwaikwayo. Wasu kuwa sun kwatanta wasu ‘yan wasa dangane aiwatarwa. Duka waxannan wasannin sun kasance wasan kwaikwayo ne waxanda a tsakaninsu sun bambanta a fagen amfani da na’urori da zaven ‘yan wasa da ma irin dangantakar da ke tsakanin ‘yan kallo. An gwada cewa

wasannin fina-finai sun samu tushensu ne daga wasan kwaikwayon dandamali. Larkin (1997) na ganin wasan kwaikwayon na Hausa da na talabijin da silma da na majigi dukkansu masu amfani da kafar sadarwa ce wajen aiwatar da kwaikwayon halaye da xabi'un da ke cikinsu ko dai don ilmantarwa da faxakarwa, ko kuma don nishaxantarwa. Malumfashi (2002) da Furniss (2003) duk suna ganin wasan kwaikwayon Hausa ya vuvvugo daga wasannin gargajiya a sakamakon dusashewar litattafan soayayya. Maganar ko dangantakarsa da sauran ire-iren wasannin kwaikwayo abu ne wanda bai sami kulawar da ta kamata ba, ko da yake akwai dangantaka da bambancin a tsakanin wasan kwaikwayon talbijin da na fina-finan Hausa. (Sulaiman, 2015:2-3). Idan an yi amfani da abin da Sulaiman (2015) ya ce wasan kwaikwayo na fina-finai yana da matsayi da daraja wanda ya samu a sanadiyyar samuwar wasannin dandamali, abu ne muhimmi a sani fina-finan da wasannin kwaikwayo na Talabijin da Majigi da Silima 'yan tsatso guda ne sai dai za mu ga cewa sunan ya bambanta ta yadda ake naxa da kuma samar da kowannensu kada manta, uban nasu dai shi ne wasan kwaikwayo na dandamali. Dukkan waxannan nau'o'in wasannin da aka zayyano sun dilmiya cikin fannonin nazarin Adabi a makarantu da yanaye-yanayen zamantakewar al'umma. Don haka, zai yi wuya a raba, a ce ai fina-finai ba nau'in adabi ba ne, sai dai a iya cewa, jaririn fage ne idan aka kwatantashi da samuwa tare da bunqasar adabin wasannin kwaikwayo na Talabijin da Silima da kuma Majigi.

Adabin wasan kwaikwayo na fim, wani reshe ne mai bayyana fasaha da hoton rayuwar Hausawa. Al'ummar Hausawa sun daxe da al'adunsu na gargajiya, a cikin ire-iren waxannan al'adu ne aka sami wasanni na yara da manya (maza/mata) waxanda masana suka ayyana su a matsayin wasannin kwaikwayon gargajiya na Hausawa. A sanadiyyar hulxa da Turawa aka

sami wasannin majigi da rubutaccen wasan kwaikwayo suka vulla, bayan waxannan, an sami bayyanar wasannin kwaikwayo na rediyo da na talbijin wanda daga baya wasannin fina-finai suka vulla. Duk da yake wasu na ganin wasannin fina-finai a matsayin wani abu daban, wannan aiki ya yi qoqarin bayana cewa wasannin fina-finai wasannin kwaikwayo ne ta hanyar yin la'akari da siffofin wasan kwaikwayo wanda shehunnan masana suka bayyana yana xauke da shi. Fina-finan Hausa su ma suna xauke da kowace irin siffar wasan kwaikwayo, kuma ana ganin hakan a bayyane a cikin wasannin fina-finan Hausar. Don haka, fim yana matsayin xaya daga cikin nau'o'in adabin wasan kwaikwayo na na'ura.

2.13 Adabi A Matsayin Taska Ga Al'umma

Adabi shi ne babban mashigi da ya gina wannan aikin kamar yadda ake gani, fim yana daga cikin nau'o'in adabin wanda akan yi qoqarin fito da tsarin xabi'un al'umma daga cikinsa. Don haka a fagen nazari, adabi tubali ne na rayuwar al'umma wacce take nuni da yanayin rayuwa da zamantakewar al'umma, wanda ya haxa fasahar qirqira da sadarwar harshe da al'adunta. Masana da dama sun yi nazarce-nazarce a kan matanoni daban-daban a cikin adabin zube da waqa da kuma na wasannin kwaikwayon gargajiya da na zamani. *Qamusun Hausa*, (2006:431) ya ce taska tana nufin xakin ajiyar kayayyaki masu daraja, musamman na maigida. Wata ma'anar kuma ita ce wani irin qaton abu mai kama da akwati da aka yi da qarfe mai qarfin gaske, musamman don ajiye kuxi ko wasu muhimman abubuwa.

Idan aka alaqanta wannan ma'ana ta taska da matsayin adabi ga al'umma, za mu iya cewa adabi gishiri ne da yake sanya xanxano a al'amarin rayuwar al'umma, wanda in ba shi, rayuwar za ta kasance lami, don haka sauran rassa na al'amarin zaman rayuwar al'umma sun jingina da adabi ne. A wata fuskar kuma, adabin na da muhimmanci wajen ilmantarwa da yin kyakkyawar tarbiyya, musamman ga matasa. Kusan kowane fanni na adabin, kamar su tatsuniyoyi da karin magana da waqoqi, kan himmantar da yara da xaukan wasu halaye na gari. Wato, ya cusa masu xabi'un qarfin-hali, da jarumtaka, da dauriya da tausayi da sanin ya kamata da sauransu. Haka kuma, adabin, kan raunana munanan halaye kamar su kwaxayi, da qarya, da shisshigi da munafunci. Alal misali, idan aka dubi tatsuniyar "Ruwan Bagaja", za a ga irin waxannan hikimomi a zayyane. A cikin Karin Magana kuma, ga misalai nan irin su:

> Na-gari na kowa, mugu sai mai shi.
> Bayan wuya, sai daxi.
> Mahaqurci, mawadaci.
> Kwaxayi, mabuxin wahala (Umar,1987:6)

Ga kuma hikimar adabin, ta koya wa yaro harshensa, ya kuma bunqasa tunaninsa, ya kyautata shi. Dubi misalan *kacici-kacici* da maganganun-kakkarya-harshe da wasa qwaqwalwa da wasannin yara, ka ga muhimmancin adabin, dangane da kaifafa qwaqwalwa yadda za ta bunqasa, ta iya rie sunayen abubuwa da siffofinsu.

Za a iya cewa adabi yana xauke da taskoki guda uku ginshiqai, wato taskar harshe da taskar al'ada da kuma taskar xabi'u an yi sharhinsu kamar haka:

2.13.1 Taskar Harshe

Harshe kamar yadda Qamusun Hausa (2006) ya ba da ma'ana tasa da cewa hanyar magana ce tsakanin al'umma iri xaya. Masana da dama sun yi nazarin gurbin harshe a taskar adabi. Kamar yadda muka gani a ayyukan su Yakasai, (2013) ya kalli tasirin fifikon rubutu da hanyoyin sadarwa na zamani bisa na gargajiya, cikin adana harshe da al'adun Hausawa. Magaji (2013) kuwa ya kalli gudunmuwar harshe ne a matsayin tubalin ginin al'ada, amma an taqaita binciken a kan gidajen rediyo. Shi kuwa Ibrahim (2013) ya nuna matsayin harshe ne wajen bunqasar tallar hajojin gargajiya a wannan zamani, ya ce harshen talla zantuka ne na walwalar harshe da masu sayar da wata haja na gargajiya ko na zamani ke yin amfani da shi domin yin tallar hajarsu irin su magungunan gargajiya da abinci da sauransu. Shi ma Ibrahim (2013) ya fito da yadda ake amfani da harshen turancin ingausa a cikin fina-finan zamaninmu, musamman ta yadda turanci yaka barazana a cikin Hausar qarni na ashirin da xaya.

Dukkan waxannan masana sun nuna matsayi da gudunmuwar harshe da tasirinsa a cikin adabin Hausa musamman a kan al'amuran da suka shafi walwalar harshe da cinikayya da samarwa kai abin masarufi da sadarwa da talla a cikin fina-finan Hausa.

Wani manazarcin wasan kwakwaiyo Shehu (2005) ya yi duba a kan tasirin harshe a wasan kwaikwayon Jami'ar Jatau na Albarkawa, a inda yake cewa: amfani da harshe shi ne qashin bayan wasan kwaikwayo na rediyo. An nuna cewa 'yan wasa kan sarrafa muryoyinsu ne don koyi da haqiqanin yadda waxanda ake kwaikwayo na asali suke yin magana. Ya qara da cewa

masu gudanar da wasan kwaikwayon Jami'ar Jatau Na Albarkawa, zaunannun 'yan wasa ne, waxanda kuma suka shahara. Baya ga yin raha, 'yan wasan kan isar da manufofinsu cikin hikima da nuna gwaninta. Sukan yi haka ne ta hanyar kwaikwayon yadda Hausawa, ko qabilu da ke maqwabtaka da su, suke magana da harshen Hausa. Wani abin lura kuma shi ne, saboda baiwar da Allah ya yi musu, akan samu xan wasa da kan iya kwaikwayon muryoyi da dama.

Shi ma Chamo (2012) ya yi nazarin yadda ake amfani da harshe da sauye-sauyen da karinsa a tsakanin rukunan jama'a a cikin fina-finan Hausa. Ya xauko wasu fina-finan Hausa irin su *Dijangala* da *Ki Yarda Da Ni* da *Guzurin Qauna* da *Gimbiya Fatima* aka yi tsokaci a kan yadda mata da miji da xa da uba da uba da 'yarsa da uwa da xa da surukai sukan sadar da magana a tsakaninsu musamman ta yadda ake amfani da harshe domin isar da saqo. Wasu lokutan akan yi ingausa (*code mixing*) ko kuma hargitsa balle (*code switching*).

Yakasai, (2015) shi ma ya yi bincike a kan harshen yaudara a kafar sadarwa ta *facebook*. Marubucin ya nuna yadda mutane 'yan yaudara sukan yi amfani da harshen wajen jera kalamai masu zaqi da xaukar hankalin wanda aka turawa saqo ta yadda zai ja ra'ayinsa domin a yaudare shi ko a cuce shi a bisa wata buqata tasu da suke son su samu daga hannun wanda ake son a yaudara. Yawanci an fi gina yaudarar ne a bisa neman kuxi da soyayya da kuma dabarun karvar dukiya a hannun mutane, duk wanda ya ba da kai bori ya yau, sai ta vare da shi.

Shi ma Mijinyawa (2015) ya bi sahun Yakasai (2015) inda ya yi bincike a kan yadda mawaqi Aminu Ala yakan yi amfani da tsofoffin kalmomin Hausa a cikin waqoqinsa. Ya ce waqoqin Aminu Alan sun zama taska wajen adana tare da fito da tsofoffin kalmomin Hausa ga waxanda ba su tava jin su ba ko kuma ba su san ma'anarsu ba. Ya buga misalai daga cikin waqoqi irin su *Jami'a* da *Lu'u lu'u* da *Angara*. Misali kalmomi irin su Qwado (wasa ne da akan yi da 'yayan qwara) da Gardo-gardo (shi ma wasa ne da yara sukan yi , inda sukan tara qasa su binne hannunsu a ciki) da Qulafuci (mutuqar son wani abu a zuci ko nacin so) da Angara (jikar da matafiya sukan rayataya a gadon baya xauke da guzirinsu) da Salka (jikar ruwa ce ta matafiya) da Bulayi (shirme ko aikin banza) da Talalavo (mutuwar jiki ko mutum mara qarfia jikinsa) da sauransu da dama. Marubucin ya fito da ire-iren waxannan kalmomi tare da ma'anarsu a fagen lugga da adabi tare da yin sharhin yadda mawaqin ya yi amfani da kaifin basirarsa wajen shigo da kalmomin cikin baitukan waqoqin ta yadda suka dace kuma suka dire.

2.13.2 Taskar Al'ada

Kamar yadda wani marubuci (Umar, 1987) ya nuna akwai kyakkyawar dangantaka tsakanin adabi da al'ada, wato sukan yi wa juna shigar giza-gizai. Marubucin ya yi bayani yanayin wasu al'adun Hausawa da suke taskace a cikin adabi. Koda yake ya fi bayar da qarfin bayanin nasa ga adabin baka da muhimmancinsa. Misali ya raba aikin nasa kashi huxu; yanayin wasu

al’adun Hausawa a addini da tasirinsu da mulki da zaman iyali da sana’o’i da jarumtaka. Kashi na biyu an kalli adabin zube na bakan gargajiya kamar tatsuniya da karin magana da take da kirari. Kashi na uku, kuwa an dubi waqa ne, a nan ma an fi ba da fifiko ne a kan waqoqin fada da waqoqin jama’a da kuma waqoqin maza. A qarshe, sai aka tattauna a kan wasan kwaikwayo na gargajiya irin su tashe da wasan ‘yan kamanci. Duka waxannan ire-iren adabi da Umar (1987) ya kawo sun fito da al’adar Hausawa qarara dangane da fasaha da tunaninsa da zantukan hikima da kuma tsarin rayuwar ta yau da kullum daga zube da waqa da kuma wasan kwaikwayo. Alaqar da wannan aiki na Umar da wannan shi ne, sun yi tarayya a kan wasan kwaikwayo. Koda yake, shi ya kalli wasan kwaikwayo na gargajiya ne a fagen taskar adabi, amma wannan aikin ya kalli wasan kwaikwayo na fina-finan Hausa ne kuma na zamani a taskar adabi.

Shi kuma Lawal (2011) ya kalli wasu al’adun Hausawa a mahangar waqoqin baka ne. Shi ma dai ya bi sahun Umar (1987) wajen fito da gurbin al’ada daga cikin adabin Hausa. Wasu daga cikin al’adun Hausawa da ya tsattsafe a cikin aikin su ne; shugabancin jama’a a kan yadda za su tafiyar da mulki. Ya kawo wasu waqoqin baka da suke yin nuni a bisa tsarin tafiyar da harkokin mulkin gargajiya irin na Hausawa. Misali waqar Musa Xan Qwairo yana yi wa sarakuna tuni a kan yadda ya kamata su tsara tafiyar da harkokin mulkinsu, sannan an yi sharhi a kan wasu matakan tsarin zamantakewar Hausawa, daga cikin matakan akwai na aure. Shi ma a nan an xauko waqar Mamman Shata, ta aure, yana mai qarfafa wa matan Hausawa da su yi aure, an sake xauko batu a kan tsarin zama a tsakanin mata da miji wato zaman aure, ta yadda miji zai bai wa matarsa haqqinta, da kuma yadda ita ma za ta ba wa mijinta haqqinsa. An kawo misalan wasu xiyoyi waqar Alhaji Xan maraya Jos. A qarshe aikin Lawal (2011) ya

tattauna a kan sana'o'in gargajiyar Hausawa, waxanda suke gudanarwa don inganta tattalin arzikinsu. Misali waqoqin sarkin Taushin Katsina ya ambaci wasu sana'o'in kamar qira da gini da jima da rini da saqa da sauransu.

Litattafai da kundayen da aka rubuta magungunanmu na gargajiya mafi yawanci cikin rubutun Ajami aka tarar da su. Kafin zuwan Turawa a qasar Hausa Ajami shi ne salon da ake amfani da shi wajen rubuta harshen qasa a sha'anin da ya shafi mulki da kuma tsarin shari'a. Da Ajami ake rubuta rasixin haraji da jangali da sauran bayanan al'amurran mulki a majalisun sarakuna. Ta vangaren alqalai da Ajami ake rubuta kundayen yadda ake gudanar da shari'a da kuma sammaci.

Sha'anin bauta da sayen bayi da ya gudana a wannan qasa duk cikin rubutun Ajami aka tarar da bayaninsu. Yadda mutum ke zama bawa da yadda ake fansa duk an tarar da su cikin Ajami. Tattalin arziqi wato sha'anin saye da sayarwa idan sun gudana da Ajami ake tattara bayanansu. Duk wata rubutacciyar waqar Hausa koda ba a rubuta ta kan jigon addini ba, to a ka tarar akwai nason addini a ciki, domin ko ba kome za a ga salonrubutunAjami ne aka aro. In haka ne ashe bai kamata mu yi godiyar maye ba, ko kuma mu yi na kaza, mai ci ta goge bakinta, mu manta da irin gagarumar gudummuwar da Ajami ya bayar ba wajen adana al'adun Hausawa da muke taqama da su a yau.

Haka zalika Sayaya (2013) ya yi nazarin gudummuwar farauta ga raya al'ada da adabin Hausawa. Marubucin ya nuna cewar farauta hanya ce da xan Adam kan bi waxansu halittu masu rai musamman namun daji da sauran qananan dabbobi domin samun abinci, su ma Hausawa sun sami kawunansu cikin fafitikar neman abinci domin ganin sun rayu a bisa doron qasa. A qoqarin yin haka, sunkan shigo da fasahar waqe da kirari da take da habaici a cikin al'adar farauta wanda hakan wata taska ce ta rayar da adabin Bahaushe a ta dalilin al'adar farauta. Misali, ban da waqa da kirari da take. Farauta ta taimaka gaya wajen samar da lafuzzan habaici, domin kuwa mafi yawancin sunayen karnukan farauta habaici ne ake yi wa wani, misali Bi-su-kare da Bar-su ga Allah da kuma A-sha-za ga. Sauran sanannun kare-karen magana sun haxa da:

> Can ga su gada, da zomo ya ji kixan farauta
> Ba ni na kashe zomon ba, rataya aka ba ni.
> Tsufan Sarkin baka, yana tsufa yana qara shiga daji

Al'ada da xabi'a Xanjuma ne da Xanjummai kamar yadda aka gani a wasu nazari na masana irin su*Qamusun Hausa* (2006) ya ba da ma'anar xabi'a da halin mutum ko kuma al'adarsa. Muhammad (2013) ya nuna yadda nasaba take taka muhimmiyar rawa dangane da fito da xabi'a a cikin al'ummar Hausawa a tubalan yabo da zuga da habaici da zambo.

A fagen al'adar nasaba za a iya ganin nasabar zamantakewar al'ummar Hausawa, a fagen malaman Al'qur'ani suna koya wa xalibai ilmin addinin Musulunci da nahawu ko lugga da hanyoyin rayuwa da adabin al'umma da makamantansu. Malaman boko suna koyar da fannonin ilimi da dama da suka haxa da fannin fasaha da kimiyyar harshen Hausa ta amfani da

haruffan Romawa, sai aka shiga koyo da koyar da darussan Hausa daban-daban a vangaren harshe da adabi da al'adu. A sakamakon irin waxannan ilmi da ya wanzu a cikin al'ummar Hausawa aka samu fasahar iya magana irin su:

> Abin nema ya samu, matar Malam ta haifi allo
> Abin gudu, Malam da xabi'un Bokaye
> Ta Malam ba ta wuce amin
> Wannan na daban ne, Malam da kuxin kixa.

A nan an yi amfani da fasahar qirqira wajen bayyana buqatar faxin abin da yake cikin zuciyar mutum ta yadda burin zuciya zai cika a falsafance, domin halin mutum xabi'arsa, don haka a dalilin zamantaekawar da ke tsakanin Malami da xalibai da al'umma, shi ya sa aka yi laqabawa Malam waxancan maganganu wa ya Allah su yi dai-dai da Malam ko kuma akasin haka.

Hakanan shi ma Yahya (2013) ya yi nazarin lalacewar tarbiyya a yau, tsokaci daga waqar yaqi da rashin tarbiyya da rashawa ta Alqali Haliru Wurno. A cikin maqalar an nuna cewar Bahaushe mutum ne mai halin xa'a da girmama na gaba da kuma kwatanta adalci da aka san Bahaushe da ita ta canza. An wayi gari shugabanci ya zama son rai da son zuciya, kowa kansa ya sani, kansa yake so shuwagabanni sun shantaqe sai masha'a da qabilanci. A irin wannan yanayi ne marubuta waqoqin Hausa suka sami aikin yi, suke rubuta waqoqi domin faxakarwa da kuma tunasarwa. Takardar ta kawo wasu xangwaye da suke nuni da lalacewar tarbiyyar shugabanni da ta Malamai tare da kawo mafita domin gyara. A taqaice maqalar ta fito da munanan halaye da ake ganin sun taimaka wajen ruguza tarbiyya tare da yin hannunka mai sanda waxanda bulalar ta daka su shiga taitayinsu.

Shi ma Xangulbi, (2013) ya bi sahun Idris (2013) wajen nazarin tasirin baqin al'adu ga tavarvarewar Hausawa a yau. Marubucin ya tabbatar da cewa kowace al'umma ta duniya tana alfahari da al'adunta da suka shafi kyawawan xabi'unsu da halayensu, wannan al'ada da al'ummomi suke tunqaho da ita, ta zama hanya ta gina kyawawan halaye da xabi'u masu kyau da qauracewa halaye da xabi'u marasa kyau. A yau sanadiyyar cuxanyar Hausawa da suka yi da wasu baqin al'adu ya sa duk abubuwan da al'adar Hausa take alfahari da su, suna neman su fi qarfin Hausawa (Xangulbi, 2013:315). Kaxan daga cikin tushen wannan bincike shi ne nazarin yadda baqin al'adu suka yi tasirin a kan al'adun Hausawa a fagen zamantakewa. An san Hausawa suna kyakkyawan tsarin xabi'u da al'adunsu na yau da kullum, kuma suna da kyawawan mu'amala a tsakaninsu kamar kara da jin qai/taimako da reno/riqon 'ya'yan dangi da ilimi da sutura da kula da haqqin maqwabtaka, haka kuma akwai auratayya da haihuwa da mutuwa da kula da addini da sadar da zumunci. Marubuucin ya xauko wasu xiyoyin waqar Alhaji Musa Xanqwairo maradun domin ba da hujja da kariya ga muhimmancin tsare kyawawan al'adu da xabi'un Hausawa na gargajiya. Ganin yadda zamani ya zo ba adamu a kare martabar al'adun ba, kowa ya bar gida, gida ya bar shi.

2.17 Zamantakewa A Al'adar Bahaushe

Yanayin zamantakewa yana xaya daga cikin tsarin rayuwar al'umma ta duniya, hakan ya bambanta daga al'umma zuwa al'umma. A tsarin zamantakewar al'ummar Hausawa, maigida shi ne mai jan ragamar gidansa ta hanyar kula da iyalansa da sauran abubuwa da suka wajaba a kansa. Sannan uwargida ita ce mai kula da harkokin gida kuma ita ce shugaba, a cikin gida. Abubuwa irin su, abinci da kula da yara da sauran duk ayyukan da suka dangace ta, kuma akwai sahihin tsari yadda kowa ya san matsayinsa, kuma yara ma suna da nasu tsarin na yadda kowane yana bai wa na gaba da shi girma. Amma sai ga shi a fina-finan Hausa da ake aiwatarwa, za ka ga yanayin zamantakewar kara zube suke ta yadda kowa yake yin abin da ya ga dama, ba tare da la'akari da tsararriyar al'ada ta Hausawa ba, ta yaya za'a iya kafa hujjar faxin haka, sai a yi bincike a ilimance. Kuma duka fina-finan Hausar ne ba su damu da nuna kyawawan yanayin zamantakewar Hausawa ba?

Masana irin su Alhassan (1988) da wasu sun nuna tarbiyya ita ce dirka na zamantakewar Hausawa. Wato mihimman halaye na nagrata, ko kuma, kyawawan xabi'u da halaye, waxanda Hausawa suka fi qarfafawa, ana gane su ta fuskar mu'amala, da yin ladabi da biyayya, da kunya da kara da zumunci da riqon addini da kuma sana'a da tsare mutunci da haquri da juriya da jarunta. To a nan, sana'ar fim ta samu shiga wannan gurbi, don haka wane irin rawa ya taka wajen nuna Bahaushiyar zamantakewa ta yadda za a ce fina-finan na Hausa ne ko kuma suna dai amsa sunan su fim da Hausa ne kawai. Qarin bayani a kan zamantakewar Hausawa: Mu'amala: Hausawa sukan ce, "Kowa am mutum, mutum ash shi!" Watau mutum, in dai mai lafiya ne, to ya kamata a san shi tare da mutane, ba a ga yana janye jiki yana zama shi kaxai ba. Ana kuma so a san mutum da sakin fuska. "fuska mai sai da riga.". To amma

wannan sakin fuska, ba so ake ya wuce gona da iri ba, watau kada arahar dariya da fara'a da walwala su sa a raina mutum, ko ma a xauke shi tavvave. (Alhasan da wasu, 1982:24-28)

Ladabi da biyayya:manyan qusoshi ne a cikin tarbiyyar Hausa. Watau muhimman halaye ne da Bahaushe yake so ya ga ana yi. Girmama na gaba da kyautata wa na baya su ne halayen da ake kira lababi da biyayya. A nan in an ce na gaba da kai, ana nufin wanda ya fi ka a shekaru ko ta hanyar shugabanci. Ma'anar girmamawa kuwa, ba wai sai ka rusunna ka gai da mutum ba. A'a sassauta magana, da saurara wa mutum idan yana yin tasa, wannan ma girmamawa ce. Haka kuma idan babba ya tashi aiki a karve shi, ita ma girmamawa ce. Bayan haka a tarbiyyar Hausa, tsoma baki cikin maganar na gaba da kai aibu ne.

Abin da ake nufi da kyautata wa na baya kuwa, shi ne a taimaka shi ya tashi ya sami abin kansa, a yi haquri da shi kuma a dangana a bar masa abu in an ga shi ma yana nema. Har ma Hausawa suna cewa, "Babba juji ne." kuma akan ce mutum ya ci girma idan ya dangana ya bar neman wani abu don na baya ya samu.

Kunya da kara:In an ce ana jin nauyin mutum ko ana jin kunyarsa, to ana girmama shi ke nan, kuma ba za a yi wasa da shi ba, sa'annan duk wani abin wargi ba za yi da shi a wurin ba. Akwai kuma alkunya. Ita kuma wata al'ada ce wadda ta hana a ambaci sunan mutum kai tsaye. Wannan al'ada ana yin ta ne tsakanin iyaye da 'ya'yansu, ko tsakanin maza da matansu na aure, ko ga surukai, ko ga dangi.

A bisa wannan al’ada, rashin ladabi ne a ji mutum ya yi farat ya ambaci sunan mahaifinsa, ko mahaifiyarsa, ko surukinsa, ko xan cikinsa, ko matarsa, ko xan uwansa na gaba da shi. Haka kuma idan kana hulxar arziki da mutum, kuskure ne ka kama sunan xaya daga waxannan makusanta nasa da aka zana.

A irin wannan hali al’ada ta nemi a voye sunan ne, watau a sakaya shi, ko kuma a yi masa kara. Saboda haka maimakon ka ambaci sunan mahaifi, ko mahifiya, sai dai ka ce, “Baba” ko “Iya” kuma xanka xan abokina ne in kana magana a kansa ba za ka ce wa abokinka “xa na wane ba, sai dai ka ce masa “xanka”.

Matarka ko abokin huxarka kuwa, kullum sunanta “iyalina” ko iyalinka” ko kuma “mai xakina” ko “maixakina”. Alkunya ba ta yarda ka kama sunanta ba. Kuma ba daidai ba ne ka ce, “matata”. Sai fa idan dama matar ba ta gaske ba ce.! Hakanan mace ba ta kiran mijinta da sunansa. Galibi takan ce masa “malam” ko “uban wane” ko “Baban wane” ko wani abu mai kama da waxannan. Da ma a Hausa idan aka ce wa mutum “ubansa” ko “uwarsa” ko gidansu”, wannan zagi ne. sai dai a ce “maigidansu” ko wani abu irin wannan.

Zumunta**:** Qokarin kusantar “yan’uwa da abokan arziki, da ziyartarsu a kai a kai, da riqe dangi ba tare da zavunta ko son kai ba, wannan ita ce zumunta. Tarbiyyar Hausa tana jaddada

ziyarce-ziyarce tsakanin ‘yan’uwa da abokan arziki. Har ma Hausawa suna cewa, “zamunta a qafa take”

Riqon Addini: A tarbiyar Hausa, ana so a ga mutum ya riqi addininsa na Musulunci ba da wasa ba. Riqon addini shi ne shaidar cikar mutum. Idan mutum yana wasa da addininsa, galibi mutane suna xari-xari da shi, kuma ba su faye kama maganarsa da qarfi ba. Dalili kuwa, shi addini kullum yana tare da gaskiya, da adalci, da dattako, da tsare mutunci, da kawaici, da rashin tsegumi ko katsalanda, da sauran halayen irin waxannan. (Alhassan da wasu,1982:26-27).

Junidu da wasu (2015) suna masu bayani kan tarbiyya ita ce halayyar gudanar da rayuwar kowanne fanni bisa wani tsari ko hanyoyin da al’umma ta keve, kuma ta karve su. Ana samun tarbiyya ne ta hanyar horo, da sharuxxa, da karva ko xaukar halayya, da cuxanya a matakai da guraben zamantakewa daban-daban. Tarbiyya babban tanadi ne na yadda mutum zai gudanar da rayuwa a matsayin cikakken kamilin mutum wanda zai iya gudanar da al’amuransa cikin al’umma ba tare da an tsangwame shi ba. Kuma yana gudanar da rayuwa ba tare da ya tsangwani wani ba, wanda hakan ke nuni da tarbiyya tana shiga jiki ne a hankali har a saba ta zama hanyar rayuwa. Wacce irin tarbiyya fina-finan Hausa suke nuna wa al’ummar Hausawa, shin tarbiyya ce da al’umma takan yi na’am da su? Kuma duka fina-finan ne ba sa nuna tarbiyyar Bahaushe? Bari mu duba ire-iren tarbiyya a al’adar Bahaushe:

Tsoron Allah: Babbar tarbiyyar da mutum zai xauka, ya riqe, ya horar da kansa ita ce tsoron Ubangijinsa. Duk abin da zai yi, ya yi domin Allah. Wannan zai kawar da son zuciya da qyamar wani, sannan zai sa ya yi gaskiya ya kuma yi tsayin daka a duk abin da ya sa'a gaba.

Tarbiyyar Zamantakewa: Wannan na nufin tarbiyya yadda mutum zai gudanar da rayuwarsa cikin al'umma. Kusan duk wani nau'in tarbiyya ya shigo qarqashin tarbiyyar zamantakewa. Tarbiyya ce ta sanin muhimmanci al'umma da tanade-tanaden al'umma a matsayin wani fage da yake renon mutum ya yi cuxanya da jama'a, ya kuma kawo ci gaban al'umma.

Tarbiyyar Tsare Amana: Tarbiyya ce ta riqon gaskiya da kula da kiyaye duk wani bayani, ko dukiya da aka ba ka ko danqa maka. Amana tana buqatar yarda da aminci tsakanin mai bayarwa da mai karva. Amana tana iya kasancewa ta ajiyar dukiya, ko ta gudanar da dukiya, ko ta yin aiki, ko ta kiyaye sirri, ko ta riqon iyali, ko ta kayan gado da sauransu. Tarbiyyar da ake buqata a nan ita ce kada mutum ya ci kowacce irin amana aka danqa masa a hannu. Wannan tarbiyyar ce za ta hana cin da karvar rashawa.

Tarbiyyar bin doka : Wannan sabawa da kiyaye qa'iodoji da tanade-tanade, da sharuxxa da aka shimfixa ne, domin a sami zaman lafiya da kare hakkin kowa a cikin al'umma. Bin doka ne zai hana rikice-rikice a cikin al'umma.

Tarbiyyar cinikayya: Tarbiyyar cinikayya, tana koya yadda za a kiyaye halayyar ciniki da yadda za'a gudanar da shi, cikin jin daxi, babu cuta ba cutarwa.

Tarbiyyar lafazi:Tarbiyyar lafazi na horo ne ga yadda mutum zai magana da wani cikin mutumci, da ba da kima. Ana kiyaye lafazin vatanci, ko zagi ko qasqantar da mutum.

Tarbiyyar Kame Kai: Wannan tana koya yadda mutum zai hana kansa shiga waxansu al'amurra da za su sa mutuncinsa ya zube. Wannan tarbiyya tana buqatar haquri da juriya.

Tarbiyyar yin Gaskiya: Wannan tarbiyya ce da take buqatar faxi ko yin abin da yake da akwai ba tare da wani qarin abu ba. Gaskiya tana hana yin qarya, da yin ha'inci, da yin sharri ko qazafi, da ba da shaidar qarya, da xaukar wa rayuwa abin da ya fi qarfinta da sauransu.

Tarbiyyar Taimakon Juna: Tarbiyya ce da take koya tausayi da jin qai da gudanar da rayuwa tare da qaunar jama'a. Tarbiyya ce ta cudene-ni na cuxe-ka yadda mai qarfi da marar qarfi ko xan uwa da xan uwa za su taimakawa juna.

Tarbiyyar Tsaftar Jiki Da Muhalli: Tsafta tana daga imani. Saboda haka tarbiyyar tsaftar jiki da muhalli ta zama dole domin kiyaye lafiyar kowa da kowa, da gudanar da ibada.

Tarbiyyar Kishin Qasa: Wannan tarbiyya ce da za a cusa wa mutum, ko ya xauke ta domin ya yi wa qasa aiki da zuciya xaya. Wannan tarbiyyar za ta sa son qasa, da aikin ci gaban qasa, da hana zagon qasa. Duka waxannan na daga cikin wasu al'amura na tsarin rayuwar Hausawa waxanda za a so a dinga jin xuriyar aiwatar da su a cikin fina-fina Hausa. A wannan bincike za a kalli waxanan yanaye-yanayen zamantakewar Hausawa dangane da batun da aka sanya xambar aikin a kansa, domin a fitar da aya daga cikin tsakuwa, za a kalli waxannan kyawawan xabi'u da tajoji a ga shin hakan suke a tsarin tafiyar da ake yau na shiryawa tare da samar da fina-fina Hausa? An yi bitar waxanan ayyuka ne, saboda suna da alaqa da yanayin rayuwar al'ummar Hausawa, kuma wannan aiki daman an gina shi a kan Hausawa ne, ana kuma danganta aiki da yanayin zamanatakewar al'ummar Hausawa a cikin fina-finan Hausa, ta yin waiwayen sigogi da yanayin xabi'a da tajojin Bahaushe na fil azal, yin bittar zai taimaka wajen ba da damar sanin yadda za a samar wa fina-finan gurbinsu ta iya tantance su a ganeshin fina-finan Hausa ne ko kuwa dai fina-finai ne da aka yi su da Hausa.

2.18 Alaqar Da Ke Tsakanin Fina-finan Hausa Da Rubutun Zube

Adamu (2004) ya yi nazari a kan yadda aka samar da wasu fina-finan Hausa daga qagaggun labaran Hausa. Marubucin ya bi diddigin tarihin samuwar rubutun zube wato gudummawar hukumar fassara qarqashin Rupert East da rawar da hukumar talifi ta taka wajen havvaka da ci-gaba da samar da rubutun zube na Hausa. Marubucin ya zayyano jerin littatafan zube waxanda aka juya su zuwa cikin fim na Hausa har talatin da uku.

Binciken nasa ya gangaro har lokacin da fina-finan Hausa suka fara kwaikwayon fina-finan qasashen Amerika da na fina-finan Najeriya na Ingilishi ana baddala su tare da sauya su zuwa na Hausa. Binciken nasa da wannan ba su da wata alaqa ta qut-da-qut, sai dai za a iya cewa sun yi tarayya a wajen bin diddigin tarihin samuwar fina-finan Hausa.

Amma wannan aiki so yake ya tantance shin fina-finan nan na Hausa ne, ko kuwa fina-finai ne da ake yin su da Hausa kawai? Wajibi ne a kula da yanayin zamantakewar Hausawa dangane da xabi'un su a cikin fina-finan .

Haqiqa rubutun zube musamman na kasuwar adabin Kano, ya samu bunqasa lokacin da aka fara xauka domin mai da shi cikin faifan bidiyo. Misali, littafin zube mai suna "*In da So* da *Qauna*" na Gidan Dabino (1990) an mai da shi faifan bidiyo a shekarar 1994. (Umma, 2009:51). Haka kuma, a shekarar 1997 aka xauki littafin da Bilkisu Salisu Ahmed Funtuwa ta rubuta mai suna "*Ki Yarda da ni*", aka ma yar da shi faifan bidiyo wanda Kamfanin Mandawari Enterprises ya shirya fim (Umma, 2008:103). Tun daga wanna lokacin ne kasuwar rubutun zube na Hausa ya samu bunqasa zuwa faifan bidiyo. Misalin wasu qagaggun labarai ko rubutun zube da aka mayar da su zuwa faifan bidiyo sun haxa da:

- Maimunatu na Ibrahim Birniwa.
- Ta Leqo Ta Koma, na Nazir Adam Salih.
- Me Ya Fi Kuxi, na Nazir Adam Salih.
- Kowa ya daka rawar wani, na Garba Buhari Yola.
- Namiji Ba Xan Goyo ba ne, na Garba Buhari Yala.
- Kwabon Masoyi na Malam Adam Yakasai (Malumfashi: 2011:361).

Shi ma Kuffi (2016) ya kalli yadda masu shirya fina-finan Hausa sukan mayar da labaran zube zuwa fim. Marubucin ya xauki labarin *Bawa mai Qusumbbi* na cikin littafin Magana Jari ce Liitafi na biyu aka mai da shi zuwa wasan kwaikwayo na talabijin wanda aka nuna shi a gidan talabijin na Tarayya, Legas daga shakarar 1995 zuwa 1996. Wanda ya ba da umurnin shirin shi ne Alhaji Qasimu Yero da taimakon Ma'aikatar Yaxa Labarai da Ma'aikatar Tsaro da Jaridar *Daily Time da New Nigerian.*

Bayan nan akwai fim *Sarki Jatau* wanda shi ma an xauko labarin ne daga *Magana Jari ce*Littafi na biyu zuwa fim na Hausa, wanda aka fara nuna shi a Ado Bayero *Hall*. Wanda ya shirya fim xin shi ne Alhaji Bashir Abdullahi Rijau. Dalilin da ya sa aka xauki labarin Sarki Jatau zuwa fim na Hausa shi ne, yana xauke da adabin qwarai, don haka aka ga akwai buqatar a juyar da adabin da yadda za a adana shi. Ko da 'yan baya sun zo, za su samu abin kallo, domin yawancin yara wannan zamani sun gwammace su yi kallo da su karanta labaran Hausa. Marubucin ya ce ana iya raba baddalawa zuwa kashi uku.

Baddalawar sako-sako *Loose Adaptation*: wato fassara kanun batun zuwa wani saqon na daban, yawancin irin wannan faasarar, takan tafi ta yadda Darakta ko Furodusa yake son abin sa, irin wannan takan sauya yadda aka tsara shiga ko fitowan fim.

Baddalawa amintacciya *Faithfull Adaptation*: a nan masu shirya fim, sukan yi bakin qoqarin su wajen fassara kanun magana gwargwadon yadda ya zo tun daga tushe, ba tare da an sauya masa ma'anarsa ta asali ba.

Baddalawar zahiri/kai tsaye *Literal Adaptation*: shi ne qoqarin fassara fitowa xan fim dangane gagarumar taimako da ya taka a aikace, kamar yadda ake ganinshi wato halayyar da xan fim yake kan aikatawa gwargwadon yadda za a fassara, a kuma yi amfani da mizanin da akan

amfani da shin a nazarin fina-finan . Ita kuwa Hauwa(2013) ta ce: Haqiqa bidiyo na rubutun zube ya samu karvuwa da bunqasa a wurin jama'a fiye da rubutun zube, bisa waxannan dalilai su ne kamar haka:

- Masu ilimi suke karanta littattafan zube na Hausa, wato waxanda suka iya karatu, musamman na Hausa, amma faifan bidiyo ba sai masu ilimi ba, wanda bai tava zuwa makaranta ba a yau kallon faifan bidiyo na waxanda asalin su littattafan zube ne.
- Masu karanta littattafan zube suna xaukar lokaci kafin su gama karanta shi amma na rubutun zube wanda aka juya shi zuwa faifan bidiyo cikin qanqanin lokaci zaka gan shi kuma ka gamsu.
- Wata bunqasa da rutubun zube da aka juya shi zuwa faifan bidiyo ya samu, idan ka ga fim xin zai yi wahala ba ka fahimci abin da yake nufi ba, ko inda ya sa ka gaba, ko da kuwa ba ka da ilimi ko ma ba ka tava zuwa makaranta ba, savanin littattafan rubutun zube wanda sai kana da ilimi, kuma ka nutsu ka tara hankalinka kafin ka fahimci inda ya sa gaba.
- Rubutun zube na faifan bidiyo ya samu karvuwa wurin jama'a, saboda mata da maza da manya da yara, da manoma, kai hatta wanda yake ruga zai iya kallon bidiyo kuma ya fahimci inda aka sa gaba ko saqon da yake qunshe a ciki,
- Yara 'yan sakandare su suka fi kowa karanta littattafan qagaggun labarai, musamman na kasuwar adabin Kano. Amma yanzu har almajirai da magidanta suna kallon faifan bidiyo na Hausa.
- Bunqasarsa ta kai har a wayar hannu ana iya ganin fim xin Hausa wanda aka juya daga rubutun zube zuwa ta kai za a iya ganinsa a *internet* (yanar gizo).

- Sannan kana zaune za a turo maka da faifan bidiyo na rubutun zube a wayarka ta hannu ko a na'ura mai qwaqwalwa cikin qanqanin lokaci, ba sai ka sha wahalar karatu da neman littafi ba.
- Bunqasarsa ta sa yanzu ba a wahala wajen shirya faifan bidiyo, a xan lokaci ana shirya shi kuma a gani. Sannan kuma ya watsu wajen cikin duniya a cikin 'yan daqiqa. Sannan ba sa shan wahala wajen a duba musu a tace nan da nan. Amma rubutun zube, sai an kai wa masana sun duba, sauqin karantawa, wanda kafin a samu yadda ake so za a xauki lokaci.
- Rubutun zube sai an buga a na'urar rubutu (*typing machine*) wanda yake shi ma wahala ne ga cin rai, ga kuma yawan kuskure a rubutun, kuma ba kowa ba ne ya iya.
- A da mata aka fi sani da kallon faifan bidiyo na Hausa, amma a yanzu maza matasa sun fi kowa kallon fina-finan Hausa. Wannan ba qaramin ci gaban rubutun zube ya samu ba, maimakon wahala yanzu ga shi a sauqaqe.
- Yawanci ba a faye sayen littattafan rubutun zube ba, sai dai idan mutum ya sayi xaya, idan ya gama karantawa sai a mayar kasuwa a ba shi wani, haka zai yi ta yi yana karanta littattafan iri-iri. Amma faifan bidiyo martabarsa ta sa aron sa ma ba a bayarwa yanzu sai dai ka mallaki naka.
- Faifan bidiyo wato fim na Hausa ba ya wahalar samu, ga su nan a shaguna da cikin unguwanni da kan hanya da kasuwa, kai har tituna cikin gari da wajen gari ga su nan ana sayar da su.
- A maimakon da da ka ga 'yan-mata da gayu na yawo da adabin kasuwar Kano a jaka, yanzu sun koma yawo da faifan bidiyo a cikinta.

Idan muka duba vangaren zamantakewa ta al'umma, faifan bidiyo ya ba da gudummawa a abubuwa da yawa, ya wayar da kan jama'a. Misali a fagen:

- **Sutura:** Bunqasar rubutun zube zuwa faifan bidiyo ya bunqasa yanayin shiga ko sa sutura a cikin al'umma, domin kuma kafin a fara juya rubutun sutura mai kyau da xunkunan da aka sa a ciki, amma masu karatu ba sa kwaikwayar abin da suka karanta. Amma lokacin da suka fara kallon faifan bidiyo sai suka fi tasirintuwa da kuma kwaikwayon irin shigar da suka gani a ciki. Kuma ya bunqasa yanayin shigar mata a gidajensu na aure. Dalilin, haka shi ne a ciki za a nuna mace ta yi wa mijinta kwalliya kuma ya gamsu, kuma ya qara mata kima da daraja a idonsa, ita ma tana gama kallon sai ta gwada ta gani.
- **Muhalli:** Masukarantalittattafan qagaggun labarai a da ba su damu da irin gidan da aka fasalta a cikin littattafan ba duk da cewa marubutan suna bayyana irin kayan qawa da aka sa a cikin wani gida na mai arziki ko na alfarma. Amma yanzu saboda bunqasar faifan bidiyo na rubutun zube da yadda ya samu karvuwa a wurin jama'a, har kwaikwayar irin tsarin da aka gani a cikin faifan bidiyo a gidan ake yi. Misali, kujeru, labule, kayan xaki, su gado, madubi da sauransu.

2.19 Fina-finan Hausa A Mahangar Qwararru

An karanto mazanarta sun yi tsokaci mai zurfi a kan batutuwan da aka gina fina-finan Hausa a bisa mataki na ilmi. Don haka an ci karo da wasu ayyuka da aka yi a kwanan nan a bisa batutuwa mabambanta waxanda suka dace a yi nazarinsu. Ahmad (2016) wanda ya yi nazarin fassara da amfaninta a cikin fina-finan Hausa ya fito da ma'anar fassara kamar yadda

masana irin su Nida (1974) da Baker (1992) Nord (2001) suka yi ittifaqi a kai cewar juyar ma'anar wani saqo ko magana ko batu daga harshen bayarwa zuwa harshen qarba shi ne harshen fassara. Ma'ana sauya magana daga harshen A zuwa harshen B, ta yadda zai ba da ma'ana gwargwadon yadda aka tsara shi daga harshen farko zuwa harshen na biyu. An kawo nau'o'in fassara guda huxu (4), wato fassarar kalma zuwa kalma, fassara kai tsaye, fassara mai 'yanci da fassarar ma'ana.

An kawo nau'o'in fassara da ake amfani da su a fina-finan Hausa. Ahmad (2016) ya ce akwai fassara ta nanatau (*dubbing*) sannan akwai fassara wanda akan fassara abin da xan wasa ya ce a rubuce a qarqashin hoon talabijin wato (*subtittle*). Marubucin ya kawo dalilai da suka asassa fassara a fina-finan Hausa zuwa harshe Ingilishi. Wannan ya biyo bayan yawaitar milyoyin 'yan kallon Fina-finan Hausa a ciki da wajen Afrika kamar su Afirka ta tsakiya da Asiya da Turai da Amirka waxanda ake yin fassara domin su fahimci abin da suke kallo a nan gida Nijeriya. Manazarcin ya zavo wasu fina-finan Hausa goma sha biyu, inda ya nuna inda aka tafka kurakurai da matsalolin da aikin fassara yake fuskanta a cikin fina-finan Hausa, ya ba da misali daga fina-finai irin su *Gida da Waje* (2011) ya nuna an yi fassara daga Hausa zuwa harshen Ingilishi, inda ya dinga fito da wuraren da ake samun kurakurai na fassara daga harshen Ingilishi.

A yayin da Adamu (2016) ya kalli matsayin mata 'yan fim a fina-finan Hausa dangane da vaxalar da suka tafka a baya da kuma irin yadda al'ummar Hausawa da malamai da gwamnati suka yi tir da abubuwan da suke aiwatarwa. Misali na farko shi ne halin Hiyana da Usman wanda ya savawa addinin Musulunci da al'adar Bahaushe. Sai su Mu'azu da Shehu, (2016) suka yi nazarin addinin gargajiya da camfi a cikin fina-finan Hausa, sun zavi fina-finai guda shida aka yi amfani da su; *As-habul kahfi (2013) da Yankin Imani (2014) da Babban*

Zaure da Birnin Masoya da Farar Qafa da kuma Daga Allah ne (2013). An raba fina-finan gida biyu inda wasu aka yi nazarin bautar gargarjiya a cikin su, wasu kuma aka fito da camfe-camfe da yadda Bahaushe ya yi imani da su a tsarin zamantakewarsa. Sun kalli bautar gargajiyar Bahaushe da Imani da camfi a cikin fina-finan Hausa. Rabi Abdulsalam (2016) ta bi salon Ahmad da ya yi nazarin aikin fassara a fina-finan Hausa daga English zuwa Hausa. Amma aikin Rabi Abdulsalam (2016) ya bambanta da na Ahmad (2016) domin ta buxa aiki, inda ta yi nazarin kalaman fassara daga turanci zuwa Hausa a fina-finan Hausa ta vangare sauyin harshe da ginin jimla da adon harshe da ladabin magana a al'ada.

Liman (2016) ya kalli baddalawa ne kamar yadda Kuffi (2016) ya yi, shi Liman ya dubi yadda ake xaukar tatsuniyoyin Hausawa a mayar da su fina-finan Hausa inda ya fito da yadda aka juyar da tatsuniyar Ruwan Bagaja ta kuma labaran zube wanda Alhaji Abubakar Imam ya rubuta, kuma daga baya aka sake mayar da shi ya kuma fim xin *RuwanBagaja*, kamfanin Sarauniya shi ya shiry ya samar da shi, tare da sauran labaran gargajiya na tatsuniya zuwa fina-finan Hausa. *Sangaya da Kishiyata da Maitatsine da Daskinda rixi*. Shi kuwa Giwa (2016) ya kalli tsarin zaman iyali mai yaxo ne a cikin fim xin *Naira*, musamman rayuwar maigida wanda yake da mata huxu a inda kowacce take qoqarin ta faranta wa mijinta rai domin ta samu ya biya mata bukatanta na kuxi ko ta mallaki wata dukiya daga wurin tunda ana nuna masa so. Sannan an kalli qarfin tsafi da sihiri a cikin fim xin kamar yadda Mu'azu da Shehu (2016) suke nuna a cikin aikinsu. Ita ma Asabe (2016) ta kalli tsarin zamantakewar aure ne ga namiji da yake da mata guda biyu, musamman an gina fim xin Xakin Amarya ne akan kishi zalla. Xan Asabe (2016) ya fito da irin tavargazar ta aka dinga yi da tashin hankali a tsakanin mata su biyu, har sai da zaman ya kai Nuratu ta fasa wa Aisha kai. Ita kuma amaryar Abubakar, ta fasa kayan kallo da gilashin jere, har da gayyatar danginta ana dambe a

gidan Abubakar a tsakanin ‘yanuwa na uwar gida da na amarya. Don haka, fim xin yana nuna rayuwar ma’aurata ne kamar yadda yakan kasance a cikin al’ummar Hausawa. Duk da haka ba su iya tantance wa mai karutu ba, wai shin fina-finan nan na Hausar ne ko kuwa an dai yi su ne da harshen Hausa? Domin ba san Bahaushe da yin aika-aika irin yarda muka gani a sakanin waxannan ma’aurata a al’adance.

Masana a fagen fina-finan Hausa sun yi qoqarin binciko umulabai’sin da suka sanya jama’a suke ta kuka da fina-finan Hausa. Aliyu (2004) ya yi tsokaci ne a cikin maqalarsa mai taken “Fargar-jaji ko Riga Malam masallaci” ya ce daga cikin sanarwar da gwamnati ta bayar za mu fahimci wasu daga cikin qorafe-qorafen da ake yi game da fina-finan Hausa, musamman ma dai waxanda suka jivanci addini da al’adar Bahaushe. Sun fi tasiri ga al’umma.

2.19.1 Addini

Yawancin mutane suna qorafi ne da yadda ake wasa da addinin Musulunci ko kuma ake fassara ayoyin Alqur’ani yadda aka ga dama a cikin fina-finan Hausa. A wasu lokutan kuma akan yi wa malami habaici ko zambo. Wannan illa ta fi fitowa a cikin yawancin fina-finan Ibro wato Rabilu Musa da Ciroki wato Bashir Bala a kalli *Jahilci ya fi Hauka* da *Addini* ko *Al’ada* da *Saliha.*

2.19.2 **Al’ada**

Akwai masu kuka da fina-finan Hausa saboda yadda suke gurvata al'adar Bahaushe musamman ma dai ta hanyar kwaikwayon al'adun wasu al'ummomi na daban, wato na Turawa da Indiyawa da sauran su. Wasu daga cikin abubuwan da Aliyu (2004) yake ganin ana nuna wa a fina-finan Hausa waxanda suka sava da al'adar Bahaushe sune kamar haka:

- Tava jikin mace da rungumarta da yin rawa da ita.
- Yin bokanci da samun nassara ba tare da nuna illar yin hakan ba.
- Faxawa rijiya.
- Barin gida.
- Qona kai saboda an hana yarinya wanda take so.
- Maganganun batsa da ashar da maganganun da za su kai mutum ga yin ridda.
- Sanya kaya masu nuna tsaraici.
- Fito da munanan al'adu waxanda suka sava wa addini.
- Cusa baqin al'adu da sauransu.

Wannan bincike yana nazarin halayar zamantakewar Hausawa bisa xabi'u da halayyar 'yan Fim a cikin fina-finan Hausa dacewarsa ko rashin dacewa, ta yadda za a iya tantance wai waxanne fina-finai ne na Hausa sannan waxanne ake kira fim da Hausa. Amma shi Aliyu (2004) bai zurfafa aikin nasa ba ta kawo misalai daga wasu fina-finai Hausar. Ya kamata a ce ya kalli fina-finan ne tukunna kafin yanke wa kansa hukunci. Sannan ya dace a ce wuri kaza an ga Wane ya ce kaza da kaza, kuma faxin hakan ya sava ko ya gurvata al'adar Hausawa a wuri kaza ko kuma a aikace. Amma wannan bincike shi ya kawo misalan fina-finan Hausa ne, a inda ya kalli fina-finan sannan aka fito da harshe 'yan wasan da xabi'unsu ta inda aka dangana su da yadda suka sava tsarin zamatakewar Hausawa wadda ba a san Bahaushe da irin wannan halin ba. Don haka aikin Aliyu ya kalli matsalolin fina-finan Hausa ne, amma ba hanyoyin magance su ba ko kuma ta yadda za a inganta su.

Alkanawy (2004) ya bi sahun Aliyu (2004) inda ya kalli fina-finan Hausa: faxakarwa ko shagaltarwa? Ya fara ne da bin tarihin wasan kwaikwayon gargajiyar Bahaushe tun daga tushe lokacin da fatake kan tsaya a zango-zango suna gabatar da wasan kwaikwayo a kan hanyarsu ta zuwa ci rani. Bayan su tashe da wasannin yara, sannan ya tattauna a kan sabobin hanyoyin nuna wasan kwaikwayo wanda turawa suka zo da su qasar Hausa,kamar rediyo da silimi da majigi da littattafan wasannin kwaikwayosun kuma kawo hanyoyin aiwatar da wasan kwaikwayo na zamani. Kafa qungiyoyin wasannin kwaikwayo a kwaleji-kwaleji da na qungiyoyin masu zaman kansu, wanda hakan ya yi sanadiyyar shigo da shirye-shirye zuwa gidajen Talabijin na NTA Kaduna da CTV Kano kaxan daga cikin wasannin da akan nuna mako-mako sun haxa da *Xanhaki da Xan Kurma da Quliya da Bakan Gizo,* daga shekarar 1976-qarshen 1996.

Marubucin Alkanawy (2004) ya tattauna a kan wasan Hausa na bidiyo wanda a nan ne muke da alaqa da shi nasa binciken. Inda ya ce: mutane da suke cikin harkar a farko suna da tunanin yaxa al'adar Hausa, kuma suna da tunanin gobe. Idan muka duba fina-finai irin su "*Munkar*" da *In da So da Qauna" da "Hoxijan" da* sauransu za mu ga haka. Har fina-finan baya irinsu "*Ki Yarda da Ni"*

da "Gaskiya Dokin Qarfe" da "Tsautsayin Takaba" an yi su ba su savawa al'ada ko addini ba, kuma babu waqa mai rawa a cikin su, amma an yi cinikin su yadda ya kamata kuma an yaba su sosai.

Ashe ke nan, da za a koma tsarin bin al'adar Bahaushe wajen aiwatar da fina-finan Hausa to, za su dinga samun tagomashi savanin kallon da ake masu a yanzu. Watikila, ba za a dinga tababar rasa yadda za a iya tantace shin fina-finan Hausa ne ko kuwa fina-finai ne da ake yin su da harshen Hausa ba?

Marubucin ya fito da kyawawan jigogin da kan gina fina-finan Hausa a kai a da. Misali, riqe alqawari da illar sava shi da addini a cikin fina-finan irin su "*Tsautsayin Takaba" da "Xan halak"*. Marubucin ya fito da varnar da fina-finan suke yi wa al'ada da addinin Musulunci, kamar yadda shi ma Aliyu (2004) ya fito da su a cikin fina-finai irin su "*Jalli" da "Khusufi" da "Xan Adam Butulu*". Don haka wannan binciken marubutan Alkanawy, (2004) da Aliyu (2004) su karkata ta fuska biyu ne, wato faxakarwa ko kuma shagaltarwa a fina-finan Hausa. Amma shi wannan aiki zai kalli yanayin zamantakewar Hausawa ne a bisa tsarin aiwatarwa a faifan bidiyon dangane xabi'un Hausawa, shin suna kan tsari ko kuwa sun bauxe hanya, ta yadda za a sanya su bisa mizanin awo don gano shin fina-finan Hausar ne ko kuwa fim ne kawai da ake yi da Hausa?. Tana iya kasancewa al'umma Hausawa suna ta sukar matsayin fina-finan Hausa don wataqila ba sa bin tafarkin al'ada da xabi'u Hausawa, to amma, tambaya a nan ita ce ina hujja a ilimance tare madogara wanda zai nuna mana cewer fina-finan ba na Hausa ba ne? Don haka wannan bincike ya zavo wasu fina-finai da aka yi tarkensu, domin an ce *inda babu qasa nan ake gardamar kokowa.*

2.19.3 Bitar Nazarin Waqa a Fina-finan Hausa

Wasu masana fina-finan Hausa, sun fi ba da fifiko a fagen nazarin adabin waqa a cikin fina-fina Hausa. A tashi gudummawar Mandawari (2004) ya ce waqa ta fara samun gurbi a fina-finan Hausa ne a shekarar 1986. A cikin wani shiri mai suna *Dausayin Soyayya,* wanda aka fi sani da *Jamila da Jamilu* mallakar gidan talabijin na NTA Kano. Sa'annan a 1994 an sake rera waqa a fim xin *Munkar.* Waqar fim xin *Munkar* ita ce waqar farko a fim xin Hausa wato fim xin da aka yi a kaset xin bidiyo amma ba na talabijin ba. *Iyan-Tama Multimedia* ne kamfanin da ya kafa kundin tarihi a fagen shirya

fina-finan Hausa domin shi ne a 1997 ya yi yunqurin da ya sami nasara ta fuskar gwama rubutacciyar waqa da kixan zamani na *key board* a cikin fim xin *Badaqala*. Sauran fina-finan da suka shaharar da waqoqin fina-finai sun haxa da *Ki yarda da ni* wanda *Mandawari Enterprises* 1997 ya shirya (Malumfashi: 2011:361). Sai sauran fina-finai irin su *Sangaya da Qilu Ta Ja Bau da Badali da Wasila da Mujadala* waxanda aka shirya su a shekarar 1999-2001. Ita kuma Umma Ado Abbas (2008) ta xauki waqoqin fina-finan ne ta yi nazarin adon harshe a daga cikin su. Wato ta dangata aikin nata ta hanyar lalubo yadda adon harshe yake a sassarke a cikin waqoqin fina-finan Hausa, musamman waxanda aka yi daga 1984-2006. Amma duk da haka, binciken ya duba tarihin vullowar da havakar fina-finai na Hausa tare da yin waiwaye tun daga wanzuwar wasannin kwaikwayo na Hausa. Haka kuma aikin ya bayyana nau'o'in waqoqin fina-finai da suka haxa da waqoqin baka da kuma rubutattu waxanda ake tsarawa da baddalawa.

Marubuciyar ta xauki nau'o'in salon adon harshe irin su abuntarwa da dabbantarwa da kambamar zulaqe da alamtarwa da kinaya da savi zarce da siffantawa da kamantawa, ta yi nazarinsu inda ta fito da su daga cikin waqoqin fina-finan Hausa tare da yin sharhinsu dalla-dalla. Idan aka haxa nazarin Mandawari, (2004) da Umma Ado Abbas (2008) sun yi hannun riga da wannan aiki domin su sun kalli gagarumar taimako da waqoqin Hausa suke takawa a ne a cikin fina-finan Hausa a bisa tarihinsu da ginuwarsu da kuma fasahar da ke tattare cikin waqoqin. Amma wannan bincike zai tarkato ayyukan masanan ne ya yi musu kuxin goro ta yin nazarinsu a matsayinsu na fina-finan Hausa ko kuma fina-finai da Hausa.

2.16.4 Tasirin Baqin Al'adu a Cikin Fina-finan Hausa

Al’ada wata hanya ce da al’umma take gudanar da rayuwarta ta yau da kullum wadda kuma ta bambanta daga wata al’umma zuwa wata. A binciken Umma Ado Abbas (2008) ta nuna sassarquwar adabi cikin adabi ne, inda ta kalli adon harshe a waqoqin fina-finan Hausa. Ta yi nazarin waqoqin fina-finan Hausa ne. Ta hanyar bin diddigin tarihin waqa a fina-finan Hausa. Bayan haka, ta kuma kawo nau’o’in waqoqin Fina-finan Hausa sannan ta kalli tarihin wasu masu shirya waqoqin fina-finan Hausa. Binciken nata ya kuma tavo jigogin waqoqin fina-finan . Ta ci gaba da kawo sigogin adon harshe a waqoqin fina-finan Hausa da yanayinsu, ta hanyar siffantawa da kamantawa da jinsintawa da mutuntawa da dabbantawa da alamtarwa da kinaya da kambarar zulaqe da gangara da savi-zarce da kuma jinkirin faxar sakamako. A taqaice, wannan shi ne qashin bayan aikin Abbas (2008) wanda yake ya bambanta da wannan aikin. Domin wannan aiki yana kallon vurbushin al’adun Yarbawa ne da suka yi tasiri a cikin fina-finan Hausa.

Umma Inuwa (2009) ta duba kutsen baqin al’adu a cikin fina-finan Hausa. Ita ma, Umma Abbas (2008) ta yi bayanin kan ‘yan wasa da masu shirya fina-finan Hausa da tarihin wasu masu shirya fina-finan da nau’o’in fina-finan Hausa da kuma yadda fina-finan suka bazu zuwa cikin qasar Hausa.

Amma, inda gizo ke saqar shi ne yayin da Umma Abbas (2008) ta dubi adabin waqoqin fina-finan Hausa sai ita kuma Umma Aminu Inuwa (2009) ta duba jirwayen al’adun maqwabtan Hausawa na kusa da na nesa a cikin fina-finan Hausa. Ta raba aikin gida biyu ne, zuwa jirwayen al’adu na makwabtan Hausawa na kusa, inda ta xauki nau’i guda-guda kawai

ta nuna yadda suka yi tasiri a cikin fina-finan Hausa. Misali, Yarbawa ta xauki tasirin goggoro da leshi da ashoke a matsayin suturar Yarbawa a sakamakon cuxanya a tsakanin al'ummomin guda biyu shi ya sa har matan Hausawa suke amfana da su, har kuma masu shirya fina-finan suke kwaikwayon amfani da suturun a matsayin kaya na musamman idan ana gudanar da wani shagalin biki suke amfani da su. Tace ana iya ganin haka a fina-finai irinsu da *Uwargida* da *Qasarmu*. Bayan haka, a layin qarshe shafi na 79 ta ce "Haka kuma an sami dangantaka tsakanin Hausawa da Yarbawa ta fuskar kayayyakin kixa" sai dai kash! Ba ta buxa aikin ba, balle ta faxa mana a cikin waxanne fina-finan i ne aka samu irin wannan alaqa na kayan kixa? A gaskiya wannan givi ne babba ta bari. Wannan bincike yana ganin fina-finan Hausa sun xauki wani salo na kwaikwayon wasu al'adun haure musamman na Yarbawa zuwa cikin fina-finan Hausa, kamar su al'adun aure da haihuwa da mutuwa da cimaka da wasu nau'o'in sutura da tsafi, na maza da mata, a yanzu kuwa abin ya ci gaba har ma ta kai yanzu ana shigo da harshen Yarbanci kai tsaye da kaxe-kaxe da waqe da xabi'u irin na Yarbawa zuwa cikin fina-finan Hausa. Ta kuma tavo al'adun Igbo kamar bokanci da tufafinsu a cikin fina-finan Hausa. Ta kuma tavo wani nau'i guda na al'adun Fulani kamar suturar affafai da riqe sanda da sanya wando tsala, ta nuna sun yi tasiri cikin tsarin tufafin Hausawa. Ta kuma kalli nason al'adun Kanuri kamar sanya zanna bukar da sanya laffaya ga matan Hausawa. A xaya gefen, ta kalli al'adun maqwabtan Hausawa na nesa a cikin fina-finan Hausa kamar al'adun Larabawa, alal misali irin su qunshi da kayan zinari da jimamin mutuwa. Sai kuma al'adun Turawa da Sinawa da Asiyawa da Indiyawa duka ta xauki nau'o'i guda ta nuna yadda suka yi tasiri a cikin fina-finan Hausa.

Ya wajaba a qwanqwance aikin Umma Inuwa Abbas, (2009) don a nuna bambancin aikinta da wannan bincike qarara, a yayin da ta dasa tushen aikinta sai ta yi masa shigar shantun qadangare, wato aikin bai dire ba, ta yadda ya kamata a ce an fito da al'adun waxannan al'ummomi maqwabtan Hausa yadda ya kamata. Al'ada fage ne mai faxin gaske, ina ganin ta xebo aikin da yawa, sai ta yanke hukunci ta xauki nau'in al'ada tufafin baqin al'ummomi kawai zalla take xaura su a bisa mizanin tasirin da suke yi a cikin fina-finan Hausa, ba ta mayar da hankali wajen binciko tasirin harshe da abinci da bukukuwa da xabi'u ba.

Wani aiki da ya kamata a fito da shi fili shi ne na Mu'azu (2006) wanda ya kalli tasirin baqin al'adu a qagaggun labaran soyayya na Hausa. A nasa aikin ya zaqulo baqin al'adun mutane waxanda Hausawa suka yi cuxanya da su ta hanyoyi daban-daban, sannan kuma halayyar mutanen ta fito a littattafan qagaggun labaran soyayya na Hausa. Ya taqaita aikin nasa daga shekara ta 1984 zuwa shekara ta 2004, watau shekara ashirin (20) daidai ke nan. Haka kuma ya taqaita binciken ta duba jirwayen al'adun Larabawa da Turawa da Indiyawa a cikin qagaggun labaran soyayya. Sannan ya dubi jirwayen al'adun maqwabtan Hausawa irin su Yarbawa da Fulani da Nufawa da Barebari a littattafan qagaggun labaran soyayya na Hausa a inda shi ma ya bi tsarin xauki xai-xai na al'adun.

Wani manazarcin fina-finan Hausa Chamo (2001) ya dubi tasirin da al'adun Turawa a cikin fina-finan Hausa. Aikin ya tavo ma'anar fim da kuma samuwar fina-finan Hausa. Ya kuma zayyano amfanin fim da rashin amfaninsa ga al'ummar Hausa. Ya yi wa aikin nasa

adalci ta zaqulo wasu fina-finan don fito da al'adun Turawan da tasirinsu a fina-finan Hausa tare da kafa hujjoji da misalai. Kamar yadda Hausawa kan yi lancin fati da kwaktal fati da kwalliyar motar amarya da ango da raba katin xaurin aure da buga kalanda da yanka kek duka a cikin tsarabe-tsaraben auren Hausawa. Amma wannan bincike ya bambanta da na Chamo, a inda wannan aiki ya kalli tasirin al'adun makwabtan Hausawa na cikin gida da na qetare a qoqarin tantance fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa.

A nan an yi bitar ayyuka da suka yi nazari a kan tasirin al'adun al'ummomin daban-daban cikin fina-finan Hausa. Misali, tasirin al'adun Turawa kamar yadda Chamo (2004) ya binciko, ya nuna cewa maqasudin shirya fim shi ne domin wayar da kai, da faxakar da al'umma da nishaxi da annashuwa da samun kuxin shiga da samar da aikin yi ga jama'a. Sannan ta hanyar fim ne za a qulla zumanta, musamman tsakanin 'yan wasa. Ta hanyar fim za a iya koyar da tarbiyya da adana al'adun al'umma. Fim na agazawa wajen gyaran halayen al'umma.

Dangane da tasirin da al'adun da Turawa suka yi a cikin fina-finan Hausa za a iya cewa abu ne da yake qoqarin wuce gona-da-iri, domin kusan dukan fina-finan da ake shiryawa dole ne sai an sami wani vangare na al'adun Turawa da ya yi tasiri. Harshe yana xaya daga cikin muhimman tubala na al'adar kowa ce al'umma, wadda da shi ne al'ummar take amfani da shi wajen sadarwa a tsakanin mutanenta wadda idan ba don shi ba, to abu ne mai wuyar gaske a iya bambance tsakanin xan wata al'umma da wata. Kuma kowace al'umma tana da wata harshen da take amfani da shi.(Chamo,2004:283).

Marubucin ya ce dangane da fina-finan Hausa, harshen Hausa aka fi son a ga ana amfani da shi, amma wasu fina-finan ba haka ba ne, sai ka ji ana tsarma kalmomin Ingilishi, watakila domin burgewa ko qwarewa, misali fina-finai kamar: *Mujadala da Xangaye da Juyin Mulki da Ki Yarda* da ni, duk suna da tasirin kalmomi turanci irin su *exactly da okey da Hello da Oh my God, da He fuck you, da Thank you da next time* da sauransu. Sauran al'adun turawan da marubucin ya tattauna a cikin aikin nasa sun haxa da abincin turawa irin su *Salad* da tasirin muhallin turawa.

Shi ma Muhammad (2004) wanda ya yi bincike a kan siyasar duniya ta harkar fim, yaya ta shafi Bahaushe musamman a cikin wannan zamani? Ya ce kowanne jinsi a duniya yana da nasa tsarin tarbiyya da kuma zamantakewarta sai dai shigowar fim ya sami damar ragargaza kyakkyawar tarbiyyar da Bahaushe yake da ita. Ban yarda da Muhammed xari bisa xari ba, da ya ce wai fina-finan Hausa ne kawai suka ragargaza tarbiyar Bahaushe.Ana iya cewa yana daga ciki. To idan ko haka ne, Muhammed (2004) ya kamata a kawo mana hujja da yadda fina-finan Hausa suka ragargazar, ya kamata ya kafa madogara daga wasu fina-finan da ya kalla. Na yarda da maganarsa cewar Bahaushe yana da kunya da kuma girmama na gaba da shi, maqwabci zai ladabatar da xan maqwabcinsa ba tare da samun wata matsala ba, amma shin haka abin yake a wannan zamani da muke ciki?

2.16.6 Gudunmmawar Mata a Fina-finan Hausa

Yakub (2004) ya nuna matsayin mata da gudunmawarsu, wato tallatawa da inganta tattalin arziqin al'ummar Hausawa a cikin fina-finan Hausa. Ba fim ba, ita kanta rayuwa, in babu mace, ba za ta yiwu ba domin haka Allah Subhanahu wata'ala ya halicci komai nasa da kishiyarsa. Shi kaxai ne ba shi da abokin tarayya. Babu wani fim da za a yi shi, a ce an yi an gama mace ba ta taka rawa a cikinsa ba. Kusan mace ita ce raunanna kuma ita ce mai qarfi a fim, tana ba da gudunmawa da dama a ciki, ita kaxai ce za ta iya futowa a matsayin uwa ko mata ko 'ya ko kaka.A waxannan matakai, sun fi kowane mataki a fim qarfi, domin ko qaramar yarinya ka xauka, ka ba ta matakin uwa, nan da nan za ka ga nutsuwa ta same ta, kuma za ta xauki wannan mataki da muhimmanci.

Aikin nata ya tattauna a kan yadda wasu mata suka xauki nauyin shirya ko su ba da labari ko kuma su xauki nauyin fim, wasu kuma sukan zuba jari ne, kaxan daga cikin matan akwai su Umma Mohammad Ali da Zayya Dantata da Rabi Ado Bayero.

Aikin Ali (2004) an kalli yadda mata sukan zuba jari ne a sana'ar fina-finan Hausa. Wanda hakan ya yi sanadiyyar kafa qungiyar mata masu zuba jari da shirya fina-finai wadda aka kafa a shekarar ta 2000. Irin gudunmawar da mata suka bayar, bai tsaya a samarwa da zuba jari ba, har ma da fito da martabar wannan masana'anta ta hanyar ba mara-xa-kunya a fannin al'adun da kuma addini. Ina ganin hakan ce ta sa Iyan-tama (2004) ya yi nazari a kan matsayin fina-finan Hausa a Musulunci. Marubucin ya kawo ayoyin Alqur'ani da suka yi nuni da a nemi na kai ta hanyar sana'a ba tare da yin zina ba, ko yin shirka ko yin abin da ba a da ilimi a kai. Ya ce addini ya koya mana a guji isar da saqon da ba zai yi amfani ba. Ya wajaba ga dukkan Musulmi da zai shirya fim ya shirya abin da zai yi wa jama'a amfani kamar yadda ya zo cewa: *lallai ka gaya wa bayina su (aikata ko faxi abin da yake alheri)*, (Qur'an 7:53). Iyantama, (2004) ya qara da cewa lallai an yi amfani da hikima ta jan hankali, sannan a canza mummuna

da kyakkyawa. Kamar yadda Yakubu (2004) da Ali (2004) suka yi tsokaci a kan matsayin mace a fina-finan Hausa. Haka shi ma Iyantama (2004) ya karkato da akalar bincikensa a kan matsayin matan a fina-finan Hausa, bayan ya gama tsattsafe matsayin fina-finan Hausa a Musulunci.

Marubucin ya ce shi kuwa al'amarin halxar mace da namiji don su yi shirin fim, shi ne ya fi tsokanewa duk jama'ar musulmi ido a maganar fina-finai. Lallai kam komai son zuciyar mavarnaci, ya san babban haxari da xigirgire ne a dukkan wata cuxanya da ke tsakanin mace da namiji da ba su halatta ga juna ba. Wannan ya bayyana a fili a inda Allah (SWT) yake umarni da cewa:

> Lallai idan za ku tambaye su wani abu (mata), ko ku tambaye su da wata kariya. Domin hakan zai tsarkake ku, su ma tsarkake zuciyarsu" (33:53)

Mene ne dalilin da ya sanya cuxanya mace da namiji ta zama haxari?Saboda kasancewar an halittawa maza jin qauna da sha'awar mata, to, gudun kada mutum ya faxawa abin da aka hana shi, alhalin an qawata masa abin, ya sa aka kange shi ga kusantar abin gaba xaya kamar yadda ya zo a surar Ahzab, aya ta 53 kamar yadda aka gani a baya.

Duk da cewa haka, wannan bata haramta yin mu'amala tsakanin mata da maza ba, sai dai lallai Musuluncin ya hana matsananciyar kevewa ko cuxanya da matan da ba su dace ba da mutum ba, ta yadda har sha'awa za ta iya shiga tsakaninsu. ya Allah a kasuwa ne, wajen ciniki, ko kuma a asibiti ne, ko kuma a cikin mota ko wajen aikin irin na shirya fina-finai. (Iyantama, 2004:426). Ba dan saboda komai ba ne aka gindaya tsattsauran tsaro illa, saboda cewar Mahalicci.

> Lallai ku sani cewa kada (ko kaxan) kusantar da kanku da zina, domin yin kusanci da ita mummunan laifi ne, kuma yana hana ga ci gaba a rayuwa (17:32). Fassarar Abubakar Gumi.

A taqaice, Iyantama (2004) yana mai cewa idan aka ce matsayin mata a fina-finan Hausa to, ba su da wani matsayi illa ma'aikata da za a kira su daga gidajen iyayensu, su yi sana'ar da aka kira su, su koma gida.

A nan Iyantama (2004) yana qoqarin nuna ma al'umma cewa mata 'yan fim ba mutanen banza ba ne, suna da daraja da matsayi kyakkyawa, sai wacce da ballagazar da kanta. A yayin da Iyantama (2004) yake ta fafutukar fito da matsayin fina-finan Hausa a Musulunci dangane da matsayin mata, sai Balbasatu, (2004) ta kalli hoton mata cikin fina-finan Hausa: Tsokaci tsakanin al'ada da zamani. Marubuciyar ta fi mai da hankali ne a kan gurvatar halayen mata cikin fina-finan zamani. Ta nuna cewar al'adar ta kasu kashi uku; akwai tsantsar al'adar matan Hausawa tun na dauri, akwai kuma al'ada da bayan zuwan Musulunci ne aka same ta amma ta zama tamkar al'adar Hausawa, misali sanya hijabi. Sai kuma al'adun da aka kawo wa matan Hausawa bayan cuxanya da baqi. Misali sanya wando ko xan guntun siket ga mata ko raye-raye da waqe-waqe tsakanin namiji da mace da sauran su.

An xauki wasu al'adu a wannan vangaren aka dubi waxanne al'adu ne fina-finan Hausa suka fi ba wa fifiko? An gano haka ta xaukar al'adun ana kwatanta su da irin waxanda ake nunawa a cikin fina-finan Hausa. Misali, kunya da zaven mijin aure da girmama aure da sutura da

waqe-waqe da kishi da mu'amala da dangin miji da dogaro da kai da riqon amana da asirin miji.

Alaqar aikin Ibrahim (2004) da wannan shi ne, wasu daga xabi'un Hausawa waxanda ba a aiwatar da su daidai bisa tsarin al'adar da aka san Bahaushe da su. Misali, zamantakewar kunya da ke tsakanin uwa da babbar 'yarta da zaben mijin aure da girmama aure da kishi da mu'amala da dangin miji. Amma duk da haka mun yi hannun riga da ita. Domin ita ta kalli al'adar matan Hausawa da fina-finan Hausa suke son ruguzawa ne. Wanda wannan aiki bai tsaya a kan mataba kawai zai kalli yanayin zamantakewar Hausawa a bisa yadda suke aiwatar da xabi'unsu a cikin fina-finan Hausa, ta yadda za a xora su a bisa mizanin awo don a tantance fina-finan Hausa da fina-finai da Hausa. Wanda a qarshe hakan zai iya tabbatar mana da cewa shin fina-finan na Hausa ne ko kuma suna dai amsa sunan fim na Hausa ne kawai.

Shi kuwa Adamu (2016) ya kalli baxalar da matan Hausawa Musulmai 'yan Arewa 'yan fim na Hausa suke yi, yana mai danganta aikin nasa da cewa baxalar da Maryam Hiyana da wani Usman Legas suka yi a wani faifai na bidiyo da aka dinga watsawa ta wayar salula a watan Yuli, 2007, wanda ya xauki minti 8 da sakan 37 ya nuna wata ballagazar al'ada wadda ba a san Bahaushe da ita ba. Manazarcin ya yi nazarin abubuwa da dama a bisa sakamakon abin da ya biyo bayan yaxuwar bidiyon, inda aka nuna Maryan Hiyana da Usman xan canjin kuxi a Legas suna kwanciya. Dalilin hakan, al'ummar Hausawa ba sa kallon 'yan fim na Hausa da daraja. Sai dai, duk da wasu suna yi musu tofin Allah tsine, masoyan fim irin su Kennass Aminu Babini ya yi rubutu a cikin jaridar Aminiya da *Leadership* cewar yana mai so da qaunar Maryam. Shi kuma Rabiu Hamdala na mai son Hiyana da cewar ai gwanda Maryam Hiyana sau dubu da wasu matan da suke zina da aurensu har su shigo da cikin shege

gidan mazajensu har ma a haifi ‘ya’yan banza (Adamu, 2016:364). Gwamnatin Kano ta yi tir da wannan hali sannan ta qarawa hukumar tace fina-finan Hausa qarfi, tare da xaukar mataki na korar duk wata ‘yar fim da aka kamata da laifi kwatankwacin wannan. Malaman addini su ma ba a bar su a baya ba, domin sun nuna mana a cikin suratun Nur (24:31) inda Ubangiji ya yi hani ga mata da nuna tsaraici ko kyansu, ya dace ne mata su rufe jikinsu sai dai ko ga mazajensu ila iyayensu da ko ‘yan uwansu na jini ne za su iya ganin jikin su.

2.20 Kammalawa

A taqaice, wannan babin an yi sharhi ne a kan ma’anar al’ada da rabe-rabenta, sannan an kawo fasalin al’adun Hausawa da kuma tarihin al’ummar Hausawa ganin a kansu aka gina aikin. Babin ya kawo ma’anar fim da ire-irensa da yadda ake shirya fim. Har ila yau, a cikin babin an kawo hanyoyin nazarin fina-finan Hausa tare da bayanin kashe-kashensu. An kuma yi bitar fim da Hausa da kuma fim cikin Hausa,tare da kawo siffofinsu da waiwayen fim a matsayin rukunin wasan kwaikawayo. An kuma tattauna a kan bambancin da ke tsakanin fim da wasan kwaikawayo, an kuma kalli fim a matsayin adabi da yake taskace al’ada da harshe da xabi’a. A qarshe an yi waiwayen ayyukan manazarta da dama, inda suka bar wani givi da ya shafi rashin iya tantance matsayin fina-finan Hausa ko kuma fina-finai da Hausa ga al’ummar Hausawa, musamman idan aka duba yadda baqin al’adun na kusa da na nesa suke mugun tasirin a cikin fina-finan Hausa. Sannan yawancin masu binciken sun fi ba da fifiko ne a bisa fito da tasirin al’adun Turawa ko na Indiyawa a fina-finan Hausa kawai, an manta da al’adun maqwabtan Hausawa irin su Turawa da Indiyawa da Sinawa da Nufawa da Gbagyi da Kanuri da Fulani da Ibo suna nan jibge a cikin fina-finan Hausa. Abin al’ajabi, shi

ne ba a duba su ba, don haka ne ake ta yin artabu a kan shin fina-finan nan na Hausa ne ko kuwa fina-finai ne dai da ake yin su da harshen Hausa. Don haka ga fili ga mai doki ga sauran manazarta. Za a yi amfani da xab'iun 'yan wasa ne domin a san yadda za a tantance fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa.

BABI NA UKU

HANYOYIN BINCIKE

5.0 Gabatarwa

A babin da ya gabata,wato babi na biyu, an yi bitar ayyukan masana da suka yi aikimasu alaqa na kusa da na nesa da wannan aikin, a bisa batutuwa mabambanta masu alaqa na kusa da kuma na nesa da wannan aiki. Shi kuma wannan babin, zai yi magana ne a kan hanyoyin da aka be wajen gudanar wannan bincike. An kasa wannan babi zuwa kashi biyu, koson kuwa su ne hanyoyi da aka yi amfani da su wajen tattara bayanai. Wato ginshiqan hanyoyi da kuma

sauran hanyoyi, an kuma yi sharhin tambayoyin bincike na wannan aikin tare da sharhin hira da aka yi da masana da masu ruwa da tsaqi a harkar fina-finan Hausa.

3.1 Hanyoyin Tattara Bayanai

Hanyoyin da aka bi wajen tattara bayanai kuwa sun haxa da ginshiqan hanyoyi da kuma sauran hanyoyi. An dogara ne a kan hanyoyi daban-daban wajen nema, da kuma tattara bayanai, don samun hujjojin dogaro na aikin. An bi hanyoyin ne domin a tara bayanai masu inganci da sahihanci. Hanyoyin tattara bayanai da mai bincike ya yi amfani da su sun haxa da:

3.2 Ginshiqan Hanyoyi

Ginshiqan hanyoyi, a nan, an fara dabuga tambayoyi da kuma rarraba su ga masana harkar fina-finan Hausa domin a cika su a garuruwan Kano da Zariya da Katsina, a matsayin zavavvun garuruwa da suke wakiltar qasar Hausa a cikin wannan aiki. An yi hira da tattaunawa da Malamai a fagen nazarin fina-finai da daraktoci da furodusoshi da ‘yan wasan fim na Hausa da kuma ‘yan kallo. An kuma yi rangadin gidajen talabijin masu zaman kansu, wato Arewa Talabijin (Arewa 24) da yake Kano da kuma na Tauraruwa da ke Kaduna. Wannan bincike ya yi amfani da wallafaffun littattafai da kuma kundayen neman digiri a fannin Hausa da waxanda aka yi su a kan nazari fina-finai a Inglishi na Jami’o’i a matakan

digirin qoli da na digiri na Biyu. An kuma fayyace adadin fina-finan da aka yi nazarin su tare da qididdige mizanin awo na amsoshin tambayoyin da aka rarraba, ta yin sharhin kowacce tambaya gwargwadon amsarta. Wato sharhin tambayoyin bincike da aka rabawa masana da masu ruwa da tsaki a harkar fina-finan Hausa.

Daga cikin hanyoyin da aka bi domin tattaro bayanai sun haxa da hira da malamai a fagen nazarin fim da ziyarar garuruwan qasar Hausa da ziyarar wasu jami'o'in Nijeriya da tattaunawa da masu harkar fina-finai musamman 'yan wasa da daraktoci da furodusoshi da kuma 'yan kallo. Sannan an buga tambayoyi a takarda waxanda aka rarrabawa malamai suka cike guraben.

3.2.1 Ziyarar Garuruwan Qasar Hausa

An kai ziyara jihohi daban-daban, wato garuruwan da ake shirya fina-finan Hausa, ana kuma sayar da su tare da samun ximbin masu sha'awar kallon fina-finan . Babu shakka, Kano na daga cikin garuruwan da suka yi fice wajen shiryawa da xaukar nauyi da tallatar da fina-finan Hausa. Kuma daga Kano fina-finan Hausa sukan tashi zuwa qasashen waje, daga Kano akan xauki fim zuwa qasar Nijar, da jihohin Arewa maso gabas da na kudanci kamar Legas (Hira da Umar mai Jalingo). An kai ziyayara kasuwar qofar Wambai da Dandalin Malam Qato *Squar*e da ke Kano, an kuma sami damar tattaunawa da masu shirya fina-finai da wasu 'yan wasan fim da furodusoshi da daraktoci da kuma 'yan kasuwar fim masu sayar da shi. Haka ta

kasance a garin Kaduna, an kai ziyara ne matattarar ‘yan kasuwar fina-finan Hausa da ofisoshin masu shirya fina-finan da ke unguwar Kawo, da na kan titin *Park* da ke nan garin Zariya. A garin Katsina kuwa an kai ziyara ne matattarar ‘yankasuwa fina-finan Hausa da ofisoshin masu shirya fina-finan da ake kira *Rex* silima. A waxannan garuruwa ne aka yi nasarar sayo fayafayen *CD* waxanda aka yi amfani da su a babi na huxu.

3.2.2 Rubutattun Tambayoyi Da Dabarun Tsattsafe su

An tsara tambayoyi guda talatin, tambayoyin an yi su a fasalin yadda mai bayar da amsa zai iya yin bayani a kan kowacce tambaya da aka yi masa, ko kuma a canki ee, ko aa ko babu kuma babu amsa. Tambayoyin nan an yi su ne musamman ga masana harkar fina-finan Hausa da ke jami’o’i, da kwaleji- kwaleji da makarantun fasaha da na sharar fegen shiga Jami’a. An rarraba tambayoyin zuwa Jami’ar Bayero, Kano da Jami’ar Ahmadu Bello, Zaria da Jami’ar Jihar Katsina da Jami’ar Jihar Kaduna, da sauran makarantun gaba da sakandare kamar yarda za a gani a gaba, kuma an ci nasarar raba tambayoyin guda xari, bayan wani lokaci aka sake fita domin karvo su, amma sai dai ba duka suka dawo hannu ba, guda saba’in da xaya (71) aka samu suka dawo.

Irin wannan hanyar rarraba tambayoyi da karvarsu ake kira da *Central Limited Theorem* wato tsarawa da rarraba tambayoyi da karvarsu bisa mizanin awo bisa xari bisa xari tare da la’akari da yawaitar faruwar abu na (*Frequency*) da wannan tsarin aka yi amfani wajen tattaro bayanai na bugaggun tambayoyi da aka rabar.An kuma raba su ga mata da kuma maza, waxanda suka

tasamma shekara ashirin da biyar zuwa sama. Sunayen makarantu da aka rarrabatambayoyin bincike da adadi sune:

S/N	SUNAN MAKARANTA	MATA	MAZA	JUMLA
1.	Ahmadu Bello Univ**e**rsity, Zaria	05	05	10
2.	Federal College of Education, Kano	04	04	08
3.	Aminu Kano College of Legal Studie	08	07	15
4.	College of Arts and Science, Kano	06	04	10
5.	Umaru Musa Uni**v**ersity, Katsina	04	02	06
6.	Nuhu Bamalli Polytechnic	03	02	05
7.	Amir Shehu Idris College, Zariya	03	02	05
8.	Federal College of Education, Zaria	03	02	05
9.	Bayero Uni**v**ersity, Kano	04	03	07
	40%	**31%**	**71%/100%**	

3.2.3 Tattaunawa Da Masana

Tun lokacin da aka xora xambar wannan bincike a kan wannan batu, aka fara tuntuvar masana waxanda suka yi fice a zamaninsu a sha'anin nazarin wasan kwaikwayon na fina-finai, ba don komai ba, sai domin neman haske da bayanai da shawarwari, kuma domin a xora mai bincike a kan hanya madaidaiciya maras gargada. Fitattun masana a harkar wasan kwaikwayo da na adabin suna da yawa, sai dai mai bincike ya ci moriyar tattaunawa da wasu Malamai da suke Jami'ar Ahmadu Bello Zaria da Jami'ar Bayero da ke Kano da Jami'ar jihar Kaduna. Waxanda aka tattauna da su a lokuta daban-daban a kan abubuwan da suka shafi wasan kwaikwayo na fim. Waxannan masana kuwa su ne: Farfesa Balarabe Abdullahi na sashen Harsunan Afirka da Al'adun, Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya. Shi ya ce fina-finan Hausa

wani fanni ne na adabin zamani, domin tushensu daga wasan kwaikwayo na talabijin ne da silima da majigi, da tafiya ta yi tafiya suka sami ‘yancin kansu saboda ci gaba da aka samu a masana’arta inda aka fara samar da fina-finai a cikin kaset- kaset da faifan *cd cd.* fina-finan ana gina su a bisa jigo daban-daban na al’amuran da suka shafi rayuwar al’ummar Hausawa. Don haka, za a iya nazarin su ta fagen nazarin dabi ko harshe ko kuma al’adu.

Shi kuwa Dr. Chamo na Sashen Kimiyar Harsuna Jami’ar Bayero, Kano ya fito da wani tsari ne da yake ganin za iya nazarin wannan batu. Yana ganin ba za a iya tantance fina-finan Hausa ta sanin matsayinsu, wato wai shin na Hausa ne ko kuwa fina-finai ne da Hausa? Har sai dai in za a yi nazarinsu ta fanin yanayin yadda ake aiwatar da tsarin zamantakewar Hausawa a cikin fina-finan Hausan, shin tsarin na haqiqa ne ko kuwa na je ka na yi ka? Misali su ne xabi’ar girmamawa da kara da kawaici, shin hotunansu suna haskaka tsarin rayuwar Bahaushe a fina-finan Hausa? Sannan an san Bahaushe yana da ladabi da biyayya da kyakkyawar tsarin makwabtaka da taimakekeniya da kuma sanin yadda zai yi hulxa da na gaba da shi. Misali, zamantakewa tsakanin xa da uba ko tsakain miji da mata ko tsakanin saraki da talaka ko tsakanin malami da almajiri ko tsakanin surukai, yaya ake nuna hoton rayuwar Bahaushe a cikin fina-finai Hausa? Shin suna bisa tsari ko kuwa sun bauxe hanya? Sai a bincika a gano, da su za ayi amfani a matsayin ginshqai na tantancefina-finan Hausa ko kuma fina-finai da Hausa?

Dr Aliyu Isa Sulaiman na Jami’ar Jihar Kaduna, shi kuma sai yake ganin ya kamata a fara fito da wasu dirkoki ko mizani da ya kamata a bi domin a iya tantance fina-finan Hausa da fina-

finai da Hausa. fina-finan da Hausa sune fina-finan da ake fassara su daga Indiyanci zuwa Hausa. Rungumar waxannan al'adu sun haifar da babbar illa ga Bahaushe ta fuskoki da dama. Da farko dai rungumar tsarin waqoqin fina-finan Indiyawa sun sa an yi watsi da namu na gargajiya waxanda suke hanyar vacewa daga doran qasa. Haka kuma, raye-raye da waqe-waqe na aro suna xauke da nuna tsiraici da xabi'u marasa kyau.

Ta wata fuskar kuwa, akwai ra'ayoyi da bayanai na mutane waxanda suke gabatarwa domin nuna cewa akwai fina-finan Hausa. Wasu daga ciki suna magana ne a kan fina-finan da suke xauke da tsari irin na gargajiya, ga wasu kuwa fina-finan da aka samu tun farkon vullowar fim a qasar Hausa su suka fi cancanta da a kira su da fina-finan Hausa. Waxannan bayanai ko ra'ayoyi mabambanta ba su bayyana wata kafa ta musamman wadda za a iya amfani da ita ba wajen tantance fina-finan Hausa. Sakamakon haka ne, wannan bincike ya yi hovvasa na ganin an tantance su, domin a san wane fim ne na Hausa, sannan wane fim ne aka yi shi da Hausa?

Shaihunan Malamai Abdallah Uba da Haruna Aminu sun ba da shawarwari da bayanai waxanda suka taimaka wa wannan aiki don ganin an inganta shi. Sun ce ya dace a fitar da wani mizani da na awo da za a iya gane fim na Hausa da kuma fina-finai da Hausa.

3.2.4 Ganawa da Ma'abota Fim

A ganawar da aka yi da masu ruwa da tsaki a harkar, sun taimaka wajen gano wasu bayanai waxanda suka tayarda komaxar wannan babi. Hira da su ta sa an sami ra'ayoyi mabambanta

cewa akwai fina-finai cikin Hausa, sannan akwai kuma fina-finai da Hausa. Hira da tattaunawa da ‘yan wasan fim na xaya daga cikin hanyar da aka bi wajen samun wasu bayanai masu amfani ga wannan bincike. Lokacin da ake gudanar da wannan tattaunawa an xauka ne a na’urar naxar bayanai wato kaset. Bayanan da suka bayar ya shafi abubuwa ne a kan wasan kwaikwayo na fim da gagarumar taimako da da ‘yan fim sukan taka a fage, da tarihin shigar su fim da gudummawar fim a cikin al’ummar Hausawa da dalilan da sukan jawo are-aren al’adun wasu al’ummomi makwabtan Hausawa zuwa cikin fina-finan Hausa waxanda yana daga cikin sauye-sauyen siffa da yanaye-yanayen fina-fina a cikin wannan zamani, wanda wasunsu sun savawa tadojin Bahaushe.

Shirya fim harkace tamkar zaman iyali, wato tun daga kan ‘yan wasa zuwa kan furodusoshi da daraktoci da ‘yan kasuwa waxanda sukan yi aiki tare. Wato ba yarda da zaman ‘yan marina ba, dole wannan na buqatar wancan, shi ya sa bincike ya haxa su gaba xaya a matsayin ma’abota harkar shirya fina-finan Hausa aka gana da su, domin a ji su kuma me nene ra’ayinsu a kan wannan batu?

Da farko dagacikin masu shirya fina-finan , akwai masu ra’ayin cewa fina-finan Hausa na Hausa ne, wato hujjarsu a nan itace, duk wani fim in dai an yi shi da harshen Hausa, kuma ana nuna wasu hotuna na al’adun Hausawa da xabi’unsu, to, shi kam wannan fim xin na Hausa ne. Don haka irin waxannan fina-finai da suka faxo cikin wannan rukuni sukan yi kwaikwayon abubuwan a bisa al’adun Hausawa, domin su isar da saqon da fim yake xauke ko ta halin qaqa, kokuma domin a sami biyan buqata na sayar da fim xin a sami kuxi kawai.

Wasu suna ganin fina-finan Hausa ba na Hausawa ba ne, domin ba Hausawa ne zalla suke aiwatar da shi ba, ana yi ne, ana gaurayawa da waxanda ba Hausawa ba waxanda suke zauna qasar Hausa. A taqaice masu wannan ra'ayi cewa fina-finan Hausa ba na Hausa ba ne sun yi tarayya akan abubuwa kamar haka:

1. Ana qoqarin fito da al'adun Hausawa a wasu fina-finan Hausa ba duka ba.
2. Mafi yawan masu yin fim xin ba Hausawa ba ne.
3. Fim xin Hausa da harshen Hausa ake yinsa kuma ake xabbaqa shi, duk da cewar ana yi wa harshen karan tsaye.

Amma wasu masu ra'ayin fina-finan Hausa na Hausa ne suna ganin cewa fina-finai irin su *Sangaya da Allura da Zare da Zarge da Linzami da Wuta* duka suna wakiltar al'adu da xabi'un Hausawa tsantsa, Da dama 'yan kallon fina-finan Hausa da Hausawa ne.

Kuma ko da kiran sunan fim xin, ka ji an ce Hausa. Wato an yi masa linzamin shi ne fim xin Hausa.

Duk da wannan, iqirari da masu ra'in cewa fina-finan Hausa na Hausa ne, su ma sun ce fina-finan Hausa suna nuna xabi'u da al'adun Hausawa, amma kuma duk da haka juyin duniya da aka samu ya sa a yanzu suna sauya akalarsu zuwa game duniya (*globalization*) suna yin amfani da yadda zamani yake tafiya suna shiryafina-finan Hausa". Kamar kwaikwayon al'adun Turawa da Indiyawa.

Sun qara da cewa tabbas fina-finan Hausa ne, sai dai akwai aron gurvatattun al'adu waxanda masu yin fina-finan suke amfani da su. Misali, raye-rayen Indiya da waqe-waqe da kuma soyayyar zamani a cikin fina-finan Hausa. Bugu da qari, wasu na ganifina-finan Hausa na Hausawa ne, domin Hausawan suka fara su don kawar da qishirwar kallo da take damunsu, musamman idan aka yi waiwaye zuwa ga irin fina-finan Hausa na farko za a tabbatar da hakan. Kenan, wannan ra'ayi yana nufin fina-finan Hausa da aka fara yi a farko-farko da daman su suna wakiltar xabi'u da al'adun Hausawa ne, idan aka kuma kwatanta su da waxanda ake yi na baya-bayan nan, za a iya cewa su kam sun yi hannun riga fina-finna farko.

Akasari masu wannan ra'in cewe fina-finan Hausa bana Hausa ba ne, suna ganin mafi yawancin jaruman "yan fim xin Hausa,ba Hausawa ba ne, hujjar su ita ce: dangane da yanayi na sa sutura da ladubban magana (harshen 'yan fim) da alkunya ba sa tafiya daidai da yanayin aiwatarwa bisa tsari na yanayin zamantakewarHausawa. Wato ana kwaikwayon al'adun Indiyawa da Turawa ana sanya su cikin fina-finanHausa har ma da na wasu qabilu maqwabtan Hausawa irin su Yarbawa da Inyamurai. A wata hira da aka yi da Furudosa kuma xan fim Muktar S. S. Zaria, ya nuna bayan tafiya ta fara nisa a shekarar 1999 zuwa yanzu (2018) akwai ximbin sauye-sauye a harkar shiryawa da samar da fina-finan Hausa, wanda tasirin zamani da caquxa da wasu al'umma da Hausawa suka yi da su ya yi tasiri a tafiyar harkar fina-finan Hausa. Don haka ake ganin fina-finan Hausa wasu bas u da asali, suna dai juyar da al'adun wasu qabilu ne zuwa fina-finai da Hausa, wannan shi ake kira wanki da xoraya a fina-finan Hausar. (Sulaiman, 2015).

Wasu kuma gani suke yi fina-finan ba sa kare martaba da al'adun Bahaushe yadda ya kamata, idan aka kwatanta su da na na kudancin Nijeriya, sun ce idan aka kalli fina-finai irin su *Sarauniyar Zazzau* da *Bayajidda* za a ga asalin labarin Bahaushen labari ne, kuma fim xin yana nuna muhallin qasar Hausa da kuma Hausawa. Haka zalika, waxanda suka taka rawa a wasan 'yan wasan kusan dukkansu Hausawa ne 'yan asalin qasar Hausa an yi amfani da suturar Bahaushe da harshen Hausa da muhallin Hausa da zubi irin na Hausa.

Wasu kuma suna ganin ai fina-finan Hausa ba na Hausa ba ne, domin sun savatadojin Hausa. Wataqila wannan hujja ba ta rasa nasaba da cewar shi Bahaushe an san shi da al'kunya da ladabi da girmama na gaba, sannan uwa uba ba ya biye ma duk wani abu da zai savawa addininsa cikin al'umma tasa. Don haka, ake ganin fina-finan suna suka tara, domin wasu ba sa haska al'adu da xabi'u na Bahaushe, sai dai suna amfani da harshen Hausa wajen isar da saqo, ta yadda xan kallo zai ji, ya gani, ya nishaxantu, don haka, ba su damu da shigo da jigon adddini ba. A qarshe, masu wannan ra'ayin fina-finan Hausa ba na Hausa ba ne, suna masu cewa fina-finan ba sa tafiya bisa haqiqanin al'adun da xabi'un Hausawa. Sun fi ba da hankali wajen qwaiqwayon wasan yanayin tsarin rayuwar maqwabtan Hausawa na kusa da na nesa. A farkon fara fina-finan Hausa maza ne aka fi ba wa fifiko wajen jarunta da kuma aiwatarwa. Amma a yanzu an ajiye maza, an fi gina fina-finanea kan mata a kuma qare da mata (Soyayya). A bisa wannan hujja, Chamo (2004) da Adamu (2012) suka ce fina-finan Hausa suna amsa suna na Hausa ne kawai. Wato, an bar wasu qabilu sun yi tasiri a cikin masu aiwatar da fina-finan Hausa musamman mata, wanda sun yi tasiri al'amura shiryawa da samar da fina-finan Hausa.Kaxan daga cikin matan da aka gano tana iya yiwuwa ba Hausawa ba ne daga xan abin da aka ji kuma aka gani a cikin al'umma da aka yi bincikea kan su, kuma suna taka gagarumar taimako a cikin harkar fina-finan Hausa su ne:

Mata :

Nafisa Abdullahi= Birom

Zainab Baka= Nupe

Aisha Humaira =Bafaranshiya/ Babur

Halima Atete = Babarbariya

Hajara Dumvaru= Igbo

Rahama Sadau = Ibgira

Fati Macijiya = Gwari

Fati Aliyu S.U= Banufiya

Ruqayya Usman =Nupe

Muhibbatu Abdulsalam =Bayarabiya

Aina'u Ade = Bayarabiya

Hadiza Kabara = Kukuruku

Kubra Dako = Nupe/ Bagwariya

Mansura Isa =Bayarabiya

Hafsat Shehu = Kukuruku/

Hadiza Gabon = Fulani

Carmen Maccain (Talatu)= Baturiyar Amirka

Rahama Hassan = Gwari

Fatima Abdulkadir =Gwari

Fati Washa = Kukuruku/ Mada

Fati Shu'uma = Fulani

Safiya Musa = Babur/Faransa

Hafsat Idris= Bayarabiya

Fati Muhammed= Fulani

Fati Abubakar = Shuwa Arab

Hauwa Waraka = Fulani

Samira Ahmad = Bayarabiya

Maryam Sparkling = Bayarabiya

Zainab Abdullahi Raji = Bayarabiya
Zainab Ishola = Bayarabiya

Bayan jerin waxannan mata da suke fitowa a juruman mata a fina-finan Hausa kuma suma taka muhummiyar rawa, akwai wasu mazan da aka gano su ma jiga-jigan tafiyar ne, wasunsu a matsayin furodusoshi ko kuma daraktoci, ko kuma jarumai, waxanda fim ba ya samuwa sai da hannunsu dumu-dumu, don haka, suna takawa muhimmiyar rawa wajen samarwa da shirya fina-finan Hausa a yau, su ne:

Maza:

I.K Moore = Inyamuri = Furodusa
Sadiq Mafiya = Inyamuri = Darakta/Jarumi
Sani Musa Danja = Bayarabe =Darakta/ Jarumi
Ali Nuhu= Waja=Darakta/Jarumi
Taye Hassan Giggs = Bayarebe = Darakta/ Furodusa
Mr Tunji A.= Bayarabe= Furodusa

Wani Malami a Jami'ar Bayero Farfesa Yusufu Adamu da Dr Murtala Garba Yakasai da Ahmad Al'Kanawy da Yakubu Lere suna masu tabbatar da cewa qabilu waxanda ba Hausawa ba, su ne suka yi kaka gida a wannan harka na fina-finan Hausa. Shi ma Farfesa Uba Adamu ya goyi bayan wannan ra'ayi inda ya ce da dama daga cikin masu yin fina-finan Hausa ba Hausawa ba ne. In kuma Hausawa ne, to akwai tasirin qananan qabilu a kansu musamman 'yan Jos da kudancin Kaduna da Legas. Ya ce an fi mayar da hankali ko qarfi ga harshe a maimakon al'adu da xabi'un Hausawan a cikin fina-finan . Misali fim xin *Mutum da Aljani* na *Nollywood*, a Hausa yanayin Aljana ai fara ce sal, ba ja ba, ba kuma baqa ba. Amma, sai a cikin fim xin an nuna aljani yana sanye da jajayen kaya masu xauke da kaloli da baqi-baqi a

maimakon ya fito fari fat. Hakanan fim xin *Hindu* an nuna Sarki yana shawara da matarsa, a tunani irin na Bahaushe ina aka tava jin Sarki da mata tasa sun zauna bainar jama'a a cikin fada suna shawara? An kuma nuna fadar Sarki ba kowa, ba fadawan Sarki, sai dai Sarkin zaune shi kaxai. Irin waxannan fina-finaan xauko su ne, amma sai an yi bincike irin wannan sannan za a iya tantance su a ga daga ina suke, sannan a wani gurbi za a sanya su?

An sami ganawa da wasu masu shirya fina-finan Hausa da masu bayar da umarni da kuma wasu 'yan fim xin, tare da wasu 'yan kallo. Tattaunawa da aka yi da su yana daga wani sashe na samun wadataccen bayanai da suka taimaka wajen gina babi na huxu. Tattaunawar ta yi tasiri domin ta taimaka wajen fayyace mana wasu fina-finai da suke na Hausa ne da kuma waxanda za mu iya cewa fim ne da Hausa, waxanda ba za su iya amsa sunan fim xin Hausa ba. Kazalika, an sami karvar sunayen fina-finan da aka yi amfani da su a babi na huxu, a kalla guda xari.

3.2.4.1 Hira Da Furodusoshi

Da farko ya kamata a san wane ne furodusa a harkar fim. Shi ne wani babban jami'i ko a ce madugu uban tafiya a yayin shirya fim. Iyantama(2011:30) ya ba da ma'anar furodusa da mai shiryawa: haqqinsa ne ya samar da qwararun ma'aikata ga 'yan fim da wadatattun kuxi na aiki, da muhalli da labaria da duk wani abu da ya shafi fim.

Yawancin furodusoshin da aka yi hira da su, sun nuna cewar sai da suka fara wasu ‘yan ayyukan fim daga tushe kafin nan suka qware, wato riqe matsayin jami’i mai kula da kaya ko yin kwalliya ko kuma yi wa shirin wata hidima idan ana xaukar fim, bayan an yi horoda ya dace har zuwa matakin fara shirya fim. An gano cewar ba Hausawa ne kawai suke tafiyar da sha’anin shirya fina-finan Hausa da kuma samar da shi ba. Don haka, baya ga manyan furodusoshi da muke da su Hausawa irin su Sani Rambo da Tahir I. Tahir da Naziru Dan Hajiya da Abubakar Bashir Mai Shadda da Umar Mai Jalingo, akwai furodusoshi waxanda ba Hauswa ba kuma suna zuba kuxi sosai a harkar shirya fim da samar da shi. Wani babban Furodusa a Kano Inyamuri wanda ya fi kowa zuba jari a harkar fina-finan Hausa shi ne Mr I. K. Moore. Sannan akwai su Mr Tunji. Don haka, masana’artar fina-finan Hausa tana da haxakar mutane daban-daban. A qalla tun daga fara samar da labari, zuwa fitar da shi, zuwa lokeshan, zuwa kastin, zuwa ma’aikatan fim xin a aikace a nan sai a tarar fim ya zama abin qaruwa har da gwamnati, hukumar tacewa ta qasa da kuma jihohi. Duk abin da ake yi a cikin fim zamantakewa ta kawo shi, misali fina-finan *Hollywood da na Bollywood* suna qoqarin kwaikwayon al’adun junansu. Haka ma, ‘yan *Nollywood da Kannywood* su ma suna yin are-aren a fagen aiwatarwa a tsakaninsu.

Sun kawo wasu nau’o’in yanayin zamantakewar da ake samunsu a tsakanin al’ummar wanda akan nuna su a cikin fina-finan Hausa , amma sun nuna babbar matsalar, rashin nuna yanayin tsarin zamanatakewar Hausawa xari bisa xari ba. Domin kowanne furodusa idan ya tashi gina fim xinsa sai ya yi qoqarin cusa xabi’arsa a cikin fim xinsa a bisa yanayin tsarin zamantakewa Hausawa, to sai ya nemi ta kai da fim xin in an gama, ba lallai a samu sayar da shi a kasuwa ba. Sai dai a wani abu da zai burge ‘yan kallo ta yadda zai samu biya buqatarsa fim ya samu

kasuwa kawai. Sun nuna ana iya gane Bahaushen fim ta nazarin furucin xan wasa, idan ance ana magana a kan bori fatanmu a tafi a kai kar a bauxe a shigo da kalamai na daban waxanda ba sa bisa tsarin borin a cikin fim. Haka zalika sutura na daga cikin abubuwan da ake dubuwa, misali an ce wannan fim xin Hausa ne kuma an zo an ga ana shigar suturar Turawa ko na Larabawa, a nan an kaucewa tsari. Muhalli na daga cikin abubuwan da aka duba wajen iya tantance Bahaushen labari, sannan akwai kuma duba tsarin qullin labara shin asalinsana Bahaushe ne ko kuwa wanki da xauraya ne.

3.2.4.2 Hira da Daraktoci

Darakta shi ne jami'i mai bayar da umarni a yayinda ake shirya fim. Iyantama (2011) ya qara da cewa shi ne wanda yakan zauna ya zavo mutanen da za su taka rawa cikin fim, tare da haxin gwiwar furodusa. Ya qara da cewa mai bayar da umarni, mutum ne mai amfani da ilimi cikin siyasa da nutsuwa tare da hangen nesa da iya tsari na sarrafa abin da ke rubuce cikin yarda don cimma abin da ya sa a gaba bisa cika alqawari da haquri. Shi ne wanda yake da alhakin sarrafa hikimarsa zuwa hoto mai motsi da sauti da kuma magana, tare da taimakon mai xaukar hoto.

A qoqarin da ake don samun bayanai ta yadda za a iya tantance fina-finan Hausa ko kuma fim da Hausa, daraktocin da aka yi hira da su, sun yi ittifaqi cewa: a duk lokacin da aka ce fim na Hausa ya shafi kafatanin duka abubuwan da ake aiwatarwa ne na mabambanta kamfanonin fina-finan Hausa. A maganar harshe da Hausa ake yi, sai dai akwai surke na baqin al'adu

daban-daban, ko kuma idan ka kalli wani fim xin tun daga farko har qarshen sa, za ka tarar sun yi hanun riga dangane da abin da ake nunawa tun daga farkon sa har qarshensa. Amma in an magana da fin na Hausa, ana nufin fim xin da aka yi shi kamo tun daga zantuttukan da ‘yanwasa ke yi zuwa muhalli zuwa labari zuwa kostum ya kamata ya nuna zallar al’adun Bahaushe, ta yadda ba za su yi hannun riga da xabi’a ko al’adun Hausawa ba. Amma, yanzu zamani ya zo sai kawai a xauki wani fim na Indiya, a juya shi ko canza shi,zuwa cikin labari da Hausa. Matsalar a nan ita ce, akwai wasu al’adu da labarin Indiyan kan zo da shi, a maimakon shi Furodusa ya sauya shi ta yadda zai xauki siffa da yanayin al’adar Bahaushe, sai kawai a bar shi ya tafi a hakan. Ka ga a nan, ba fa zai amsa sunansa na fim xin Hausa ba, domin tun a qullin labarin, an sami tasgaro, ba Bahaushen labari ba ne, labarin Indiya ne kawai aka juya shi zuwa Hausa. Labarin za a wanke a xauraye shi a dawo mana da shi zuwa harshen Hausa. Idan aka kalli fim irin wannan za a ce an dai yi shi da harshen Hausa, amma qunshiyar labarin ba shi da wata alaqa da al’ummar Hausawa. Misali, a wasu fina-finan za a nuna yadda yara suke gudanar da yanayin zamantakewa da iyayensu, wato Bahaushe mutum ne mai kunya. Akwai wasu maganganu waxanda ba zai iya faxa a gaban iyayensa ba, amma irin fina-finan mu da ake yi yanzu sai ka ga xa yana taqaddama da ubansa ko mahaifiyarsa. Misali, fim xin kamfanin KEFD wanda ake kira *Hallaci***,** an nuna suturar ‘yar wasan fim xin ya sava wa shigar sutura irin ta Bahaushe ga shi kuma fim ne na Hausa.Amma duk da hakan, ana samun fina-fina Hausa da suke nuna tsantsar xabi’u da al’adun Hausawa, sai dai ba su kai yawan waxanda suke wa al’adun Hausawa karan tsaye ba. Yawancin mata ne da matasa suka fi kallon finan-finan Hausa, wataqila shi ya sa ake ta qoqorin shigo da wasu al’adu makwabtan Hausawa zuwa cikin fina-finan Hausa. Misali, idan yaro yana zaune a kan kujera, sai wani baqo ko babba ya shigo gidansu, to, zai yi maza ya tashi ya ba wa baqon kujerar ya

zauna, shi kuma ya koma qasa ya zauna, amma fina-finan mu da ake yi yanzu ba su cika nuna hakan ba. Misali, fim xin *Gwaska* an nuna yadda wani mutum ya dinga zuwa yana amfani da qarfi yana qwatan dukiyar mutane yana bai wa waxanda ba su da shi. Kwatakwata, wannan bai cikin xabi'u da al'adar Bahaushe, har da za iya cewa fim xin Hausa ne yake nuna irin wanann tsarin zamantakewar. Wadda har ta kai wasu a nan al'ummar suna irin wanann shigar Gwaska suna tsoratar da yara a makarantu wanda dole sai da gwamnati ta tashi tsaye aka zo aka hana, kuma a cikin fim xin Hausa aka shigo da wannan tsarin zuwa cikin al'ummar Hausawa. An ce fim xin Gwaskan ma na Indiya ne wato fim xin *Krish*, don haka an shigo da al'adar Indiyawa zuwa cikin fina-finan Hausa.

3.2.4.3 Hira da 'Yan Fim Ko Jarumai

Jama'ar gari sukan kira masu taka rawa a cikin fim da 'yan fim, amma Iyantama (2011) ya kira su da jarumai. Ya ce jarumi, wani irin mutum ne da ya yarjewa kansa cewa shi mai iya sauya kammani ne, kuma ya yarda komai aka ce ya zama zai iya zamaa filin dave ko a kyamara. Jarumi yakan kasance mai basira da hikima, domin ya isar da wata buqata ko saqo. Idan jarumi ya sauya kamanni yakan iya fito a siffar talaka, ko mahaukaci, ko mai kuxi, ko varawo, ko malami, ko likita, ko ko direban mota da sauran matsayi daban- daban da za iya takawa a cikin fim.

Da dama daga cikin 'yan fim da aka yi hira da su, sun nuna cewar sun fara shiga wannan harkar sana'ar fim ne daga wasan dave musamman mazansu. Amma, matan su kam dai sun yi wa sana'ar haye ne. An sami cakuxe-cakuxe na yanayin tsarin zubi da xaukar 'yan fim daga

wata nahiya zuwa wata zuwa cikin fina-finan Hausa, ko kuma mu ce xaukar ‘yan fim zuwa cikin fina-finan Hausa daga wannan gari zuwa waccan. Don haka, a qoqarin da ake nashayar da fina-finan Hausa qishirwar da take damunsu na rashin mata ‘yan fim da za su dinga taka rawa, shi ya sa aka dinga kareme-karemen nema da sanya duk wadda ta kawo kanta don taka rawa a cikin fina-finan Hausa. Ba a cika kula daga ina mutum ya fito ba, ko kuma a ce ina asalinsa, wasu ma ba a ma san daga inda suka fito ba. Buqatar maje hajji dai Salla, shi ne a dai samu a aiwatar da fim sannan a fitar da shi jama’a su kalla kawai shi ne burin xan wasa. Bai cika damuwa da kula da duk wani abu da zai kare martabar al’ada ko xabi’ar Bahaushe ba. Amma fa duk da haka, akan samu wasu fina-finan da suka yi qoqarin kare martaba da muradun al’adun Hausawa a fina-finan Hausan.

Wasu daga cikin ‘yan fim xin da aka tattauna da su, sun yarda da wasu daga cikin fina-finan Hausa ba na Hausa ba ne, ana dai yinsu ne da harshen Hausa. Hujjarsu ita ce, wasu labaran da akan gina fina-finan Hausa, ba sa bisa tsarin Bahaushen labari, sannan muhalli da sutura da harshen ‘yan fim duka ana yi musu karan tsaye. Amma, idan ana batun fina-finan Hausa za a so a ga an xora su bisa tsarin yanayin da sigar al’adun Hausawa. Sun ce abubuwan da suka sa su yi aro a fina-finan Hausa shi ne, wataqila ana so a ga wane mai xabi’a iri kaza a cikin fim, to a nan dole sai a sauya masa kamanni, sai an sabanta masa kaya irin na masu xabi’ar. Misali ana so a ga Tibi a cikin fim, sai a nemi wani mai kama da Tibi a horar da shi da yadda suke magana da halayarsu, in kuma an sami Tibi wanda yake jin Hausar to ta kwana gidan sauqi.

3.2.4.4 Hira da Masu Kallon Fina-finan Hausa

A yayin da ake gudanar da wannan bincike, an yi amfani da hanyar tattaunawa da kuma ganawa da wasu mutane masu sha'awar kallon fina-finan Hausa. Wannan hanyar ta buqaci mai bincike ya ziyarci gidajen kallo da wurare daban-daban da gidajen Talabijin masu zaman kansu da ake nuna wasan fim na Hausa. Kamar su gidajen Talabajin masu zaman kansu na Tauraruwa da kuma gidajen nuna fina-finan Hausa na cikin unguwanni da gari-gari, sukan sanya 'yan kuxi kamar naira 20 zuwa 50 domin shiga a yi kallon fim na Hausa. An tattauna da masu kallo da dama sun nuna, sukan koyi darussa daban-daban na harkokin rayuwar al'amuran Bahaushe. Sun ce wasan fim yana xauke da raha da ban dariya, wasu kuma sukan vata musu rai ko xaga hankalin mai kallo, sannan wasu na xauke da al'ajabi da al'adun Bahaushe na gargajiya wadda aka gada tun iyaye da kakkani. Amma, kuma wasu fina-finan suna xauke da baqin al'adun ne na Turawa da Larabawa da wasu al'ummomi maqwabtan Hausawa kamar Inyamurai da Yarbawa da Kanuri da Gwari da Fulani da sauransu. Wasu daga cikin waxanda aka tattauna da su suna ganin shigar baqin al'adun cikin fina-finan Hausa alama ce ta ci gaban harkar adabin fim. Domin duk al'ummar da ba ta aro, ba lallai ne ta mori ci gaba ta fusahar qirqira na rayuwarta ba, har ma da bunqasar arziqi. Sun ce hatta a fagen harshen, Hausa ta yalwatu da kalmomin Larabci, wadda hakan ta sa harshen Hausa ya zama sha-kundum ka jiyar harshe a nahiyar Afirka. To, idan aka kwatanta yadda ake shirya fina-finan Hausa a shekarun baya da dabarun aiwatarwa da sutura da fitilu da hoto da sauti, sai a ga yanzu an fi samun cigaba idan aka kwatanta da shekarar 25 baya. To, haka ma, abin yake, a harkar shirin fim sai an shigo da sababbin tsari da are-are na waje da na gida daga nan sai a ga jama'ar gari sun fara xokin son kallo tun kafin ya shiga kasuwa don a ga me fim ya zo da shi.

Amma, wasu na ganin *kowa ya bar gida, gida ya bar shi*. Don haka, a dai tsaya a tsohon tsarin shirya fim na dauri, wato, duk abin da za a nuna kar a shigo da baqin al'adu, don gudun kar a manta na baya.Wasu daga cikin waxanda aka gana da su sun ba da haxin kai dai dai gwargwado, wasu kuwa sun qi yarda su ambaci sunayensu. Wannan tattaunawar da aka yi da jama'a aka tattara aka adana a na'urar naxar magana domin nazarin bayanai dalla-dalla a babi na huxu.

3.3.1 Sauran Hanyoyi

Sauran hanyoyin da aka bi wajen tattaro bayanai na wanna aiki, sun haxa da ziyarar xakunan karatu a inda aka karanta kundaye da maqalu daban-daban masu alaqa ta kusa da ta nesa da wannan aiki. Sannan an kai ziyarar kafafen yaxa labarai na Arewa 24 da Tauraruwa talabijin, an yi zama na musamman don kallon fina-finan da aka tattaro domin a tattsafe su yadda ya kamata. A qarshe an kawo ra'in bincike.

3.3.1.1. Xakunan Karatu

Wata hanyar da aka bi mai inganci wajen tattaro bayanai na wannan bincike ita ce; yin amfani da wallafaffun littattafan karatu waxanda suka danganci wannan fanni na fina-finai waxanda aka wallafa a harshen Hausa, da kuma wasu harsuna. Haka kuma, an yi amfani da wasu fitattatun qamus na Turanci da na Hausa waxanda suka yi magana a kan harshe da adabi, suntaimaka wajen bayar da haske a kan ma'anar wasu kalmomi waxanda wannan bincike ya

yi amfani da su. Sannan su ma wallafaffun littattafai da aka yi amfani da su sun taimaka qwarai da gaske wajen sanya mai bincike kan hanya, ana iya ganinsu a manazartar aikin.

3.3.1.2 Kundayen Bincike da Muqalolin Qara Wa Juna Ilmi

Wannan bincke ya yi amfani da kundayen bincike da maqalun waxanda aka saba gabatarwa a taron qarawa juna sani akan adabi da fina-finai. An kuma duba wasu ayyukan masu kama da wannan bincike da aka rubuta ko aka buga a harshen Hausa da kuma wasu harsunan. Haqiqa, waxannan kundayen, da muqaloli an yi amfani da su wajen gudanar da wannan bincike saboda ganin cewa za su samar da hanyoyi ingantattu da madafa dauwamammiya wajen gudanar da wannan bincike. Waxannan kundaye da muqaloli, da qasidun, da mujallun da aka yi amfani da su, an tattarasu a qarshen aikin nan domin masu karatu su gani da kuma a samar masu da hanyoyin samun qarin bayanai.

3.3.1.3 Ziyarar Kafafen Yaxa Labarai

Har ila yau, a yayin gudanar da wannan bincike an yi amfani da hanyar kai ziyarce-ziyarce ga wasu fittatun gidajen talabijin domin tattara bayanai tare da neman wasu fina-finan wasan kwaikwayo. A lokacin kai ziyarce-ziyarcen, mai bincike ya je gidan talabijin na Arewa da ke Kano. Wannan kuwa, an yi shi ne saboda ganin cewa kusan al’amari xaya yake faruwa da sauran gidajen talabijin, amma da yake masu zaman kansu ne, ba mallakin gwamnati ba, sun fi raja’a ne a kan nuna fina-finan Hausa zalla ko yaushe, in aka kwatanta su da na gwamnati.

A waxannan gidajen talabijin ne kuma aka ziyarci sashen adana kayayyaki da fayafayen wasannin kwaikwayo.

3.3.1.4 Kallon Fina-finan Hausa

Wannan wata babbar hanya ce da aka bi aka tantance bayanai. An tattaro fina-finan guda Talatin (32) aka tantance fina-finan Hausa dakuma fian-finai da Hausa. Fina-finanda aka yi su daga shekarar 2000 zuwa 2017 wato shekara goma sha bakwai kenan. Duka fina-finan da aka yi su a tsakanin waxannan shekaru, wannan bincike yana lale marhaban da su.

An zauna, zaman dirshen inda aka kalli fina-finan , kuma an ci nasarar zazzaqulo wasu abubuwan waxanda za a iya kafa hujja da su kan cewar wannan fim na Hausa ne ko kuma ba na Hausa ba ne, amma an dai yi shi ne da Hausa. Don haka an rarraba fina-finan bisa tsarin batutuwan da ake son cimma buri. Kamar yadda aka karkasa su a cikin wannan babin.

3.3.1.5 Ra'in Bincike

Ra'in nazarin al'adun ul'umma (*Ethnograpy Theory*) qamusun kevavvun kalmomi ya fassara shi da ilimin tarihin qabila, wannan fassarar da qamusun kevavvun kalomomi ya yi,ta bambanta da na su Chamo (2012) da Qamusun Ingilishi (2007) da Bhadmus (2016) inda suka fassara shi, ra'in nazarin al'umma da al'adunsu. Hanya ce ta nazarin al'adun mutane. A nan, mai nazari zai xauki wani vangare na nazarin rayuwar al'umma ya yi nazarin wani sashe daga ciki. Wato, ma'ana a nan, ita ce ya wajaba mai nazari ya fita fage domin ganawa ko ya kai

ziyarar gani da ido domin a kauce wa son zuciya ko kuma son rai ta yadda za a iya ba da ainihin rahoton abin da yake gudana.

Asalin kalmar "*ethnography*" an samo ta ne daga harshen Girka. "*ethnos*" ma'ana kamfani daga baya kalmar ta juye ta koma "*nation*" wato jama'a mazauna babbar qasa guda. "*Graphy*" yana nufin fage na nazari. Don haka, wannan mazahaba ta fi ba da fifiko ne bisa hanyar nazarin al'adun al'ummomi da suke da daxaxxiyar alaqa a tarihance. *Ethnography* ingantacciyar taswira ce ko hoto da ke nuna wa mai nazari ko bincike yadda zai yi nazarin yanayin cuxanyar shige da fice na zamantakewar xabi'u da al'adu da halayya da imani da camfi da tasirin al'adun da harshe a tsakanin al'ummomi mabambanta ta yadda za a fito da inda suka haxa ko suka rarrabu a tsakaninsu.

An fara amfani da wannan hanyar nazari a qasar Turai da Ingila a cikin qarni na goma sha tara. Mazhabar ta bazu har zuwa qasar Amirka a cikin farko qarni na ashirin (20). Daga cikin masana da suka ba da gudummuwa wajen havaka wannan mazahaba sun haxa da: E.B. Tylor, (1833-1917) xan qasar Birtaniya ne, da kuma Morgan, (1818-1881). Haka kuma wasu Amerikawa sun yi amfani da wannan mazahaba yayin wani bincike da suka yi, a in da suka yi amfani da hanyar domin yin nazari a kan yanayin zamantakewar al'ummar qasar Turai da Amerika. Su ne qungiyar manazarta Amirikawa waxanda suka yi tunanin nazarin dangantakar al'ada daga cikin adabi. Wanda suka kira shi *the idea of cultural relativism to the literature*, sune; Fanz Boas (1958-1942) da Bromislaw (1858-1942) da Ruth Benedict da Margaret (1901-1987). Malinoski (1942), ya qara da cewa ya wajaba ga mai bincike da ke kan wannan

tafarki ya yi tattaki zuwa fagen da ake bincike domin a sami sanayya da kyakkyawan alaqa da al’ammar da ake nazarin al’adunsu. Malinowski (1942) ya yi amfani da wannan ra’i a aikace, inda ya tafi tsibirin *Trobriand* da ke gabashin qasar *Guinea*. Ya fara da koyon harshen mutanen, sannan ya zauna na xan lokaci. Wannan dabarar gudanar da bincike ta zama sananniyar hanya a cikin qarni na goma sha tara (19). Manazarta sun duqufa wajen nazarin tsarin yanayin zamantakewar al’umma da al’adunta musamman ta kallon tasirin zamananci a cikin al’adu. Har wa yau, a nan gida Nijeriya wani manazarci Chamo (2012) da ya xauki wannan ra’i ya sadar da shi wajen nazarin fina-finan Hausa.

A bisa tsarin wannan mazahaba a kan kula da wasu qa'idoji ko sifoffi wajen aiwatarwa:

- Mai nazari ya xauki wani nau’i guda na matsalar da ta haifar da bincike ya warware.

- Bin diddigin bincike daga tushe (primary source) don tattaro bayanai.

- A ba da fifiko wajen amfani da tushen bayani a maimakon amfani da dabarun gwajin hasashe.

- A tabbatar an tattauna da jama’a, musamman ta yadda za a gano yanayin tsari da walwalarsu a cikin al’ummarsu. Ba a cika son amfani da dabarar gudanarwa ta kimiyya ba, an fi so duk abubuwan da aka gano a tattauna su ne a zube.

Wannan hanya ko ra’i ta fi ba da fifiko ne a bisa tattauna al’adun al’umma. Manya da qananan al’ummu, ko don a kwatanta yanayin zamansu ko kuma a fito da nazarin yanayin rinjayar al’adun wata al’umma a kan wata masu zama tare.

- An so mai bincike ya shiga cikin al'ummar da ake bincike a kansu, a saki jiki a wataya da su. Musamman domin ganawa, da gani da yadda suke aiwatar da al'adunsu da rohoto ko xaukar hoto da hira da sauran abubuwan da za su taimakawa mai bincike wajen tattaro bayanai.

- Ya wajaba ga mai bincike ya kula da tunanin al'ummar da yake bincike a kansu dangane da al'adunsu. Ya ya imaninsu da tunanin su bisa yadda suke amfani da harshesu da sauran harkokin yau da gobe, kuma me aka gano dangane da hallayar su a tasu tunanin a bisa yadda suke tafiyar da ita?

3.4 Hanyoyin Tace Bayanai

An yi amfani da wasu dabaru da hanyoyi wajen tace bayanai da aka tattara, an fara da yin sharhin waxansu tambayoyi da aka rarrabawa masana fina-finan Hausa da suke a jami'o'i da kwaleji da suke qasar Hausa. Amsoshin da suka ba da an tace su kamar yadda za a gani nan gaba. Sannan an raba mizanin awo na tacewar zuwa kashi biyu, wato tacewar na bayan fage da na cikin fage.

3.4.1 Sharhin Tambayoyin Bincike

An yi sharhin kowace tambaya gwargwadon iya amsar da jama'a suka ba da, bisa yawa da kuma kaso mafi yawa da qaranci. An tantance kowace tambaya ta yin sharhin yawan abin da kowanne kaso ya samu, kamar haka:

Tambaya ta 1

Waxanne qabilu ne aka fi samun vurvushin al'adunsu a cikin fina-finan Hausa? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason waxanda suka zavi qabilun da aka fi samun vurvushin al'adunsu a cikin fina-finan Hausa. Sakamakon binciken na zube a Tebur na **3.4.1a** da Tebur **3.4.1a**

Tebur 3.4.1a: Qabilun qasashen waje da ake samun vurvushin al'adunsu a cikin Fina-finan Hausa

Lamba	**Qasashen Waje**	**Yawa**	**Kaso (%)**
1	Indiyawa	38	44.19
2	Turawa	35	40.7
3	Sinawa	3	3.49
4	Larabawa	8	9.3
5	Amerikawa	2	2.33
Jimla		**86**	**100**

A cikin Tebur 4.01a, ana iya ganin yawa da kason qabilun qasashen waje da aka fi samun vurvushin al'adunsu a cikin fina-finan Hausa. Idan aka duba za a ga, mutane 38 (44.19%)

cikin mutane 70 sunce an fi samun vurvushin al'adun turawa cikin fina-finan Hausa fiye da sauran qabilu. Mutane 35 (40.7%) kuma sunce an fi samun vurvushin al'adun Indiyawa. Kamar haka dai, za a ga cewa vurvushin al'adun Sinawa 3 (3.49%), Larabawa 8 (9.3%), da Amirikawa 2 (2.33%) bai kai yawan adadin na Indiyawa da Turawa ba.

Tebur 3.4.1b: Qabilun cikin gida da ake samun vurvushin al'adunsu a cikin fina-finan Hausa

Lamba	**Kabilun Gida**	**Yawa**	**Kaso (%)**
1	Igbo	14	17.72
2	Yoruba	22	27.85
3	Kanuri	4	5.06
4	Fulani	15	18.99
5	Gwari	3	3.8
6	Mutanen Jos	1	1.27
7	Nupe	1	1.27
Jimla		**79**	**100**

A cikin Tebur 3.6.1b za mu iya ganin, mutanen da suka amsa tambayoyi sun nuna cewa a cikin qabilun cikin gida da ake samun vurvushin al'adunsu a cikin fina-finan Hausa, Yarbawa suna da kashi mafi tsoka 22(27.85%). Qabilar Fulani da Igbo nada 15 (18.99%) da 14(17.72%) kowannensu. Vurvushin al'adun sauran qabilun kuma (Kanuri, Gwari, Mutanen Jos da kuma Nupe) ba su da wani tasiri a cikin fina-finan Hausa sosai.

Tambaya ta 2

Ga darajoji guda shida (6) a wace za ka iya xora fina-finan Hausa wajen agazawa tunanin Bahaushe da rayuwarsa ta zamantakewrasa a cikin al'umma tasa? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason waxanda suka zabi darajojin da za iya xora fina-finan Hausa wajen agazawa tunanin Bahaushe da rayuwarsa. Sakamakon binciken na zube a Tebur na **3.4.2**.

Tebur 3.4.2: Yawa da kaso na darajojin da za iya dora fina-finan Hausa wajen agazawa tunanin Bahaushe da rayuwarsa ta fanin zamantakewarsa a cikin al'umma tasa.

Lamba	**Daraja**	**Yawa**	**Kaso (%)**
1	A	5	8.2
2	B	6	9.84
3	C	30	49.18
4	D	13	21.31
5	E	2	3.28
6	F	5	8.2
Jimla		**61**	**100**

Idan aka kalli waxannan darajoji da idon basira, za a ga kaso na ajin C shi ne ya fi xaukar kaso mafi yawa na 30 (49.18%) wanda wannan yana nuna mana fina-finan Hausa suna tsaka-tsaki ne dangane da gudummuwarsu a fagen havaka al'adu da xabi'un Hausawa a cikin al'aumma, musamman a fagen inganta fasaha da yadda jama'a ke kallon fina-finan. Don haka, ko a mayar da hankali wajen ci gaba da riqe al'adu da za su daraja rayuwar Bahaushe ta yadda darajar fina-finan za su yi sama wataqila su kai darajar B ko A nan da zuwa wasu shekaru

kaxan masu zuwa. Ko kuma, in aka sakaci darajar ta su ta yiwo qasa wanwar su rasa tirmin daga tasu zuwa darajar D ko E.

Tambaya ta 3

Bayyana wasu hanyoyin da ka sani, waxanda za su inganta masana'antar fina-finan Hausa su bi tsarin aiwatar da fina-finan Hausa bisa Bahaushiyar al'ada kamar yadda aka san su a da can baya. An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason waxanda suka zabi wasu hanyoyin da ka sani, waxanda za su inganta masana'antar fina-finan Hausa su bi tsarin Bahaushiyar al'ada kamar yadda aka san su a da can baya. Bayanin na rubuce a tebur 3.6.3.

Tebur 3.4.3 Yawa da kaso na wasu hanyoyi da za su inganta masana'antar finafinan Hausa su bi tsarin aiwatar da finafinan Hausa bisa Bahaushiyar al'ada kamar yadda aka san su a da can baya.

Lamba	**Amsa**	**Yawa**	**Kaso(%)**
1	A da can suna nuna kyawawan xabi'u	35	43.75
2	Ba don neman kudi ake yi ba	20	25
3	An san sunan da aka raxa musu	25	31.25
Jimla		**80**	**100**

A dangane da wannan tambayar, an gano a da can baya shekarar 1999-2000 lokacin da fina-finan Hausa suka fara tashe an fi raja'a a fagen gina jigogin fina-finan bisa kyawawar xabi'un Hausa. Za a iya tabbatar da hakan ta duban kaso 35 na (43.75%) na yawan waxanda suka

xauki wannan matsaya cikin xarin. Haka kuma Kaso 25 (31.25) wanann yana nufin a da can fina-finan Hausa ba domin neman kuxi ake shirya su ba kamar shekara ashirin baya.

Tambaya 4

Waxanne xabiu ne aka fi qyama a cikin fina-finan Hausa? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason waxanda suka zavi xabi'un da aka fi qyama a cikin fina-finan Hausa. Bayanin na rubuce a Tebur 3.6.4.

Tebur 3.4.4 Yawa da kaso na dabi'un da aka fi kyama a cikin finafinan Hausa

Lamba	**Amsa**	**Yawa**	**Kaso (%)**
1	Raye Raye/Waqa	16	21.33
2	Soyayyar Zamani	14	18.67
3	Magana	10	13.33
4	Tufafi	7	9.33
5	Babu kunya	10	13.33
6	Babu Kara	10	13.33
7	Babu Ladabi	8	10.67
Jimla		**75**	**100**

Dangane da sakamakon xabi'un da aka fi kwaikawayo a cikin fina-finan Hausa, sakamakon ya nuna raye-raye da waqe-waqe na da kaso mafi yawa mai nuni da 16. (21.33%). Wannan ya nuna mana ba a san Bahaushe da yin rawa a filin Allah Ta'ala ba. Kuma, wannan ya nuna mana cewar raye-raye da ake yi ba xabi'ar Bahaushe ba ce. Kaso da ya biyo shi ne mai 14. (18.67 %) wanda yake nuna mana ana gini fina-finan Hausa a bisa jigon soyayyar zamani a maimakon bayar da fifiko a bisa jigoggin da suke kyautata zaman al'ummar Hausawa. Sannan kaso na uku da ya yi kankan da kaso na biyu shi ne wanda yake xauke da 10 (13.33%) rashin ladabin magana da 10 (13.33%) babu kunya da 10 (33.33%) babu kara. Wato, a sannan, an una wasu daga cikin fina-fanan suna nuna xabi'ar Bahaushe na rashin iya magana a gaban wanda ya girme shi ko mahaifansa ko kuma malaminsa. Sannan ba a kula da kiyaye al'adar kara da kunya a yayin aiwatar da fina-finan Hausa ba. Sauran kaso na yawan mutune yana mai nuna kashi 8 (10.67%) na tsarin tufafi. Kaso 7 (9.33%) a matsayin mafin karancin kaso, a nan sakamako ya nuna cewar za a iya kiyaye kaucewa raye-raye na zamani a cikin fina-fina Hausa. Domin shi ne ummul aba'isin da yake ruguza sauran kyawawan xabi'u irin su ladabin magana da su tufafi da kunya da kara da mutuntaka da biyayya ko ladabi da soyayyar zamani.

Tambaya ta 5

Fayyace qalubale da masana'antar fina-finan Hausa take fuskanta a yau. An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason waxanda suka fayyace qalubalen da masana'antar fina-finan Hausa take fuskanta a yau. Bayanin na rubuce a tebur 3.6.5.

Tebur 3.4.5 Yawa da kaso na qalubalen da masana'antar Fina-finan Hausa take fuskanta a yau

Lamba	Amsa	Yawa	Kaso (%)

1	Rashin Jagoranci	21	29.17
2	Rashin Tallafi	18	25
3	Rashin Horo/Ilimi	23	31.94
4	Rashin Tarbiyya	10	13.89
Jimla		**72**	**100**

Sakamakon wannan tambaya ya nuna qarara rashin ilimi da hororsa wa a fagen masu faxa a ji ‘yan kunji-kunji a harkar fina-finan Hausa na rashin iya gudanarwa da wannan harka yana kawo naqasu. Don haka, akwai buqatar aje a nemi ilimin da ya dace ga kowanne vangare ya nema, domin yawan 23 cikin kaso (31.94) ya nuna hakan. Sannan kaso da yake biye masa shi ne uwa uba rashin jagoranci wanda yake da yawa 21 kaso (29.17%) , wannan ya nuna mana akwai matsala mutuqa a fagen jagorancin hakar fina-finan Hausa. wataqila wannan ba za ta rasa nasaba da yadda ake ta samu varaka a fagen baxala da kuma yadda wasu sukan shirya fim a bisa wasu al’adun da suka savawa al’adu da addini da xabi’un Bahaushe. Sauran kaso 18 (25%) wanda rashin tallafi, yana daga cikin abubuwan da suke kawo zaman ‘yan marina a wasu sassa ta masana’artar, musamman rashin tarbiyya na daya daga cikin qalubale dake addabar masana’artar, kuma tarbiyyar nan tana daga ginshiki da suke gina kowacce al’umma tun daga sama har qasa.Kaso 10 (13.89%) ya tabbatar da cewa akwai vukatar yin hukunci mai tsanani a kan duk wani wanda aka kama da laifi a hukumance, ko a qungiyance a cikin wannan harka ta fina-finan Hausa, yin hakan zai taimaka wajen yi wa ko seti tabbatacciya.

Tambaya ta 6

A bisa tsari irin ta zamantakewar Bahaushe, shin ka yarda fina-finan Hausa sun yi tasiri a cikin al’ummar Hausawa? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason ra’ayin

tsarin zamantakewar Bahaushe a fina-finan Hausa da tasirinsu a cikin al'ummar Hausawa. Bayanin na rubuce a tebur 3.6.6.

Tebur 3.4.6 Yawa da kaso na tasirin fina-finan Hausa a zamantakewar Bahaushe

Amsa	**Yawa**	**Kaso (%)**
E	38	66.67
A'a	11	19.3
Ba matsaya	8	14.04
Jimla	**57**	**100**

A cikin tebur na 3.6.6. ana iya ganin yawa da kaso na tasirin fina-finan Hausa a zamantakewar Hausawa. Idan aka duba za a ga cewa mutane 38 (66.67) cikin mutane 57 sun ce tabbas fina-finan Hausa suna tasiri mutuqa a cikin al'ummar Hausa. Wannan ko ba zai rasa nasaba da yadda wasu yara sukan kwaikwayi wasu xabi'un aro zuwa cikin al'umma daga fina-finan kamar aski da kwalliya da sutura kodayake ba su san illar yin hakan ba. Mutane 11 (19.3%) kuma sun ce a'a fina-finan Hausa ba sa yin wani tasiri na a zo a gani a cikin fina-finan Hausa.

Tambaya ta 7

Cikin waxannan hanyoyin ba da magani na gargajiya a fina-finan Hausa, wane aka fi amfani da shi? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason hanyoyin ba da magani na gargajiya a fina-finan Hausa da aka fi amfani da ita. Bayanin na rubuce a tebur 3.6.7.

Tebur 3.4.7 Yawa da kaso na hanyoyin ba da magani na gargajiya a Fina-finan Hausa da aka fi amfani da shi

Lamba	Amsa	Yawa	Kaso (%)
1	Tsubbu	5	9.43
2	Rufa-ido	3	5.66
3	Bokanci	30	56.6
4	Malanta	15	28.3
Jimla		**53**	**100**

A nan sakamako ya nuna kaso mafi tsoka na 30 (56.6%) ya nuna, an fi amfani da hanyar bokanci wajen samar da maganin gargajiya a cikin fina-finan Hausa. Haka kuma hanyar samar da magani ta Malantar yana da kaso 15 (28.3%) na samar da magan a cikin fina-finan Hausa. Kaso mafi qaranta shi ne tsubbu da rufa-ido waxanda suke xauke da kaso na 5 (9.43%) da 3 (5.66%)

Tambaya ta 8

Shin wace irin gudummowa malaman addinin musulunci suke ba da wa a cikin harkar fina-finan Hausa? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason ra'ayin da ke nuna ko Malaman Addini suna ba da gudummowa a cikin harkar fina-finan Hausa. Bayanin na rubuce a tebur 3.6.8.

Tebur 3.4.8 Yawa da kaso na ra'ayin da ke nuna ko Malaman Addini suna taka rawa a cikin harkar Fina-finan Hausa

Lamba	Amsa	Yawa	Kaso (%)
1	E	31	56.36
2	A'a	14	25.45
3	Ba matsaya	10	18.18

Jimla	**55**	**100**

A cikin tebur na 3.6.8 an nuna shin malaman addini suna taka rawa a cikin harkar fina-finan Hausa? Yawa da kaso na ra'ayin masu nuni da ee malaman addini suna taka rawa a cikin harkan fina-finan Hausa sun fi xaukar kaso mafi tsoka 31 (56.36%). Wannan yana nuna irin gudunmawar da malamai addinin kan ba da a wa'azance ko faxakarwa ko kuma a matakan gargaxi da nisiha. Ke nan addinin Musulunci yana gurbi a cikin fina-finan Hausa kaso 14 (25.45%) shi ne suka nuni ga malamai ba su da wata rawa da suke takawa a cikin harkar fina-finan Hausa. Sannan kaso 10 (18.18%) sun nuna ba su da matsaya.

Tambaya ta 9

Shin yadda ake aiwatar da wasu bukukuwan al'adu a cikin fina-finan Hausa yakan canja tsarin al'adarsa? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason ra'ayin da ke nuna ko yadda ake aiwatar da wasu bukukuwan al'adu a cikin fina-finan Hausa yakan canja tsarin al'adarsa. Bayanin na rubuce a tebur 3.6.9.

Tebur 3.4.9 Yawa da kaso na ra'ayin da ke nuna yadda ake aiwatar da wasu bukukuwan al'adu a cikin fina-finan Hausa yakan canja tsarin al'adarsa.

Amsa	**Yawa**	**Kaso (%)**
Ee	3	6
A'a	32	64
Ba matsaya	15	30
Jimla	**50**	**100**

Tebur na 3.6.9 ya nuna amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kaso ra'ayin da ke nuna ko yadda ake aiwatar da wasu bukukuwan al'adun Hausawa a cikin fina-finan Hausa yana sauya tsarin al'adun sa? Tabur din ya nuna yawa da kaso 32 (64%) ya nuna fina-finan Hausa suna sauya al'adun Bahaushe zuwa wasu al'adun na daban, inda yawan mutane 15 (30%) suna da matsaya a'a wato kaso 3 (6%) sun ce fina-finan Hausa bas a sauya tsarin al'adun Hausawa, wato duka yanayin rayuwa da ake nuna wa a cikin fina-finan Hausa suna cikin tsari rayuwar Hausawa.

Tambaya ta 10

Shin fina-finan Hausa suna gurvata al'ada? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason ra'ayin da ke nuna ko fina-finan Hausa suna gurvata Al'ada. Bayanin na rubuce a Tebur

Tebur 3.4.10 Yawa da kaso na ra'ayin da ke nuna ko fina-finan Hausa suna gurbata Al'ada

Amsa	**Yawa**	**Kaso (%)**
Ee	34	82.93
A'a	2	4.88
Ba matsaya	5	12.2

Jimla	**41**	**100**

A tebur na 3.6.10 ya nuna mutane 34 (82.93%) suna da ra'ayin fina-finan Hausa suna gurvata xabi'u da al'adun Hausawa, wanda kashi 2 (4.80%) sun nuna fina-finan Hausa ba sa gurvata al'adar Bahaushe, amma yawan mutane 5 (12.2%) sun nuna ba su da matsaya.

Tambayoyin Bincike 11

Tambaya ta Goma sha Daya

Shin fina-finan Hausa, na Hausa ne? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason ra'ayin da ke nuna ko fina-finan Hausa, na Hausa ne. Bayanin na rubuce a tebur 3.6.11.

Tebur 3.4.11 Yawa da kaso na ra'ayin da ke nuna ko fina-finan Hausa, da fina-finai da Hausa.

Amsa	**Yawa**	**Kaso (%)**
Ee	40	57.14
A'a	25	35.71
Ba matsaya	5	7.14
Jimla	**70**	**100**

Tebur na 11 ya yi qoqarin fayyace matsayin fina-finan Hausa, wai shin fina-finan da na Hausa ko kuwa fina-finai da Hausa? Idan aka dubi yawan mutane da suka amsa wannan tambaya mutum 40 masu xauke da kaso (57.14%) sun nuna rinjaye na lallai fina-finan Hausa ba na Hausa ba ne. Amma, yawan 25 na mutane (35.71%) sun nuna ba haka ba ne, ai fina-finan Hausa na Hausa ne, su kuwa 5 (7.14%) ba su da matsaya.

Tambaya ta Goma Sha Biyu 12

Me yake haifar da aron al'ada a cikin fina-finan Hausa? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason da ke nuna abubuwan dake haifar da aron al'ada a cikin fina-finan Hausa. Bayanin na rubuce a tebur 3.6.12

Tebur 3.4.12 Yawa da kaso na ra'ayin da ke nuna abubuwan dake haifar da aron al'ada a cikin Fina-finan Hausa

Lamba	**Amsa**	**Yawa**	**Kaso (%)**
1	Cudanyar Zamantakewa	29	42.65
2	Juyin Zamani/Kasuwanci	24	35.29
3	Rashin Ilimi	15	22.06
Jimla		**68**	**100**

A tebur na 3.6.12 an ba da sakamakon na yawa da kaso na ra'ayin da ke nuna abubuwan da ke haifar da aron al'ada a cikin fina-finan Hausa da 29 (42.65%), shi ne kaso mafi tsoka da ya sanya are-aren al'adun da xabi'u zuwa cikin fina-finan Hausa. Kaso 24 (35.29%) ya nuna saauyin zamani da kuma neman kuxi shi ne ya yi sanadiyar yayyafar aron al'adu a cikin fina-finan Hausa. Kaso na uku shi ne mai nuna yawan mutane 15 (22.06%) wanda su kuma suna ganin akwai buqatar masu shirya fina-finan su mayar da kai wajen neman ilimi, rashin ilimi ba qaramin koma baya ba ne ga ci bagan harkar samar da fina-finan Hausa.

Tambaya ta Goma Sha Uku 13

Ko ka yarda za a iya amfani da fina-finan Hausa wajen kyautata rayuwar al'ummar Hausawa? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason da ke nuna ko za a iya amfani da

fina-finan Hausa wajen kyautata rayuwar al'ummar Hausawa. Bayanin na rubuce a tebur 3.6.13

Tebur 3.4.13 Yawa da kaso na ra'ayin da ke nuna abubuwan dake nuna ko za a iya amfani da fina-finan Hausa wajen kyautata rayuwar al'ummar Hausawa

Amsa	**Yawa**	**Kaso (%)**
Ee	44	60.27
A'a	27	36.99
Ba matsaya	2	2.74
Jimla	**73**	**100**

Yawan kaso 44 (60.27%) shi ne kaso mafi tsoka wanda yake nuna ana amfana da fina-finan Hausa wajen kyautata rayuwar al'ummar Hausawa. Sannan kaso 27 (36.99%) suna masu ra'ayin cewar ai fina-finan Hausa ba sa kyautata rayuwar al'ummar Hausawa sannan kaso 2 (2.74%) sun nuna ba su da matsaya.

Tambaya ta Goma Sha Huxu 14

Yaya fina-finan Hausa suke a yau? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason da ke nuna yadda fina-finan Hausa suke a yau. Bayanin na rubuce a tebur 3.6.14.

Tebur 3.4.14 Yawa da kaso na ra'ayin da ke nuna yadda fina-finan Hausa suke a yau

Lamba	**Amsa**	**Yawa**	**Kaso (%)**
1	Sun kaucewa al'adar Bahaushe	32	45.71

2	Hadin Gambiza	28	40
3	Bunqasarsa a duniyar zamani	10	14.29
Jimla		**70**	**100**

Dangane da yawa da kaso na ra’ayin da ke nuna ra’ayin mutane dake nuna matsayin fina-finan Hausa a yau 32 (45.71%) suna masu ra’ayin fina-finan Hausa sun kaucewa al’adar Bahaushe. Amma mutane masu kaso 28 (40%) suna ganin ai haxin gamin gambiza da cakuxe-cakuxen shi ne ya fi yin tasirin a fina-finan Hausa a yau, amma kaso 10 (14.29%) suna ganin ya bunqasar a duniyar zamani ta bunqasa harshen Hausa a yau.

Tambaya ta Goma Sha Biyar 15

Waxanne dalilai ne suka sa ba a iya tsara fina-finan Hausa bisa tubalin Bahaushiyar al’ada? An amsa wannan tambayar ta hanyar duba yawa da kason dalilai da suka sa ba a iya tsara fina-finan Hausa bisa tubalin Bahaushiyar al’ada. Bayanin na rubuce a tebur 3.615.

Tebur 3.4.15 Yawa da kaso na ra’ayin da ke nuna dalilai da suka sa ba a iya tsara Fina-finan Hausa bisa tubalin Bahaushiyar al’ada

Lamba	**Amsa**	**Yawa**	**Kaso (%)**
1	Rashin kishin al'ada	31	44.29
2	Rashin tallafi daga gwamnati	15	21.43
3	Neman abin duniya (Kudi)	15	21.43
4	Babu matsaya	9	12.86
Jimla		**70**	**100**

Ra’ayin mutane ya raja’a a kan kaso 31 (44.29%) rashin kishin al’ada ne ya jawo ba a tsara fina-finan Hausa a bisa tubalin Bahaushiyar al’ada. Amma, kaso 15 (21.23%) suna ganin rashin tallafi daga gwamnati da masu hannu da shuni shi ne babban matsalar, sannan wani kaso 15 (21.23%) suna ganin neman abin duniya ne kawai da kuxi ’yan fim suka sa a gaba, ba xaukaka al’ada ba, amma kashi 9 (12.86%) ba su da matsaya a kan wannan tambaya.

3.4.2 Sauran Hanyoyin Tace Bayanai

Wannan bincike ya kawo wasu dabaru da za a iya bi domin a iya tantance fina-finai na Hausa da kuma fina-finai da Hausa. An yi amfani da mizanin tantancewa na bayan fage da na cikin fage.A qoqarin tantance fim na Hausa an rarraba su bisa nau’o’i guda shida, to ya wajaba a yi amfani ko dai da wasu daga cikin waxannan matakan ko kuma dukkansu. Sulaiman (2017) ya goyi bayan wannan ra’ayi. Domin kuwa a wani lokaci yana da wuya ka iya amfani da mataki xaya ko siffa guda wajen wannan tantancewar. Kamar haka:-

1. Qirqira
2. Asali
3. Wanki da xauraya
4. Fassara
5. Kwaskwarima
6. Baddalawa

Idan aka ce fina-finai da Hausa a nan ana magana ne a kan fina-finan da aka yi su da harshen Hausa, kuma Hausawa ko ba Hausawa ba su suka aiwatar da wannan fim. Suna iya zama fina-finan waxanda aka yi amfani da harshen Hausa ne kurum a matsayin harshen sadarwa, amma

ba sa nuna sanannen tsarin rayuwar Bahaushe. Wannan tsarin rayuwa ya haxa tun daga al'adu da tsarin zamantakewa da tattalin arziki da shugabanci da tarbiyya da maqwabtaka da dai sauran al'amuran zaman rayuwa na yau da gobe. Amma, idan aka ce fina-finan Hausa, ana nufin fim wanda yake nuna tsari da siga irin na Hausawa, kuma fim ne wanda tun daga kan tsarin muhalli da tufafi da kayan wasa da halayyar 'yanwasa da labari da uwa uba harshen 'yanfim duka su kasance cikin yanayin xabi'u da al'adun Hausawa (Sulaiman, 2017:6). Domin a iya tantance haka a wannan fage na ilmi ba shaci faxi ba, an kawo waxannan dabaru kamar haka na tantancewa:

3.4.2.1 Qirqira

Zainab (2017) ta ba ma'anar qirqira a matsayin hanyar qago wani laqabi ko wata magana don bayyana wani baqon abu. *Qamusun Hausa* na Jami'ar Bayero, Kano (2007) ya bayyana qirqira da qago ko gano hanyar yi ko samar da wani abu. Ke nan idan ana so fim ya amsa sunan da aka raxa masa gudun kar a shiga ruxani, sai a qago labari mai xauke da asalin xabi'u da al'adun Hausawa kyawawa.

Sulaiman (2017) ya ba da ma'anar adabi a matsayin hikima da fasaha ta al'umma wadda aka qirqira sa'annan aka adana ko dai aka ko kuma ta hanyar wanzarwa a rubuce ko a aikace. Wannan hikima galibi takan bayyana hoton rayuwar al'ummar da aka yi domin ta. Ta nazartar ire-iren waxannan hikimomi ake fahimtar tunani da falsafar al'umma game da rayuwa. Fasihai waxanda Allah ya ba su baiwar qirkirar abubuwan adabi kan kasance sun tasirantu da wasu

abubuwa na rayuwa waxanda suka tava faruwa ko kuma suke faruwa a wannan lokaci ko kuma ake hasashen faruwarsu nan gaba. Waxannan abubuwa suke fitowa a ayyukan adabi. Idan an sami fim wanda ya kasance tsarin labarinsa qirqira aka yi, wanda ba shi da wata nasaba da aro ko fassarawa ko makamancin haka a qagaggen labari na zube ko tatsuniya. Za a iya kiransa da adabi tsantsa na Hausa, za a iya cewa shi ne Bahaushen fim. Misali fina-finai irin su *Sarki Jatau* da *Burin Zuciya* na kamfanin Mandawari *Enterprises* da *Zarge* da *Allura daZare* na Kamfanin Sarauniya *Films*. Manufar a nan ita ce, a tantance kowane fim aka xauka, kafin a ayyana shi a matsayin fim na Hausa.

Wani hanzari ba gudu ba, za a iya samun yanayin zamantakewar da ke cikin fim ya yi kama da zamantakewar wata al'ummar ta daban. Ma'ana, idan aka sami haka sai a duba a ga ko akwai dangantaka da tasirin wancan al'ummar ko babu, idan babu to ya zama fim tsantsa na Hausa.

Hanyoyin da za a iya samun tabbacin tsittsige ko usuli na fim su ne tattaunawa da waxanda suka shirya fina-finan , ko kuma ta tuntuvar waxanda suke da masaniya kan yadda aka samar da fina-finan da ake nazari. Ko da yake sai an yi hattara, domin ana iya samun bayanai marasa sahihanci in an tunkari wasu daga cikin marubuta tsarin labarin. A wasu lokuta masu shirya fim da qwararru da jama'ar gari za su taka muhummiyar rawa wajen faxin asalin fim.

3.4.2.2. Asali

Asalin fim, a nan ana nufin asali ko tushe ko dalilin qirkirar labarin da aka gina fim a kai. Don haka, mai nazari na buqatar binciko usuli ko tsitstsigen da aka yi amfani da su wajen samar da kowane fim kafin ya yanke hukunci a kan wannan fim xin (Sulaiman, 2017:8). Akwai wasu fina-finan Hausa waxanda wannan aiki ya yi qoqarin binciko asalinsu. Yana da kyau a ambaci qoqarin da wannan bincike ya yi domin nemo asali ko tsittsige ko tubalin ginin wasu fina-finan domin fahimtar inda aka dosa. An yi haka ne domin tantance al'adu da xabi'un da ke ciki sun dace da na Hausawa ko kuwa kayan aro ne. Wasu daga ciki ana iya sanin asalinsu, wasu kuwa sai da aka kai ga tattaunawa da waxànda suka shirya fina-finan . Ko shakka babu fim na *Kara Da Kiyashi da Ki Yarda da ni da Jamila da Jamilu* sun vulla sakamakon baddala wasu littattafai na zube. Buba da Gidan Dabino (2003) sun tabbatar da haka ta hanyar nuna cewa fina-finan Hausa sun samo asali ne daga rubutun zube. Kuma sun xauki wasu murubuta guda huxu da littattafan da suka rubuta domin kafa hujja. Xaya daga ciki akwai In *da so da Qauna* na Ado Ahmad Gidan Dabino, sai *Alhaki Kuikuiyo* na Balaraba Ramat Yakubu ga kuma *Naira Da Kwabo* na Nazir Adam Saleh da *Kara da Kiyashi* na Zuwaira Isah Dallami Jos. An gwada cewa wasu daga cikin ire-iren marubuta ba su ji daxin wannan satar fasaha da aka yi masu ba. Wasu kuwa da yardarsu aka yi, sai dai an sami rashin jituwa a tsakani domin an sauya musu manufa da tunani, ba kamar yadda yake a cikin littafan ba. A nan ma akwai abin faxi domin sai an yi hattara, hattarar kuwa a nan ita ce, su litattafan da aka kwaikwaya suna bisa turba ta Hausa ne ko kuwa su ma duk je ka na yi ka ne? In haka ne ashe ba ta sauya zani ba.

Wani lokaci kuma labarin da aka gina fim kansa kan kasance ya tava faruwa a cikin al'umma, nan ma sai an tantance gaskiyar al'amarin. Misali, shirin fim na *Kishiyata* da kuma na *Aziza*,

kwatankwacin wani labari ne da aka riqa yayatawa a cikin al'ummar Hausawa wanda ya nuna haka ya tava faruwa a rayuwa ta zahiri. Labarin *Kishiyata*na magana kan wata mata wadda ta tafi Makka domin yin ibada, amma sai ya kasance a wurin xawafi ta yi ta zagaya xakin Ka'aba amma ba ta ganinsa, har kama hannunta aka yi aka aza a kan xakin amma ba ta ji komai ba Sulaiman (2017). Wannan labari na abin da ya faru a rayuwa ta zahiri shi aka yi amfani da shi wajen qirqirar fim na *Kishiyata*. Ashe masu tsara labarin fina-finai na iya xaukar abubuwan rayuwa na al'umma waxandu suka faru a zahiri don yi masu kwaskwarima a samar da fina-finai suna nan. Wannan ba wani abin kunya ba ne matuqar dai an yarda da cewar adabi madubi ne mai haskaka rayuwar al'umma. Don haka, abubuwan da ke faruwa a cikin al'umma ya kamata masu shirya fina-finai su xauka don yin hannuka-mai-sanda ko faxakar da al'umma ko kuma ilmantar da su ga wani abu sabo.

3.4.2.3 Wanki Da Xauraya

Ma'anar wanki da xauraya a zahiri na nufin wanke tufafi ko wani abu, ko wanke allo bayan Malam ya tabbatar xalibi ya iya karatun da aka biya masa. Idan kuwa datti ne ko najasa, ana wankewa da ruwa domin a sami tsarkin a kaya, ko wuri don ibada ko guje ma qazanta. A ma'ana ta ilimi kuwa a *Kamusun Hausa* (2006) ya ce wanki na nufin cuta ko zambata ta hanyar yaudarar mutum a dukiyarsa ko abin da ya mallaka.

Xauraya kuwa a zahiri na nufin xauraye duk wani abu da aka wanke. Wannan wankewar na iya kasancewa an yi da sabulu, ko omo ko kanwa ko toka ko gishiri da fatar fitar da datti a

jikin abin nan da aka wanke. Domin tabbatar da wankin ya wanku, sai a xàuraye kumfar abin nan da aka yi wanki da shi da wani ruwa mai tsafta na daban don wankin ya inganta. ‘Wanki da Dauraya’ a Fina-finan Hausa na nufin ‘satar fasaha’ daga wani fim zuwa wani, ma’ana a nan ita ce yadda ake wanko kuma a xauraye wani fim na wata al’umma ta daban don a samar da wani fim na Hausa ba tare da an bar komai ba. Shi ma wannan, ana yin sa ta fuskoki biyu. Fuska ta farko kan kasance gaba xayan fim ake wankewa kamar yadda muka gani a wasu fina-finan Indiya zuwa na Hausa ko kuma wanda aka yi kwanan nan wato fim xin *Indon Kauye* wanda yake wanki da xaurayar fim na turanci mai suna *Dumebi?* Sa’annan fuska ta biyu ita ce wadda ake wanke wani fanni na tsarin labari daga wani fim wanda ba na Hausa ba zuwa fina-finan Hausa. Ba tsarin labari kaxai ba, hatta sutura da muhalli yakan kasance wani vangare na wannan wanki da xaurayar. Misali, fim xin *Gwaska* wanda asalin labarin daga Indiya ne mai suna *Kirishna* aka juya labarin zuwa Hausa, Adamu Zango ya shirya ya kuma ja gwarzon fim xin.

3.4.2.4 Fassara

Ma’anar fassara ko ga manazarta ilimin harshe ba ta wuce mayar da ma’anar wata kalma ko juyar da ma’anar wata kalma ko bayanin da aka yi cikin wani harshe zuwa wani harshe ba *Qamusun Hausa* (2006). A taqaice, fassara na nufin mayar da ma’anar wani bayani ko sauyawa daga harshen bayarwa zuwa harshen karva. Malumfashi (2010) da Yakasai (2012) da Sarvi (2012) sun ce fassara a fina-finai kuwa ba ta bambanta da ma’anarta ta asali ba. Domin kuwa fina-finan da aka fassara, fina-finai ne waxanda aka yi su da wasu harsuna, sannan aka fassara su zuwa harshen Hausa. A lura da cewa a yayin da aka yi wannan fassarar, in an

sassauya abubuwan da ke ciki har ta kai ba a iya tantance daga fim xin da aka yi fassarar wani abu ne daban. Fassarar da wannan aiki ke magana a kai ita ce wadda har yanzu take tashe inda ake fassara fina-finan lndiya da na *Chin*a kai har ma da na mutanen Amirka zuwa harshen Hausa. Ba a sauya komai na asalin yadda aka tsara labarin, ko matsayin 'yan wasa ko tufafinsu haka za a sake su, illa zantuttuka da kalamai na 'yan wasa ake sauya su daga wani harshe zuwa harshen Hausa. A mafi yawan lokuta ma, idan fim na Indiya ne, ba a cika fassara wake-waken da fim yake xauke da su ba. Wannan ya nuna qarara cewa fina-finai ne da Hausa amma ba fina-finan Hausa ba.

3.4.2.5 Kwaskwarima

Kwasakwarima, wato mayar da abu naka ta yadda mai shi ma ba ya iya sanin wannan abin daga gare shi yake, ana samun wasu fina-finan da wannan siffar. In har an sami wannan sauyin da ta kai ma ba a iya tantancewa ga asalin inda aka yi aron ko kuma muwafaka aka samu ta al' adar da ta kusa zama xaya to nan ma a iya ayyana irin waxannan fina-finan a matsayin na Hausa. Dole a yi taka tsantsan don gudun kada a xauki wasu al'adun a matsayin na Hausawa. A ra'ayin Larkin (1997) kusan a iya bayyana fina-finan Hausa sun kwaikwayi abubuwa ko kuma sun aro abubuwa da dama daga Indiyawa waxànda su ma da can an zarge su tamkar yadda ake zargin na Hausawa cewa sun xauki tsarin fina-finan Turawa ne. Ya nuna cewa idan aka yi aron ana sauya yanayin tsarin ne don ya dace da abin da al'umma ke son gani, idan dai ana son ya zama karvavve.

A iya cewa Hausawa ma sun bi wannan tsarin wajen xaukar baquwar al'ada da sauya ta don ta dace da al'ummar da aka yi dominta. Misali da za a iya bayarwa a nan shi ne kamar yadda mawaqan bandiri suka kwaikwayi tsarin waqoqin Indiya aka mayar da su na waqoqin yabon Annabi. Fina-finan Hausa ma sun ci moriyar yin amfani da waxannan baqin abubuwa. Sun aro ire-iren waxannan daga fina-finan Ibo da littattafansu, daYarbawa da littafan soyayya da dai sauransu inda aka sauya waxannan domin su dace da tsarin al'adun da koyarwar addini. (Sulaiman, 2017:11).

Wannan shi ma wani sabon salo ne da ake amfani da dabbarbaru wajen juya wasu fina-finan makwabtan Hausawa a mayar da su fina-finai da Hausa. Mai rubuta labari ko furodusa yakan zauna ya kalli wani fim da aka yi da Inyamuranci ko na Yarbawa ko kuma Nufawa, sai ya samar da labari zuwa Hausa. To, nan marubucin zai yi amfani da dabarar sadarwa fim xin da ya kalla zuwa labari da Hausa, ta yadda fim xin zai dace da al'adu da xabi'u irin na Hausawa. A maimakon ya wanko kai tsaye, a'a, sai ya yi masa kwaskwarimar da in ba wanda ya tava kallon wancan fim xin na asali ba, kai ka ce daman fasahar mai fim xin ne. Don haka, shi a kwaskawarimar fim ana mutuqar qoqarin kwatanta shigo da wasu kyawawan yanayin muhalli da sutura da tsarin zamantakewa irin ta Hausawa.

3.4.2.6 Baddalawa

Ko da yake wasu na ganin an fara cin moriyar wannan hanya ce ta mayar da wasu daga cikin sassan adabin baka zuwa rubutaccen adabi (qagaggen Iabarai da wasan kwaikwayo). Wannan fasahar ta bayar da wata kafa ta bunqasa adabin Hausa. Tambayar dai a nan ita ce, shin

baddalawa ake yi ko kassarawa ce? Manufa, abubuwan da aka baddala sun yi daidai da sigarsu da manufarsu ta asali? Kuma ta yaya suke bayyana al'adun Hausawa? Idan an sami wannan baddalar, dole ta kasance ba ta sava da sannanen tsarin tunani da xabi'u da tsarin zamantakewar Bahaushe ba. Sauya baquwar al'ada ko cancanza ta da wadda mutane suka sani na xaya daga cikin abubuwan da ke taimakawa baddalawa. Dole ne a sami sauyi wajen tufafi da abinci da gine-gine da abubuwan sadarwa, a sake masu kama, su zama na Hausawa, ta yadda mai karatu zai xauka dama can a qasar Hausa aka tayar da ainihin labarin. Domin haka, Abubakar Imam ya yi, ya cancanza baqin al'adu da waxanda Hausawa suka saba da su. A maimakon keken dawaki ya kawo keken shanu. Qorunan giya suka koma buhunan hatsi, kayan gidan mai keken dawaki da yanayin rayuwarsa ta Turawa, duk ya canza su don su dace da xabi'un qasar Hausa. Sulaiman (2017).

In an sami haka a fina-finan Hausa sai a yanke hukunci da cewa duk da yake baddalawa aka yi, ire-iren waxannan fina-finai na Hausa ne. Za a iya kafa hujja da shirin *Salmasalma Duduf da Daskin da Rixi da Ga Fili ga mai Doki* baddalawarsu aka yi daga nau'o'in adabin baka na Hausawa ya samar da su. Haka kuma idan an duba shirin *Karaga* za a tarar kwatankwacin tsarin uwar labarin da ke cikin *Magana Jari Ce* na xaya. An gwada saboda kwaxayin haihuwa da Sarki yake da shi, sai ya tara malamai arba'in waxanda suka kwana ar'abin suna addu'a sa'an nan matar Sarki ta sami ciki. Sarki da iyalansa har da jaririn da aka haifa ba su tsira daga sharri da makircin Waziri ba, saboda buqatarsa ta ganin ya zama Sarki. Wannan tsarin labarin haka yake a uwar labarin *Magana Jari ce* na xaya. Ga wasu masanan, wannan tsarin labarin *Karaga* na *Magana Jari Ce,* wanda shi ma ya samo asali daga wani littafin mutanen Farisa

mai suna *Tuti -Name* wanda shi ma fassarar wani littafin mutanen Indiya ne mai suna *Sukasaptati* (Sulaiman, 2017:10). Wasu da yawa daga cikin manazarta sun tabbatar da cewa an sami baddalawa daga wani nau'in adabi zuwa fina-finan Hausa. Ayuba (2007) ya nuna irin tasirin da adabin baka ya yi ga fina-finan Bidiyo na Hausa. Ya xan tavo ire-iren abubuwan da suka samar da fina-finan, kamar tasirin rubutun zube inda ya ambaci irin gudummawar da wasu littafan zube suka bayar wajen samar da fina-finan Hausa. Ya dire bincikensa a kan cewa kusan babu wani wasan da za ka gani ba tare da yana da jivi da gargajiya ba. Ma'ana ba tare da yana da dangantaka da adabin baka ba. Ya kawo tasirin tatsuniyoyin da sukasauya sheqa zuwa wasan kwaikwayo kamar tastuniyar *Sumbuka, da Daskin da Ridi, da Dongani da ta Xan Musa da kuma ta Ruwa Bagaja.* A nan, asalin labaran da aka baddala masu alaqa da labaran gargajiyar Hausa ne, don haka ko da an gina fim a kan ire-iren su, za su iya zama fina-finan Hausa. Amma, idan aka badallar da labaran gargajiya Kanuri ko na Ibo a misali da wuya ya yi dai-dai da na Hausawa, domin sai an sami wasu wurare da zai nuna givi bambancin asalin al'ada ko xabi'u da na asalin Bahaushe musamman a fagen aiwatarwa. Misali, fim xin *Ahlil Kitabi* asalinsa labarin daga Larabawa ne, wato labarin mutanen kogo, shi ya sa suturar 'yan fim da kalamansu da wasu aiwatarwar ya shafi al'adun larabawa a cikin fim xin.

3.3 Tace Fina-finan Hausa Ta Bayan Fage

Waxannan su ne wasu manyan ginshiqai a fagen shiryawa da samar da fina-finan Hausa, su suke taka muhimmiyar rawa tun daga tushe. Sannan, su ba haska su ake ba, balle a gan su a kyamara, yawanci ayyukansu sukan yi su ne a bayan fage, ba a ganin su, kuma in ba su, to, ba fim. Su ne kamar haka:

-Maqirqirin labarin fim

- Marubucin labari fim
- Furodusan fim
- Darakta fim

3.3.1 Qirqirar Labari

Domin a iya tantance fim na Hausa da kuma fim cikin Hausa, wannan bincike yana ganin ya wajaba a bi diddigin asalin labarin da aka gina fim akansa. Akwai abubuwa guda biyu da ya kamata a kula da su: shin labarin qirqirarren labari ne ko kuwa labari ne da aka xauko shi daga wani fim aka maida shi fim da Hausa.

Abin da ake nufi da qirqirar labari shi ne duk wani labari da aka zauna aka rubuta shi ne aka tsara shi a bisa kyakkyawan tsari na al'adu da xabi'u da tunani irin na Bahaushe sannan ba a tsarma wasu baqin al'adu a cikinsa ba. Ma'ana, an tafi kai tsaye wajen nuna ainihin kyawawan hutonan rayuwa irin ta Bahaushe, Fina-finan da suka zo da irin wannan tsarin su ne ake kira da Fina-finan Hausa a bisa qullin labari. A wasu lokuta ana iya gina labarin fim ya xauko wasu labarin gargajiyar Hausawa domin a gina fim akai. Alal misali, daga zube na gargajiya irin su tatsuniya, qissa da hikaya da tarihihi da tarihi labarun baka na Hausa da sauransu. A wani vangaren kuma ana iya xauko rubutattun labarun zube a gina fim a kan sa,misali, irin su *Magana Jari ce* da *Ruwan Bagaja*. Don haka, ya kamata a san waye ya qirqiri labarin fim, sanin asalinsa a wannan mataki yana mutuqar muhimmanci. Al'adunsa da xabi'unsa za su iya yin tasari a fim musamman idan ba Bahaushe ba ne.

3.3.2 Tushen Labarin a Fina-finan Hausa

Tushen fim shi ne labari, labari kuma shi ne fandisho na gina kowane irin fim wanda ‘yan kallo za su iya yaba wa ko kuma su kushe. Da dama wasu labaran akan gina su ne ta bin waxannan hanyoyi kamar haka:

- Kallon fina-fina qasashen waje kamar na Indiya da Turawa da Labarawa a mayar da su labarin fim da Hausa.
- Kallon fina-finan Ibo da Yarbawa da na Afirka a mayar da su labarin fim da Hausa.
- Gina labari a bisa tunani da xabi’un wasu furodusoshi waxanda babu su a cikin harkar samar da fina-finan Hausa.
- Ta yadda akan zauna kawai a qulla labari domin a samar wa kai kuxi misali fim xin *Rumfar Shehu* da *Doya da Manja*. Waxannan ba su da wata alaqa da al’adu da xabi’un Hausawa.

Yawancin iri-iren fina-finan da aka gina su a bisa wannan turbar labari, ba sa nuna hoton al’adu da xabi’un Hausawa.

3.3.3 Marubucin Labari

Ya wajaba a san shin wane ne marubucin labarin fim. Bahaushe ya ce ka san mutum ka san asalinsa. Shin yawancin marubuta fina-finan Hausar nan Hausawa ne masu son kare muradun al’adu da xabi’un Hausawa? Don haka, a duk lokacin da aka ce fim, bai amsa sunansa da fim xin Hausa ba to sai a bi diddigin tarihin marubucin labarin fim xin. Idan kana so ka gano hakan, za ka iya ganin tasirin harshen marubucin ko al’adunsa ko xabi’unsa a cikin labarin da

ya rubuta, wannan tasirin shi ne zai tafi har sai ya yi tasiri a yayin aiwatar da fim. Amma a yayin da ake so fim ya amsa sunansa da Bahaushen fim, ya wajaba shi marubucin labarin ya kasance Bahaushe ne. Domin, ana sa ran Bahaushe yana da qoqarin kare martabar al'adarsa da xabi'usa, kuma zai guji saqala wasu xabi'un baqi a cikin fim wanxanda za su iya savawa tunanin Bahaushe.

3.3.4 Furodusan Fim

Ya dace kamar yadda aka bi diddigin tarihin sanin marubucin labari. Hakanan, ya kamata a bi, domin gano asalin tarihin furodusa. Domin, shi furodusa shi ne wanda yake da haqqin mallakar fim, kuma shi yake da wuqa da nama na gayyato daraktan da za su yi aikin tare da shi. Furodusa shi ne wanda zai zavi yan fim da za su taka rawa a fim tare da darakta, mai bayar da umarni, domin a sami cancantar gagarumar taimako da kowa zai taka. Furodusa shi ne yakan yi uwa da makarviya a fim xinsa. Don haka, yana da matuqar muhimmaci a san wane ne shi furodusa idan ba xan Hausa ba ne, tana iya yiwuwa zai so ya sanya nasa ra'ayin da son zuciyarsa a cikin fim. Zai yi hakan ne ta yadda shi kwalliyarsa za ta biya masa kuxin sabulu, amma idan kwalliyar ta savawa tsarin zamantakewar Bahaushe a cikin fim, sai a bincika a gano waye furodusan. Idan kuwa ta kasance furodusa xan Hausa ne, kuma aka yi sa'a yana da aqida da ra'ayin kare martabar al'adunsa a lokacin shirya fim. To sai a yi hamdala, misali furodusoshi irin su Mandawari da Iyan Tama da Ado Ahmad, da Sarauniya sukan samar da fina-finan da suke kare martabar al'adu da xabi'un Hausa.

3.3.5 Daraktan Fim

Shi ne jami'i da akan xauko shi domin ya bayar da umarni a fim. Darakta kan zamanto wanda yakan xauko kowanne xan fim ya sanya a bisa gagarumar taimako da zai taka bisa cancanta da qwarewarsa bisa gagarumar taimako zai taka a wasa. Ya wajaba kowane xan fim da zai taka rawa a fim ya naqalci littafin karatu na sikirif xin fim xin tun kafin ranar da za fita lokeshan. Sanin tarihin darakta da qabilarsa yana da mutuqar muhimmanci a wannan zango. Domin darakta shi ne qirjin biki, shi ne wanda zai zavo duk wani ko wata wanda za ta taka rawa a cikin fim. A qoqarin yin hakan, wasu baqin daraktoci sukan shigo da son zuciya da ra'ayinsu wajen zavo waxanda suke yi musu biyayya kawai, ba tare da an yi la'akari da cancanta ba. Ma'ana rashin sanya waxanda suka dace su taka gagarumar taimako da ta dace a fim, wani lokaci kuma shigo da wanda yake qabilarsu guda ce ko kuma aboki ko abokiyar yinsa ce ba tare da cancanta ya taka rawa a cikin fim ba. A qoqarin yin hakan, sai fim ya kaucewa yanayi da sigar da aka gina shi a kai, domin an sanya waxanda ba su dace ba. Misalin Daraktoci waxanda ba Hausawa a cikin harkar fina-finan Hausa akwai su Inyamuri Chukwuma Maffy. A dalilin cuxayarsa da Hausawa 'yan fim ya Musulunta, aka sauya masa suna zuwa Abubakar Sadiq Mafiya. Wani darakta wanda ba Bahaushe ba ne, kuma shahararre shi ne, wani Bayarabe Taye Hassan wanda aka fi sani da Hassan Gigg . Bugu da qari, ga Sani Musa Danja wanda ko a yanayin yadda yake tafiyar lamuran fina-finan sa da xabi'unsa ka san al'adar Yarbawa ta huda shi, Ali Nuhu shi ma an ce ba Bahaushe ba ne daga xan abin da aka ji a bakunan jama'a, duka suna taka muhimmiyar rawa wajen bayar da umarni a fina-finan Hausa, kuma halayyarsu tana tasiri mutuka. Ba abin mamaki ba ne, idan xabi'unsu sun yi tasiri a

cikin fina-finan Hausa. Kuma a duk lokacin da suka aikata hakan, dole ne ba za a ce an ga fim xin Hausa ba, sai dai a ce an ga fim da aka yi da Hausa.

3.4 Tace Fina-finaiA Cikin Fage

Kamar yadda ake qoqarin tantance fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa, an raba dabarun tantancewar gida biyu. Wato na bayan fage kamar yadda aka gani a baya. Sannan dabarun tantancewa na cikin fage. Adabi,na zube ko na waqa suna da hanyoyi ko dabaru n da akan bi domin a yi nazarin su. Hakannan ma abin yake a nazarin fim, akwai mizanin nazarin fina-finai kamar yadda masana irin su Kofoworola (1987) da Abdullahi (2015) da Aminu (2012) da Chamo (2012) suka nuna. Wato kallon sigar fim; ta duban tsarin labarin fim, (Souce of the story line) da gagarumar taimako da ‘yan wasa suka taka (*characterization*) da harshen ‘yanwasa (*dialogue*) da nau’in kwaliyyar (make up) da kayan wasan na zahiri (properties/artifacts) da tufafin ‘yanwasa (*costumes)* da rakiyar sauti (*sound track*) da kuma tsarin tafiyar da rawa wato (*Adaptation of Music/Dance/Chroagraphy*). Don haka, a nazarin fim na Hausa, akan yi amfani da wannan mizanin nazarin fina-finai. Wannan bincike yana ganin za a iya tantance kowanne irin fim na Hausa ta amfani da waxannan dabarun nazari domin a san shin fim xin Hausa ne? Ana iya duba xaya daga waxannan dabaru kamar haka, amma wannan bincike yana ganin za iya yin qari da duba tsarin zamantakewar al’umma a matsayin qari a daburun nazarin fina-finan Hausa da tantance su:

- Jigon fim.
- Zubin fim
- Tarihi da halayyar xan fim.
- Harshen ‘yan fim.
- Suturar ‘yan fim.

3.4.1 Tarihi da Halayyar ‘Yan Fim

A yayin tantance fina-finan Hausa da fim da Hausa, ya kamata a san kowane tsuntsu kukan gidansu yake yi, bugu da qari kama da wane ba ta wane. E, an yarda Bahaushe yakan qarvi al’ummomi daban-daban su zauna tare da shi, wani lokaci ma yakan nashe da su idan zama ya yi zama, kuma a tafi tare musamman a bisa yanayin rayuwa na kasuwanci da neman ilmi da maqwabtaka da sauran su. Masu iya magana sun ce hali zanen dutse, wato xan Adam idan yana da wani hali da ya shiga jikinsa da wuya ya iya barinsa. Don haka, cikin fina-finan Hausa, ana iya tantance fim na Hausa ko kuma fim da Hausa ta kallon gagarumar taimako da xan fim ya taka a cikin fim xin. Ana iya duba tarihinsa da kuma sanin daga ina ya fito kafin ya samu kansa a Kano ko Zazzau ko kuma Katsina inda yake harkar aiwatar da fim.

Halayyar xan fim ita za ta qara nuna shi, a san ko wane ne shi, kuma za ta nuna matsayinsa da gagarumar taimako da yake takawa a cikin fim, ta hakan za a iya tantance shi, ko shin Bahaushe ne ko kuma xan wata qabilar ne? Domin idan aka ba wa Bahaushe umarni ya aiwatar da abu kaza wanda bai cikin tsarin rayuwa tasa, zai iya ba da uzuri cewar ya savawa xabi’arsa da al’adarsa ta al-kunya. Idan kuma dama ba Bahaushe ba ne, take zai ce da kai an gama, ba rawa ba, ko me ake so a yi zan yi. To daman can shi a al’adarsu kunya da kawaice da kara babu ita. Misali a dubi fim xin *Rumfar Shehu* ana bikin suna matar Bosho ta haihu, Jamila (Jamila Nagudu) da mijin nata Shehu wato (Bosho) haka ta fito kanta ba xan kwali tana tiqa rawa da maigidan nata gaban surukai maza da mata ana waqa ana masu liqi a qofar gida. A kalli fim xin *Hadarin Qasa* duk da cewar ana magana a kan illar bariki da dadiro irin

ta’asar da ‘yanmatan fim xin suka dinga nunawa a fim xin, abin ya wuce min sharri, domin ban da fitsara da rashin kunya da zagi ba abin da ya cika fim xin. Matan kuwa sun haxa da Fati Shu’uma da Jamila Nagudu da Maryam Hiyana da Fati Waraka.

3.4.2 Harshe ‘Yan Fim

Harshe shi ne qashin bayan samar da fina-finan Hausa. Domin in babu harshe, babu sadarwa, babu fahimta, kuma babu ji. Don haka harshe babban dirka ne na tantance fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa. A nan, an raba harshen fim zuwa gida biyu:

- Baqon harshe a cikin fina-finan Hausa
- Baubawanburmin harshe a cikin fina-finan Hausa.

Idan aka ce baqon harshe a nan ana nufin shigo da wani harshen na daban wanda ba Hausa ba cikin fim xin Hausa. Misali, Turanci ko Larabci ko Indiyanci ko Yarbanci ko Inyamuranci ko Fulatanci kai tsaye cikin fim, wato hargitsa-balle. A yayin da xan fim ya furta wata magana wacce ba ta cikin farfajiyar harshen Hausa yayin da yake magana a cikin fim, to, tabbas a nan ya sava qa’idar sadarwa ta fina-finan Hausa. Domin, fim xin Hausa na Hausa ne, ya bambanta da fim cikin wani yare na daban. Misali fim xin *Hadarin Qasa* , a lokacin da Rabi ta biyo Ali Nuhu gidansa wai ita lallai tana sonsa, ransa ya yi mutuqar vaci inda ya kore ta da maganganu kamar haka: *Will you get out from this House? Get out! I said get out!!* .

Baubawan burnin harshe a cikin fina-finan Hausa. Wannan yana nufin kalamai da ‘yan fim waxanda ba a furta su bisa qa’idojin sautin Hausa ba. Misali, idan xan fim yana magana, daga

jin harshensa za ka san ba Bahaushe ba ne, an fi samun irin waxanan gwaranci a fina-finan Jasawa da na ‘yan kudancin Jihar Kaduna. Amma fina-finan Hausa ba za a iya canza musu suna ba, duk da hakan fina-finan Hausar za a kira su don ba a canzawa tuwo suna. Akan samu ire-iren waxannan tasgaro na rashin iya ladabin magana da batsa da zagi a harshen ‘yan fim wanda sun sava ma xabi’u da al’adun Bahaushe. Amma shi xan fim ba matsalarsa ba ce, tun da shi a tsarin zamantakewarsa ko qabilarsa ba wani abin kunya ba ne don ya yabawa na gaba da shi magana ko kuma akasin haka. Idan aka kalli gidajen talabijin masu zaman kansu, irin su *Nakowa* da *Tauraruwa* da *African Magic* da *Arewa 24*za a yi ta ganin ana nuna fina-finan Hausa masu magana da harshen Hausa, amma ba Hausa ake yi ba, domin kwavar da gwaranci da ake yi, idan ka ji abin haushi. Wani lokaci idan ka ji kamar ka yanke mutum da mari. Waxannan fina-finai ba sa cikin yankin fina-finan Hausa sai dai a ce fina-finai ne da Hausar gwari ko a ce baubuwan burmin Hausa. Domin daman Bbaubawan burmi a Hausa ana nufin wanda bai ji Hausa ba ko wanda yake ji amma karin harshen Hausar ba ya fita. Idan har ana so, su amsa sunan fina-finan Hausa, sai a dinga zuba ‘yan Hausa, masu Hausa a baka kuma waxanda suke iya sarrafa harshen Hausa. Misali a dubi fina-finan fassara Hausa na *Mr Johnson.*

3.4.3 Kwalliyar ‘Yan fim

Kwalliya na xaya daga cikin wani muhimmin al’amari a cikin rayuwar xan Adam musamman mata. Yin kwalliya yakan qara wa mace kyau. Kwalliya a fagen fim ya bambanta da kwalliya da aka sani na gida. A fagen wannan nazari ana nufin sauyawa mutum kamanninsa na asali zuwa ainihin kamanin da ake so ya hau a mayar da mutum saurayi ko tsoho wannan aikin mai

yin kwalliya ne a fim shi ake kira (*make up*). A wannan nazari kwalliyar na daga cikin hanyoyin da za a iya tantance fina-finan Hausa da fim na Hausa. Dabarar ita ce, kowace al'umma ta duniya tana da yadda takan yi kwalliyarta wanda da zarar an ganta babu tambaya an san qabila kaza ce take da irin wannan kwalliya. A wasu fina-finan Hausar za ka ga ana haska kwalliyar da ta yi hannun riga da al'adar Hausawa. Misali, dubi kwalliyar da ake yi wa Sarki a fim xin *Basarake*.

Babu inda aka tava ganin Sarkin Hausawa ya sanya murjani a wuya da tozali a ido raxa-raxa, ga suma cunkus sannan fadawan kansu babu hula, balle rawani, an yi musu kwalliya da wani roxi-roxin farin fanti a kai. Ga duk wani xan kallo, ya san an keta tsarin al'adar Bahaushe a fada a fagen kwalliya, don haka ba za mu karvi fim xin *Basarake*a matsayin fim xin Hausa ba. Amma idan ka kalli fim xin *Sarki Jatau*, wanda aka xauko labarin daga littafin *Magana Jari Ce*, littafi na biyu, idan aka kwatanta zubin zaman fada da na fim xin *Basarake*, za ka ga lallai fim xin *Sarki Jatau* ya haskaka tsarin al'adar fadar Hausawa kamar yadda aka santa. Don haka, ga duk wani mai son gane fina-finan Hausa da fina-finai da Hausa ya wajaba ya kula da kwalliyar 'yan fim.

Idan aka kalli fim xin "*Zo Ki Ji*" an nuna Sani Danja a matsayin Sarki to amma wai sai ga shi a zaune a bisa karaga yana riqe da "izga" a hannunsa da kuma "murjani" rataye a wuyansa. A Bahaushiyar al'ada ai Sarki ba ya rataya murjani a wuya da wuyan hannu. Wannan al'adar Sarakunan *Igwee ko na Oba* ce, su aka sani da wannan shiga wadda ba ta cikin tsarin shigar Sarki ko ta muqarrabansa a fada. A wata fita kuma, an nuna wasu fadawan Sarkin da aka ma

kwalalliya a kansu, an sanya masu xigo-xigo farin alli a kawunan su, suna sanye da jajayen dogayen riguna, wannan ba ta cikin tsarin kwalliyar bayin Sarki a fadar qasar Hausa.

An fi samun irin wannan shigar a fadojin sarakunan Yarbawa ita ma shigar ta bayin Sarki ce masu yi masa hidima. Mahaifin Sani Danja wanda ba a bas hi wani sun aba face Sarki, shi ne ya rasu a fim xin, inda aka naxa Sani a matsayin sabon Sarki. A cikin fim xin an yi bikin mutuwar Sarki. A lokacin bikin mutuwar a maimakon a ce duka mahalarta taron suna sanye da suturar Hausawa, a'a sai aka sauya musu kwalliya, mazansu da matansu zuwa baqaqen kaya da baqar hula, mata kuma baqaqen kaya da farin xankwali da baqaqen tabarau. A nan, wannan kawlliya ba Bahaushiyar kwalliya ba ce, kuma a xabi'ance Bahaushe yana bikin mutuwa ne bayan ya karvi Musulunci? Amsar ita ce a'a, a dai wannan zamani Kiristoci aka sani da irin wannan kwalliya idan ana bikin mutuwa.

Sauran fina-finan da aka yi ma 'yanwasa kwalliyar ko tsagun gargajiyar Yarbawa da Inyamurai sun haxa da fim xin "*Rumfar Shehu" da "Hindu" da "Birnin Masoya".* Ga duk wani mai nazari fina-finan Hausa, zai ka iya tantance waxannan fina-finai da cewar tana iya kasancewa asalin labarin ba Bahaushen labari ba ne, wanki aka yi da xauraya. Ba a yi wa fim xin kwaskwarima da ta dace ba, ta yadda wataqila da an yi kwaskwarimar yadda ya dace, watiqila da an share duka waxannan varaka da aka gano tun a farkon labarin wataqila da fina-finan sun amsa fim xin Hausa. Kwalliyar da karuwan fim xin *Hadarin Qasa* suka yi ba ta dace da kwalliyar da Bahaushiyar karuwa takan yi ba, a maimakon a yi musu kitso sai aka sa musu gashin doki, wato *attachement.*

3.4.4 Suturar ‘Yan Fim

Kamar yadda Hausawa sukan ce sutura ita ce mutum, Bahaushe bai yarda da qazantar tufafi ba. Domin suturar takan fassara matsayin al’umma da darajarta a idon duniya. Don haka, kowacce al’umma ta duniya tana da irin nata suturar da takan sanya, wadda da ita ake iya fasaltata. Misala, Turawa da Larabawa da Inyamurai da Yarbawa da Tibi da sauransu. A yayin da fim ya saki ainihin suturar Hausawa ya xauki waninsa ya kama na wani, to, anan hukuncin da za a yanke wa fim xin shi ne bai hau qa’idar da ake so ba, ko da an yi da Hausa. Domin, kowacce al’umma takan amsa tsarin suturarta ne a yayin gudanar da fim. A duk lokacin da aka haska kamara aka ce wannan malami ne, to, za a so a gan shi sanye da doguwar riga da hula da carbi har ma da rawani. Ko kuma a ce can makarantar allo ce, amma ba a sanya wa almajiran tufafin da za su fito da su a matsayin almajiran allo ba, sai aka gan su sanye da shat da wando turoza har da zanzaro. Ke nan, suturar ba ta hau yadda ya kamata ba a bisa tsarin suturar da ya dace su amsa sunansu na almajirai ba. Kodayake Al-Kanawy (2005) ya nuna cewar kusan kashi 95 cikin xari na qorafin da ake yi a kan fina-finai yana da alaqa da vangaren ‘yanmata ne, musamman yanayin suturar da suke sanya wa a fim xamammu masu nuna tsaraici. Dalili, kashi 85% na masu kallon fim xin yara da mata ne, don haka mutane suke damuwa. Abu ne mai sauqi a koyi abu mai kyau ko maras kyau a cikin fim xin Hausa, fiye da sauran fina-finai domin shi da Hausa ake yi, saqon na isa ne da Hausa a sami sauqin fahimta, don haka shi ma yaro zai iya aikata abin da ya ga suke yi. Kuma yawanci ‘yanmatan da ake sawa su aikata waxannan abubuwa ba Hausawa ba ne, an dai haife su a qasar Hausa, sun tashi a cikin Hausawa. Kamar yadda aka gani a babi na biyu na wannan aikin an kawo ma’anar tufafi da nau’o’insa na Hausawa. Idan aka dubi tasirin tufafin da aka yi amfani da su a cikin fim mai taken “*Zo Ki Ji*” an sanya sutura wadda ba ta Bahaushe ba. Idan aka kalli

suturar da Ahmed (Sani Danja) da Ibrahim (Baballe Hayatu) suka sanya a shiga ta biyu lokacin da suka shiga gida suna yi ma mahaifiyarsu magana wai suna jin yunwa. Bayan an ba su abinci suna cikin ci sai mahaifiyarsu ta ka da baki ta kalle su, ta ce:

Hajiya: Wane irin kaya kuka sanya haka" wannan suturar ba al'adar mu ba ce kai! Don ka yi zaman legas ne, shi ne za ka koya wa xan uwanka sanya kaya irin wannan?

Haka zalika, Faisal (Ali Nuhu) shi ma ya yi shigar wata riga da ake kira *Bankole*. Suna shirin tafiya gidan Sarki, take mahaifiyar ta ce da shi:

Hajiya: Koma ka je ka cire kayan nan, ka sa suturarka ta gado". Ali Nuhu ya ce; "*Ai wannan xinkin shi ake yayi yanzu shi ne ake kira Bankole ko kice Abuja style Mum.*

Shi ma ya tavo tasirin suturar aro a cikin sa. An nuna Ladidi Tiblas a inda ta fito a matsayin dattijuwa bokanya. Don haka, a matsayinta ta mai irin wannan qarfin tsafi ta yi shiga irin ta manyan matan matsafa, a nan ya dace a yi mata shiga irin na 'yar masu ganye ko in ma bokanyar ce, sai a sanya mata sutura irin ta 'yan bori mata ko masu girka a misali. Amma, sai aka tafi aka sanya mata suturan aro na ;yan kudanci qasar nan. An nuno ta, ta yafa kayan saqi wadda ake kira da "*Aso ofi*", sannan ta xaura wani "*joji*" ta kuma xaura wani farin yadin majanyi wato *ojaa* a kanta ya zuba har kafaxarta kuma jajaye irin na iyamurai. Zubin kayan xakin nata ararriyar al'adace, na kayan saqi masu xauke da kaloli da ratsin ja kamar gidan.

Fim xin "*Gugar Zana da Hargowa*" an nuna inda mijin Sadiya wato Mai Shinku ya sanya kayan "*Leshi*" ruwan toka da hular "*gonga*" a yayin da zai fita gida a inda ita kuma Fati 'Yar Kano ta sanya *Leshi* xinkin "*Buuba*" duka waxannan ararrun suturu ne.

Idan aka duba irin shigar da boka ya yi a fim xin *Birnin Soyayya* ba dai-dai yake da irin shigar Bahaushen Boka ba. Hatta fadawan Sarkin yanayin suturunsu da suka sanya da shi kan sa Sarkin ba ya cikin tsarin suturar Bahaushe, ya za a ce an bafade yana zaune a fada kan sa ba hula balle rawani, an fi samun ire-iren wannan shigar a fadojin qasar Yarbawa. (Hira da Dr. Ayilara). Haka zalika, a fim xin *Hadarin Qasa* matan duka sun sanya wandon *jins* ne da riga an sanya hula hana Sallah.

3.4.5 Kayan Wasa

Abin da ake nufi da kayan wasa a cikin fina-finan Hausa dangane da wannan bincike shi ne, ana nufin duk wasu tarkacen kaya da ake amfani da su a muhalli ko kuma gida yayin aiwatar da fim wanda zai qara fito da ainihin muhallin fim ta yadda zai amsa sunansa, kayan su za su kara qayatar da muhallin yadda ya kamata. Misali, yayin da aka haska gidan attajiri, za a so a ga gidan ya sha zanen makuba da tuntuna da jakuna da dawakai da masu yi masa hidima na kai kawo.

Amma, yayin da aka ce gidan attajiri a cikin fim xin Hausa, za ka ga an nuna gidan zamani na bene *(duplex*), ga motoci jere da wurin wanka na zamani maiamakon rafi (*swimming pool*) da lambuna da shiga fulawowi (*garden*), in har aka tsara fim a haka, to, a nan wannan fim ya karye ba zai amsa sunan fin xin Hausa ba. Sai dai ana iya cewa fim ne da Hausa, muhallin kayan wasa na fage bai amsa sunan yanayin Hausar ba.

Don haka, duk wani fim na Hausa, ya kamata muhallinsa da kayan wasan muhallin na cikin fage su kasance masu nuna Hausa da Hausawa. Kayan wasa a nan ba ana nufin kayan sa wa na tufafi ba, ana nufin *Properties* wato duk wasu kaya da za a shirya su a wata fita da za ta nuna yanayin wuri ya yi qaye a cikin fim (*side attraction*). Misali, a fadar Sarki, akan ga kayayyaki masu ban sha'awa kamar tumtum da karaga da maficin jimina, in kuma a gidan qauye ne za a ga turmi da tavarya da ludaya da qorai da maficin kaba da sauransu. A cikin wasu nau'o'in fina finan Hausa, akan shigo da ire-iren wasu kayan wasa waxanda ba a san al'adar Bahaushe da su ba. Misali, idan aka dubi fim xin *"Ashabul Kahfi"*. An shigo da wani gunki sassaqaqqen sunan sa "*Barbuna*". Wannan abin bauta a kan kira shi "*Masquarade*". Domin akan sa masa wasu abubuwa ne kamar zare masu tarin yawa da safa. Tsari da yanayin yadda aka sassaqa abin bauta *Barbuna* bai yi daidai da tsarin kayan bautar gargajiyar Hausawa ba.

A cikin fim xin "*Basarake*" mun ga nau'o'in kayayyaki da aka jiye kamar gumakan ado a cikin xakin mahaifiyar Sarki, waxanda aka sassaqa su da itace wasu kuma da tavo. A Bahaushiyar al'adar, Bahaushe ba ya ajiye kaya masu xauke da nau'o'in gunki a gida duk da

cewa a da can kafin zuwan Musulunci Bahaushe an san ire-iren bautarsa da ya yi ba sa wuce irin bautar gida da bori da bautar gari kamar yadda aka yi a Kano (bautar Tsumburbura). Amma a iya karance-karance da aka yi babu inda aka ce Bahaushe ya bauta wa gunki sai dai Adamu (2014:128) ya yi magana a kan yadda Bahaushe yake bautar gumaka a wurare daban-daban, ko da yake shi ma ya nuna bautar Tsunburbura abin bauta a Kano. Idan muka kalli fim xin "*Fansa*" an yi amfani da wasu kayan fage na adon gida wadda ba a san al'adar Bahaushe da su ba.

3.4.6Rawa da Waqa

Kixa da waqa na daga cikin wani kaso mai tsoka da yake taka rawa a fina-finan Hausa. Sai dai irin gagarumar taimako da yake takawa a wajen wasu masu kallo abin yabawa ne, kuma cigaba ne a sha'anin shirya fina-finan Hausa. Amma wasu kuma suna ganin ai rawa da waqa ba su da muhalli, a al'adar Hausawa. Dalilin idan aka dubi yadda mata da maza samari kan gwamutsu ana rawa a cikin fim, lallai a ce akwai alamar tambayar idan aka yi kallo irin kallo na kunya da kawaici a al'adar Hausawa. Ko da yake, an nuna cewa tasirin kallon fina-finan Indiyawa da suke nuna rawa da waqa wanda Hausawa suka saba da su yana daga cikin musabbabin shigo da rawa da waqa zuwa cikin fina-fina Hausa. (Gandu, 2006:88).

An san Hausawa suna kixa da waqa a tsarin rayuwarsu. Amma tambayar a nan ita ce, yaya tsarin kixan Hausawa yake, kuma mene ne muhallinsa a al'ada? A duk lokacin da aka nuna rawa da waqa na kalangu, ko na tauri ko na bori a cikin fim, na san wannanal'adar gargajiyar

ce irin ta Bahaushe. Amma a duk lokacin da aka nuna dandazon mata da maza ana kixan *fiyano ko keyboard* ana gagarumar taimako*solo* a cikin fim, xan kallo zai ce wannan ba al'adar Bahaushe ba ce, amma fa duk da an san al'adun zamani sun yi tasirin sosai a harkokin shagulgulan bukin hausawa a cikin wannan qarni.. A yayin nazarin tantance fim na Hausa ko kuma fina-finai ne da Hausa, ya wajaba a duba shin fim xin wace iren rawa da waqa aka aiwatar? Idan suna kan turbar al'adar Bahaushe, za a iya cewa fim xin yana kan tsarin fim xin Hausa. Amma idan ya faxa bisa tsarin waqoqin wasu qabilu maqwabtan Hausawa, da waqoqin zamani to sai a ce akwai kwaskawarima ko aron tsarin wasu al'adu da xabi'un wasu al'umma a cikin fim, amma a sani cewar an dai yi amfani da harsher Hausa wajen isar da saqon fim ne kawai. Don haka, wannan fim an dai yi shi ne da Hausa amma ba na Hausa ba ne. A duk lokacin da aka cika sanya raye-raye na wasu qabilu maqwabtan Hausawa a cikin fim, to lallai a binciki fim xin. Zai iya kasancewa asalinsa kwafo shi aka yi, ko kuma labarin fim xin ba shi da tushe da Hausa, wanko shi aka yi daga wata nahiya. A tsarin shirya fim akan shigo da sautuka don a nuna wani yanayi da ake ciki ko a tabbatar ma da xan kallo ai yanzu ana wata nahiyar ne ko qasa ta daban. Idan an tashi daga qasar Hausa zuwa qasar Hausa Inyamurai ne. To sai a saka sautin rakiyar taken qasar Inyamurai, wato za a xauki kixa ko waqar Iyamurai a sanya shi a bisa fitowar bayan an kawar da amon 'yan wasa sai a ga hoto da aiwatarwar ana bi kawai. Misali, jirgin sama ya tashi da xanwasa zuwa qasar Indiya, domin a nuna ya sauka a qasar Indiya, sai a sanya sautin kixa ko wani amo da zai nuna wa xan kallo yanzu jirgin da ya xauko xan wasa daga Nijeriya zai sauka ko ya sauka a Indiya. Wannan shi ake kira "*Sound Narration*" ko kuma a kira shi da "*Sound Track*".

An ba da misali daga wani fim mai suna "*Naira*" an nuna wani xansanda wanda ya yi kuxi ta hanyar al'mundahana, nuno shi da aka a yi, kawai sai aka gan shi yana tuqa wata babbar motar alfarma tare da rakiyar kixan da waqar *Olumide* wani mawaqi daga cikin mawaqan zamani na jihar Legas. Wannan waqa ararriya ce, in ma ana son sanya waqa a fim ne duka ximbin waqoqin Hausa da muke da su a rasa wanda za asa a fim xin Hausa ,sai waqar Olumide?Ko da yakeUmma Aminu Inuwa (2009) ta ce, ta vangaren kayayyakin kixa akwai dangantaka mai qarfi tsakanin waxannan al'ummomin guda biyu wato Hausawa da Yarbawa ta fagen kayan kixa. Ta kafa hujja a da dalilin kusan kayayyakin kixansu akan samu tasirin kayan kixan wata al'umma a cikin wata al'umma kamar kalangu da ganga. To, a nan wannan bincike ya gano akwai wasu kayan kixa waxanda asalinsu ba a san Bahaushe da su ba. Binciken Gusau (1988) ya zayyano nau'o'in kayan kixan Hausawa na gargajiya. Sannan a cikin wani aiki nasa Gusau (2010), sai ya qara fito mana da tasirin zanananci a cikin kayan kixan Hausawa wadda suka aro daga baqi da kuma makwabtan Hausawa. Don haka, wannan bincike ya gano cewar wasu daga cikin gangunan da aka yi amfani da su a cikin fim xin "*Ahlul Kitabi"* aro su aka yi. Misali, an nuna wani wuri da ake bautar gargajiya inda wani daga cikin jagora matsafan ya ajiye wata doguwar ganga ana dukanta da hannu dum-dum! Wato *"gangan" ko "Omele*" waxanda aka yi amfani da su a cikin fim xin *Ahlul Kitabi.*

3.7 Kammalawa

Wannan babin ya yi hovvasar ganin an warware tare da zayyano hanyoyin da aka bi wajen tattaro bayanai da tace su. Wato sun haxa da tattaunawa da masana adabin fim. Haka zalika an yi tattaki zuwa jahohi da ke da ruwa da tsaki a harkar shirya fian-finan Hausa a inda aka gana

da malaman jami'o'i damasu ruwa da tsaki a harkar shirya fim. A xaya vangaren kuma, an nuna yawan bugaggun tambayoyi da aka rarraba tare da lissafo yawan makarantun da aka rarraba su domin cika guraben da ake neman bayanai daga masana. An kuma yi sharhin kowacce tambaya dangane da kason maki na waxanda suka amsa tambaya. Bayan haka an yi sharhin tambayoyin bincike, sai aka zayyano mashigai na mizanin tantance fina-finan Hausa ko kuma fina-finai cikin Hausa na cikin fage da na bayan fage dangane da sifoffinsu da yanaye-yanayensu.

BABI NA HUXU

YANAYI DA SIGOGIN FINA-FINAN HAUSA

6.0 Gabatarwa

A wannan babi za a yi amfani da wasu dabarun nazarin fina-finan Hausa domin yin taciyar fina-finai da Hausa da kuma fina-finai cikin Hausa. An yi amfani da manyan turakun nazarin fim wajen tantancewar, waxanda suka haxa da nazarin zubin fim da jigon fim da harshen ‘yan fim da tufafin ‘yan fim da kuma uwa uba halayyar ‘yan wasan (‘yan fim).An raba babin zuwa kashi biyu, kashi na farko, an xora fina-finai cikin Hausa a bisa hanyar nazarin fina-finai tayin nazarinsu a matsayin fina-finan Hausa. Sannan kashi na biyu, ya qunshi nazarin fina-finan da aka yi su da Hausa, amma wannan bincike yana ganin ba na Hausa ba ne, domin yanayin yadda aka aiwatar da su ba sa wakiltar Hausa da al’adunsu.

Wannan babi ya rattabo fina-finai waxanda binciken ya zavo, domin a nuna matsayin fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa a fagen nazari. Binciken ya zavo fina-finai guda goma waxanda aka raba su gida biyu, dangane da matsayin tantance su. Wato fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa. An xauki waxannan fina-finai xaya bayan xaya aka nazarce su tare da fito da dalilan da suka sa suka kasance a gurbin da aka yi musua cikin aikin. A taqaice an yi bayanin kowanne fim dangane da mashiryansa (kamfani) da lokacin da aka yi

shi, da bayanin dukkan masu ruwa da tsaki wajen shirya shi ma'ana 'yan bayan fage a fim xin.A qarshe sai aka yi bayanin fim xin a jimlance, sa'annan aka xauki kowanne fim aka xora shi a mizanin nazari domin ana fata hakan ne zai ba da damar tantance fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa. An fara da bayanin fina-finan da za a iya cewa fina-finan ne cikin Hausa saboda sun xauko siffa da yanayin irin na al'adun da xabi'un Hausawa.

Fina-finan da ake fata za sun amsa sunan fina-finan Hausa, a cikin wannan aiki, sun haxa da fim xin *Bori da Juyin Sarauta da Qafar Ungulu da Na Hausa da kuma Malam Zalimu*.

4.1Tsokaci A Kan Fina-finan Hausa

An yi tsokaci a kan waxannan fina-finai ne domin a fito da bayanin abin da kowanne fim ya qunsa a matsayin matshiya:

4.1.1 Bayanin Fim *Xin Bori*

Fim ne wanda Umar A. Umar wanda aka fi sani da Mai Jalingo ya shirya a garin Zariya a shekarar 2014, kuma Falalu A. Xorayi shi ya ba da umarni. Kamfanin *M.J Video Palace* da ke kan titin Fak, Zariya ya xauki nauyin samar da shi. Fim ne wanda ya ke nuni a kan aladar Bautar Hausawa ta gargajiya tun lokacin Maguzanci, Kodayake fim xin ya fi karkata a kan al'adar bori. An faro fim xin da labarin Ibrahim Sarkin Bori wanda aka nuna ya mutu tun farkon fim xin. Don haka sai taqqadama ta harqe tsakanin 'ya'yansa a kan wanda zai gaje shi.

Daga cikin ‘ya’yan marigayi Sarkin Bori akwai Jaada (Ibrahim Xandolo) da Rabilu Musa (Ibro) da Xan Bori (Sulaiman Bosho) da kuma Wakilin Sarkin Bori (Sani Xan Gwari)waxanda dukkaninsu suke jiran wannan sarauta.

Waxannan magada masu jiran gadon sarautar, Sani Xangwari ya fi cancantar ya gaji Sarkin Bori, domin shi ya yi ta nuna bajintar borin gaske a lokacin da aka kira su fili bori ana gwada qwarewar kowannensu. Wato fim ne wanda aka yi amfani da ainihin suturun ‘yan bori da kixan borin da kayan bori da nuna muhallin bori da harshen ‘yan bori da kuma halayyar ‘yan boriwanda aka kwaikwaya kamar yadda aka saba gani a rayuwa ta zahiri. An nuna yadda ‘yan bori sukeyi idan sun hau bori, wato yadda suke sauya kama idan wani Iska yahau su, kamar Iskoki irin su Soja da Baturiya da Sarkin Malamai da Rabi Mahaukaciya da Sarkin noma da sauran su. Fim ne wanda yake nuni da cewar kowa ya bar gida, gida ya bar shi. Duk da an san bori al’adar Hausawa ce tun fil azal, sai da zuwan Musulunci ya rage tasirinta ga al’ummar, dominhaka a iya cewa wannan fim wanda ya taskace al’adar bori da matsayinsa a wajen Bahaushe.

4.1.2 Bayanin Fim Xin *Juyin Sarauta*

Juyin Sarauta fim ne wanda kamfanin *Ramat Productions Limited* da *DogaraiQuarters Women Film L.t.d.* suka shirya a shekarar 2016 a garin Kano. *Juyin Sarauta* shiri ne da aka yi shi bisa tsari, tun daga qirqirar labari a kan masarautar qasar Hausa. Quduri da burin*Juyin Sarauta* shi ne ya kawo sauyi inda mai kallo zai samu gamsuwa a fagen ilimi da kuma

nishaxantuwa. Wannan burin ne ya sa Balaraba Ramat Yakubu, ta tsaya tsayin daka har shekaru uku domin tabbatar da cewa an fito da fim mai nagarta da aminci wanda zai wakilci Bahaushe a ko'ina yake a duniya.Wanda ya ba da Umar umurni fim xin shi ne Falalu A Xorayi.

Hikima da basira da kuma sanin makamar rubutu da Balaraba Ramat Muhammed ta yi a wannan labarin na Juyin Sarauta ya jawo hankalin manazarta da kafofin yaxa labarai masu bibiyar al'amuran Hausawa a sha'anin adabi da al'ada musamman rayuwar mata, matan aure da kuyangi da qwarqwarori da suke gidajen sarauta qasar Hausa.

Saboda haka aka gwada yadda iyalin Sarkin Jadarwa Yusufa, (Ado Gidan Dabino)(lokacin da tsufa ya cim masa) suka shiga faxi tashi kowacce na nema wa xanta ya zama sarki. Mata suka shiga kamun qafa a wajen 'yan majalisar Sarki da Fadawa da manyan bayi. bayan zuwa wajen bokaye da 'yan bori da kuma malaman tsubbu. Amma daga qarshe aka warware taqqadamar ta hanyar ilmi da zaven mutum mai nagarta da riqon addinin Musulunci da kuma hazaqa da kuma taimakon marasa qarfi, wanda ake ganin shi ne zai zamo shugaba na qwarai.

4.1.3 Bayanin Fim Xin *Qafar Ungulu*

Qafar Ungulu fim ne mai qunshe da al'adun Hausawa a fagen tafiyar da sha'anin mulki,wato yadda ake gudanar da mulkin sarautar Hausawa ta gargajiya a tsanake. Wanda ya shirya fim

xin shi ne Sulaiman Abubakar, sannan Muhammad Sani Galadima shi ne ya tsara labarin Mansoor Sadiq ya ba da umarni, sai Garba Sale (Braza) ya xauki nauyi. Fim ne wanda kamfanin *Flying Bird Productions* suka samar da shi a shekarar 2004 an yi aikin fim xin a garin KundumJihar Bauci.

Fim xin *Qafar Ungulu* kamar yadda aka fara bayani a baya, an gina shi a kan tsarin mulkin sarautar Hausawa ta gargajiya. Amma shi bai xauki salon fim xin *Juyin Sarauta* ba, wanda ake ta taqaddama a kan cewa kowacce uwa tana son xanta ya gaji kujerar mahaifinsa. Shi fim xin Qafar Ungulu an tsara shi domin a nuna al'adar Bahaushe ta iya tafiyar da harkokin mulkin al'umma tare da jan ragamar al'amuransu a bisa gaskiya da riqon amana. Sannan fim ne da yake nuna cewa Bahaushe yakan girmama na gaba da shi tare da nuni da cewar masarautar qasar Hausa suna qarqashin kulawar Gwamnati ne, a duk lokacin da aka naxa sabon sarki dole ne sai sarkin ya yi mubaya'a da Gwamnati. Sannan kuma in an sami akasin na rashin jituwa a masarauta ko gunduma, ana fata za a kai rohoto gaban Sarki domin a yi sulhu.

4.1.4 Bayanin Fim Xin *Na-Hauwa*

Fim xin Na-Hauwa fim ne wanda kamfanin *Meenah Investment* suka samar da shi. Wanda ya tsara labarin shi ne Kabiru Ali, wanda ya xauki nauyin shirya fim xin shi ne Zahradeen Malami tare da taimakon Kabiru Ali. Daraktan Fim xin kuwa shi ne Aminu S. Bono. An shirya fim xin a garin Xan Zakara, a jihar Kano a shekara 2016. Fim ne wanda Falalu A.

Xorayi ya fito a matsayin Na-Hauwa ita kuma Jamila Nagudu ita ce mata tasa wato Hauwa. Amma duk tsawon shekarun da suka kwashe a matsayin mata da miji babu haihuwa. A al'adar Bahaushe kuwa duk matar da ba ta haihuwa ana mata kallon ita juya ce. Don haka hankalin mahaifiyar Na-Hauwa ya tashi matuqa. Har ta kai ga nema masa auren wata yarinya daban wato Atika. Zama ya zo ya rincave daga baya, domin an yi ta samun savani tsakanin Hauwa da Atika da kuma suruka, wato Aisha Xan Kano, a qarshe duk lokacin da ranar girkin Atika ya zo, Na-Hauwa ya dinga Allah Allah gari ya waye ya koma xakin Hauwa domin ita ce rabin ransa.

Allah ya taimaki Atika ta sami juna biyu. Amma sai dai kuma kash! Ta haihu xan da aka haifa ya koma. Ana cikin haka sai Allah ya sa ita ma Hauwa ta samu juna biyu wanda Allah ya amsa addu'arta ta haifi yara uku lokaci guda. Duk da daman can ita Atika da ta haifi xa xaya ance ba za ta sake haihuwa ba, domin ta gamu da larura a mahaifa ba za ta iya xaukar juna biyu ba.

A taqaice dai fim xin yana son ya nuna cewar duk abin da Allah ya tsara wa bawa, a cikin rayuwar xan Adam sai ya bi shi. Sannan a dinga rungumar qaddara. Atika wadda Inna ta aura wa Na-Hauwa ga shi ta sami matsalar mahaifa, Hauwa kuma da aka ce juya ce, sai kuma ga shi Allah ya ba ta juna biyu ta haifi 'yan uku. Sannan fim xin yana gargaxi ga iyaye mata su daina muzgunawa 'ya'yansu maza da takura musu a kan lallai sai sun qara aure, aure-auren ba shi ne zai sa samun jikoki ba. A daina biye ma zuciya da sharrin shaixan na lallai sai an tara zuri'a.

4.1.5Bayanin Fim Xin *Malam Zalimu*

Fim xin *Malam Zalimu* fim ne da ake ganin yana cikin rukunan fina-finan da aka yi su cikin Hausa. Domin idan aka kalli labarin fim xin, an xauko shi ne daga qagaggen labarin littafin *Malam Zalimu* na Ado Ahmad Gidan Dabino wanda aka buga shi a shekarar 2009, ya ci gasar tunawa da Injiniya Bashir Qaraye.

Abba Almustapha ne ya nemi izinin marubucin littafin aka mayar da shi fim. Kamfanin *Jaga World* su ne suka samar da fim xin da haxin gwuiwar Abba Al-Mustapha Movies a shekarar 2011. Wanda ya xauki nauyin shirya fim shi ne Abdulaziz xan *Small*, sa'annan Kamal S. Alkali ya ba da umarni fim xin a garin Kano.

Taurarin fim xin mutane biyu ne wato Malam Zalimu (Ibro) da kuma Abba Al-Mustapha wanda ya fito a matsayin *Alaramma*. Kalmar Alaramma asalinta daga harshen kanuri ne, kuma tana nufin mutum makarancin Al'aqur'ani An nuna al'adar Bahaushe irin yadda yake neman ilmin karatun Al-qur'ani a tsangaya da kuma yadda ake tafiyar da karatun allo a qasar Hausa. Babban abin da ya fi mamaye fim xin daga qarshe-qarshe, shi ne fito da yadda idan gardi ya riqa a gari, to, ba ya son ya ga wani ya xara shi. Sai dai a ce duk wani abu da za a yi a garin to shi ne a gaba, idan kuwa mutum ya kuskura ya ja ragamar sallah ko raxin suna ko xaura aure da wurin addu'ar mutuwa a garin don yana ganin shi ma Malam ne, in har ba Malam Zalimu ne ya je ya aiwatar ba, to lallai kashinsa ya bushe. Don zai yi wuya in ba a nakasa shi ba. Sai dai in ya yi maza ya nemi tuba ko kuma ya yi a kan bai sani ba.

A kwana a tashi sai ga wani Alaramma ya sauka garin Bilwa, wato Abba ke nan, rashin sani ya sa shi jan sallah domin ranar malam Zalimu ya makara, kafin yamma Alaramma ya zama kurma sannan ba ya tafiya dai-dai. Malam Zalimu ya nuna masa qarara shi ne ya maida shi hakan, in kuma yana da wani abu da zai yi sai ya yi a gani.

Alaramma ya je ya yi ta yi wa kansa magani har Allah ya ba shi lafiya ya warke, da ya warke sai ko ya xauki anniyar sai ya rama, kuma masu iya magana sun ce ramuwar gayya……. Nan fa aka fara gabzawa, Alaramma ya ce to, da wa Allah ya haxa shi ko, in ba da Malam Zalimu ba. Nan fa shi ya kama Malam Zalimu ya mayar da shi biri. Aka kama Malam Zalimu ranga-ranga sai bakin kasuwa, can aka dinga wasa da shi ana samun kuxin.

Wato fim xin yana nuni da abubuwa guda biyu: idan za ka gina ramin mugunta gina shi gajere kamar yadda muka ga ta faru a kan Malam Zalimu. Sannan an nuna yadda ainihin gardawa waxanda suka karantu sukan yi wa junansu jifa da sihiri. Abu na biyu, an nuna wasan gardanci a matsayin wata al’adata Bahaushe. Dama an san wasan irin na gardawa sukan zagaya gari-gari ko kuma kasuwa-kasuwa suna wasa da kura da biri da kada da maciji suna ba da magani ana ba su sadaka. Ibro da aka mayar da shi biri, shi ma ya faxa cikin dabbobin da aka yi wasan gardawa da su.

4.2 Tsokaci KanFina-finaiDa Hausa (Ba Al’adar Hausa Ba)

Kamar yadda aka yi bayanin a kan waxanccan fina-finai waxanda ake ganin zubinsu da yanayinsu da halayyar ‘yan wasan ya yi dai dai da al’ada da xabi’un Hausa tun daga tushen labarinsu har zuwa yanayin aiwatar da su. To haka a nan za a kalli yanayin da muhallai da zubi da tsarin labarin fina-finai da ake ganin ba na Hausa ba ne, kuma idan aka kyautata lura za a ga fina-finan asalinsu da kuma inda aka samo labarin fina-finai ba na Hausa ba ne, kuma ba sa wakiltar Hausa ko da an kalle su. A nan ma an taqaita, an kawo misali daga fina-finan *Gwaska da Ibro Hotiho da Qara’i da Su Ma Mata Ne da kuma Doya da Manja.*

4.2.1 Bayanin Fim Xin *Gwaska*

Fim ne wanda yana daga cikin fina-finan da ake jin an yi su da Hausa na kamfanin *Prince Zango L.t.d.* Wanda ya shirya fim xin shi ne Falalu Xorayi, sa’annan wanda ya ba da umarni shi ne Adam A. Zango, fim ne wanda ya fara fito wa a shekarar 2015 ya kuma ci gaba da yin tasiri a cikin sabon tsari na Gwaska *returned*Gwasaka ya dawo a shekarar 2017.

Babban jarumin fim xin shi ne Gwaska wato Adam Zango, yana da wasu gungun matasa abokan tafiya wadda su qudurinsu su farma duk wani mai kuxi wanda ba ya taimakon al’umma da arzqinsa.Wasu lokuta sukan kai farmaki zuwa ga jami’angwamnati wai lallai sai sun yi wa talakawa adalci amma fa ga waxanda ba sayi wa talakawa adalcikawai.

Gwaska dai ya addabi mutanen garin Kaduna domin yakan faxa gidan gwamnati a rasa ta ina ya shiga, sannan har ta kai ya hallaka wani babban malami a garin saboda an ce malamin ya fito kafafen yaxa labarai yana faxin cewar Gwaska xan ta'adda ne. Gwaska yana abin da ya ga dama har ta kai ya shiga gidan Minista ya yashe gidan karkaf. An zuba 'yan sanda na ciki da masu sa kaya su kamo Gwaska amma ya gagare su. Har ta kai mutanen garin Kaduna sunyi zanga-zanga cewar Gwaska ya addabe su kuma ya kashe babban malamin garin. Wato fim ne wanda aka xauke shi daga fim xin Indiya na Kirish, domin yadda Gwaska ya dinga amfani da bindigogi da manyan makamai abin ya wuce misali, wato yanayin shigar shi tauraron da muqarrabansa za ga an ya savawa al'adar Bahaushe.

Su ma jam'an tsaro baa bar su a baya ba wajen tofa alabarkacin bakinsu a kan yadda suke kallon Gwaska. Sun ce Gwaska ba mutumin kirki ba ne, xan ta'adda ne, domin har ta kai ana faxin in ana tunanin Gwaska a matsayin xan qaramin qwaro ya wuce nan.In kana tunaninsa a matsayin xan qaramin vera ya wuce nan.In kana tunaninsa a matsayin xan qaramin zaki ya wuce nan, Gwaska zaki ne, kuma ingarman zaki, a ankare yake yana amfani da qwaqwalwarsa.Shin al'ada Bahaushe ta yarda a yi wa mutum irin wannan shaidar? Kuma a cikin fim xin Hausa?

'Yan sanda irin su DSP Abu Sarki da *I.G. P* da Gwamna da Minista duka Gwaska ya hana su saqat, domin yakan yi shigar da ba a iya kama shi ko da ya je ya aikata fashin ko kuma qwace dukiyarsu. Har ta kai *I.G.P* yana faxawa 'yan sanda wai mutum xaya ya gagare duka jami'an tsaron na gwamntai shi Gwaska sipirit ne?

Wato fim ne da ya qayatar da ‘yan kallo a dai-dai lokacinsa, wato yayin da fina-finan Hausa suke raja’a a kan jigon soyayya da rigingimun auratayya tsakanin miji da mata na aure. Saishi wannan furodusa na Gwaska ya yi tunanin yin warki da xauraya a fannin fina-finan Hausa. Wato ya xauko yadda jaruntar take fina-finan Indiya ya mayar da shi fim xin Hausa. Yawancin waxanda suka taka rawa a fim xin ‘yan Jos ne irin su Lilisko da M.B Jos da Oshere, da shi kansa Adamu Zango da su Hauwa Maina daga Kaduna da su Baban Mulika da su Obinna. Fim ne wanda shigarsa da tsarinsa da muhallin da aka yi amfani da shi za mu iya cewa baifito da al’adun Hausawa ba, don haka wannan bincike yana ganin fim xin Gwaska ba ya cikin jerin fina-finan Hausa amma dai za a iya cewa fim ne wanda aka yi shi da Hausa. Fim ne wanda ya fi maida qarfi wajen nuna tsarin rayuwar Turawa da na Indiyawa.

4.2.2 Bayanin Fim Xin *Ibro Hotiho*

Fim ne wanda *M.J .Video Palace* da ke Zariya suka shirya, furodusan fim xin shi ne Umar Mai Jalingo, wanda ya ba umarni Falalu A. Xorayi a shekarar 2012. Rabilu Musa (Ibro) shi ne jarumin wajen wanda ya sami timako irin su Hudu mai Sinima da Sani Xangwari da Hadiza Kabara da Yusuf B.Chinedu da Rabi’u Daushe da kuma Aisha Zaria.

Shi dai Ibro mutum ne wanda Allah ya sanya masa qaunar kallon fina-finan Indiya, wanda sanadiyyar son da yake yi wa fim xin Indiya har yake qaunar ya tafi qasar Indiya domin ya

sadu da jaruman Indiya.Kullum in yana taxi babu maganar da take fito daga bakinsa sai Indiyanci da batun shi yana so ya je ya ga Hema Malin da su Shashikafur da sauran manyan jaruman Indiya. A taqaice suka yanke shawara da abokinsa Daushe su tafi wurin Shitu mai gidan Siliman da sukan je kallo kullum dare, don ya yi musu jagora zuwa birni watakila su yi dace tafiya, Daushe ya zuqe ya bar Ibro Hotiho,. Ibro ya sayar da duka kadarori ya nufibirni, aka yi sa'a aka haxa su da Baban Cinedu wanda shi ne zai yi masa hanya zuwa Indiya.

A qarshe Ibro ya ci da zuci, ashe ana ta gwada shi ne ko zai iya riqe amana ko ba zai iya ba a nan gidan da ya sauke, wato xauke-xauke ya dinga yi musu a gidan Baban Cinedu. Ya qaraci buge-bugensa a birni, tafiya Indiya ba ta yiwu ba, domin sun samu savani da ubangidan nasa Baban Cinedu wanda shi kuma ya kore shi. Ita ma matar Ibro da ta jira mijinta shiru-shiru bai dawo ba, sai ta bi sahu, ta yi ta cigiyarsa a birni har Allah ya sa ta tsince shi a kan layi kwance an buge shi ya faxi sumamme cikin saura a sanadiyyar kwartanci da ya je ya yi a wani gida. Ashe gidan Baban Cinedu xin ma haxama da xauke xauke da ya dinga yi ya sa aka kore shi. Ibro ya tashi a tutar babu, ba shi ga tsuntsu ba shi ga tarko. Nan gida ya sayar da kadarorinsa ya yi guzuri zai tafi Indiya, ya kuma dawo gida babu makama. Fim xin Hotiho daga jin sunansa an san ba Bahaushen fim ba ne, an aro sunan ne daga fim xin Indiya na Hotohi wanda aka nuna a sinima da dama a arewacin qasar nan tun daga daga shekarar 1983.An xauko wasu sunaye wadda ba a sauya su ba a haka aka bar shi. Sai dai qarin da aka yi na sa sunan tauraron fim xin Ibro a matsayin Hotiho, wato Ibro Hotiho. Har wa yau, duka wasan an gina shi ne a bisa rayuwar Indiya da al'adunsu a maimakon na Hausa, waxanda suka taka rawa a fim xin Hausawa ne kamar yadda aka nuna. Amma kayan cikin fim xin tun daga sutura da harshe da xavi'ar 'yan wasa ba sa nuna al'adar Hausa.

4.2.3 Bayanin Fim *Xin Qara'i*

Fim xin Qara'i yana cikin sahun fina-finan da aka samar cikin shekarar 2013. Wanda kamfanin *Garga Production* suka yi shi kuma Rabi'u Garga shi ne furodusa, sannan Taye Hassan Giggs shi ya ba da umarni.

Fim ne wanda aka gina shi a kan wasu dattawa uku wato Halliru da Lado da Barau, su dai talakawa ne, amma sai Allah ya yi musu gyaxar dogo, suka gamu da wani Alhaji a inda suke zaman kashe wando ya ba su jarin kuxi naira dubu xari biyar kowannen su. A maimakon su ja jari kowa ya kama sana'ar da yake so, sai suka yi shawara wai zamanin da suke yara matasa ba su yi rayuwar matasa ba don babu kuxin holewa na rayuwar samartaka, don haka sai suka yanke hukunci su yi qara'in waccan rayuwar da ba su yi ba lokacin da suke matasa. Suka kwashi qafa, sai gidansu wani tantirin xan bariki Sani Sauti, kai daga jin sunansa Sani sauti, ka san da magana. Sani Sauti ya koya musu yadda za su yi shiga irin ta Turawa da tafiya da kalamai 'yan zamani da rawa da zuwa gidan disko da neman mata da shan sigari da kuma qin mayar da hankali wajen sallah a kan kari. Waxannan munanan xabi'u da dattawan suka xauka ya canza tunaninsu suka koma yin rayuwar irin ta Turawa.Har ta kai ga hatta abinci ma sai dai a tafi gidajen abinci na zamani wanda akan kira su da *fast food*. Bayan wasu 'yanwatanni kuxin suka qare, motar da suka haxa kuxi suka siya wacce ake gayu da ita, ita ma aka sayar da ita, abinci babu a gida, kuxin makarantar yara an kasa biya, ido ya raina fata. Da kansu babu shiri da suka ji wuya suka dawo wajen malamin da yake ta gargaxinsu da su daina munanan

xabi'un da suka sa kan su ciki, su tuba suka qi, wai don Allah yanzu sun shirya za su bari. Wato bari ba shegiya ba ce. Fim xin ya xauko salon wani fim xin qasar inyamurai mai suna *Re-birth*. An wanko shi ne aka mayar da fim da Hausa. Domin idan aka kalli suturan 'yan wasan da muhallansu da kalamansu da xabi'unsu, musamman manyan jaruman fim xin za a iya cewa bai yi dai-dai da xabi'un Hausawa ba.

4.2.4 Bayanin Fim Xin *Su Ma Mata Ne*

Fim ne wanda aka yi a shekarar 2015, kamfanin *Uzee Concept* suka shirya shi, qarqashin mai ba da umarni Umar S. Kofar Mazugal. Amma kamfanin *U.K Entertainment* ya xauki nauyin fitar da shi.

Fim ne na haxaka wanda rabin sa an yi a jihar Legas da kuma birnin tarayya Abuja. A farkon fim xin an nuna Alhassan Kwalle yana da matarsa, hatsaniya ta haxa su har ya sake ta, ya kore ta gada gadansa a tsakar dare, ta kuma bi daren da fita gida a cikin birnin Legas a inda suke da zama shi da iyalinsa, an nuna ya dinga dukanta da belt, sannan ya kore ta , ta fita gida da 'yarta a hannu , ya bi ta ya qawace 'yar. Tana cikin tafiya tsakar dare sai ta yi kicivis da wasu mutane, ashe mutanen nan masu bautar tsafin Yarbawa ne wanda aka fi sani da "*Oro*". A bisa tsari kar a manta Yarbawa suna da wata al'adar bautar tsafi da suke yi shekara-shekara wadda har kwanan gobe suna yin ta, sukan kira ta da "*Oro*" kuma a dokar ba a yarda duk wata mace

ta yi ido biyu da su ba , in ko har hakan ta kasance to za a fille mata kai, kuma ta zama abar tsafin na wannan shekarar.

A garin neman tsira sai wanann mata ta faxa hannun matsafan Yarbawa, waxanda suke bautar ‘Oro” a wannan daren. Duk mutanen gari kowa yana kulle cikin gida, can sai ga matar Zahra ta yi kicivus da Yarbawan take suka fille mata kai suka sa kan cikin wani qoqo. Sanadiyyar haka rigima ta varke tsakanin Hausawa mazauna Legas da matasan Yarbawa, aka yi kare jini biri jini, aka qona dukiya da asarar rayuka da dama.

Fim xin ya nuna yadda Hausawa mazauna Legas sukan yi rayuwar bariki da zama gidan dandi, da irin gagarumar taimako da ‘yan daudu sukan taka a gidan magajiya da na karuwai. Ado Gwanja shi ne ya fito a matsayin Xan Daudu, sa’annan Ladidi Tubless ita ce ta fito a matsayin Magajiyar Karuwai. Sauran matan gidan akwai su Hauwa Waraka da ‘Yar Lubus da su *BabyNice*.

Daga baya sai fim xin ya karkato garin Abuja gidan wani mai kuxi Alhaji kuma mahaifin Al’amin. An nuna *Baby nice* ta bar Legas ta koma Abuja gidan su Al’amin tana yi musu girki ana biyanta, ashe itace yarinyar da ta tava yi wa Al’amin fashi lokacin da yake bautar qasa a Legas. Da ya gan ta a gidansu bayan ya dawo daga qasar waje tunda shi yakan yi tafiya lokaci-lokaci, sai bai nuna ya gane ta ba. Ya bi ta hankali har ya gano, larura ce ta sa yin aika-aika da ta yi masa, har ta faxa bariki. Ashe ita ce “bebi nice” xiya ga Alasan Kwalle wacce aka kashe uwarta a Legas. Kuma a qarshe dai an binciko danginta aka xaura musu aure da Al’amin.

4.2.5 Bayanin Fim Xin *Doya da Manja*

Fim xin *Doya da Manja*an yi shi ne a qaramar hukumar Sabon garin Zariya, kamfanin *M.J Vedio Palace* suka fitar da shi shekarar 2017 a qarqashin furodusa Umar Mai Jalingo, sa'annan wanda ya ba da umarni shi ne Falalu A Xorayi.

To da jin an ce doya da manja an san an haxa wasu abubuwa ne guda biyu wanxanda akesa rai ba lallai ne su zamana su zauna da daxi ba. Fim xin *Doya da Manja* fim ne wanda aka shirya shi domin a qulla zumuncin aure tsakanin al'ummar Hausawa da kuma Yarbawa. Sannan an kuma jingina wani sashe na fim xin da nuna yadda 'yan siyasar zamanin suka yi wadaqa da dukiyar al'umma wanda bayan sun bar kujera, sai ido ya raina fata,Haka kuma, an nuna yadda jami'an tsaro na 'yan sanda da hukumar da take hanawa tare da hukunta masu yiwa dukiyar qasa ta'annati suka dinga farautarsu. Da suka ga sabuwar gwamnati da aka kafa qasar tana son kama su ta hukunta su, sai suka koma ga boka domin ya agaza masu don kar ma a neme su, balle a kama su. Boka ya ce sai a zo da mace fara da ita za a yi asirin. Suka yarda, aka sa 'yan daba da sara suka su nemo mace fara budurwa, suka sami wata mace suka buge ta, ashe Bayarabiya ce mai suna Fasila, a kan hanyarsu ta zuwa gidan Boka, suka yi gamo da 'yan sanda masu binciken ababen hawa, ana cikin bincike sai aka ganta sun danne ta da buhuhunan harawa. Babban jami'in 'yan sanda da ke wurin Bahaushe ne, kuma sunansa Balarabe. Da dai suka ga suka ga kama su za a yi suka ranta cikin na kare aka kuma cafke na cafkewa saura suka gudu.

Bayan an yi bincike aka gano ashe waxancan ‘yan siyasa, sune suka haxa baki da ‘yan daba domin kama Fasila a yi tsafi da ita. Haqiqa Balarabe ya taka rawa sosai domin ganin ya ceto Fasila daga hannun mugaye. Sannu a hankali soyayya ta qullua tsakanin Balarabe da Fasila, har suka yi aure.

Amma fa sai da aka kai ruwa rana tsakanin dangin Fasila da iyayen Balarabe kafin a yi auren, saboda su iyayen Balarabe sun kafe a kan ba za su yarda xansu ya auri Bayarabiya ba, wai domin Yarbawa ba su da kunya sannan babu tarbiyya in ji Malam Sulaiman wato mahaifin Balarabe. Ita kuma mahaifiyar Fasila ita ma ta qeqasa qasa tace ‘yarta ba za ta auri Bahaushe ba dominHausawa akwai su da yawan sakin mace in ji ta. Sa’annan shi ma saurayin Fasila, wato Balarabe yace shi fa, dole sai an aura masa Fasila, domin wanccan tsohuwar budurwarsa Bahaushiya da ya so ya aura, ta yaudare shi kuma yanzu ga shi ya sami wata sai a hana shi, alhalin suna son juna? A qarshe dai an zo an yi ta nuna al’adu da xabi’un Yarbawa da tadodinsu na aure musamman lokacin bikin auren Balarabe da Fasila.

Daga wannan bayani da aka yi na kowane fim kamar yadda aka aiwatar da shi, za a iya cewa wannan bincike yana ganinkowanne fim zai iya amsa sunansa dangane da yadda aka gudanar da shi. Wato fina-finan da ake ganin na Hausa ne sun amsa sunan da aka yanka musu na Hausa domin tun daga kwalliyar ‘yan wasa da suturarsu da kalamansu da muhallinsu da aiwatarwarsu da zubinsu da harshensu fina-finan na Hausa ne.

Amma fina-finn da ba na Hausa ba, su ma ana ganin sunan da aka raxa musu ya dace da su, idan an dubi yadda aka aiwatar da su, musamman idan aka kalli halayyar ‘yan wasan fim xin da harshen ‘yan fim da suturar ‘yan fim xin da kuma zubin fim xin gaba xaya, basa nuna ko wakiltar al’adu da xabi’u na Hausawa.

4.3 Fina-finai Cikin HausaA Mizanin Nazari

An xauki hanyoyin nazarin fina-finan Hausa aka xora fina-finan bisa sikelin na tantance su. Fina-fina kuwa su ne fim xin *Bori* da *Juyin Sarauta* da *Qafar Ungulu* da *Na-Hauwa* da *Malam Zalimu*. An fara da kallon zubin fina-finan tummmkunna, a matakin farko.

4.3.1 Zubin Fina-finai Cikin Hausa

Kamar yadda aka faxa a baya, zubin fim, shi ne yadda fim yake farawa, ya tafi bisa tsari tiryan-tiryan, daga wannan mataki zuwa wancan har zuwa qarshensa, ba tare da an sami karyewar qullin zubin wasan ba. A nan an kalli zubin waxanann wasanni ta kawo dalilai da madogara daga cikin fina-finan. Amma kar a manta tun a farkon wannan babin an yi tsokaci a matsayin matashiya na kowane fim domin a san inda kowannensu ya sa gaba.

4.3.1.1 Zubin Fim Xin "*Bori"*

Shi wannan fim an tsara shi ne a kan bori ko tsafin bori ko wasan bori. Dalilin da ya sa binciken ya kira bori da suna uku shi ne, masana irin su Kofoworola (1978) da Ahmed (1985) suna ganin bori a matsayin wani nau'in wasan kwaikwayo ne na Hausawa. Amma masana irin su Adam (1997) da Umar (1987) da suna ganin bori ba wasa ba ne, bauta ce ta addinin gargajiyar Bahaushe kafin ya karvi Musulunci, Umar (1987) ya ce irin wannan matsayi nasa, xan Adam ya bauta wa abubuwa da dama, kamar duwatsu da aljannu har ma da dabbobi.

Da wannan jawabai na masana da ya gabata, za a iya cewa "bori" al'ada ce ta Bahaushe wadda har yau ana yi a wasu sassa na qasar Hausa. Kuma ga shi har ya sami wurin zama a cikin adabin fina-finan Hausa. Domin yanzu za mu kalli zubin fim xin bori kamar yadda aka wanzar da shi.

Fim ne wanda aka tsara shi a bisa yadda Bahaushe ya yi imani da bori, wato tsafi gaskiyar mai shi. An ga yadda Bosho wanda yana xaya daga cikin manyan 'yan borin garin ya zo fadar sarki ya isar da saqon Aljannu cewa:

Bosho xan Bori: Aljanu suna gaishe ka kuma suna qaunarka, mun sha zubar da

hira da su a kanka…….

Sarkin Gari: Hahahahahaha!, gaya min da sauri, me saqon?

Bosho Xan bori: Abin da suka ce ranka ya daxe, tozon hularka, idan ka tashi rawani kakan yi shi zanqeqe da hularka, suka ce wannan tozo daquwa yake musu, idan ba a daina ba, za su juyar da kanka….

Abu na biyu, za a yi wankan sarkin bori, domin sarkin bori ya mutu, don haka za a yi shirin duk wasu abubuwa da kan yi na al'ada da izininka….

Wato wasa ne mai xauke da zubi guda biyu, vangare xaya a kan imani da kuma siddabaru na nuna qarfin tsafi a tsakanin 'yan bori. Sannan a duk lokacin da wani ba shi da lafiya ko yake da wata buqata a gari, akan tafi gidan sarkin bori domin a sama masa magani, ko mafita daga matsalar da ya shiga, wani lokaci ma girka ake yi wa maras lafiya. Mutanen gari suna amfana sosai daga magungunan da waxannan 'yan bori suke bayarwa a cikin wasan, ke nan kamar yadda yake a al'adar Bahaushe cewa "tsafi gaskiyar mai shi", tun daga kan sarki har sauran mutanen gari sun yi na'am da tsubbace-tsubaccen da ake yi musu. Wannan fim ya nuna qarara a al'adar Bahaushe bori abin bauta ga wanda ya yi imani da shi.

A zubin fim xin na biyu sai kuma aka shigo da harkar ilimi da bincike a cikinsa, za mu iya ganin haka lokacin da aka nuna wata xaliba mai suna Asma'u 'yar gidan Rabi'u take son ta gano wai shin wace irin fasaha ce take cikin bori ne, har al'umar Hausawa suka karkata tunaninsu a kai suka yi imani da shi? Nan da nan, ta nemi izinin mahaifinta ta tafi wurin wani malami, inda shi kuma ya karanta mata yadda ya kamata ta tsara aikin binciken nata a kan bori kamar haka:

Lakcara: A kan bori za ki yi binciken naki?

Xaliba: In har za a sa min hannu, na fi son na yi a kansa

Lakcara: Yana da muhimmanci, amma sai kin yi bincike da kyau, a kan menene bori? Da rabe-rabensa, sannan kuma sai kin yi bincike a kan matsayinsa a cikin addinin Musulunci da kuma gargajiyar Hausa, yaya tunanin Bahaushe yake a kan bori?.

Xaliba: Ba matsala duk zan iya, dama akwai wani xan bori a qauyensu mahaifiyata zan je na gana da shi.

Lakcara: Da kyau!Ki ci gaba da aikinki Allah ya taimaka, amma zai yi kyau ki nemi littattafai kamar *Gadon Fexe Al'ada* na Farfesa Bunza da kuma *Hausa a Yau* na Ibrahim Yaro Yahaya da kuma *Qamusun Hausa* na Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero,Kano.

Xaliba: Gaskiya na gode Malam, kuma Insha Allah zan neme su.

Ranar bikin ta zagayo, mutanen gari da baqi an hallara, da sauran masu bincike a kan bori. Mawaqin bori Magaji Jikan Hansai shi ya yi kixan bori a ranar. Kaxan daga cikin 'yan bori da suka taka rawa a ranar sunhaxa da Baturiya da Soja da Xansanda da Rabi Mahaukaciya da sauransu sun taka rawa sosai xaya bayan xaya, duk wanda aka kaxa masa takensa zai shigo cikin fili, sannan shi ma sabon sarkin bori ya zo yahau nasa borin. A qarshe, fim xin ya nuna al'adar bori a Bahaushiyar al'ada wato na gaskiya, musamman a kan yadda tsarin shugabanci da tsare-tsare da tsarabe-tsaraben naxin sabon sarkin bori, sannan an nuna yadda 'ya'yan sarkin bori sukan jefi junansu da tsafe-tsafe da halaka junansu domin kowa yana so ya gaji mahaifinsa. An kuma nuna tsarin kixa da rawa da waqar bori a zahiri. Sannan an nuna yadda Bahaushe ya yi imani da aljani a matsayin abin bauta. Wato fim ne wanda yake nuni da kowa

ya bar gida……Don haka, wannan bincike yana ganin zubin wannan fim na bori yana nuni da wani fanni na al'adun Hausawa kuma za a iya sa shi a cikin sahun fina-finai da Hausa.

4.3.1.2 Zubin Fim Xin *Juyin Sarauta*

A taqaice fim xin juyin sarauta, yana nuna yadda mata suke taka rawa a gidajen sarauta a qasar Hausa. Fim xin ya fara ne da nuna rayuwarmata, matan aure da kuyangu da suke a gidajen sarauta a qasar Hausa inda kowacce mata tana kai kawo yadda xanta zai gaji sarautar gidan. A fito da ire-iren gagarumar taimako da matan sarkin Jadarwa suka taka shekara xari da suka wuce, musamman wajen zaven sabon Sarki duk lokacin da kujerar sarautar ta faxo. Saboda haka, iyalan Sarki Yusufu suka shiga yi wa junansu tsaface-tsaface da zuwa wurin malaman tsubbu da bokaye da 'yan bori, domin ganin xanta ya gaji gujerar mahaifinsa, daman sun ga tsufa ya cimma Sarki, yau lafiya gobe babu, don haka a kowanne lokaci sarki na iya mutuwa, don haka kowace ta fara kama qafa wajen 'yanmajalisar Sarki da fadawa ana ta haxa munafurci da kutungwila. Yau sai a ji xan wancan mata ya haukace, gobe xan wancan ya shiga daji, jibi xan wannnan ya zama xan giya ko ya shiga daji.

A cikin fim xin sarki yana da mata huxu sannan yana da qwarqwarori uku in an haxa bakwai kenan, sarki yana da ‘ya’ya da yawa. To dukkansu masu ‘ya’ya suna ta qoqarin suma ‘ya’yansu su gaji wannan sarauta, sai suka shiga yi wa junansu jefe-jefe a tsakaninsu. Xaya an kashe shi, bayan kwana xaya da ba shi sarauta, wani an sa shi ya zama mashayin giya, wannan an laqa masa sata aka zane shi aka kore shi daga garin, wannan an haukatar da shi. Wani kuma aka xauke shi aka tafi da shi Sakkwato karatu, wanda shi ne ya gaji sarautar daga baya.

Wato fim xin, yana nuna irin badaqala da qiyayya da gwagwarmaya da asiri da matan sarakunan qasar Hausa sukan yi wa junansu ne domin qoqarin ganin kowacce xanta ya gaji sarautar gidan. An ga yadda matan sarkin suka sa shi ya shiga cikin garari da tashin hankali, wanda duk matan ne suka sa shi cikin wannan yanayi da ya sami kansa a ciki. A qarshe ma da aka gano wata daga cikin matan tana da hannu a cikin irin wannan mummunar xabi’a, sai da sarki ya sa aka kai ta kurkuku aka rufe ta sannan ya ce ba shi ba ita, amma dai ta ci gaba da zama a gidan saboda tana da yara da shi. A qarshe wanda ba su zata zai gaji sarautar garin ba, shi ya zo ya yi, shi xin ma Allah yana tsare shi, domin tun yana yaro ake so a sa masa ciwo, sai Allah ya sa aka yi maza aka kai shi karatu sakkwato, da yake Allah ya yi shi xin ne zai gaji sarautar, sai wata rana ya faxawa malaminsa zai je ganin gida. Daga nan, da yake yana da rabo, bai daxe da sauka ba, sarki ya faxi ya mutu, shi kuma aka xora shi a kan kujerar Sarkin Jadarwa.

A taqaice masarautar Jadarwa babbar Masarauta ce, mutanenta suna da ilimi da arziqi, babbar daula ce da al’umma suke alfahari da ita. Burin duk wani xan sarki ya ga ya zama sarki ko ya

rayu a cikin gidan sarauta. Babban tashin hankali a wancan lokaci shekara xari baya shi ne biyan jangali da haraji. An tsara fim xin a bisa al'adar sarautar Hausawa zalla, tare da kula da tsarin bautar gargajiya, irin su amfani da matsafa da 'yan bori ko bokanya da malaman gargajiya. Fim ne da aka yi amfani da tufafi da kayan wasa da muhalli da harshe da kwalliya irin waxanda aka san na Bahaushe ne ba na aro ba. Don haka shi ma wannan bincike yana gani shi ma wannan fim ne da aka yi cikin Hausa.

4.3.1.3 Zubin Fim Xin *Qafar Ungulu*

Fim xin *Qafar Ungulu*fim ne wanda aka tsara shi a kan sha'anin sarauta. Amma shi ba na masarautar gari ba ne, an taqaita shi a bisa gundumar Hakimi ne. Fim ne wanda aka tsara shi a bisa tsarin tafiyar da mulkin al'umma bisa adalci tare da yi masu jagora a kan abubuwan da suka yi amanna, wato ba a son shugaba ya dinga mulkin danniya, ko kuma na kama karya. Zubin Fim xin ya faro ne da labarin wani Hakimi mai mata da 'ya'ya da yawa kuma yana qoqarin son kare haqqin jama'a da martaba gaskiya a cikin al'amuran mulkinsa. Sai ya kwanta ciwo, a qarshe Allah ya karvi ransa. Mutuwarsa kenan, sai rigimar mulki ta kaure a tsakanin 'yan wannan xakin da wancan ko da yake daga baya an kai rigimar zuwa gidan sarkin qasar gaba xaya, wanda yake shi ne ya yanke hukunci wanda ya cancanta a naxa sabon Hakimi, aka kuma naxa babban xan marigayi Hakimi wato Ibrahim.

An ci gaba da zuba zarenfim xin ta hanyar qulla matsaloli a cikin fim xin, aka yi ta yin manaqisa da zagon qasa, wanda mai sarauta wanda aka fi sani da Masun gari da maiunguwa suka dinga yi da muqarrabansu, a kan ta yaya za a yi a samu a kashe sabon Hakimi domin shi ma ya gaji sarautar. Har ila yau matan gida su ma ba a bar su a baya ba, musamman mace mai bi ma uwargida ita ma ta shiga cikin gungun masu son ganin bayan Hakimi. Dole sai da aka xauki matakin sulhu har Allah ya taimaka aka samu zaman lafiya a gidan. Don haka, tun da an nuna yadda al'adar Bahaushe ta zamantakewa take a zubin fim xin, ana ganin shi ma wannan fim ne da aka yi shi cikin Hausa.

4.3.1.4 Zubin Fim Xin *Malam Zalimu*

Fim ne da yake nuni a kan malamai gardawa ta yadda suke amfani da asirai da yawan gaske. Ta haka ne aka samu wani malami ya zama limamin gari, to, daga zama limamin gari, sai ya fara girman kai, yana tinqaho, yana tafiya irin ta malaman qauye, wanda duk abin da za a yi na addu'ar suna ko xaurin aure ko sallar gawa shi zai yi. Idan ko ba shi ya yi ba aka sa wani ya yi, to akwai fitina, sai ya jefe shi, ko ya raunata shi ko ya nakasa mutum. To, ana cikin haka sai ya gamu da wani wanda asirinsa ya fi nasa, domin da Malam Zalimu ya raunata wancan malamin saboda ya yi limanci a masallacin malam Zalimu a dalilin makarar Malam Zalimu halartar masallaci a ranar. Wancan malami ya koma naqasasshe ba ya iya tafiya. Har Malam Zalimu yana cewa:

Malam Zalimu: Yau, na nakasa almuri, sai in ga da wacce qafar za ka taka ka je masallaci ka yi masu limanci. Hya hya hya kawai.

Ashe malamin nan da Malam Zalimu ya nakasa, shi ma wani shu'umi ne, don haka, sai ya nemi bara a wajen sauran 'yanuwansa gardawa, inda ya mayar da Malam Zalimu biri domin ya karya asirin da ya yi masa, aka xauki Malam Zalimu sai cikin gari ana wasan gardawa da shi ana samun kuxi. Bayan haka, sai aka cire shi daga limanci aka bai wa wanda ya kwantar. Labari ne dai, wanda yake nuna shu'umanci da jifa da gardawa suke yi wa junansu a tsarin al'adar gardanci. Wanda hakan yakan fara ne tun daga tsangaya har zuwa birni. Wato in zaka gina ramin mugunta……..Da man an san gardawa da irin wannan xabi'a a Bahaushiyar al'ada, don haka a bisa yadda aka tsara fim mai xauke da zubin wasu nau'o'in al'adun Hausawa, za a iya cewa shi ma wannan fim ne na Hausa.

4.3.1.5 Zubin Fin Xin *Na-Hauwa*

Fim ne wanda aka yi zubin labarinsa a kan soyayya tsakanin Na-Hauwa da budurwarsa Hauwa. Soyayya ce irin ta gargajiyar Bahaushe tun zamanin da ya shuxe shekaru can baya. An xan xauki lokaci kafin a yi auren, xaukar lokacin da aka yi ba a yi auren ba shi ne ya haifar da rikita-rikitar fim xin ya amsa sunansa. Domin shi Na-Hauwa saurayi ne mai dogon buri, yana so sai ya tara dukiya, kafin a yi aure. Ko da yake bayan wata uku an yi shagalin bikin auren nasu, kamar su gudu da lugude da yaushe gamo da gaxa da kai amarya dakin ango da su sayen baki da sauran wasannin al'adar gargajiyar Bahaushe da tadodin aure da aka san

Hausawa suna yi shekarun baya. An tsara kowane muhallin fim yadda ya kamata. Misali xakin amarya mun ga jeren tasoshi da su kwalla da su karauni da su langa da sauransu. An yi shekaru da xan dama da auren Hauwa ba haihuwa, ga ta kuma tana da kishi don ba ta son ta ga mijinta ya matsa daga nan zuwa can, don kar yace zai mata kishiya. Amma dole mahaifiyar Na-Hauwa ta fara hura wa Na-Hauwawuta dole sai ta samar masa wadda zai aura, kuma haka xin aka yi, auren da aka yi babu zaman lafiya, tashin hankalin yau daban na gobe daban.

Bayan wani lokaci mahaifiyar Na-Hauwa ta fara qorafi a kan shekara da shekaru babu haihuwa. Don haka, ta tasa Na-Hauwa a gaba ta na ta yi masa faxa ga yadda suka tattauna:

Na-Hauwa: Umma don Allah ki yi haquri, in aka bi a hankali sai ki ga Allah ya bayar.

Umma: Kamar yaya, ba zai yiwu ba fa sam!!! Ba zan lamunci wannan ba, matuqar kana son zama da matarka, to zan qaro mata uku, domin a cike gurbin, shekarun da aka rasa. In kuma ba haka ba in xaga maka nono ka bi duniya ……..

Daga nan aka tafi asibiti, an yi gwaji Na-Hauwa da matarsa, sakamakon bincike ya nuna matar Na-Hauwa ce take da matsala a mahaifarta. Ita kuma Hauwa ba ta son a yi mata kishiya. Baqin ciki ya isheta domin mahaifiyarsa ta qeqashe qasa dole sai an yi mata abokiyar zama kuma sai da aka yi mata kishiya. Aka aura wa Na-Hauwa Atika. An yi ta xauki ba daxi tsakanin uwar miji da uwargidan Na-Hauwa wato Hauwa. Ko yaya ya xan motsa zai tafi gidan Hauwa sai mahaifiyar ta ce ina, ba inda za shi. Daga baya mahaifiyar Hauwa da ita kanta Hauwar suka duqufa da addu’a har sai da Allah ya karvi addu’arta Hauwa ta sami juna biyu.

An nuna muhimmancin addu'ar iyaye ga 'ya'yansu a fim xin. Ita kanta Atika da samu juna biyu, amma da ta haihu xan ya koma.

Burin mahaifiyar Na-Hauwa shi ne, ta ga an tara mata jikoki birjik. Don haka, sai ta ce da za ta qara masa auren mata ta uku, ta ce zata aura masa 'yar gidan Malam Dikko mai tallar awara. Samun juna biyu da Hauwa ta yi ya sa jikin mahaifiyar Na-Hauwa ya yi sanyi suka rankaya gidan Na-Hauwa ta tabbatar, sai murna, ta yi addu'a ta kuma nemi gafarar Hauwa a bisa rashin mutunci da ta dinga aikatawa.

A qarshe abin nema ya samu, wato duk abin da haquri bai ba da ba, rashin haquri ba zai bayar ba. Hauwa ta zo ta haifi yara uku ringis wanda a ta dalilin hakan gwamnati qaramar hukuma da Jiha ta ba wa Na-Hauwa tallafin kuxi zunzurutu naira miliyan shida da gonaki ga yara 'yan uku. An biya wa yara da iyayensu baki xaya su je su yi aikin Hajji.

Tunda an kalli zubin fina-finan gaba xaya, a matsayin wani mashigi na tace fina-finai cikin Hausa. Za a ga zubin fina-finan suna nuni da xabi'u da al'adu na Bahaushe ne, ba a cin karo da wata fita wadda ta savawa al'ada da xabi'ar Hausawa tun daga farko har qarshe fina-finan ba, wato furodusoshin fim xin da daraktocin sun yi bakin qoqarinsu, wato su ga an kare martabar al'adar Bahaushe.Wannan ya sa fina-finan suka shiga wannan gurbi na fina-finai cikin Hausa. Wani mashigin tacewa da za a duba nan gaba shi ne jigogin da suka gina fina-finan Hausa.

4.3.2 Jigo A Fina-finai Cikin Hausa

Kamar yadda aka yi bayani, a babi na biyu, masana sun kalli jigo a fagen nazarin fina-finan Hausa da manufa ko ginshiqin da aka gina fim a kansa. Wato saqon da fim yake xauke da shi domin a nusar da shi ga jama'a, don faxakarwa ko ilimantarwa ko nishaxantarwa ko wa'azantarwa da sauran al'amuran zaman rayuwa na yau da kullum wanda za a iya zayyano shi ga jama'a domin su ga amfaninsa ko kuma illarsa ga ruwar xan Adam.

4.3.2.1 Jigon Fim Xin *Bori*

Jigon fim xin *bori*, shi ne fim xin da ya taskace al'adar Bahaushe a fagen bautar gargajiya da samar da waraka ga cututtuka na aljanu da sukan shiga jikin xan Adam. Sannan qananan jigogin sun haxa da tsarin da akan bi wajen naxa sarkin bori a qasar Hausa in ya mutu. Wani qaramin jigo shi ne nuna yadda akan yi sihirce-sihirce da siddabaru da jefe-jefe a tsakanin 'ya'yan sarkin bori masu son hawa kujerarsa bayan ya rasu. An kuma nuna yadda Bahaushe ya yi imani da abubuwan bauta irin na aljannu da sauran abubuwan voye, sukan iya yi wa mutum lahani idan aka yi musu laifi.

4.3.2.2 Jigon Fim Xin *Juyin Sarauta*

Babban jigon fim xin *Juyin Sarauta* shi ne rigingimun gado na neman sarautar ‘ya’yan Sarkin Jadarwa Yusufa shekara xari da suka shuxe. Sannan fim xin ya fito da al’adun Hausawa dangane da yadda ake tafiyar da sha’anin zamantakewa a cikin gidan sarauta a qasar Hausa tun daga qasa har sama. Fim xin ya nuna tsarin tattalin arziqin Hausawa na sana’o’in gargajiya da sha’anin jangali da haraji da ilmin addini (karatun allo) da malantar gargajiya da wasannin gargajiya da sauran al’amuran rayuwar irin na gargagajiyar Hausawa wanda suka gada tun iyaye da kakanni.

4.3.2.3 Jigon Fim Xin *Na-Hauwa*

Manufa ko jigon fim xin shi ne tawakkali da imani da Allah a kan duk yadda xan Adam ya samu kansa a rayuwa, to ya dinga godiya, wata rana Allah zai amshi addu’ar buqatunsa, kuma kar ya yi qasa a gwiwa wajen jajircewa da nema. Domin an ce mai nema yana tare da samu. Haka ta faru ga Ladidi mahaifiyar mijin Hauwa wanda Allah bai ba shi haihuwa da wuri ba, a maimakon a bi abin a hankali, shi ne ta dinga yi masa aure-aure, wanda waxanda aka auro xin ba su haihu ba, kuma aka yi ta tayarda fitina, amma Allah cikin ikonsa, sai kuma wadda ake wa gori, wato Hauwa ta haifi yara uku rigis lokaci guda. To, a nan rashin haqurinta ya vata alaqarta da surukarta da xanta, wanda daga baya ta zo ta ji kunya. Amma haqurin da Na-Hauwa ya yi da mahaifiyarsagaskiya ya yi masa rana. Domin ya sami arziqi bayan haihuwar

yara nan ‘yan uku, har aka ba shi kujerar makka da kuma miliyoyin kuxi daga hannun gwamnatin jiha da ta qaramar hukuma da masarauta. Mahaqurci mawadaci shi ne saqon.

4.3.2.4 Jigon Fim Xin *Malam Zalimu*

Jigon wannan fim xin shi ne gargaxi a kan hana yin zalunci. Kuma in za ka gina ramin mugunta a gina shi gajere. Za a iya tabbatar da haka, idan aka ba da misali da irin yadda gardawa sukan jefi junansu da asiri a qoqarin son mallakar abin duniya, ko don su aure matar wani, ko su raba tsakanin saurayi da budurwa ko su mallaki dukiyar wani da sauransu. Za mu iya ganin irin wannan muguwar xabi’a a cikin fim xin, yayin da Malam Zalimu ya jefi wani gardi saboda yana ganin ya hana shi sakat, wato yana yawan shigewa gaba domin ya ja mutane salla, wanda dalilin haka ya sa Malam Zalimu ya gurgunta Malam Tukur, koda yake, shi ma Malam Tukur xin ya rama domin sai da ya mayar da malam zalimu ya koma biri. Wanda kuma qarshensa kenan. Aka naxa Malam Tukur a matsayin Malam Zalimu wato limamin gari kuma duk wasu al’amuran malamai na garin shi yake jagoranci.

4.3.2.5 Jigon Fim Xin *Qafar Ungulu*

Shi kuma jigon fim xin *Qafar Ungulu* an gina shi ne a kan tsarin tafiyar da mulkin sarauta a bisa adalci, shi ne saqon da aka fi mayar da hankali a kai musamman a gundumar Hakimi ba

qasar gaba xaya ba. Da kuma yadda masu sarauta sukan yi wa junansu zagon qasa a sha'anin mulki.

4.4.3 Harshe 'Yan Wasa A Fina-finai Cikin Hausa

Shi ma harshen 'yan fim wata babbar siffa ce wadda ake amfani da ita wajen tace dacewar kalaman jarumai a cikin fim, wato duba da sauraren harshen xan fim bisa dacewarsa da matsayinsa na xan wasa. Sannan shin ba ya wuce gona da iri a wajen amfani da harshensa?Kuma shin wajen isar da saqon da ya kamata ya isar a kan lokaci ba tare da yana koma gaba, koma baya ba? Ko kuwa yana inda-inda da kuma kame-kame tukunna? Duka waxannan abubuwan dubawa ne a yayin nazarin harshen xan fim a cikin fim. Kiyaye kalaman raini da na batsa a wuraren da ba su dace ba, fitar da kalaman girmamawa da na tarbiyya a muhallansu, hakanan kuma kalaman ba da umarni da na tsawatarwa shin su ma an yi amfani da su a wuraren da suka dace a cikin fim? A nan ma za a kalli fina-finan da suke na Hausa domin a yi nazarin harshen jaruman fim xin bakin gwargwado. Su ne fim xin *Bori* da *JuyinSarauta* da *Malam Zalimu* da *Na-Hauwa* da *Qafar Ungulu*.

4.4.3.1 Harshe 'Yan Wasa A Cikin Fim Xin *Bori*

Yawanci 'yan wasan fim xin bori sun yi amfani da kalaman borin a wurare da dama, kuma a inda suka dace. Wannan yana tabbatar mana da cewa fim xin ya amsa sunansa dangane da

harshen ‘yan fim. Misali, lokacin da sarki ya mutu, matarsa da wani xansa sun sa gawar a gaba suna ta kuka, sai can matar ta kada baki ta ce da xanta Jaada:

> Matar sarkin bori: Jada sarki ya faxi na shiga uku na lalace, Jada a cikin aljannu da yake mulki, ba za a sami wanda zai dawo da ran Sarki ba?
>
> Jaada: Ai ba iskoki yake mulki ba, mu ‘yan bori yake mulki.

A nan daga jin harshen Jaada ya nuna wa xan kallo a fili cewa, sarkin bori mutane ‘yan bori yake mulka, don haka mutum ba ya mulkin Al’jannu, sai dai ya mulki ‘yanuwansa mutane, haka kuma shi ma aljani ya mulki aljannu ‘yan uwansa.

Wani misalin da za a sake bayarwa shi ne lokacin da xaya daga cikin manyan ‘ya’yan sarkin bori ya je fadar mai gari, yana sanar masa da mutuwar sarkin bori, bayan ya gama isar da saqonsa sai ya ce :

> Yaa Badakuwa uwar su Badeni
> Yaa Badakuwa uwar su Badeni
> Ke ke ganinmu mu ba ma ganinki
> Ku sakko, ku sakko

A nan an nuna, ‘yan bori suna ta’ammali da iskoki, kuma ya yi amfani da harshen da babu wanda ya iya fahimtar abin da yake faxawa aljan Badeni a yayin ganawarsu.

Kalaman da Liman ya yi bayan tafiyar xan borin nan, suka ne, tare da jan hankalin maigari da kar ya yi imani da abin da ya zo ya faxa masa wai “Aljannu suna qorafi, Amawalin hular sarki tana sukar su”. Sai Liman ya ce:

> Liman: wa iyazu billahi, ka bari sun yi tasiri, yallavai an san Aljanu gaskiya ne amma shi Allah ya halicce shi ko? Duk wani abu da xan bori zai zo da su, wallahi qarya ce, shirka ce, duk lokacin da aka yarda da abin da suka faxa an bar Allah. Kuma wannan abu da ya yi shirka ce.

A nan liman ya nuna cewar Musulunci ya haramta bori, don haka maigari ya yi hattara don kar a dulmiyar da shi da jama’arsa su zama ‘yan shirka. Ina ai mai gari bai ko kula shi ba. A nan liman ya taka gagarumar taimakosa na liman a kalamansa, ya yi amfani da harshen limamai a Musulunci ya gyara abinda ya gani wanda bai dace ba, kamar yadda hadisi yake nuna mana, cewar in ana aikata wani abu mara kyau wanda ya sava wa Musulunci ana iya gyara shi da hannu, in ba za a iya gyaran da hannu ba a yi shi da baki, in an kasa da baki, sai aqi abin da zuci, amma fa wannan shi ne ma fi raunin imani.

4.4.3.2 Harshe ‘Yan Wasa A Cikin Fim Xin *Juyin Sarauta*

Fim ne da shi ma aka yi amfani da kalamai a kan harshen sarauta a wurare da suka dace a yi amfani da su. Misali lokacin da xan Sarki wanda aka tura shi Sakkwato karatu ya zo gida

domin ya ga mahaifiyarsa, a nan Sarki ya yi amfani da kalamin umarni kai tsaye wanda faxin haka babu ja balle a yi gardama:

Xan sarki: Allah ya taimaki Sarki, ina so in ga mahaifiyata don na daxe ban sa ta a ido ba…

Sarki: Ba za ka ganta ba, tashi ka koma!!

Xan Sarki ya yi qanqan da kai wajen ajiye kalamansa na qasqantarwa a gaban mahaifinsa kuma sarkin gari. Shi kuma uban nasa kuma sarki mai mulki ya yi amfani da harshen umarni da kuma iko da isa akan xan nasa cewar, tun da har bai nemi izini kafin ya baro sakkwato ba, to ya koma ba zai ga mahaifiyar tasa ba.

Haka zalika, a lokacin da asirin su Galadima da muqarrabansa ya bayyana, musamman yadda ake ta haxa wasu makirce-makirce don nakasa ‘ya’yan sarki tare da haxin bakin wasu matan gidan akan ana son a gaji sarautar sarkisai suka yi azamar gudu, a qoqarin haka ne Galadima ya kira wani Bafade yana cewa da shi:

Galadima: Asirinmu ya gama tonuwa, shawara xaya zan ba ka, ka yi qoqari ka bar garin nan, bayan kwana biyu idan qura ta lafa zan aiko makada iyalinka……

Bafade: A daren ke nan za mu gudu?

Galadima: A’a bari gari ya waye za ka yabawa aya zaqinta…..

A nan Galadima, ya yi amfani da salon magana inda ya dace. Domin, in banda kai Bafade, an ce in har gari ya waye kashin ka za a yi, ka gudu wai sai kuma yake tambayar Galadima a daren nan ne zai gudu? Shi ya sa shi kuma Galadima ya gwale shi ya ce, a'a ba a daren ba, ya bari gari ya waye: wato, in har ya bari gari ya waye masa a garin, to sunansa gawa. Wato a nan ana nufin, "ruwa cikin cokali ya ishi mai hankali wanka".

4.4.3.3 Harshe 'Yan Wasa A Cikin Fim Xin *Malam Zalimu*

Za a iya ganin yadda gardawa suke amfani da fasahar karatun zaure wajen juya magana ko isar da saqo ga sauran gardawa yayin da ake zaman tankiya a tsakaninsu. Misali a dubi yadda ta kasance tsakanin kalamin Malam Zalimu da babban gardi:

> Babban Gardi: Ku faxawa Malam Zalimu idan yana cin qasa ya kiyayi ta shuri, idan na tashi aiko da nawa saqon, ba zan yi amfani da hatimin yasin mai qafa casa'in da tara ba…..
>
> Malam zalimu: Ga ni nan, tsohon munafuki sai in mayar da kai xan taure a yi qauri da kai…….
>
> Babban Gardi: Ni biri zan maisheka ta yadda za a dinga morarka ana yawo da kai gari-gari, jama'ar gari suna samun abin kallo, ana wasa da kai, ko a samu abin masarufi ……

A nan za mu iya ji da kuma ganin sa-in-sar kalamai da ta shiga tsakanin malaman nan, ta kai kowannensu yana tinqaho da kalaman sihiri ko asiri da zai lahanta mutum ko nakasa xan uwansa in ya yi masa wargi, ko kuma ba dai-dai ba.

4.4.3.4 Harshen ‘Yan Wasa A Cikin Fim Xin *Na-Hauwa*

Shi ma wannan fim xin, kowanne xan fim ya taka gagarumar taimako da ta dace da shi musamman a fagen kalamansu dangane da guraben da kowannensu ya hau. Misali mu dubi kalaman Hauwa a matsayinta na matarsa, uwargidan Na-Hauwa, ta yi amfani da kalamai masu tausasa zuciyar miji tare da jan hankalinsa, wato ya yi tawakkali a bisa ibtila’i ya faxa masa, wacce ta lamushe duka rumbunan hatsin da ya tara. Na-Hauwa ya yi tagumi yana ta kuka, ga kalaman Hauwa:

> Hauwa: Ka xauka wannan abu da ya same ka jarrabawa ce daga Ubangiji, sai ka ga ya kankare maka zunubanka. Amma shi ne kake zubar da hawaye, fi sabillillah! Rayuwata ba za ta tava zama cikin walwala ba idan kana zaune a haka. Ashe ni ban isa in gaya maka gaskiya ba, Haba Na-Hauwa! Haba Na-Hauwa!!.....

Bari mu sake xauko wani misali na kalaman mahaifiyar Hauwa tana magana a cikin fushi a gaban Hauwa, a kan har yau, Na-Hauwa ya kasa fitowa a xaura aurensu da Hauwa, kowa ya

huta da gutsiri tsoma na mutanen gari, domin jama'ar gari sun fara cece-kuce a kan yarinya ta girma an qi yi mata aure, sai soyayya kawai suke ta yi a gari

> Ummar Hauwa: Wai ke! Ina maganar da na gaya miki ne? Nace ki gaya masa ku san me kuke ciki game da maganar aurenku. Kuna neman ku mai da abin shiririta…

Rufe bakin mamanta ke da wuya, sai Hauwa ta yi karayar zuciya ta ce:

> Hauwa: Innarmu maganar nan sai fa an bi a hankali, saboda kin san, mai qaramin qarfi ne.
>
> Maman Hauwa: Me kike nufi!! Ke kin tava ganin inda mutum ya xauko maganar aure ba shi da kuxi ba sana'ar yi, shi ke nan haka za mu zauna kara zube mu zuba maku idanu? To ni dai na gaya miki wannan ita ce magana ta gaskiya, ku ba ku san zuru ba?
>
> Hauwa: Innarmu yi haquri zan gaya mai.

A gaskiya kalaman Hauwa sun nuna cewa ita 'ya ce mai xa'a, domin duk da cewar mahaifiyarta tana ta faxa, amma ba ta kuskura ta xaga mata murya ba. Da a ce 'yan wasan fina-finan da Hausa ne, da tuni ta mayar wa da uwarta da martani. Sannan kalaman mahaifiyar Hauwa sun faxo daidai lokacin da ya dace domin ba ta yi wata-wata ba, ta yi maza ta yi wa tufkar hanci wanda a sanadiyyar nuna isa da 'yarta da ta yi, hakan ya sa Hauwa ta tafi dandali ta sanar da saurayinta Na-Hauwa halin da ake ciki, wanda hakan shi ma ya sa shi ya xauki mataki cikin gaggawa aka xaura masu aure, domin ba ya son ya vatawa iyayensa rai. Wannan salon magana da maman Hauwa ta ce "ku ba ku san zuru ba……", wato zuru ya ishi xa kunya, an zuba masu ido ne a ga ko za su sauya domin a san abin yi a kan batun auren, amma

da ta ga ba su tanka ba,sai ta ce to ba ri ta fito fili ta bayyana masu abin da ke zuciyarta. Harshen Mahaifiyar Na-Hauwa ya ba da kai a kan batun aurensu ga abin da take cewa: “ Addu’a za mu yi ta yi, an san komai da lokacinsa, sai Allah ya yi, sannan aure rai gare shi. Tawwakali da kuma tura al’amuran rayuwa ga Allah yana daga cikin xabi’ar Hausawa.

4.4.3.5 Harshe ‘Yan Wasa A Cikin Fim Xin *Qafar Angulu*

Shi ma fim xin *Qafar Ungulu* an gina shi bisa tsarin tafiyar da mulki tare da wakilci a gundumar Hakimi musamman a kan al’amuran da suka shafi adddini. Wato matsala ce aka samu wajen miqa wanda za a naxa sabon limamin unguwa. Sai aka yi son rai a inda shi wani mai sarauta wai shi Masu da Mai unguwa suka haxa baki aka gabatar da Alhaji Rabi’u domin a naxa shi liman saboda kwaxayin abin duniya, alhalin bai cancanta ba. Ashe Hakimi ya wakilta wazirinsa a kan cewar a bincika domin a kawo wanda ya cancanta, don haka shi kuma Waziri saboda wasu uzuruka sai ya wakilta Galadima, Galadima shi ma ya wakilta Masu da Mai unguwa. Su kuma suka yi abin da suka ga dama. E haqiqa akan samu irin wannan matsalar a cikin al’umma. Wato a nan ana so a nuna yadda tsarin tafiyar da mulki tun daga tushe irin ta gargajiya takan warware matsala sannu a hankali a bisa yanayi na mulkin sarauta ba tare da an tayarda hankali ba. Ga harshen ‘yan wasan kamar haka a cikin fadar Hakimi:

Hakimi: Wanene ake so a qaddamar ya maye gurbin marigayi liman?

An gabatar da Alhaji Rabi’u amma sai Hakimi ya ce:

Hakimi: A qa’ida ta naxa shugaba, sai an tambaya an ji ko akwai wani mai qorafi?

Nan take Malam Abdulkarimu ya ce: Tunda ake Salla a unguwar, ba a tava turo Alhaji Rabi'u ya wakilci liman ba. Hakimi ya tambayi Ladan, shin haka ne wanda aka qaddamarba ya wakiltar tsohon liman? Jama'a suka ce e.

Don haka sai Hakimi ya ce:

Hakimi: Waye ke wakiltar liman in ba ya nan?

Sai aka ce Malam Aminu ne, nan take aka gabatar da Malam Aminu, sannan Hakimi ya ce kowa ya fita amma 'yan majalisarsa su tsaya. Sai Hakimi ya fara jawabin bincike,a kan yaya hakan ta faru?

Hakimi: Waziri yanzu a matsayinka na wazirin garin wanda idan bana nan kai ke tafiyar da harkokin mulki, ya aka yi aka qaddamar da mutumin da ba shi jama'a suke so ba, a naxa shi a limamin unguwa? Ka san limanci ba wasa ba ne, ka san kosalla daga liman takan vaci. To a naxa wanda limancinshi zai sa sallarmu ta vaciranar Juma'a kowani lokaci? Me ya faru?

Waziri: Na miqa komai hannun Galadima lokacin ni ina da uziri.

Hakimi: Galadima ka ji abin da Waziri ya ce, ya miqa wannan nauyi a kanka ya aka yi haka?

Galadima: Allah ya taimake ka wannan magana haka take, Galadima ya kira ni, ya zartar da komai a hannuna, ni kuma ganin Mai unguwa, ya fi ni sanin 'ya'yan marigayi liman, don haka na danqawa mai unguwa da shi da Masu, kuma na ce, lallai a yi bincike a cikin almajiransa ko 'ya'yansa a zo mana da mutum guda. To ni inda muka tsaya ke nan.

Hakimi: Mai unguwa, kuna salla masallaci xaya da marigayi, kana nufin ba ka san halin ‘ya’yanshi ba? Aka qaddamar da wanda bai kamata ba.

Mai unguwa: Ranka ya daxe zan faxi gaskiya, Masu ne, ya zo ya same ni ya ce, ya kamata mu tanadi tsufa tun muna da quruciya. Masu ya ce in aka tabbatar da Alhaji Rabi’u liman ga abin da za yi mana.

Masu: Na karvi laifina, Allah ya yafe mana, tuba muke.

Hakimi: Yanzu ku sani mun rantse da Alqur’ani za mu yi wa jama’a aiki. Bai dace kuna irin wannan ba don haka za a hukunta ku.

A nan an nuna matsayin sarauta da mulki bisa wakilci da kuma adalci ta yadda akan ja ragamar al’amuran jama’a bisa amana. Hatta waxanda suka so vata kansu, masarauta ta hukunta su bakin gwargwadon laifinsu.Sannan idan aka dubi kalaman Hakimi yana amfani da zavavvun kalamomin umartau da tausasawa a matsayinsa na shugaba, ta yadda ran kowa ba zai vaci ba duk an yi masa laifi, kuma sai da gaskiya ta bayyana. Babu ashariya ko cin mutunci ko muzgunawa wani don yana gaba da su.

4.5.4.1 Tufafin ‘Yan Wasa A Cikin Fina-finan Hausa

Bahaushe ya ce sutura ita ce mutum, ko da ba ma a harkar wasan kwaikwayon fim ba, a rayuwa ta yau da gobe tufafin da mutum yakan sa a cikin al’umma yakanbayyana matsayinsa. Misali idan basarake ne, za a gan shi ya yi shiga irin ta sarakai, idan malami ne, za a gan shi

cikin suturar malamai, haka idan talaka ne suturar ita ma za ta nuna shi a talaka, haka attajiri ko da ba a faxa ba, za a gan shi a cikin tufafin attajirai. A tunani irin na xan Adam zai iya yankewa kansa hukunci a duk lokacin da mutum ya yi shiga irin ta matsayinsa a cikin al'umma. A nan ma an xauki waxannan fina-finai an kuma kalli tsari ko zubin tufafin 'yan fim xin dangane da matsayinda kowane xan fim ya hau.

4.5.4.1 Tufafin 'Yan Wasa A Cikin Fin Xin *Bori*

Kamar yadda bayani ya gabata, fim xin bori ne wanda aka gina shi a kan bori, da kuma hanyoyin samar da maganin gargajiya da kuma yadda ake naxin sarkin bori a al'adar 'yan bori. Don haka, a kusan kowane mataki na fim xin an yi amfani da suturun da suka dace da kowanne xan fim a muhallan da suka dace. Xan Sarkin bori da sarkin bori da jama'arsa kowannensu ya sanya suturar da ta dace da shi. Wato sa rigunan saqi da hularta da xaura kambuna da guraye da layu a jiki. Sauran jama'ar gari kowa ya sanya sutura daga mai jamfa da wando, sai babbar riga 'yar riga da wando da hula da rawani. Wasu kuma suna sanye da 'yar shara da wando. Matan gida suna sanye da riguna da zane xaurin qirji da xan kwali a kansu. Misalin tufafin da sabon Sarkin bori ya sa a jikinsa, da gani babu tambaya, an san lallai sun dace da matsayin da ya hau na Sarkin bori, ya sa rigar saqi da rigar fata da janjami da jidare ko walki da xammamu kamar layu da maras layun da jaka an rataya hagu da dama, sa'annan ya sanya hula havar kada da akayau da amila da kuma warwaro. Sauran 'yan abi Yarima da suka mara masa baya sun haxa da Bature Kafaran shi ma ya sa tufafin kaki, wato *uniform* ya yi xamara da *belt* da janjami hagu da dama, yana kuma sanye da hular 'yan sanda

da takalmi sau ciki. Ita ma wata ‘yar bori wacce aka fi sani da Rabi Mahaukaciya, an nuna ta sanye da kaya yagaggu irin na mahaukata, ga ta nan dai hargitsatsa-bu-tsatsa. Akwai wani xan bori mai suna Arne Kar Duwatsu wanda shi ma ya xaura bante na fata da hular gashi yana riqe da xan gatari.

Wani xan bori da ake ganin shigarsa ta hau matsayinsa shi ne Buzu aljani yana sanye da baqaqen kaya riga doguwa mai dogon hannu tana da faxi da wando yana kuma sanye da rawani irin na buzaye, shi ma yayi xamara da hamilu guda biyu. Sai kuma Bafillatana Barhaza ita ma ta sa kayan Fulani riga da zani da xankwali tana riqe da qorai da fai-fai da ludayi, sannan ta sanya xamaru da warwao na hannu.

Har wa yau an nuna Mai Dawa Adamu , shi ma ya sanya riga baqin saqi ‘yar shara da wando, sannan ya sanya fata a kwankwaso ya xaura xaya, ya rataya xaya. Yana riqe da izga a hannunsa da xammara a jikinsa.

Wani xan bori da ya shahara shi ne Muhammadu Xangaladima wanda aka fi sani da Basaraken bori, wanda qananan ‘yan bori sukan je su yi masa gaisuwa, shi ma yana sanye da warki guda uku, xaya ya xaura a kwankwaso, xaya a qirji, xaya kuma ya yafa, sai kuma hula ta saqi da ya sa, ya kuma sa xamaru yana mu’amala da goro a bakinsa kodayaushe da kuma turare. Sannan shigar da sauran jama’ar gari suka yi kamar na Naburaska an nuna shi yana sanye da suturar Hausawa wato hula dankwara da riga ‘yar shara da wando sannan ta takalmi faxe.

Da wannan ne, wannan bincike yake ganin za a iya cewa tufafin da aka yi sanyawa duka ‘yan wasa a cikin wannan fim ya amsa sunansa a al’adar bori ta zahiri don haka, wannan fim xin bori ana ganin Bahaushen fim ne dangane da yanayin tufafin ‘yan wasan.

4.5.4.2 Tufafin ‘Yan WasaA Fim Xin *Juyin Sarauta*

Tufafin ‘yan fima cikin fim xin juyin sarauta shi ma kamar fim xin bori, an yi amfani da suturun sarakai a muhallai daban-daban da suka dace. Kamar a fadar Sarki mun ga yadda Sarki da hakimansa suke zaune tare da shi dama da haga cikin zubin suturar sarakai, Sarki yana sanye da alkyabba da qoquwa a kansa, da rawaninsa da babbar riga aska biyu, wasu fadawan kuma suna sanye da rigunar bulla da aska biyu da wundi da girken nufe da ‘yar Kumasi da jabba da sace da rigar gwanda da rigar kwakwata da rigar aganiya da zubuni da jar dara da takalmi hubbi. Hakanan ma makarantar Malam, an zuba almajirai suna sanye da riguna ‘yar shara da huluna dankwara a kansu. Shi ko Malam yana sanye da rawaninsa da babbar riga mai kwaxo da linzami. A taqaice an yi amfani da manyan rigunar sarakai yadda ya dace. Hatta bayin sarki su ma an yi musu shiga irin tasu. Ita ma bokanya ta yi shiga irin yadda aka san bokaye na shiga a qasar Hausa. Shi ma wannan fim xin kusan duka tufafin da kowane xan wasa ya sa, ya dace da shi, ba a sami suturun baqi sunyi kutse a cikin fim xin ba. Daraktan fim xin ya kiyaye wajen tabbatar da an yi amfani da suturun gargajiyar Hausawa. Za a iya ganin haka a yanayin shigar Bokanya wacce ta sanya rigar saqi a jikinta da zanin saqi da kuma xaurin xankwali na saqi. Sarki Yusufa shi ma duka shigar da ya dinga yi sun dace da tufafin suturun sarakunan qasar Hausa.

Idan muka koma kan suturun da kuyangi da bayin Sarki suka sanya za a ga su ma suna sanye da zani ne da xaurin qirji a wasu wurare, wasu kuma suna sanye da riga da zani da kuma wanda suka yafa a kai. Da haka wannan bincike yake ganin za a iya cewa an yi amfani da tufafin Hausawa a cikin wannan fim, kuma zai iya amsa sunansa da fim xin Hausa.

4.5.4.3 Tufafin 'Yan Wasa A Fim Xin *Qafar Angulu*

Tufafin 'yan fim a cikin fim xin *qafar ungulu* ba shi da wani bambanci na a zo a gani da na fim xin juyin sarauta. Sai dai bambancinsu ya fito qarara a bisa jigo da zubi da harshen 'yan fim da kuma rawa ko kuma halayyar 'yan fim xin daga nan zuwa can. Hakimi ya sanya babbar riga aska biyu da rawaninsa da jar dara da kuma alkyabba. Hakanan su ma hakimai irin su Alhassan Kwalle da Gado-da-masu da sun yi shigar su irin yadda aka san hakimai qasar Hausa sukan sa tufafinsu, misali Mai unguwa Ciroki ya sa babbar riga mai xauke da aikin kwaxo da linzami da kewaye a kansa. Don haka, wannan fim shi ma suturun da aka yi amfani da a cikin wasan sun yi dai-dai da irin ta Bahaushiyar al'ada, hakan za a iya cewa fim xin na Hausa ne.

4.5.4.4 Tufafin 'Yan Wasa A Fim Xin *Na-Hauwa*

Kamar yadda aka gani a cikin fim xin, fim ne da wanda ya fito da muhalli da yanayin rayuwar mutanen karkara a qasar Hausa. Don haka shi ma, duka manyan mata da suka fito a fim xin sun sa suturar da aka san manyan matan Hausawa sukan sa na gargajiya kamar yadda muka gani a jikin mahaifiyar Hauwa da mahaifiyar mijin Hauwa wanda aka fi sani da Na-Hauwa. Haka zalika jama'ar gari, su ma kowannensu yana sanye da riga da wando da 'yar tagiyarsa ga manyan maza ke nan. Haka ma, 'yan mata qanana an yi musu xaurin qirji da xankwali a kan su suna gaxa.A wannan fim xin Na-Hauwa, a kowanne xan wasa ya sanya suturar da ta dace da shi. Misali a dubi kayan da surukai suka sa, Jummai mahaifiyar Hauwa da kuma Ladidi mahaifiyar Na-Hauwa. Kowace tana sanye da tufafin rigar atamfa da zani da xankwali, kalar riga daban da kalar zani, wato shiga dai irin ta mutanen qyauye, ga atamfar dagaja-dagaja ga murjani an sa wuyansu. Hakanan shi ma Na-Hauwa yakan sanya suturar mutanen karkara kamar 'yar shara da wando da kuma tagiyarsu. Su ma 'yan matan garin kowaccen ta yi shigar da take nuna lallai su 'yan matan garin ne za mu iya ganin irin wannan shiga a jikin su Bele da Altine sanye da riga da zani kalolinsu daban-daban sun xaura xan kwali a kai. Hatta yaran da suke gaxa a bakin rijiya su ma sun yi xaurin qirji ne da zani kawai sai kuma xan kwali a kansu. Haka ma a wajen bikin aurensu Na-Hauwa an yi kixan lugude da kixan shantu, inda kowacce mace da take dandalin ta sanya suturar matan Hausawa. Ranar xaurin auren Na-Hauwa da Hauwa. Na-Hauwa ango ya sanya babbar riga da 'yar ciki da wando farare tar da baqar hula qube a kansa.

Idan muka koma tsarin tufafin da aka sa qofar gidan mai gari da jama'arsa, shi ma an nuno shi sanye da babbar riga da jan rawani ya yi kewaye da shi ya sanye da jar dara. Sauran

jama'ar gari da suke zaune gefe da gefe su ma su sa dogayen riguna, wasu riguna masu gajerun hannu, wasu 'yan shara, wasu babbar riga da 'yar ciki da wanda. Don haka wannan bincike yana ganin cewa suturun da aka yi amfani da su a wannan fim za a iya cewa sun dace da a kira fim xin Bahaushen fim dangane da yanayin tufafin 'yan wasa.

4.5.4.5 Tufafin 'Yan Wasa A Fim Xin *Malam Zalimu*

Shi zubin tufafin 'yan fim xin malam Zalimu, shiga ce irin ta gardawa, wadda ba ta wuce 'yar shara da wando ko kuma babbar riga da 'yar ciki da wando da kuma babbar riga da 'yar ciki da wando da kuma hula. Sannan matansu su ma suna sanye da rigunan atamfa da zani da xaurin xankwali. Wasu sanye da murjani kamar yadda aka gani a wuyan matar Liman wato Malam Zalimu.

Daga abin da wannan bincike ya gani na tsarin shiga ko tufafin 'yan wasa a cikin waxannan fina-finai za a iya cewa sun yi daidai, domin ba su yi amfani da suturun aro ba, wato sanya tuffin Turawa ko na Iyamuri ko na Yarbawa da sauran su. An taqaita wajen sanya tufafin gargajiyar Hausawa a kuma muhallan da suka dace. Misali sarakuna da hakimai da suka fito a fim xin *Qafar Ungulu* da *Juyin Sarauta* sun yi shigar sarakai kamar su babbar riga da aska biyu ko tara da wuyan wundi da aganiya da girken Nufe da rawani da hula. Magidanta sun sa kayan da aka san maigida a qasar Hausa yakan sa, wato doguwar riga da wando da hula ko kuma 'yar shara da wando da hula.

Haka su ma matan da suka fito a fina-finan sun yi shiga irin ta Hausawa sun sa riga da zani da xankwali da kuma gyale ga manyan mata kenan, amma matasan mata ba su yafa gyale ba. Da waxannan ire-iren shiga a za a iya cewa waxannan fina-finan sun cancanta da a kira su da fina-finan Hausa, domin fina-finai ne waxanda suka kare martabar suturar Hausawa a cikin kowanne fim da aka xauko.

4.6.5 Halayyar ‘Yan Wasa a Cikin Fina-finan Hausa

Hali zanen dutse in ji masu iya magana. *Qamusun Hausa* na jami’ar Bayero (2007) ya ce hali mufradi ne na halaye ko a jam’i, shi ne xabi’a, musamman ta mutum. A fagen nazarin fina-finan Hausa, akan kalli halayyar xan fim a cikin fim, domin a ga shin ya taka gagarumar taimako da ta dace a bisa matsayin da aka xora shi a kai? Ko kuwa ya bauxe wa umarnin darakta yana wuce gona da iri? Aminu, (2012) ya kira wannan siffa da “yan wasa”. Kamar yadda aka yi nazarin fina-finan a bisa zubinsu da jigonsu da harshensu da tufafinsu, to, a wannan fage an kalligagarumar taimako da ‘yan wasa suka taka ne dangane da matakin da kowannensu ya hau a cikin fim.

4.6.5.1 Halayya ‘Yan Wasa A Cikin Fim Xin *Bori*

Kusan dukkan ‘yan fim xin kowannensu ya taka gagarumar taimakosa kamar yadda ya dace bakin gwargwado. Misali, “gado sai xan gado” wannan batu ya tabbata a lokacin da xaya daga cikin ‘ya’yan Sarkin Bori ya tara yara ya tambaye su, me suke so, suka ce alewa, nan da nan ya yi wa aljannu magana suka aiko masa da alewa ta cikin qoqo, ya dinga raba masu. A nan ya nuna bajintarsa ta lallai shi xan bori ne, mai ta’ammali da aljannu. Ga yadda ganawar tasu ta kasance da aljani:

Xan Sarkin Bori: A’a a’a, ga mu gare ka sarkin Aljan Tuwitan reni,

Ga ni gare ka sarkin Taiki, ga ni gare ka Burhaza,

Gani gare ku Cagum, kuma kar ku zo yanzu Balala

Haba Rabi mahaukaciya kar ku zo yanzu akwai yara agabana,

Yau muna so mu ci kasuwar sama, yara!

Yara me kuke so? Waina? Qosai? Quli-quli? Biskit?

Duka suka ce a’a, sai ya ce me suke so? Suka ce alewa na leda. Can sai ya xaga wata qwarya sama ya kira Bagiro!!! Kafin ka ce kwabo, sai ga qwarya ta sauko daga sama cike da alewa taf, aka raba wa yaran…..

Xan Sarkin Bori: Ya fara kirari “sai ni babban sarkin bori, maganin qanana-qanana ‘yan bori, duk wanda ya ga ba zai iya ba ya ja da baya in ba haka ba wuta ta kama shi……”

Gagarumar taimako da sabon sarkin bori ya taka a cikin fim xin ta fito da al’adar ‘yan bori, misali idan yana buqatar wani abu take zai yi magana da aljannu su aiko masa, mun ga inda aka dinga aiko da shinkafa da kayan marmari da na lambu da su alewar xinya da sauransu. A

cikin fim xin Bori tsakanin sabon Sarkin Bori da yaran gari da ya tara mun ga ya yi musu kyautar alewa wanda bayan ya gama ‘yan surkullensa ya ba wa aljannu umarni su aiko da alewa, can sai ga alewa daga sama.

Babban tauraron fim xin shi ne Sani halayyarsa a fim xin ta dace da na xan bori.Musamman yadda ya riqa nuna alaqarsa da sauran ‘yan bori. Haka kuma ya qara fito da halayyar ‘yan bori a wajen hawa da sauka a filin bori, yakan kuma yi gagarumar taimako borin sosai. Za mu iya tabbatar da haka a ranar naxin Sarkin Bori. A matsayinsa na babban tauraro ya ba da kuxi da kyaututtuka daban-daban ga sauran ‘yan bori na kuxi naira dubu-dubu. Wanda hakan ta sa shi ya burge abokan hamayyarsa.

Shi ma limamin gari, a duk lokacin da aka zo zama a gidan maigari, yakan nuna halayyar malamai musamman wajen faxin gaskiya, Allah ya ce, Annabi ya ce, misali lokacin da ake yunqurin za a yi gidauniyar haxa kuxin gina sabon masallacin garin, wanda ya fito a matsayin Limamin gari shi ne xan Barno, wataqila an yi la’akari da cewar muatanen Borno masana Al’qur’ni ne, liman yakan jajirce lallai sai an yi wa addini hidima, don haka ya kawo shawara cewar kowa ya ba da kason kuxi da za a gina masallaci, don Allah.

Hatta lokacin da wani xan bori ya zo ya sanar da maigari saqon Sarkin aljannu, take Liman ya nuna bai kamata a yarda da maganar xan bori ba, domin shirka ce. Wato liman dai koyaushe ya kan nuna shi na Allah ne a cikin fim xin kuma duk lokacin da ya kamata ya taka gagarumar taimakosa ta malamin addini Musulunci yakan yi, tare da yin nasiha da kuma gargaxi a kan

Allah ya ce annabi ya ce: ga ma inda yake cewa: Babu wani abin bautawa da gaskiya sai Allah. Kuma addini “nasiha ne”.

Sauran qananan taurari a fim xin da suka taka rawa sun haxa da Gizago direban gidan su Asma’u wanda shi ya yi mata jagora zuwa gidan ‘yanbori ta yi bincike. Daman an san direbobi da halayyar shaye-shaye da kula da iyayen gidansu wajen yin biyayya da kuma gyara motar da suke tuqawa lokaci-lokaci.

Baban Asma’u da mahaifiyar Asma’u taurari ne da suka taka gagarumar taimako a fim xin bori. A lokacin da Asma’u ta shigo da tsarabar da kayan bori wanda sarkin bori Sulaiman ya ba ta, zuwa gida, an yi ta samun taqaddama tsakanin mahaifiyar ta da mahaifinta. Shi uban Asma’u yana ta murna da farin ciki ‘yarsa ta yi nasarar yin bincike tun da ga shi ta shigo da tsarabar qorrai da fatu da kambuna da guru da manyan layu tana bayyana amfaninsu ga jikin xan Adam a Bahaushiyar al’ada. Domin ilminsa bai kai nan ba, shi yana farin ciki shi ne ya ga ‘yarsa ta zo da wani abu sabo, kuma har hoto ma suka xauka shi da ita da kayan bori, yana mai cewa za a ajiye su domin tarihi saboda ‘yan baya. Amma ita kuma mahaifiyar Asma’u ta nuna ita fa ba ta son waxannan tarkace, don haka a tafi a zubar da su domin ba su da wani amfani. A qarshe dai, mahaifin Asma’u Talle da ‘yarsa Asma’u sun ci nasara a kan mahaifiyarta, domin shi kam ya goyi bayan ‘yarsa har ta kammala karatun digiri a Hausa, kuma ta rubuta kundin bincikenta a kan “Bori”.

Da waxannan halayen gwarazan taurari da sauran ‘yan a bi Yarima na cikin wannan fim xin to za a iya cewa shi wannan fim ne cikin Hausa, saboda halayyar ‘yan fim xin bai savawa

yanayin da aka san Hausawa da su ba, wato sun ginu ne a bisa tsarin da aka san Hausawa musamman Bori da yadda ake aiwatarwa da shi.

4.6.5.2 Halayyar‘YanWasa A Fim Xin Juyin Sarauta

Shi ma wannan fim na *juyin sarauta*, ‘yan wasa sun taka gagarumar taimakosu gwargwadon hali, Sarki da muqarrabansa duk sun nuna halaye irin na fada. Misali, an nuna halayyar munafukan fada da matan sarki da kuma ‘yan bori da bokaye. Sannan bari a xauki halin da bokanya ta nuna wajen yin asirai daban-daban da kuma karya wasu asirai da ‘yan bori suka yi wa wani xan sarki mai wuyan karyewa. A lokacin da wata matar sarki take son bokanya ta karya jifar da ake yi wa xanta wanda ya haukace ga abin da take faxa mata:

> Bokanya: Ai wannan asirin yana da wuyar karyewa, saboda da baqin aljani aka yi shi…..

Haka nan ma a lokacin da wani xan sarki ya dawo gida daga Sakkwato yana xan gagarumar taimako kai, tun da shi bai zauna gida ya ga yadda ake tafiyar da sarauta ba sai wani xan sarki Hayatu ya nuna shi faya qware a harkar iya mulki da nuna sarauta:

> Xan sarki Hayatu: Saka kayan sarauta ba yana nufin mutum shi ma ya zama mai sarauta ba, ya kamata ku zaunar da shi ku dinga koya masa yadda ake gaida sarakai.

Wato dai shi xan Sarki Hayatu yana nuna cewar shi fa ko a yanzu Sarki ya mutu to yana iya hawa karaga, domin daga ganin yadda halayyarsa take ka san ya goge. Bayan haka a sanar da

sauran ‘ya’yan sarki “ruwa ba tsaran kwando ba ne”. Shi kam ya fi kowa sanin yadda ake tafiyar da al’amuran sarauta.

Hakanan kuma gagarumar taimako da Malam na sakkwato ya ba da wato Sani ke nan ta dace da shi, ya kuma nuna cewar shi malamin allo ne domin an gan shi yana takarar Al’qur’ani mai tsarki da ka, sannan nan gefe yana koyawa wasu karatun litattafai na addinin Musulunci, can kuma ya zuba wasu suna rubutun Al’qur’ani a bisa allo, nan gefen kuma an hura wuta qananan almajirai na ta karatu babu qaqqautawa.Babban tauraron fim xin shi ne Sarki Yusufa,ya fito da matsayinsa na Sarki a qasar Hausa ta nuna juriya da xaukar fitintinu da kuma rigingimu da suka yi ta kunnowa a cikin gidan sarautar tun daga kan matansa da fadawansa da kuma ‘ya’yansa duka shi yake xauka. Wato idan tai daga-daga na qurya kan sha kashi, neman sarauta ya tayarda zaune tsaye. A cikin fim xin an ga yadda gidan sarauta ya shiga cikin ruxani, inda aka dinga bin malamai a fim xin da matsafa, an kuma bi dare, an bi rana, munafukai da magulmatan bayi suna ta kai komo tsakanin qarya da gaskiya. Amma duka waxanann faxi tashi Sarki Yusufa ya shanye su duka a bisa na matsayinsa na mai gwagwarmayar tabbatar da gaskiya da amana a fadarsa da cikin gidan da kuma na masarautar baki xaya.

4.6.5.3 Halayyar ‘Yan Wasa Fim Xin *Qafar Ungulu*

Shi ma kamar fim xin juyin sarauta ‘yan fim sun taka rawa bakin iko, bari mu ba da misali da gagarumar taimako da Hakimi ya taka wajen kashe wata matsala da ta kunno kai mai kama da

cin hanci da rashawa wajen naxa limamin wata unguwa. A inda aka yi wa masun Hakimi da mai unguwa alqawarin in an naxa Alhaji Rabi'u liman za a yi masu wani abu, alhalin ba shi ya canacanta a naxa ba. Jama'ar unguwa da suka ga za a naxa masu wanda bai cancanta ba, nan da nan suka kai qara gidan Hakimi cewa ba da sa hannunsu aka miqa Alhaji Rabi'u ba. Hakimi ya yi amfani da qwarewarsa a kan taqqadamar ya xauko aininhin wanda jama'a suke so, aka naxa shi a matsayin Liman. Sannan kuma ya naxe jawabin nasa da cewa:

> Hakimi: Yanzu a matsayinku na shuwagabannin al'umma da aka sa muku qur'ani kuka rantse, bai kamata ku cuci al'umma ba, mu muka ce ba za mu yi son zuciya ba, amma shi ne kuka yi irin wannan xanyen aiki……

Sun nemi gafara a wurin Hakimi, Hakimi ya yafe masu. Amma ya yi gargaxi kar a sake samunsu da irin wannan aiki. A lokacin da rigimar naxa sabon limamin unguwa ta kunno kai. Hakimi ya nuna halayyar dattaku da halin ya kamata wajen shawo kan matsalar. Abin da Hakimi ya yi shi ne, ya yi bincike ne, bai yarda muqarrabansa sun juya shi ba, kuma bai biye wa ra'ayin ba. Abin da Hakimi ya yi shi ne tambaya idan akwai wani mai qorafi a kan Alhaji Rabi'u, caraf sai Malam Abdulkarim ya ce shi yana da qorafi, wato sanin su da Alhaji Rabi'u bai tava zama wakilin Liman mai rasuwa ba, su Malam Aminu suka sani. Wanda shi ne wakili a kodayaushe. Hakimi ya tambayi Ladan shin haka ne? Wannan Alhaji Rabi'u da aka gabatar ba shi ne jama'a suke so ba? Ya ce e. Hakimi ya sa aka kira Malam Aminu ya tambaye shi kai ne kake wakiltar Liman mai rasuwa a harkokin na addini? Ya ce ee. Hakimi ya ce kowa ya fita amma, duka muqarrabansa su tsaya. Hakimi ya tuhumi Galadima da Wazirin gari, ta yaya suka gabatar da wanda jama'a ba sa so a matsayin sabon Limamin Unguwa? Kkuma bai da ilimin addini. Suka amsa Allah ya ba ka nasara ee haka aka yi, amma su ma sun danqa wa mai

Unguwa da Gadodamasu aikin binciken, in sun kammala su kawo masu rahoto domin a gabatarwa Hakimi. Daman an san sarakunan Hausa a fagen mulkin sarauta su ne masu jan ragamar al'amuran jama'arsu domin tabbatar da tsaro da zaman lafiya da kuma yin sulhu a tsakaninsu idan savani ya zo. Don haka, binciken da Hakimi ya yi sai gano Galadima da Waziri ba su da hannu a sauyin naxin mai unguwa. Waxanda aka wakilta ne suka yi halin cin amana, wato sun karvi kuxi hannun abin duniya a hannun Alhaji Rabi'u domin su sa a naxa Liman.

Halayyar wannan Hakimi Qasimu ya nuna cewar shi mai dattaku ne da sanin ya kamata, don haka wannan bincike yana ganin gagarumar taimako da Hakimi ya taka da kuma waxanda suka haddasa hatsaniyar wato 'yan fada, su Gadodamasu da Maiunguwa ya yi dai-dai halayar masarautun qasar Hausa.

4.6.5.5 Halayyar 'Yan Wasa A Fim Xin *Na-Hauwa*

Shi ma kamar sauran fina-finan da suka gabata. An gano cewar kowanne xan wasa ya taka gagarumar taimakosa bakin gwargwadon hali. Sai dai a wani wuri xaya tal, Na-Hauwa yakan zaqe tare da nuna damuwarsa wajen yin magana gatsai ga mahaifiyarsa, yin haka ya savawa al'adar Bahaushe. An xauki lokaci Hauwa ba ta haihu ba, domin haka mahaifiyar Na-Hauwa ta ce a tafi asibiti a aje a yi gwaji, a ga shin matsalar rashin haihuwar a jikin mijin ne ko matar? A qoqarin da likita yake bayani a kan matsalar, da ta hana haihuwar, ya ce ai matarsa ce take da matsala a mahaifa, sai Na-Hauwa ya buxe baki ya ce "**qarya kake likita**". Sannan

ya qara kallon mahaifiyar ya ce “**Ba ke kika ce mu zo ba, kin ga irinta!**”. Wannan halin da ya nuna akwai zaqewa kuma a gaban mahaifiyarsa. Kodayake, ita mahaifiyar tasa, ta burge ‘yan kallo, domin take ta taka masa birki, har ta so ta yanke shi da mari. Alamar cewar Na-Hauwa bai yi daidai ba, domin mahaifiyar cewa ta yi “**zan kwaxa maka mari Na-Hauwa**”, ka ji ko, ka kyale shi a ofishinsahar ka ce da shi munafiki da yake kai qaton qauye ne”.

A nan an nuna halayyar Na-Hauwa, bai yi daidai da xabi’ar Bahaushe ba. Kuma mahaifiyar tasa ta yi maza ta gyara halin nasa. Kuma da yake fim xin qauye ne, sai ga shi Na-Hauwa ya amsa sunansa da qaton qauye a bisa halayyarsa a wannan fitowar da ya yi. Tabbas kowanne xan wasa a cikin fim xin nan ya taka rawa bakin gwargwadon hali. Amma halayyar jaruman wasan wato NaHausa da matarsa Hauwa ya qayatar. Misali bari mu fara da ita Hauwa a matsayinta ta matar Na-Hauwa, ta taka muhimmiyar rawa domin jawo hankalinsa da sanin qaddara da ibtila’in da ya faxa masa, cewa daga Allah ne, musamman lokacin da gobara ta lanqwame rumbunan hatsinsa. Lallai NaHauwa ya shiga damuwa bai iya cin abinci ba ya barci duk ya bi ya zazzautu. A dalilin haka ga abin da matarsa take faxa masa:

Hauwa: Ka xauka wannan abin da ya same ka jarrabawa ce daga Ubangiji, sai ka ga sanadiyyar haka, idan ka yi haquri, sai ka ga ya kankare maka zunubanka, amma shi ne nan sai ka zauna ka yi ta tagumi, kana zubar da hawaye fisabilillahi, rayuwa ta ba za ta tava samun walwala da farin ciki ba, idan kana zama haka. Ashe ni ban isa in faxa maka gaskiya ba. Ashe ba za ka yarda da qaddara ba.

Hauwa ta yi iyakar iyawarta na ganin ta dawo da hankalin maigidanta ya koma dai-dai, amma ina fa, sai rusa kuka yake yi, yana ta surutai kamar wanda ya zauce. Kodayake ga abinda NaHausa ya ce:

Na-Hauwa: Ba zan yarda ba! Akwai wanda yake nema na da baqin ciki, an je an banka wa runbuna wuta. Don haka, wajibi ne in je in sami malami ya buga min qasa ya gaya min waye ya zo ya hurawa rumbuna wuta, don haka ki ja bakinki ki yi shiru wajen mai kara-kara zani …….. duk wanda ya ce kara-kara lalacewa ce ta qare a kansa.

Idan muka sake komawa kan taurarin wasan wato Hauwa da Na-Hauwa, a lokacin da suke samari, lallai sun yi soyayya irin ta da can wacce aka san Hausawa da ita a dandali, in kuma zuwa taxin ne akan yi ne da abokiyar rakiya, ko kuma da rana ido na ganin ido, tare da faxin kalamai masu daxi.

Ladidi mahaifiyar Na-Hauwa ta taka gagarumar taimako gazawarta na rashin samun jika daga xanta Na-Hauwa bayan an yi masa aure, daman an san iyaye mata sukan taka rawa irin wannan a cikin al'umma. A taqaice, ta aika aka kira NaHauwa ga abin da take cewa:

Ladidi: Ba gaira, ba dalili, auren shekara da shekaru ba haihuwa? Ban ga 'ya'ya da masu yi mini yiyi ba? Ina so in ga jikokina, kar ka mai da ni mai baqin baya, in gama rayuwa, in bar duniya ban ga jikokina a gabana ba, ina dalili!!!

Na-Hauwa: Umma a yi haquri, mu bi abin nan a hankali in Allah ya yi da rabo ……

Ladidi: Kamar ya? Ba zai yiwu ba, tunda ka zavi zama da matarka, sai ka shirya mu je asibitin birni a gwada, idan matsalar a jikinta take zan aura maka mata uku a rufe gurbin da aka rasa. Idan matsalar a jikinka take mu rungumi qaddara…….

A nan Ladidi ta taka rawa sosai, domin ta nuna tana da iko da xanta, kuma daman an san da dama iyaye mata sukan nuna irin wannan halayyar idan aka samu matsalar rashin haihuwa daga ‘ya’yansu a rayuwa ta zahiri.

4.6.5.5 Halayyar ‘Yan Wasa A Fim Xin *Malam Zalimu*

To, halayyar ‘yan fim xin ta yi dai-dai bakin gwargwado a cikin wannan fim na *malam Zalimu*, wadda za a iya cewa lallai fim xin Hausa ne a bisa halayyar ‘yan wasan. Domin duka ‘yan wasan da su kansu gardawan kowannensu ya aiwatar da abin da aka ce ya aikata bakin hali daga darakta . Sai dai malam Zalimu, ya so ya wuce gona da iri, bayan an mayar da shi biri. Domin ya shiga tsorata matan unguwa da kuma neman ya dinga bin matar wancan gardin da ya mayar da shi biri. Wato wannan shi ne ake kira wace gona da iri a fim, wato “*over reacting*” a cikin harshen Ingilishi. Gardawan da suka dinga wasa da kura da biri a dandali ya qayatar, kuma sun taka gagarumar taimako da ta dace da matsayin da suka hau na ‘yan wasa.

Mun ga inda Talle gardi, ya ba biri umarni ya zauna ko ya tashi ko ya kwanta ko ya yi tsalle kuma duk yana yi.

Sannan idan muka dawo kan gardawan tsangaya, a nan ma, gardin da ya baqunci qauyen da Malam Zalimu yake ya nuna bajintarsa inda ya maida Malam Zalimu biri. An kuma nuna Malam Zalimu a lokacin da yake koyar da almajiransa karatun allo a tsangaya yana tilawa kamar yadda aka san malam allo sukan yi, yana cikin tilawa almajirai sun dawo daga bara, sai ya ce kowannesu ya kawo abincin da ya samo daga wurin bara ya tava tukunna, wanda ya fi daxi ya ce a kai wa matar malam domin shi yau gidansa ba a xora sanwa ba.

Su ma halayyar da almajiran Malam suka nuna ta yi daidai da gagarumar taimako da suka taka, an nuna su sun tafi samo karan da za a hura wuta karatun dare, sannan a hanya faxa ya kaure a tsakaninsu wanda haka ya yi sanadiyyar gudun wani, don kullum ba abinci, sannan in ya samo abincin manyan su qwace.

A nan mun ga yadda aka tattake wuri dangane ta tsattsafe fina-finai guda biyar masu xauke da sifoffin fina-finai cikin Hausa. Fina-finan kuwa sune na *Malam Zalimu* da *Qafar Ungulu* da *Na-Hauwa* da *Bori* da kuma *Juyin Sarauta.* Yanzu gaba kuma za a kalli sauran fina-finan guda biyar masu zubin fina-finai da Hausa.

4.7Fina-finai Da Hausa A Mizanin Nazari

Kamar yadda aka faxa a baya cewar, kashi na biyu na wanann babin, zai ba da fifiko ne a kan fina-finan da aka yi su da Hausa, an yi haka ne don a xora su bisa mizanin nazarin fina-finan Hausa; zubin ‘yan wasa da jigon wasa da harshen ‘yan wasa da tufafin ‘yan wasa da kuma halayyar ‘yan wasa a cikin fim.

A babi na biyu na wannan aiki, masana sun ba da ma’anar zubin wasa a matsayin yadda aka qulla labarin fim ta hanyar wanzar da shi daki-daki, daga wannan fitowa zuwa waccan fitowa ba tare da qulin zaren labarin ya tsinke ba a yayin aiwatarwa har zuwa qarshen fim xin. (Aminu, 2012:109). A wannan vangare an kalli zubin fina-finai da Hausa na fim xin *Gwaska* da *Ibro Hotiho* da *Qara’i* da *Su ma Mata ne* da kuma *Doya da Manja*. Kamar yadda aka faxa a baya, an yi amfani da siffofi nazarin fim wajen tace waxannan fina-finai. An fara da kallon zubin fina-finan ne, domin ko ba komai wata dama ce da za ta ba da matashiya domin a san inda kowanne fim ya sa gaba kafin a yi nisa da qwanqwance fina-finan xaya bayan xaya.

4.7.1 Zubin Fim Xin *Gwaska*

Kalmar Gwaska karin harshe ne na rukuni da ‘yan damfara, ko a ce da su ‘yan hanya ko ‘*yan yahoo-yahoo* suke amfani da shi ga wanda ya qware ko shugabansu a wannan harkar. Amma a Hausa za ta iya zama wanda ya gagara a kowanne fanni, kamar wanda ya fi kowa kuxi, sai a ce gwaskan mai kuxi ne, wanda ya fi kowa iya kasuwanci, sai a ce ai wane shi gwaskan ‘yan

kasuwa ne. (Hira da Adam Zango 20/1/2018). Ganin yadda shi jarumin fim xin kuma Daraktan fim ya xauko wasu abubuwa daga fim xin *Kiript* da *Krish* na Indiyawa shi ya sa shi ma ya yi tunanin bari ya xauko wata kalma ta Hausa za ta yi daidai da gagarumar taimako da jaruman Indiyawan suka taka, ya saka wa nasa fim xin, wato ita ce Kalmar Gwaska. Wato shi ya fito a matsayin mugun jarumi wanda ya qware a wajen shiga gidajen mutane da al'umma domin ya taimaka musu.

Fim ne wanda Adam Zango ya shirya kuma ya ba da umarninsa. Gwaska yana xaya daga cikin fina-finan da zubinsu ya yi dai-dai da zubin fina-finan Indiya da Amurka. Wannan kuwa ba zai rasa nasaba da wanko fim xin Indiya na Krish da kuma na Amurka mai suna *Power Ninja* da aka yi ba. In ban da 'yan qare-qare, da kwaskwarima da aka yi tare da amfani da harshen sadarwa na Hausa a fim xin, da kuma sauyin muhallai na fitowa-fitowa inda aka yi amfani da gidajen irin na Turawa.

An tsara fim xin ne a bisa yadda wasu matasa suke haxa kansu don su dinga taimakon 'yan uwansu matasa wajen qwatar wa kansu 'yanci daga hannun azzulaman mutane. Shi dai Gwaska yana da dabara da wayau da yake yi domin ya qwatowa al'umma haqqinsu. Yana iya shiga ko'ina da irin xabi'u nasa da dabaru, wannan ya ba da dama ya je yana qwatowa marayu haqqinsu, ko kuma shugaban da ya ci dukiyar al'umma. Shi dai Gwaska yakan bi manyan azzalumai gari da masu kuxi da gwamnati yana karvar dukiyarsu yana rabawa talakawa, kamar yadda mukan gani a wasu fina-finan Indiya irin su *Kirish* da *Pul au Angar*. Kodayake, Falalu Xorayi wanda shi ne daraktan fim xin ya ce, ba wai ana nuna fashi ba abu ne mai kyau ba. Amma dai shi Gwaska duk wanda yake xan fashi ne ko kuma qasurgumin varawo da ya gagari al'umma, to in dai Gwaska ya sami labarinsa to, zai je da jama'arsa su qwatowa

mutanen wannan gari ‘yancinsu tare da xibar dukiyar azzaluman ya rabawa jama’a, ka ga kamar shi ma yana fashin kenan.

Gwaska yana da baiwa guda biyu: na xaya yakan tashi sama, gas hi da qarfi wai don qartai goma sun riqe shi yana iya zubar da su. Don haka, duk qoqarin da aka yi domin a kama shi ya faskara.

Shi dai Gwaska tun yana yaro, Allah ya yi shi mutum ne da ba ya sonzalunci. Ganin ya taso a gidan Basawa masu harkar hodar Ibilis tun yana yaro, ya qyamaci mummunar sana’ar, shi ma Gwaskan qaddara ce ta faxa masa har ya sami kansa a gidansu. Lokacin da Basawa suka je kwaso ganima aka haxo da shi, har aka raba shi da iyayensa, koda ya je daga baya, ya gamu da wata halitta da takan zo masa da dare tana taimaka masa. Sannan har ta shiga jikinsa, suka saba da ita. Daga baya ya fita daga gidan Basawa ya je ya kafa nasa sansanin. Yana amfani da dodon fuska (*marsk)* ya rufe fuskarsa, yakan sa wata baqar riga mai fika-fikai wadda da ita yakan tashi sama. A taqaice, sai da Gwaska ya je ya tarwatsa waxancan Basawan, sannan ya kwashe dukiyar da suka tara, ya rabawa talakawa, ba tare da shi ya xauki ko da qwandala ba. Zubin wannan fim bai bi tsarin rayuwar Hausawa ba, daga xan abin da aka ji kuma aka gani shi ne ya sa wanann bincike yake ganin fim xin ya xauki siffar fina-finai da Hausa, amma ba za ace fim xin Hausa ne ba.

4.7.2 Zubin Fim Xin *Ibro Hotiho*

Fim ne wanda aka gina shi a kan wasu mutane da ke garin Faxisonka kuma ma'abota zuwa silima kullum. Sukan gayawa junansu abin da za a nuna a silima tun da rana tare da ba wa gidan silima muhimmanci a rayuwarsu, burinsu dai su kalli fim xin Indiya. Wataqila wannan ba zai rasa nasaba da yadda aka san Bahaushe da son kallon fim xin Indiya tun shekaru da dama da suke shuxe ba. Amma su dai burinsu a nuna fim xin Indiya na "Hotiho" kuma shi Hotihon ya tafi wajen mai gidan kallon Shitu mai silima wai sai ya nuna masa hanyar da zai bi ya je Indiya. Don haka, yana matuqar son yarinyar cikin fim xin *Hotiho* wato "Hema Malima". Aka rubuta masa kwatancen yadda zai samu gidan shi aihinin Inyamurin da yake rarraba kaset-kaset na Indiya, wanda yake zaune a Birni wato "Baban *Chinedu*". Abu kamar da gaske, Ibro ya xauki hanya sai birni. Domin sai da takai Ibro ba ya iya barcin kirki a kan qaunar da yake wa matar da ya sa wa suna Hotiho alhalin shi Ibro ne Hotihon. Ga ma abin da yake cewa abokinsa Daushe.

Ibro: Indiya da muka kallo, wallahi sai na ji qaunarta ta shiga raina.

Da na yi juyi sai na ji ana yin waqar a kunnena, ban yi isasshen barci ba, da

zarar na yi juyi, sai in ji ana yi min waqar Hotiho

Daushe: Mu je wurin Shitu mai silima ya ba mu adireshin, ogan nasu na

Cikin birni. Wai za su ga baqo a Indiya …

Bayan kwana biyu Ibro ya haxa guzurinsa, ya yi shiga irin ta Indiyawa, ya kuma gayyato duka abokansa da suke kallon fina-finan Indiya a silima, su zo su yi rakiya. Kowa ya ba da saqon

abin da Ibro zai sayo masa idan ya sauka a Indiya: Daga masu cewar idan ya je Indiya a gaida masa da Karishma Kafur, sannan a taho da hotonta, wani ya ce ‘yaruwarsa daman Madam Hori ce don Allah a gaida ita. Wani ya ce a gaishe min da Kadarkan zai ba ka takalma masu lanqwasa ya kawo masa. Wani ya ce idan ka je, ka gaida min Reka da Darakta John Liver.

Ibro ya kai birni, ya sauka gidan Baban Cinedu, aka ba shi masauki da abinci kuma Baban Cinedu yana ta hidima da shi, amma babu alamar tafiyar, domin Ibro ya vata gagarumar taimakosa da tsalle, ya ci amanar Baban Cinedu ya tsiri halin xauke-xauke da kashen-kashen kuxin ubangidansa, da haka har asirinsa ya bayyana, aka fatattakeshi daga gidan Baban Cinedu. Da matar Ibro ta ji shiru-shiru maigidanta bai dawo ba, sai ta je ta sami Shitu ta bi sawunsa. Aka kuma yi sa’a suka yi kicivis da Ibro yana yashe a cikin tafasa bayan ya sha bugu a hannun mijin wata mata da ya je yana mata maganar kwartanci.

A mataki na biyu na zubin fim xin Ibro ya fito a Hotihon namiji domin ya zama mijin tace, shi ne wanke-wanke, da shara da wankin kaya da guga da girki da yin duk wasu ayyuka da ya kamata a ce matar gida take yinsa. Ga kaxan daga irin wainar da aka toya tsakanin Ibro da matarsa, yana mata habaici, yana wanke-wanken kwanukan gidan.

Hotiho: Duk wanda ya takura mana, Allah ka takura masa, ko waye, don alfarmar Annabi, ke! ke!! ke!!! Ni fa na daina wannan wahalar, ee

Matar Hotiho: Daman waxannan addu’o’in da kake yi da ni kake?

Hotiho: Ina yi ne domin ki ji

Matar Hotiho: Kana nufin ba za ki yi wanke-wanken ba? Xan zaki ya girma? Sai ka yi wanke-wanken nan!!!

Hotiho: Ke ni fa na cazawa kaina, sai da aka ce ban isa auren nan ba, na ce sai na yi. Aka ce masifa ce …

Matar Hotiho: To dole sai ka yi, in kuma ba ka yi ba, ba kai ba cin abinci a gidan nan.

Hotiho: To na ji, zan yi, amma don Allah kina qaunar Allah? To don Allah idan na yi, ki ba ni abinci, kuma a kula da ni.

Matar Hotiho: To dole in bayar da abinci, amma in dai aka ce za a bijire min, to za a ga bijirewa, Don Allah ka yi maza. Ina so in ga gidan nan an tsaftace shi.

Hotiho: Wannan masifa Allah ya raba ni da ita.

Bayan haka, an nuna, da wuya ta yi waya Ibro ya gudu, zuwa birni, matarsa zaman kaxaici ya isheta, dole ta tafi birni neman mijinta Ibro. Allah ya taimake ta, ta gan shi ta dawo da shi gida. Kuma ta tuba ta yi masa biyayya.

Sai da kuma kash! Hotiho, bai cika burinsa ba, na zuwa Indiya, domin ya vata gagarumar taimakosa da tsalle. Matar Hotihodaman ta san mijinta kumama ne, domin ita ce, takan tare masa faxa a wasu lokotu, yana da baki amma babu qarfin qwanji. Shi ya sa ya ci suna biyu a fim xin watoIbro Hotiho, mutum kumama, malalaci, sannan suna na biyu shi ne na sunan Indiya na fim xin, yana son ya je Indiya ya ga Indiyawa masu suna Hotiho. A nan, za mu iya

cewa wannan fim bai xauki tsarin fina-finan Hausa Hausa, domin zubinda aka yi masa ba shi cikin tsarin tadodin Hausa.

4.7.3 Zubin Fim Xin *Qara'i*

Dattawa uku ne, Lado da Barau da Halliru, dukkansu magidanta ne, masu zaman kashe wando a gari kullum suna zama gindin bishiyar tsamiya babu aikin fari balle na baqi. Yau a yi gulmar gidan wancan, gobe a leqa matar wannan. Matansu da 'ya'yansu kullum cikin rashi a gidansu, babu kuxin makarantar yara, balle na abinci. Zuciyar tasu ta qeqashe an kasa zuwan neman na kai, ga sana'o'i irin su turin-ruwa da faskare, aiki qasa da dako da buga bulo duka sun qi. Wanda har ta kai matansu suna yi masu Allah wadarai da irin wannan hali nasu na zaman kashe wando,wanda ba su samu yardar al'ada da addini ba, in matar Lado:

Matar Lado: Ni ba zan ce Allah ya ba da sa'a ba don ba neman halak aka je ba, sa ido sana'ar banza, abin da addini da al'ada ba su sa hannu ba, su kuka mai da aiki.

Suna cikin irin wannan zama ne, wani Alhaji ya zo wucewa ya yi masu albishir da zai ba su jari cewar wannan zama da suke bai dace ba, a qarshe kuma ya danqa masu naira dubu xari biyar-biyar su je su ja jari. Sai dai kuma kash! Ana zaton wuta a maqera sai ga ta a masaqa. Abin da ya biyo baya shi ne sai suka zuba kuxin nan a harkar duniyanci, suka sayi mota, suka sayo suturun Turawa, ana zuwa *party* da gidan *disco*. A taqaice dai sunan fim xin *qara'i*, wato

sa’ad da suke yara, ba su more rayuwarsu ba, don haka, sai suka xibi kaso mafi tsoka na kuxin aka dinga holewa, har sai da kuxi suka qare. Ido ya zo ya raina fata. Daga qarshe suka tuba, suka koma zuwa sallah a kan lokaci da kuma aikata ayyukan alhairi bayan sun ga uwar bari. Ga abin da Barau yake cewa a tasa shawarar da ya ba su, kuma sai aka yi rashin sa’a suka biye masa, da yake masu iya magana sun ce “mai rabon shan duka ba ya jin kwave” ga yadda ganawarsu ta kaya:

Lado: Ina Barau, me shawararka a kan wannan kuxi?

Barau: Don Allah zan tambaye ku, tun yaushe rabonku da ku ji wani daxi da hutu a jikinku? Ni a tawa shawarar, qara’i ya kamata mu yi, kamar ba a yi salla ba ne, domin akwai basussuka a jikinmu, na farko tukuna, jin daxi bamu tava jin ta ba, sai ga wannan kuxin a hannunmu, sai mu xan ji daxi, tukunna, daga baya sai mu zo a dawo. Layi wannan shi ne qara’i.

Lado: Ina Halliru, na fahimci Barau, so yake mu ajiye girmanmu mu xan tava harka, Allah wallahi! Allah wallahi, ni ina ciki, barin ka za mu yi a tasha Halliru.

Halliru: Wato ni yanzu qara’in, a ajiye ko za mu canza gari, ko za mu nemi Sani sauti domin ya samu a hanya …….

Sai suka tafi, wurin Sani sauti, ya tsara yadda za su yi shiga irin ta ‘yan zamani. Gundarin baqi ba ‘yan kame-kame ba. Sanda muke matasa ba mu samu kuxi mun hole ba, yanzu za mu hole.

A qarshe dai girma ya yi gardama domin sutura ita ce mutum, Bahaushe xan mutunci dattijo xan shekara saba'in (70) ba zai sa riga *Polo* ko *shirt* ba da wando *jeans* ya kafa tabarau baqi qwalele ya yi zanzaro yana ta yawo a gari. Domin a tabbatar da halin tir da al'ummar Hausawa ta yi da irin wannan sutura.

Ga kaxan daga cikin kalaman mata dattawa wanda yake nuni da cewar halayen mazajensu sun savawa al'adar Bahaushe.

Matar Halliru: Malam lafiyarka kuwa? Inna lillahi wa inna raji'una.

Matar Lado: Mene ne haka? Me ya sameka? Me ya haxa Bahaushe da irinwannan shiga?

Matar Barau: Malam me zan gani haka? Sai ka ce dattijon biri?

Qarshen tika-tika-tik, kuxi sun qare, aka sayar da mota, Sani sauti ya sayi mota dubu saba'in. aka koma gidan jiya. Da na sani qeya ce. Daga ganin zubin wannan fim xin an san bai bi sahun zubin fina-fina Hausa ba, kenan ba zai samu shiga cikin sahun fina-finan Hausa ba , sai dai a ce fim ne da aka yi shi da Hausa.

4.7.4 Zubin Fim Xin *Su Ma Mata Ne*

Fim ne wanda aka tsara shi ta fuska biyu zuwa uku. Fuska ta farko an tsara shi ne domin a nuna irin zaman doya da manja da yakan auku a tsakanin Yarbawan Legas da Hausawa mazauna can. An sami hatsaniya da kashe-kashen rayuka da qona dukiyoyi a dalilin wani bukin tsafin Yarbawa da sukan yi shekara-shekara na “oro”. Bisa sharaxin mata ba za su fita waje ba a wannan rana. In ko har mace ta yi ido biyu da matsafan, lallai za su kashe ta ne. Domin qa’idar bautar ke nan matan Yarbawa su dama sun san haka, don ba sa fita a irin wannan rana. An yi rashin sa’a Alhassan Kwalle mijin matar da aka kashe Bahaushiya, sun sami savani shi da matar, ya kore ta daga gida tsakar dare. A kan hanyarta neman tudun mun tsira, ta yi gamo da matsafan. Ta faxa hannunsu suka fille kanta, kashe ta da aka yi, ya yi sanadiyyar tashin hargitsi tsakanin matasan Hausawa da na Yarbawa a Legas. Ana ta sare-sare da qone-qone. Matasan Hausawa lallai sun fusata, domin ko da suka kai kuka gidan sarkin Hausawan, sarkin ya fara jawabinsa a kan su yi haquri a bi abin a hankali qi suka yi. Ga jawabin sarkin:

Sarkin Hausawa: Ku saurara, ku saurara duka na ji qorafe-qorafenku, amma ina jawo hankulanku da ku yi haquri. Za mu xauki mataki na shari’a, domin mu qwatowa kanmu ‘yancinmu……

Matashi: Allah ya ba ka lafiya, yanzu a ce abin ya qazanta har matanmu ake yankawa a je ana yin tsafi da su? Kuma a ce mu yi haquri, to wallahi ba zai yiwu ba, kawai inna rududu za mu yi musu, mun san sun fi qarfinmu a nan Kudu, mu je mu yi iya qoqarinmu, in sun kashe mu, ‘yan uwanmu da suke Arewa za su rama mana.

Wani saurayi ya shigo fada da gudu yana haki: Yallabai wallahi mutanenmu suka je suka qona gidan Bayarabiyar nan mai abinci, kuma ga samarin Yarbawa nan

runduna guda, sun taho xaukar fansa, wallahi ba za mu iya ba cimmusu ba, sun fi mu yawa……..

Wani saurayi: wallahi ba za mu yarda ba, qasa xaya ce, Nijeriya ta kowa ce qasa xaya, al'umma xaya.

Wato dai a nan ana so, a nuna cewar tashin hankali da yakan auku tsakanin al'ummar kudanci da Arewaci ba shi da alfanu kuma babu inda zai kai qasar nan, face ci baya, dole a yi haquri da juna a zauna tare, duk da yake ana da bambancin al'adu da kuma xabi'u.

A xaya zubin fim xin, an nuna yadda Hausawa karuwai da 'yan daudu suke zaman barikanci a Legas. Magajiyar karuwai tana rarraba karuwan zuwa ga mabuqata irin su Dayo da su Femi. Daga qarshe shi xan xaudun *Ado Gwanja* ya kai wa Dayo *baby nice* kuma ya sake dawowa ya xauki wata ya kai masa domin a ci gaba da rawan gaban hantsi kamar yadda aka san bariki take.

Zubi na gaba shi ne an nuna gidan wani Alhaji, uban Al'Amin wanda shi Al'Amin ya yi karatu a qasar Turai ne, kuma shi Al'Amin ya dage lallai yana son ya yi bautar qasa a Legas ne, duk da yake Alhaji ba ya so Al'Amin ya yi nisa da gida, haka nan ya haqura ya bar shi, ya tafi. Wata rana yana cikin tafiya da motarsa sai wata yarinya *baby nice* ta nemi taimakonsa ya rage mata hanya, ashe varauniya ce, aka haxa baki da ita, suka qwace masa kuxi, ta je ta biya kuxin xaki.

Daga baya Alhaji ya sanar da kwamishinan ‘yan sanda na jihar Legas domin a kamo varayin da suka yi wa Al’Amin fashi, kuma an ci nasarar kama su. Alhaji ya sanar da Al’Amin ya tafi Legas ya xebo kayansa ya dawo gida daga nan sai ya ga yarinyar da ya ce an haxa baki da ita aka yi masa fashi. Domin shi ma Alhaji ya ce zai so ya ga yarinyar da Al’Amin ya taimakawa, ita kuma ta cuce shi. Daga qarshe dai *Baby nice* ta koma Abuja da zama, gidan da aka kai ta aiki, ashe gidan Alhaji ne baban Al’Amin wanda ta yi wa fashi a Legas. *Baby nice* tana ta faman aikinta a gidansu Al’amin, shi kuwa daman ya sake komawa qasar waje domin aikin Alhaji. An yi sa’a ana ta yabon *baby nice* ta iya girki mai daxi kuma takan mayar da hankali wajen aikinta. Ashe *baby nice* ba varauniya ba ce, ta dai taka sawun varawo ne, tace ta shiga matsala ta rayuwa, amma ba a son ranta aka yi wa Al’Amin fashi ba. Kuma da aka yi fashin ita ta hana a kashe shi, ta hana a tafi da motarsa, ta hana a harbe shi ko a buge shi. Ta je neman aiki gidansu Al’Amin ne ba tare da ta san gidansu ba ne. amma tana neman afuwa, kuma ta ce ita ba karuwa ba ce amma yanayin quncin rayuwa ya sa ta samu kanta inda take a bariki.

Idan za a iya tunawa Alhassan Kwalle wanda ya kori matarsa daga gidansa tsakar dare har ta faxa hannun matsafan nan, tana xauke da wata qaramar yarinya, ashe da ta fito zuwa ta yi ta danqata ga maqwabta, su maqwabtan ne suka riqe *Baby nice* har ta girma ba ta san uwarta ba balle ubanta, daman tuni aka kashe uwarta. Daga qarshe bayan Al’amin ya zaunar da Alhaji ya yi masa bayani dalla-dalla a kan baby nice cewar ita ce yarinyar da ta yi masa fashi, amma fa ba ‘yar fashi ba ce, larura ta sa ta yin fashin.

A qarshe *Baby nice* an sauya mata suna da Rahma sannan kuma Al'Amin ya aure ta bayan sake aikawa Legas wajen wanda ya riqeta. Ashe shi kuma yayan Alhaji suna wa da qani ne da mahaifin Al'Amin. A qarshe Al'Amin ya auri Rahma. Shi ma wannan fim xin kamar sauran fina-finai da suke cikin wanann rukuni ba za a kira da shi da fim xin Hausa ba, sai dai a ce fim ne da aka yi shi da Hausa, domin ya savawa tsarin rayuwar Hausawa tun daga farko har qarshensa.

4.7.5 Zubin Fim Xin *Doya da Manja*

An gina labarin fim xin ne akan wani xan sanda da wata mace. Bayan an kafa sabuwar gwamnati a qasar, kuma waxansu aminai da suka taka rawa a tsohuwar gwamnati da ta shuxe sun shiga ruxani domin sun saci kuxi maqudai. Wanda zuwan sabuwar gwamnati ta fara binciken gano su aka fara neman binciken sunayen tsofoffin manyan 'yan sanda, gudun kar a bayyana sunayen asirinsu ya tonu, sai suka fara tunanin ya za su yi ta yadda za su kawar da fitar da sunayen daga hannun gwamnati. Kar ma a kira su. Daga nan sai suka sami wani bokansu da zai danne sunansu ko da an kira su, ya zamana sunan ba zai yi tasiri ba, domin kiran sunan zai iya jawo masu matsalar a kai su gidan yari ko kuma a gicciye su. Sun je wurin boka, boka ya ce sai an yi yanka, yankan da za a yi ba na dabba ba ne, na mutum ne, kuma mace za a yanka fara, kyakkyawa. To dama Xansanda Balarabe yana da wata budurwa Bahaushiya, amma saboda wasu dalilai na zaman rayuwa, suka sami savani suka rabu. To a ranar da suka rabu xin, yana wurin aiki, binciken motoci. Ta yi masa wulaqanci ta zavi wani a kansa, to ana cikin haka, ashe waxancan manyan jami'an 'yansanda sun ci nasarar kamo wata

yarinya fara kyakkyawa kamar yadda boka ya umarce su. Suka nemi wasu ‘yan sara suka, suka qaddamar da aiki. A kan hanyarsu ta zuwa gidan boka sai ‘yan sanda suka tare motar, aka fara bincike ashe yarinyar nan tana cikin buhhunan ciyawa sun danne ta da su cikin motar, bayan an bincika, sai varayin suka ranta cikin na kare. Xan sanda ya ceto rayuwar yarinyar nan mai suna Fasila. Ashe Bayarabiya ce, shi kuma Bahaushe kafin ka ce me, soyayya ta qullu a tsakaninsu, har ana batun aure.

Da aka zo batun aure, sai wasu daga cikin dangin yarinyar suka ce ba za a ba Bahaushe auren yarinyar ba akwai matsala, domin Hausawa suna da saurin saki, wasu dangin yarinyar suka ce, ai ya kamata a ba shi ita ya aura, mutumin da ya ceci yarinya, haba jama’a! Kuma suna zauna a Arewa ne, ashe duk wannan badaqalar da ake yi, boka yana jiran a kawo masa abin yanka. A qarshe jami’an ‘yansanda suka faxawa boka, ai yarinya ta gudu. Sai yace to, ai dole ita xin za a nemo duk inda take, in ba haka ba, asirinsu zai bayyana kuma qarshenta duk mutuwa za su yi. Jin haka, hankalinsu ya qara tashi, sai aka sake bai wa wasu ‘yan ta’addar dama su je su cafkota duk inda take. A qoqarin neman nata, sai labari ya kai kunnen saurayinta xansanda, don haka, aka qara xaukar matakan tsaro, wata rana ta fita suka biyo ta, suka sake cafketa, ashe ‘yan sanda masu farin kaya suna bibiya, a qarshe aka kama su, aka hukunta su bisa laifuka biyu manya na xaya ga su varayin gwamnati na biyu, sun yi niyyar kisan kai.

A qarshe an dai sakarwa Balarabe ya auri Fasila. Shi ma wanann fim xin cike yake da tsarin xabi’u na baqi maqwabtan ko kuma a ce abokan zaman Hausawa kamar Turawa da Yarbawa,

don haka wannan bincike yake gani ba fim xin *Doya da Manja* ba zai amsa sunansa da fim xin Hausa ba, amma dai za iya sa shi cikin fina-finai da Hausa ko kuma a ce fim ne da aka yi shi da Hausa kawai.

4.8 Jigon Fina-finai da Hausa

Qamusun Hausa (2006) ya nuna cewa ana ganin jigo a matsayin ginshiqi ne ko manufar da aka gina fim kansa. Kuma dama manufar fim ita ce a isar da saqon da fim yake qoqarin isarwa ga ‘yan kallo. An kalli jigogin fina-finan Hausa waxanda aka gina su da Hausa kamar fim xin *Qara’i* da *Ibro Hotiho* da *Gwaska* da *Doya da Manja* da kuma *Su Ma Mata Ne.*

4.8.1Jigon Fim Xin *Qara’i*.

Kamar yadda sunansa ya nuna ana nufin ramako na wani abu da mutum bai yi ba a baya wanda ya wuce shi, kamar sallah qara’i. To shi wannan fim xin, xan wanki da xauraye ne daga fina-finan Nijeriya wanda su Mr Ibu da Ukpana Ukwa suka yi. Don haka, jigon fim xin ba Bahaushen jigo ba ne, ya savawa al’adu da xabi’un Bahaushe dangane da yadda aka ga dattawa suna shigar suturar turawa da cin abincinsu da zuwa kulob-kulub da *party* ana shan giya da taba sigari a cikin gari a qauye ba birni ba, kuma wai su a tasu fahimtar sanda suke yara matasa, ba su samu sun hole ba. To, tunda yanzu an samu ‘yan daloli, bari a xan yi qara’in abubawan da aka ba a yi ba a baya.

A tsarin tunani irin na Bahaushe wanda yake zaune a karkara, wanda in ya sami waxannan kuxaxe yana xan shekara hamsin a duniya zai yi tattalinsu, ya gina kansa kuma ya ja jari ta yadda zai taimakawa al'umarsa. To, amma da yake fim xin kwafo shi aka yi, daga fina-finan iyamurai shi furodusan Rabi'u Garga da Daraktan Hassan Giggs ba su yi la'akari da cewar yanayin al'adun inyamurai da na Hausawa suna da bambanci ba, tana iya yiwuwa su a al'adarsu yin hakan ba matsala ba ce. Amma a al'adar Bahaushe akwai matsala, duk mutumin da aka ga yana irin waxannan halaye da aka nuna dattawan nan suna yi a cikin fim xin Qara'i, to lallai za a ce tsufa ya yi gardama kamar yadda wata yarinyar da suka tare a hanya da niyyar Barau yana sonta a matsayin wacce za su yi soyayya da ita ta faxi. Kuma al'umma garin suka yi yi musu tir da waxannan halaye nasu. Don haka wannan bincike shi ma yana ganin jigon wannan fim na Gwaska ba ya wakiltar tadojin Hausawa, don haka ba za kira shi da fim xin Hausa ba, sai dai ana iya kiran sa da fim da Hausa. Sai dai kuma a iya cewa guvatar al'adu na Bahaushe na iya kawo hakan a rayuwa ta zahiri, wato a sami dattawan da ke da wannan xabi'ar a cikin Hausawa.

4.8.2JigonFim Xin *Ibro Hotiho*

Shi ma wannan fim xin, kamar qara'i ne daga jin sunansa, ko ba a faxa ba an san yana da alaqa da Indiya. Jigon fim xin shi ne "so" ko kuma "qauna" wadda daman an san da dama daga cikin Hausawa mutane masu son kallon fim xin Indiya da son nuna fifikon son jarumansu na fina-finan Indiya. Wannan ko, ba zai rasa nasaba da, yadda al'umar Hausawa

suka kasance ma'abota kallon fina-finan Indiya sama da shekara hamsin da suka shuxe, a silima da kuma gidajen talabijin mako-mako. (Adamu 2004 da Gandu, 2006).

Ibro shi ne jarumin fim xin, kuma ya fito qarara inda yake son ya tafi Indiya domin ya je ya kai wa Hema-malina ziyara, wacce ta fito a jarumar fim xin Hotihon Indiyar gaske. Sannan akwai qaramin jigo wanda yake marawa babban jigo baya shi ne, shi karan kansa Ibron ya amsa sunansa na Hotihon, wato mijin Hajiya ko kuma a ce mijin ta-ce. Domin nuna yadda matarsa Marka wato Hadiza Kabara ta dinga juya shi a gida, tana sa shi yana ta yi mata aikace-aikace da share-share, sannan ba shi da wani iko a gidan a matsayinsa na maigida, alhalin shi ya kamata a ce yana juya akalar jagorancin gidansa. Jigon fim xin Hotiho Indiyanci da kuma mallakar miji da mata sukan yi wa mazajensu. Don haka, fim xin Ibro Hotiho wannan bincike yana ganin ba ya cikin sahun jigogin fina-finan Hausa saboda waxanccan dalilai da aka aka rattavo a sama.

4.8.3 Jigon Fim Xin *Su Ma Mata Ne*

An gina shi a kan jigon kaddara da ya faxa kan matar Alhasan Kwalle, a Legas, ta faxa hannun matsafan Yarbawa, suka fille kanta, hargitsi ya tashi tsakanin al'ummar Yarbawan Legas da Hausawan mazauna Legas aka yi qone-qone da kashe-kashe, wato xaukar fansa ita ta yi sanadiyar faxaxar yamutsi a tsakanin al'ummomin biyu. Yadda 'yar da matar Alhassan kwalle sake faxawa hannun mutanen kirki suke riqe ta a Legas, har ta girma, bayan uwarta ta ajiye ta kan layi. Ita kuma yarinyar garin neman kyakkyawar hanyar rayuwa ta faxa bariki

gidan karuwai a legas, tunda daman ba uwa ba uba. Nan fa ta shiga qungiyar ‘yan fashi amma ba da niyyar fashin ba, sai don ta ceci rayuwarta, qaddara ta sake xaukarta, ta faxo Abuja gidan wanda ta yi wa fashin don samun aiki, sannan bayan an bi ba’asi aka gano ba ‘yar fashi ba ce. A qarshe shi Al’amin xan Alhaji Dauda ya aure ta a qaddara, bayan ta taso a *Baby nice*a qaddara, aka canza mata suna ta koma Rahama shi ma a qaddara. Don haka, shi Bahaushe har a kullum yakan ba wa ‘ya mace fifiko wajen tabbiyartar da ita tun tana qarama har ta balaga ta kai munzili aure, ya aurar da ita, fatansa ke nan, to, amma ba haka muka gani ba a cikin fim xin Hausa irin wannan ba. Fim Xin *Su Ma Mata Ne* ya yi wa al’adar Hausawa karan tsaye, don haka, wannan fim ne da aka yi shi da Hausa, amma ba fim xin Hausa ba ne.

4.8.4 Jigon Fim Xin *Gwaska*

Jigon fim xin shi ne kasada ko “tarar aradu da ka” da kuma tausayin marasa galihu da shi gwaskan yake yi a cikin fim xin. Inda yakan qwatarwa talakawa haqqinsu daga hannun gwamnati ko kuma ‘yan mulkin kama karya ko kuma Basawan azzalumai da suke gallazawa al’umma.

Jigon da aka gina wannan fim xin ba a gina shi a bisa tsarin rayuwar Hausawa ba, kamar yadda aka yi bayani baya, don haka wannan fim ba za a ce fim xin Hausa ba ne, sai dai a ce fim ne aka yi da Hausa.

4.8.5 Jigon Fim Xin *Doya da Manja*

Fim ne da aka gina shi ne a kan gina qasa xaya al'umma xaya, duk da bambancin qabila da addini, a zo a zauna lafiya. Babban jigon dai shi ceton mutum a rayuwa, ko da baka san shi ba zai iya yi maka rana. A dalilin ceton fasila (Bayarabiya) da Balarabe (Bahaushe) Xansanda ya yi, daga hannun masu garkuwa da mutane, hakan ya haifar da kyakkyawar alaqa a tsakaninsu, har aka samu auratayya a tsakanin al'umomin biyu. Duk da cewar an yi ta xauki ba daxi a tsakanin dangi ango da na amarya, amma daga baya an samu masalaha aka yi auren.

Idan aka kalli jigogin duka waxannan fina-finan da Hausa, waxanda suka faxo qarqashin wannan kaso, za a ga an gina su a sanadiyar zamantakewa tsakanin wasu qabilu maqwabtan Hausawa ko a ce abokan zaman Hausawa na kusa ko kuma na nesa. Misali fim xin *Hotiho* yana xauke da tasirin al'adun Indiya, fim xin *Qara'i* yana xauke da tasirin al'adun turawa da Iyamurai, fim xin *gwaska* shi ma tasirin al'adun Indiya da Amurka. Fim xin *Su Ma Mata Ne* da *Doya da manja* akwai tasirin maqwabtaka da Yarbawa har da yanayin zamantakewar bikin aure.

Idan aka kalli jigogin ko manufofin waxannan fina-finai za a ga ba sa wakiltar wani vangare na fito da al'adu ko xabi'un Hausawa ko da wasa, sun mayar da hankali wajen yaxa ala'dun wasu al'ummomi na nesa da kuma na kusa da su. Misali fim xin *Gwaska* da *Hotiho* sun nuna tsarin rayuwa Indiya, fim xin *Su Ma Mata Ne* da *Doya Da Manja* ya nuna tsarin danagantakar rayuwa Hausawa da Yarbawa, sannan fim xin *Qara'i* ya nuna tsarin rayuwar Turawa da

tasirinsa ga al'aummar Hausawa. Don haka wannan bincike yana ganin ba za a kira waxannan fina-finai da na Hausa ba, sai dai a ce fina-finai ne da Hausa.

4.9 Harshen 'YanWasa A Cikin Fina-finai da Hausa

Aminu (2012) ya ce abubuwan lura game da harshen 'yan wasa ('yan fim) sun haxa da, harshensu ya dace da irin gagarumar taimako da suke takawa, haka kuma lallai ne a iya bambancewa tsakanin kalaman umarni da na buqata, da kuma sassaqa magana da ta barazana, sannan kuma da kalamin tambaya da na amsa, da dai sauransu. Wannan bincike yana ganin za iya qarawa da ce kalaman 'yanwasa a gina su akan abubuwa guda uku, dacewar kalaman xanwasa da matsayin da yahau, na biyu ya guji faxin batsa (saye) sa'annan a kula da kalmomin aro da xanwasa ya faxa.

4.9.1 Harshen 'Yan Wasa A Fim xin *Ibro Hotiho*

Fim ne mai xauke da kalaman da suka savawa al'adar Bahaushe da kuma na aro daga harshen Indiya da Ibo da Yarbanci,kodayake yawancin harshen 'yan wasa ya dace da gagarumar taimako da suka taka, sannan su ma 'yan wasan kalamansu ko a ce harshen yana xauke da karin harshe na nahiya sosai. Misali bari mu kalli ganawar da ta biyo bayan fitowar su Daushe

da Gatari daga silima a sakamakon kallon fim xin Indiya, sannan suna shirin zuwa kallon fim xin *Hotiho* da dare a sakamakon haka har waqar Indiya suka vuge da yi:

Hotihooo-hotihoooo
Hotilike ba ni bane risi ba na……..

Harshen ‘yan fim xin su biyu, ya nuna cewar lallai su ma’abota kallon fina-finan Indiya ne. Haka harshen da Shitu Mai silima ya yi amfani da shi wajen magana da su Ibro “kai ba ku da hankali” bai dace ba, a faxawa baqo haka ba, a tsarin xabi’ar Bahaushe.

Ibro yana yawan zagi da faxin baqar magana da cin mutunci da gugar zana a cikin fim xin. Misali: ya kwatanta halittar da Allah ya yi masa a fuskarsa misali kalamai irin su:

Ibro: Hancinka iwa qofar gari

Daushe: Hancinka sai ka ce lope, ko napkin zan wa hanci

Ibro: Wannan taya-ni-munin, wallahi tallahi akwai wanda in ya gani kawar da kansa zai yi, ai yanayin nonon jatumar ke nan.

Baffa wanda ya fito a xan daudu shi ne wanda ya yi wa Ibro jagora zuwa gidan Baban Cinedu da yake a birni. Ya yi amfani da karin magana a muhallan da suka dace. Misali lokacin da Ibro yace da shi, shi Indiya za shi sai xan daudu ya ce: Abin dariya yaro ya tsinci haqori. Wai yanzu kai har Indiya za ka? Sauran kare-karen magana da xan Daudu ya dinga yi a tsakanin sa da Ibro sun haxa da:

Xan Daudu: Abin dariya yaro ya tsinci haqori

Qarfin hali varawo da ihu

Xaukar dumar Magaji da nishi

Ibro: Shan koko xaukar rai

Haka ne ra'ayi cin xanwake da diga

Xan Daudu: Mai hankali, shi ke gane xingishin kwaxo

Ibro: Da rashin kira karan bebe ya vata

A nan an yi amfani da fasahar harshe cikin karin magana, wanda ya qara qawata harshen 'yan wasa, ba tare da an xaga jijiyar wuyar ba, idan aka kalli kare-karen maganar da ta afku tsakanin Ibro da Xandaudu za a ga an yi amfani da karin maganar wajen yin zance a tsakaninsu, wannan salo ne mai armashi kuma fasaha ce mai daraja a harshen 'yan fim. Daman ko a cikin al'ummar Hausawa an san 'yan Daudu da iya zuba karin magana da baqar magana da habaici da gugar zana da sauran ire-iren adon harshe ko salon sarrafa harshe.

Tattaunawa tsakanin Baban Cinedu da Ibro, shi ma harshen ya bauxe, domin an yi shigo da kalmomin aro da hagitsa balle, ga misali :

Baban Cinedu: The babbar riga, *the* bargo *we you are put for here, culture* na mu fa..

Ibro: Kai ka san wannan shi ke nan kuma, dama *you are no* nama

Baban Cinedu: Da ka shiga Indiya, ka ce na zo, na zo, ba wanda bai sani ba. *Nkejukwu onapo, You get money plenty*.

Ibro: Ai ni na *plenty money I dey*.

A fagen harshe an yi amfani da harshe na kalmomi hargitsa balle wato "*code mixing*" tsakanin Ibro da baban Cinedu. Wannan ba zai rasa nasaba da cewar baban Cinedu Inyamuri ne, kuma ba iya faxin Hausa sosai, shi kuma Ibro babu Ingilishi. Don haka dole ta sa aka dinga haxa harshen Hausa da Ingilishi a matsayin harshensu ta sadarwa har suka fahimci juna. Shi ma wannan fim xin ya saki layin na sahun fina-finan Hausa, domin wannan bincike yana ganin in har za a yi fim xin Hausa bai kamata a dinga haxa harshen Inglishi da Hausa ba, ko kuma a dinga magana da Iyamuranci a cikin fim xin da aka ce na Hausa ne, kamar yadda muka gani ta kasance tsakanin Baban Cinedu da Ibro.

4.9.2 Harshen 'YanWasa A Cikin Fim Xin *Qara'i*

Shi ma fim xin qara'i yana xauke da wasu kalamai da aka yi amfani a wuraren da ba su kamata a faxe su a muhallin ba, ko bai dace a faxawa wanda aka yi wa magana da harshe irin wannan ba, ko kuma faxin harshen da bai dace a ce mutum mai daraja ko qima a cikin al'umma ya faxa ba. Misali an nuna Sani sauti yana cikin tafiya sun yi karo da Barau ya bangaje shi. Bangazar da Barau ya yi wa Sani sauti, a maimakon ya ja bakinsa ya yi shiru ko kuma ya tausayawa dattijon da ya bangaje shi, da yake Sani yaro ne sai ya nuna halin rashin tarbiyya, sai ya fara faxin kalamai kamar haka:

Sani sauti: *Shit*! *What fucking man like this*? Kai me haka? Wane irin sakaran mutum ne haka.

Barau: Kai kana da hankali kuwa?

Sani sauti: Ya kai ma kana da hankali? Haba, ya mutum ya xau wanka kwalabo Malam, za ka zo, a buge don Allah, *old man sheet*. Ka ba za ka je ba ne? old man sheet. Ka ba za je ba ne? kawai malam ya vata min wanka. Au kallo na ma kake, lallai ka sha wahala……

A nan bai kamata Sani ya buxe baki ya faxawa dattijo xan sama da shekara hamsin kalamai irin waxannan na rashin xa'a ba, waxanda babu tarbiyyar harshe a cikinsu, ba ya cikin tsarin rayuwar Hausawa qarami ya yavawa babba magana haka, don haka fina-finai masu xauke da rashin kunya irin wannan ba za a kira su da fina-finan Hausa ba, sai dai a iya cewa fina-fina ne da aka yi su Hausa.

4.9.3Harshe 'YanWasa A Fim Xin *Gwaska*

Shi ma fim xin ya bijire ma harshen Hausa da aka ce an gina fim xin a kan sa, a wurare da dama, ga kaxan daga ciki a matsayin misali:

Minister: *In that case we have to postpone this meeting.*

Gwamna*:* *Why? Just because I lost one out of my four wives. Even if its you died, this meeting will continue.*

An ce fim xin nan an yi shi don Hausa da Hausawa ne. amma kuma, sai aka yi ta tsarma harshen Turanci a ciki, a muhimman wurare da bai kamata a ce an yi magana da Ingilishi ba, domin hakan, zai iya kawowa xan kallo cikas ya rasa fahimtar inda wasan ya sa gaba musamman ma in ba ya jin harshen Ingilishi don babu salon fassara a fim xin. Sanna ga kalaman batsa da aka dinga sakawa misali:

Wani harshen da aka lura cewa samsam ya savawa ladabin magana ga al'adar Bahaushe, shi ne lokacin da Gwaska ya haxu da budurwarsa suna taxi a cikin mota, sai take yi masa qorafi a kan ya daxe bai je wurinta ba, sannan ma bai nemanta ba, wato an dade ba a haxu ba, ga yadda hirar tasu ta kasance:

Budurwar Gwaska: Ka san ina sonka?

Gwaska: Ki kwantar da hankalinki

Budurwar Gwaska: Ka sa min sonka a cikin zuciya, amma lokuta-lokuta ba ka zuwa ba-ruwa.

A nan, a al'adar Bahaushe ina aka tava ganin budurwa tana faxawa saurayinta magana, gatsai haka babu sakayawa, har da cewa ya dasa mata son shi a cikin zuciyarta, sannan ba ya zuwa ba-ruwa. A nan magana ce mai harshen damo. Wasu za su fassara barruwa da saduwa ta kwanciya, don haka sai wannan bincike yake ganin da an nemi wata kalmar an yi amfani da ita maimakon ba-ruwa domin a sakaya ta, wato ana nufin tarayyar kwanciya tsakanin mace da namiji. Domin Bahaushe mutum ne mai kawaici da sakaya maganar alkunya. A nan za mu iya cewa wataqila tasirin zamananci yake neman kakkave kyawawan al'adun ladduban magana da aka san 'ya'yan Hausawa da shi.

Haka zalika, idan muka koma gidan Gwaska da yake harkar hodar Ibilis a fim xin, za a ga yadda shi ma ya yi amfani da wasu kalaman batsa da na nuna rashin iya kaxaita Allah a cikin harshen nasa. Wannan ya faru ne, bayan taqqadamar da aka yi tsakaninsa da yarinyar da ya yi garkuwa da ita. A dubi waxanan zantuka:

Bos: Kin yi min a rayuwa, zan xaga mutuwarki zuwa wani lokaci

Budurwa: To sai yaushe?

Bos: Sai na yi miki ciki……

A nan, ta yaya mutum musulmi zai dinga faxin zai xaga mutuwar wani sai zuwa wani lokaci, alhalin shi ba Allah ba ne. wato, a nan harshen da xan wasan ya yi amfani da shi bai dace a tunani irin na Bahaushe ba kuma musulmi.

Kodayake ba abin mamaki ba ne, domin shi wanda ya taka wannan gagarumar taimako xan Jos ne, wataqila ya yi amfani da irin tasa Hausar ne ya faxi abinda yake ganin dai-dai ne a wurinsa, alhalin kuma a bisa al'adar ladabin magana da Musulunci ba daidai ba ne. sannan faxin kalmar "sai ya yi mata ciki" sannan zai sake ta ba dai-dai ba ne a al'adar saye a Bahaushiyar al'ada, sai dai a ce juna biyu da sauran kalmomin da za su nuna ladabin magana a al'adar Hausawa. Sannan akwai maganganu irin su *I will kill you* zan kashe ka, kai tsaye. Wannan al'adar Turawa ce, su ne suka fi faxin irin waxannan maganganu a fina-finansu. Don haka saboda waxannan dalilai ba za mu sa wannan fim a cikin sahun fina-finan Hausa ba, amma dai za a iya cewa fim ne wanda aka yi shi da Hausa.

4.9.4Harshen 'YanWasa A Fim Xin *Su Ma Mata Ne*

Shi ma wannan fim xin cike yake da hargitsa-balle na harsunan Turanci da Yarbanci, wanda hakan ba zai sa ya amsa sunansa da fim xin Hausa ba, sai dai dai a ce fim ne aka yi shi da Hausa. Yana da matuqar yawa sai dai shi xin ma kamar xan uwan xayan ne, domin ya take al'adu da xabi'un Bahaushe wajen fitar da wasu kalaman 'yan wasan ba tare da an yi dabarar fassararsu ba. A cikin wani fim aka yi hargitsi tsakanin Yarbawa da Hausawa na jihar Legas mai suna *Suma Mata ne* wadda sanadiyar bautar "Oro" ne ma'ana tsafin da Yarbawa kan yi a fitar dare i zuwa xakin wani baqin shuri shekara-shekara ya yi sanadiyar haifar da rigimar, domin a bakin shurin ne aka kashe matar Alhasan Kwalle, ga irin harshen Yarbanci da aka yi amfani da shi a cikin fim xin lokacin tsafin bautar "*Oro"* binciken ya samu taimakon Dr

Ayilara wanda shi ya fassara mana kalaman nasu zuwa harshen turanci, shi kuma mai bincike ya fassara zuwa Hausa, Ga kalaman nasu:-

Yarbanci	**Hausa**
Oro Baba ooo	Kirarin kiranyen bautar Oro
Edun omo odede	Surkulle
Eranwa kojade nibi tawayi	Dole abin yankanmu ya fito yanzu
Onidandani tai dan	A yau xin nan ba sai gobe ba
Oro muo loni	Oro ya kama ki yau
Awo soro seo, awo soro seo	Asiri na da wuya, ba kowa kan iya shi ba
Ogberi oma pe awo soro se o	Oro ba qashin yarwa ba ne

A cikin wannan fim an nuna inda aka yi amfani da aron harshe Yarbanci aka yi surkulle, wato*incantation.*Har wa yau a cikin fim xin dai, a wani shago kuma an nuna, inda wani xan sandan ciki ya zo yake wa mai shagon Yarbanci zai sayi lemo. Ga abin da yace:-

Bawo ni nkan?	Ya al'amura
Miniral wani to tutu funmi	Akwai lemo mai sanyi, ba ni

A wani wuri kuma a cikin fim xin akwai inda Xansandan yake ma DPO waya cewar *Baby nice* da suke nema ga ta nan a shagon da yake cewa:-

Helo oga, omo ibinrin yen ni gan	Ranka ya daxe, Yarinyar da muke nema ga ta.

An yi ta cin karo da kalaman aro daban-daban a cikin fim xin, wanda yake ba a fassara su zuwa harshen Hausa. Hakan ya sava qa'idar nazari, ya kamata a yi amfani da salon fassara baqin kalmomi ne, ta yadda saqon da ake so a isar zai dire yadda ya kamata. Ire-iren waxnnanfina-finai wannan bincike ya yanka musu suna da fina-finai da Hausa.

4.9.5 Harshen 'Yan Wasa A Fim *Xin Doya da Manja*

Saboda zaman tankiya da aka yi ta yi tsakanin surukai Yarbawa da Hausawa a cikin fim xin *Doya da Manja* hakan ta haifar da bayyanar are-aren harsuna daga Turanci da kuma Yarbanci zuwa cikin fim xin. Misali a lokacin da aka je gaisuwar iyayen Fasila, aka ce da iyayen ango su yi Idobale kafin a bas u izinin aurenta, ga abin da aka yin a kalaman 'yan fim:

Suruka Uwar Fasila: A ni idobale

Uban Ango: Nawa nawa ake sayar da Idobale?

Fasila: Mun bi yi lere kolo se fun yi, Ina tambayar ku me ya yi muku da ba zan aure shi ba?

Uban Fasila: Fi okon re balele ni suru, ki kwantar da hankali ki qara haquri

Uwar yarinya: lai se igi lo joko kale, alhalin mu ba itatatuwa aka jibge a nan ba?

A nan ana taqqadama tsakanin uban Fasila da uwarta a kan batun shi uba yana goyon bayan a bar wa Balarabe ‘yarsa ya aura ko da ba a yi duka tsarabe-tsaraben aure da al’adar ta tanadar ba. Ita kuwa uwar yarinyar ta qeqasa qasa ta ce atafau ba ta yarda ba, duk da suna Hausawa, tun da har sun ga ‘yata suna sonta da aure, to fa dole sai sun yi duka tsare-tsaren da al’adarsu ta shimfixa.

A lokacin biki, wanda kuma wani Bayarabe ya jagoranta bikin (master of ceremony) yana mai cewa: *Gege be ishe wa lo do ebi awon iya iyawo, Ati ibe awonoko ko wonwa fi*

Ise ra ijo ni sin. (Kamar yadda na gayyato iyayen amarya suka taka rawa, a yanzu zan gayyaci iyayen Ango su fito kan dandamali su yi rawa yanzu)

Wato kamar yadda yake a bisa tsari, ina kiran dangin amarya da kuma dangin miji da su fito kan dandamali su taka rawa. A nan an fito qarara an nuna yadda al’adar Yarbawa take, ta yin rawa a wurin biki ko a gaban waye kuma, komai shekaru, mutum sai dai abu mafi muhimmanci a nan, yadda aka yi shigo da harshen da ba na Hausa ba ne a fim xin. Sannan kuma saqon da harshen yake xauke da shi harshen ya tsiru ne a bisa al’adar Yarbawa a cikin fim xin.

Idan aka kalli duka waxanan fina-fina guda biyar, za a ga harshen ‘yan wasan ba da Hausa suke magana ba, wasu ‘yanwasan suna Yarbanci a cikin fim xin da aka ce na Hausa ne, wasu na Turanci kai tsaye, wasu ‘yanwasan ma idan suna magana sai ka xauka Gwaranci suke yi wannan ya sa wannan bincike yake ganin fina-finan nan ba za su hau matsayin fina-finan Hausa ba, sai dai a iya kiran su da fina-finai da Hausa.

4.10 Tufafin ‘Yan Fim A Cikin Fina-finai Da Hausa

Tufafin ‘yan wasa (‘yan fim) wani muhimmin abu ne a fannin nazarin fina-finan Hausa. Kamar yadda Aminu (2002) ya ce tufafi wani muhimmin vangare ne na nazarin wasan kwaikwayo da kuma aiwatar da shi. A nan murubucin yana nufin ba za a iya aiwatar da kowane irin wasa ba, dole sai an sanya sutura wadda za ta dace da gagarumar taimako da xan uwansa zai taka.

Wannan bincike ya gano cewar za a iya tantance fim da Hausa da kuma fim cikin Hausa ta nazarin suturun ‘yan fim da sukan sa a cikin fim, ma’ana shin suturar da aka sa a fina-finan Hausa suna nuna ko fito da yanayi suturun Bahaushe kamar yadda aka san su a al’adance? Ko kuma sun sava wa ala’ada? Ya kamata a sani duk gagarumar taimako da xan wasa zai taka a fim ana la’akari ko fata zai sa suturar da za ta fito da shi, wanda ko ba faxa ana kallonsa an san wane ne ya fito.

4.10.1Tufafi ‘Yan Wasa A Fim Xin *Qara’i.*

Fim xin an yi amfani da tufafin Turawa sosai, musamman ga dattawa ‘yan sama da shekara hamsin sun koma suna sa suturun Turawa kamar *shirt*, da *polo* shat da sa wando *jins wizi* da *kolabo* da *ifizi*, an sanya wani qwalelen baqin gilashi da takalmi kanbas ana zanzarewa ga hula hana salla an kafata a ka. Misali bari mu je gidan Lado mu ji abin da matarsa take faxawa mijinta da ta gan shi ya sanya qananan kaya jins da riga shat an kafa hula da baqin gilashi ga shi kuma suna da ‘ya’ya manya wanda ita matar ba ta son yaran su ga mahaifinsu da irin wannan shigar da ya yi domin shi ne babban damuwarta. Abin da ya sa matarsa ta damu shi ne, shigar da Lado ya yi ya savawa al’adun Hausawa, a ce dattijo kamar Lado ya koma saurayi, sannan har tana gudun ba ta son ‘ya’yansu su ga mahaifinsu da wannan shiga, gudun kar su kwaikwaya domin mummunan xabi’a ce a al’ada irin ta Bahaushe.

Matar Lado: Malam magariba ta yi ka zo ka yi alwala. Ai kuwa waigowar da za ta yi sai ga malam a tsuke kawai, ya yi fuska, za tafi shan iska a bariki. Sai ta ce:

Innalilllahi wa’inna ilaihi raji’un

Lado: Ba ki gane ni ba ne? Lado ne fa mijinki.

Matar lado: Waye? Meya same ka?

Lodo: Shaqatawa!!!

Matar lado: Me ya haxa Bahaushe da irin wannan shiga?

Ta durkusa: Kana yi wa darajar Annabi kar ka zubar min da mutunci, qwave wannan kayan, kar ka zubar min da mutuncina. Yanzu Malam haka, za ka fita ba kunya ba tsoron Allah?

Shi ma a can gidan Barau an samu haka tsakaninsa da matarsa a bisa suturun daya sa, a matsayinsa na dattijo a gari wanda wani lokaci Sarki yakan aika a kira shi domin neman shawararsa akan wasu al'amuran mulkin garin. Ga yadda ta kaya tsakaninsu:

Barau: *Baby Baby*(yana kiran matarsa)

Matar Barau Malam me zan gani haka?

Sai ka ce dattijon biri?

Barau: Wannan shigar, shi ake ce da shi *London must come*, kuma da kike cewa na sanya kayan dattijon biri, wannnan ne dattijon biri? A haxa kayan xakinki gaba xaya ba su sayen wannan kayan.

Matarsa: Wallahi qarya kake!! Duk wanda ya ba ka wannan shawara, ya baka shawarar banza. Malam hauka ka fara, da ganinka da tsunfanka, ka kai wajen shekara tamanin (80), Malan na shiga uku!

Tun farko matansu sun yi tir da irin suturar da dattawan ma suka sanya, cewar don Allah kar su fita gari a gan su a haka gudun kar a ce girma ya faxi, amma duk da gargaxi da damuwar da matan nasu suka nuna, a banza, tun da an yi niyyar ana so a je a shakata ne, dole sai an yi shiga irin ta Turawa kenan, domin a saje. Har ila yau, xabi'unsu ya bambanta da xabi'ar Hausawa dangane da gagarumar taimako da suka taka a fim xin. A maimakon yadda suka fara sanya tufafin doguwar riga da wando da hula da kuma riga kufta ko kaftani da babbar riga da 'yar ciki da wando da hula qube ko zanna bukar ko damanga ko dara wato sutura ta al'ada kamar yadda aka san Bahaushe da su, sai suka bauxe, suka saki reshe kama ganye.

4.10.2 Tufafin ‘YanWasa A Fim Xin *Hotiho*

An yi koqari wajen amfani da tufafin da suka dace da kusan kowane xan fim dangane da gagarumar taimako da kowannensu ya taka da kuma muhallinsu. Misali lokacin da Ibro ya qudiri anniyar tafiya Indiya, sai aka naxa masa kewayen rawani irin na Indiyawa a al’adarsu ta sanya sutura, a gaskiya kai ka xauka Baindiye ne, in ban da shi baqar fata ne, kuma dama sananne ne ba za ka iya gane shi ba.

A gaskiya rigar da Shitu mai silima ya sa ba ta dace da gagarumar taimako da ya hau ba, ya sa wata riga shimi mara hannu duka rabin jikinsa a waje duka ana ganin qwanjinsa a waje. Wannan ya sava da qa’ida a matsayin fim xin Hausa, sannan ya zo ya kafa hula hana sallah a gaban goshi. Kodayake dama shi ya sa wannan bincike ya kira ire-iren waxannan fina-finai da fim da Hausa. Shi ma Baban Cinedu da ya fito a Inyamuri ya sanya kaya irin na Inyamurai bakin gwargwado ya sanya hular sanyi ya rataya murjani a wuya, sannan ya riqe wani kwagiri a hannu, ga izgar doki ya ajiye gefe guda.

4.10.3 Tufafi ‘YanWasa A Fim Xin *Gwaska*

An yi amfani da suturun da suka dace da fim xin a matsayin fim xin Turawa amma a cikin harshen Hausa a wuraren da suka dace tun daga ofishin ‘yan sanda da kasuwa da shigar gwamna da shugaban qasa da ministoci da ‘yan jarida da malamai da samarin fim xin. Haka

kuma suturun da gwaska yake sawa shi da yaransa duka na turawa ne da na *American Ninja* wato baqar riga ce mai fuka-fukai ana sanya *mask (dodon fuska)* a fuska domin kada a gan shi balle a gane shi. Fim ne da aka yi amfani da duk wani kaya da aka san Bature yana sa wa, kamar su *shirt* da *Trouser* da *facingcap* da *suit.*

4.10.4 Tufafi 'YanWasa AFim Xin *Su Ma Mata Ne*

Shi ma wannan fim xin an yi shi a garuruwa biyu, wato Jihar Legas da qasar Hausa don haka a yayin da aka kai xan kallo qasar Yarbawa akan nuna suturar Yarbawa a fim din sannan in aka dawo qasar Hausa ta yanayin suturar 'yan wasan takan sauya. Misali matsafan Yarbawan da suka fille kan matar Alhasan Kwalle a Legas Yarbawa ne, kuma sun sanya suturar da ta dace da gagarumar taimako da suka taka, wato farar 'yar shara da gajeren wando fari da hula havar kada. Sannan shima Al'amin tun da ya dawo daga qasar turai ya qi ajiye Tufafin turawa, ya kamata ya xauki suturunmu na gida ya maida su tufafinsa, don haka wannan bincike yana ganin tun da Al'amin ya dawo gida Nijeriya, bai kamata a matsayinsa xan babban mutum a cikin al'umma, Bahaushe Musulmi ya ci gaba da sanya qananan kaya ba, ya kamata ya dawo gida ya ci gaba da sanya suturunmu na gado. Haka nan suturun da 'yanmatan gidan Alhaji Dauda suka sa, sun savawa al'adar Hausawa, xamammu ne, kuma suna nuna tsaraicinsu. Don haka haka ba za mu iya kiran wannan fim xin da fim xin Hausa ba, sai dai a ce fim ne aka yi shi da Hausa.

4.10.5. Tufafi 'Yan Wasa A Fim Xin *Doya Da Manja*

An yi amfani da tufafin Yarbawa a fim xin, wannan ko ba zai rasa nasaba da cewar fim ne wanda ya haxa Hausawa da Yarbawa ba. Wato a tattaunawar da aka yayin gudunar da bincike, Malam Umar Mai Jalingo ya tabbatar mana da cewa, ai Yarbawan gaske aka nemo aka zuba a fim xin dukkansu mazansu har matansu, wanda a wasu lokutan, sune sukan faxa masa yadda ya kamata a sanya sutura iri kaza ko da aiwatarwa iri kaza a muhalli kaza. An sanya atamfa da leshina ga dukkan maza da mata da suka fito daga dangin uwar Amarya. Sannan an kai wa dangin ango, su ma domin sanya kalar atamfa iri guda da na surukansu, su ma maza da mata kamar yadda muka gani a fim xin. Mata sun yi xaurin gwagwaro a ka, sannan mazan wasu kawunansu ba hula, wasu kuma sun sanya hular Yarbawa, wato irin doguwar hula wadda akan tanqwaso ta gefe guda bayan an sa ta. Matan fim xin musamman dangin mata sun sanya *anko* har kala uku, baqar atamfa mai roxi-roxin fari da jar atamfa da kuma leshi mai zubin ruwan xorawa. Wato anko xin ma kashi uku aka raba, ankon iyayen mata daban, ankon dangin miji daban, sannan ankon amarya da qawayenta shi ma daban. A nan, wannan bincike ya nuna yadda tsarin suturun Yarbawa ya yi tasiri a cikin fim xin a bisa dacewar yadda Yarbawan suka taka rawa a cikin fim xin*Doya da Manja*. Wato tufafin da duka ‘yan wasan suka sanya ya dace da al’adarsu ta Yarbawa, haka nan Hausawan su ma kowannensu ya sanya tufafi irin ta al’adarsa.

Tufafin da aka yi amafani da fim xin Gwaska ba na Hausawa ba ne, tufafin Turawa ne, haka nan ma taurarin da suka fito a fim xin *Qara’i* sun kwaikawayi sa tufafin Turawa ne, idan muka juya kan fin xin *Qara’i* za a ga shi ma babban tauraron wasan Ibro bai yi shiga irin ta Hausawa ba, tufafin Indiyawa ya dinga sawa. Idan aka kalli fim xin *Su Ma Mata Ne*, an sanya

suturun Yarbawa da Turawa a wurare da dama, kamar wurin bautar *Oro* da kuma tsarin suturun da matan gidan Alhaji Dauda suka sa ya nuna tsaraicinsu. Haka kuma fim xin *Doya da Manja* shi ma za a ga hatta dangin ango da ake ganin Hausawa ne, su ma an mayar da su Yarbawa a tufatarwa, domin sai da aka tabbatar ranar bikin Fasila da Balarabe kowa ya sa ankon atamfa yara da manya, maza da mata ga xaurin gaggwaro, wasu mazan ma leshi suka sa. Wannan bincike yana ganin waxannan fina-finai ba za a kira su da fina-finan Hausa ba, sai dai za iya cewa fina-fina ne da aka yi su da Hausa, domin yanayin suturun da aka yi amfani da su a fina-finan ba na Hausa ba ne.

4.11 Halayyar ‘Yan Wasa A Fina-finai Da Hausa

Kamar yadda Aminu (2012) da Sulaiman (2016) suka nuna cewa a tsarin halayyar ‘yan fim ya kamata a ga abubuwa na cancantarsa a kan matsayin da ya hau a fim xin. Wato dai yadda duk abin ya faxa, to, ya aikata ta yadda zai dace da gagarumar taimako tasa da matsayin da aka xora shi, ta yadda zai isar da saqon a fim. Sannan abu na gaba shi ne hawa kan matsayin da ya dace, misali, inda ake so a ga babban mutum ya fito ko mai kuxi dattijo bai kamata a ga yaro ya hau matsayin ba. Kuma ya wajaba xan fim ya mallaki duk wasu halaye ko xabi’u na matsayin da ya hau, misali duk wanda zai xauki matsayin liman dole ya zamanto natsattse ne yana da sura da kamala irin ta limamai.

Kamar yadda aka yi nazarin siffofin fim a bisa zubin fim da jigon fim da harshen fim da tufafin fim to haka nan anan za a yi nazarin halayyar ‘yan fim daga wasu fina-finai da Hausa,

su ne fim xin *Hotiho* da *Qara'i* da *Su Sa Mata* ne da *Gwaska* da *Doya da Manja*, don haka an tace su, an ga irin gagarumar taimako da 'yan wasan suka taka na dacewa da rashinsa a bisa yanayi da sigar matsayin da suka hau a aikace a cikin fim xin.

4.11.1.Halayyar 'Yan Wasa A Fim *Xin Hotiho*

A cikin fim xin Hotiho, Hotiho yana yawan wuce gona da iri da zaqewa a wasu fitowa da ya yi misali a lokacin da ya je gidan Daushe ziyara a kan neman shawararyadda zai tafi indiya ya tarar Daushe yana yi ma matarsa faxa a kan ba ta dafa masa abincin da yake son ci ba. Ganin haka sai Daushe yan kama faxa yana cewa "**matarsa ba 'yar arziki ba ce ba!!** Kai Ibro da ka zo, ka ji ana wannan rigimar ai sulhu ya kamata ka yi a tsakanin mata da miji, haka aka san Bahaushe da xabi'ar yin gyara. Abin mamaki abin da ya fito daga bakinsa shi ne " **ai iri waxannan mata 'yan matsiyata ne, tsinannu ne**" Wannan halayya ba ta dace ba, an yi azarvavi da yawa. Daushe ne ya ba da kafa har Ibro ya zagi matar tasa, Daushe kuma da ya ga zagin ya fara yawa sai xaga hannu yace "**Ibro kar ka sake zagin min mata**" sai kuma Ibro ya sake cin kwalar rigar Daushe, kai ka ji qarfin hali varawo da sallama, mutum da matarsa ka biyo har gidansa kana nuna masa bai isa da gidansa ba, har sai da aka yi doke-doke. Wannan gagarumar taimako gaban hantsi ne Ibro ya je ya taka, a muhallin da bai dace ba.

4.11.2 Halayyar 'Yan Wasa A Fim Xin *Qara'i*

A cikin fim din *Qara'i,* duk da yake an ce Malam Halliru da Malam Mati da Malam Lado suna *Qara'i n*e, amma duk da haka akan bar halas don kunya. A lokacin da suka zo wucewa ta gaban gidan limamin gari suna taku xai-xai, an sa wando*wizi* ko kuma*assdown*(sa wando zuwa rabin xuwawu jins) sannan ga taba sigari an riqe a hannu, da suka yi kicivis da liman ya ce:

Liman: Malam Halliru, Barau, Lado me zan gani?

A nan sai su yi maza su nuna halin alkunya wanda aka san Bahaushe da shi idan ya ga na gaba da shi, kamar mahaifinsa ko sarkin garinsa ko limaminsa. Amma wai cewa suke "**ga malam ya fito bari mu je a zubar masa da sitamina, muna xan basarwa ne kaxan**" suka gama raye-rayensu a gaban Malam. Malam ya ce "**amma kun bani mamaki**, **kun yi qarkon kifi daga ruwa kun faxa wuta**", malam ya bi su da kallo yace**"amma fa shaixan mugu ne, mutane da 'ya'yansu da jikokinsu amma suke irin wannan ta'asar haka…**…."

4.11.3 Halayyar 'Yan Wasa A Fim Xin *Su Ma Mata Ne*

Fim na gaba shi ne "*Su Ma Mata Ne*" a fim xin matasan Hausawan nan sun wuce makaxi da rawa. Domin lokacin da suka kawo qorafinsu ga sarkin Hausawan Legas a kan matasan Yarbawa sun kashe musu mata, ya dace su saurari Sarkin ne tare da bin shawarar da ya ba su

ya ce "**ku saurara duka na ji qorafe-qorafenku, za mu xauki mataki na shari'a domin mu qwato wa kawunanmu haqqinmu……".**

Da Allah ya sa sun bi shawarar Sarki da wataqila rigimar ba ta kai inda ta kai ba, domin matasan sun xauki fansa a kan matasan Yarbawan, sun yi qone-qone da sare-sare da sauransu. Ai fada ta fi gaban wasa, kuma yadda suka dinga hargowa ana rantse-rantse da tsine-tsine bai dace ana haka a fada ba, ya kamata su nutsu tukunna Sarki ya gama jawabi, kafin su watse, ba su bari ya gama jawabi ba, suka kaxa kai suka yi gaba. A nan an taka gagarumar taimako da ta savawa al'ada a tsarin tarbiyyar Bahaushe tun daga gida.

4.11.4 Halayyar 'Yan Wasa A Fim Xin *Gwaska*

Wani fim da shi ma ya bi sahun waxancan fina-finai a zubin halayyar'yan fim shi ne na *Gwaska*. Dama fim ne wanda aka aro wasu al'adu da xabi'un Turawa aka gina shi da su, kodayake akwai 'yan qare-qaren da ba a rasa ba. Misali a lokacin da Gwaska ya addabi mutanen qasar, jami'an 'yan sanda sun sha bazama neman sa su kama shi, amma kama shi ya faskara. Har ta kai babban sufetana 'yan sandar qasar ya so ya wuce makaxi da rawa a lokacin da ya fusata, ganin har yau ma'aikatan nasa sun kasa kamo Gwaska. Wato yana cikin faxa, "**kun kasa aikinku na police**" sai wani xan sanda ya ce "**Insha Allahu za a kama shi**" sai *I.G* ya ce "**don't say Insha Allah, ba insha Allah nake tambaya ba, ku kawo min Gwaska".** Wannan bincike yana ganin a tsari irin na halayyar xan wasa bai kamata a ce shugaban 'yan sanda dake kan wannan kujerar ya dinga barin shauqin mulki yana kwasarsa

yana faxin kalamun da ya ga dama. Har yana faxin kar a ce **Insha Allahu kawai a je a kawo masa Gwaska**. To abin da wannan bincike ya gano a nan shi ne, ya kamata a sanya wanda ya xan manyanta a kujerar *I.G* ne ba matashi ba. Domin da a ce dattijo ne a kan wannan kujerar tunaninsa ba zai zama xaya da na wancan matashi ba, sannan kuma da wataqila saboda gogewarsa a aiki, da an sami mafita tuni. Ba kamar yadda shi wanda yake kan kujerar yake ta shirme da gagarumar taimako kai ba a kan kujerar tasa ta sufeta na ‘yan sandan qasa guda.

Ba ya cikin halayyar Bahaushe a ce an kashe mutum kai tsaye da bindiga *AK47* ba tare da wani dalili ba.Babban tauraron fim xin Gwaska ya kashe wani babban malami a Kaduna wai don yace shi Gwaska xan ta’adda ne, ina aka tava haka? Sannan a dubi yadda ake sha giyar *wine* a gidan Gwaska ana tara ‘yanmata.

4.11.5 Halayyar ‘Yan Wasa A Fim Xin *Doya Da Manja*

Kowanne xan fim a cikin fim xin *Doya da Manja* ya taka gagarumar taimakosa bakin gwargwado. Sai dai a wasu lokuta Bosho wanda ya fito a matsayin uban Balarabe yana wuce makaxi da rawa a yayin aiwatarwa. Sannan duk da cewar an yi masa kwalliya da za ta nuna cewar shi tsoho ne mai shekaru ganin xan nasa ya girma kamar sa’anni suke Balarabe, da ya dace ne a nemo wani wanda ya girmi Bosho ya xauki wannan matsayin uban, domin da xan da uban kusan shekarunsu guda a zahiri. Sannan an xauki Hajiya wacce aka fi sani da Hajara ta hau matsayin matar Kawu wato Bosho, don haka wannan binciken yana ganin a al’adar Hausawa mace ba ta cika girmarmijinta a shekaru na aure ba, sai dai shi mijin yakan girmi

mace da shekaru masu xan dama. Don haka halayyar Bosho akwai yarinta a ciki, matarsa ta fi shi dattaku.

Rawar da Baban Mulika ya taka a matsayin Liman Wasiu (Bayarabe) ya dace, Baban Mulika shi ne wanda ya jagoranci salla a unguwarsu. To duk bayan salla, sai ya ja addu'ar nan ta: *Rabbana la tazig qulubana, ba'ada iz hadaitana wa hablana min ladunka rahamatan innaka antal wahhab*. Baban mulka ya karanto addu'ar cikin waqe kamar yadda aka san Yarbawa suna yi a cikin masallatansu,yin addu'a da siffar waqe-waqe.

Haka zalika halayyar da Balarabe ya nuna ba ta yi daidai da al'ada ko xabi'ar Hausawa ba, ta fito qarara inda yake nuna cewar babu ruwansa da Hausawa shi soyyayar Bayarabiya ta rufe masa ido cewa, kai tsaye yake faxawa mahaifinsa haka a cikin gidansu, don an ce ba zai auri Bayarabiya ba, ga abin da ya ce :

Ni gabaxaya harkar Bahaushe ba na so

Ni sai Bayarabiya, ba ruwana da wata Bahaushiya.

A nan ya za a yi a ce domin saboda Balarabe ya yi soyayya da Bahaushiya sun sami matsala aurensu bai yiwu ba, sai ka qi naka? Hausawa sun ce naka-naka ne, sannan an ce hannunka ba ya ruvuwa ka yanke ka yar. A gaban iyayensa fa Balarabe yake irin wannan hali. Wannan ya savawa al'adar Bahaushe tunda, ai su Hausawa ne a fim xin.

Har ila yau Balarabe a matsayinsa na tauraron wasan, ya sake aikata wani hali wanda ya sava wa al'adar Bahaushe a yayin tattaunawarsu da mahaifinsa a kan shi lallai sai an aura masa

Fasila, shi kuma mahaifinsa ya ce Yarbawa ba su da tarbiyya don haka ba zai aureta ba, ga tattunawar kamar haka:

Baban Balarabe: Na sha faxa masa kar ya auri ‘yarsu saboda rashin tarbiyya, idan ka ce babu ruwanka da Bahaushiya, to, ke nan babu ruwanka da uwarka ga ta nan a zaune…..

Balarabe: Wa? Ba maganar qwaila ake…….

Baban Balarabe: Ko ba qwaila ba ce amma dai Bahaushiya ce.

A nan bai kamata Balarabe ya nuna qarara a gaban iyayensa ga abin da yake ransa ba, babu girmamawa qarara, balle kawaici. Qwaila ita ce Budurwa da ta xan fara taso wa amma ba ta gama balaga ba. Siffofin balagar mace sun fara nuna wa a jikinta amma kuma ba ta gama cika ba. An savawa al’adar Bahaushe a gaban mahaifasa da mahaifiyarsa ana faxin kalmar “qwaila”. Babu xa’a a kalaman don su ba shawara ko zavi irin matar da kamata Balarabe ya aure.

Rawa da waqa da aka dinga yi a cikin wannan fim ya savawa ala’dar Hausawa, a kalli lokacin bikin Fasila, an haxu maza da mata, ana cakuxa da juna ana rawa ana liqi ana juya kwankawaso, wasu kuma suna kixa, an kafa tanti da kujeru ana kai kawo. Shin Bahaushe yana irin wannan hali a biki aure? A’a ai mata suna cikin gida suna sha’aninsu ne, in ma za yi kixan qwarya na mata ne, su ma xin can ya-su-ya-su ne mata. maza kuma ana can wurin xaurin auren, su ma in za a yi wani sha’ani can tsakaninsu ne.

Halayyar xan wasa wani babban al'amari ne a fagen nazarin fina-finan Huasa, domin yana qunshe da abubuwa da dama, halayyar mutum takan nuna ko shi waye a cikin al'umma. Don haka, a fagen nazari irin wannan akan so daraktocin fim su dinga xaura taurari da suka cancanta a kan rawar da za ta dace da kowa. Wasu sukan wuce makaxi da rawa, wasu kuma sukan yi sanyi , yin hakan sai ya hana fito da matsayin da taurari suka hau ya yi armashi. Sannan abu na biyu akan kula da halayyar da al'adu jama'ar da ake fim xin don su, domin a guje aika halayyar da ta savawa tadojin al'ummar Hausawa a cikin fina-finan Hausa,kamar nuna tsaraici da rawa baxala maza da mata a cakuxe, kamar shan taba da giyar *wine* kamar yadda aka gani a fim xin *Gwaska* an taru da abokanai an sha taba ganye da giya , can gefe an sa kixan *disco* mata da maza ana cashewa. Haka ta kasance a cikin fim xin Doya da Manja, bai cikin xabi'ar Hausawa yau a ce an haxa surukai a filin Allah su zo suna rawa ana yi musu liqi. Za mu iya ganin haka a lokacin da ake bukin aure Fasila da Balarabe, inda aka kira dangin uwar amarya da dangin uwar ango aka haxa su a kan dandamali suka cashe ana yi musu liqi.

4.12Kammalawa

A wannan babin an fi ba da fifiko a kan nazarin fina-finai guda goma waxanda aka xauko a matsayin samfur, domin a tantance fina-finai da Hausa da kuma fina-finai cikin Hausa. An yi haka ne ta xora kowanne fim a bisa mizanin awo na nazarin fina-fina Hausa na Jigo fim da zubin fim da tufafin fim da harshen fim da kuma halayyar fim.

Wannan bincike ya gano za a iya tantance fina-finan Hausa da kuma fina-fini da Hausa, ta hanyoyin nazarin fina-finan. A nan an gano nazarin jigon da aka gina fim a kan sa wajibi ne, domin shi zai fito da manufar fim xin shin na Hausa ne ko kuma da Hausa aka yi shi. Wato jigon da ya gina fim xin yana bisa al'adu da xabi'un Hausa ne? Ko kuwa jigo ne wanda yake ba shi da dangantaka da yanayin rayuwar Hausawa? A nan idan jigon ya hau burtalin yanayin rayuwar Hausa, to, za a iya cewa Bahaushen fim ne, amma idan ya zama jigon ba shi da wata alaqa da yanayin tsarin rayuwar Hausawa tun daga matakin haihuwa da aure da mutuwa da kuma sauran matakan zama wanda xan Adam dole sai ya ci karo da su a tsarin rayuwa tasa, to, lallai ba za a iya sa wannan fim xin a cikin sahun fina-finan Hausa ba. Sai dai a ce fim ne aka yi shi da Hausa.

Wannan bincike ya gano cewar zubin fim yana daga cikin dabarun da za a iya amfani da su wajen ware fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa. Abubuwan dubawa a nan sun haxa da qullin labarin fim. Shin labarin fim yana da tushe da kuma asali? Ma'ana tsittsigen labarin daga ina aka xauko shi? Shin qirqirarren labari ne mai nuni da tsarin rayuwar Hausawa? Ko kuma an xauko wani adabin rayuwar Hausawa ne aka gina labarin akan sa, kamar tatsuniya ko labarun gargajiya, sannan aka tsara labarin fim a kan sa, sannan aka aiwatar ya zama fim? To, lallai ana fata fim xin zai fito da tsarin rayuwar Hausawa a cikinsa. Amma idan ya kasance labari ne wanda aka xauko ko aka juyo shi daga labarun fina-finan Indiya ko Larabawa ko Sinawa ko Turawa daga waje kenan, to gaskiya ba lallai ba tsarin labarin fim xin ya nuna ainihin tsarin rayuwar Hausawa. To, a nan ko da an shirya fim xin ya fito sai ya nuns tushen labarin ba na Hausa ba ne. Ire-iren waxannan fina-finai wannan bincike yake ganin za a iya kiran su da fina-finai da Hausa.

Tufafin ‘yan wasa yana daga cikin wani muhimman turke da wannan bincike ya yi amfani da shi wajen iya tace fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa. Haka kuma, duk fim xin da aka samu an yi amfani da sutura ta al’ada za a iya cewa wannan fim zai iya amsa sunansa da Bahaushen fim. Amma a duk lokacin da aka ga shigar da ‘yan wasa suke yi ba ta dace da suturar al’adar Bahaushe ba, to, a nan fim xin ba zai amsa sunansa da fim xin Hausa ba, sai dai fim ne da aka yi shi Hausa. Misali an ga ‘yan wasa suna ta yin shiga ta sa riga shat da wando turoza ko kuma su yi shigar Inyamurai ko shigar Yarbawa ko Larabawa a cikin fim. A nan wannan fim ya savawa dokar wannan bincike, wanda ba za a ce fim xin Hausa ba ne ba, sai dai a ce fimne da Hausa.


Halayyar ‘yan wasa ita ma abin nazari ce a fanin nazarin fim ko wasan kwaikwayo, wanda wannan bincike yake ganin ya gano wajen tantance fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa, misali dacewar da cancantar xan wasa a muhallin da ya dace da shi a bisa tsarin rayuwar Hausawa abin dubawa ne a cikin kowanne irin fim xin Hausa. Bai dace a xauki dattijo ko mai shekaru da yawa a ce ya hau muhallin saurayi ba, ko kuma a ce budurwa ta hau matsayin uwa, ko kuma xaukar matashi yaro a ce shi ne maigida har da mata huxu. Ya kamata a sanya dattijo ko wani mai xan shekaru a muhallin, ta yadda idan ya hau matsayin zai taka rawar da ta kamata. Abin nufi a nan, rawar da xan wasa zai taka, ta yi daidai da al’adu da xabi’un Hausawa kamar yadda aka sani a rayuwar Hausawa ta zihiri. Ba a san Bahaushe da munanan xabi’un yi garkuwa da mutane, da xaukar bindiga ana haxa gungu ba. Watau kamar *secret cult* ko zagin iyaye ko zama wuri xaya na surukai, wato babu kunya a cikin fim. To

fina-finan da suke nuna irin waxannan halayyar ba su cancanci a kira kira su da fina-finan Hausa ba, sai dai a ce fina-finai ne da aka yi su da Hausa.

Amma idan halayyar fim ya zo da tsarin xabi'ar kawaici da kara da kunya da sanin yakamata, ko kuma nuna wasu tsarin al'adu bori ko dambe ko kokawar gargajiya ko sarauta duka waxannan halayya waxanda an san na Hausawa ne, za iya sa fina-finan da suka zo da irin waxannan halayya da fina-finan Hausa.

Harshen 'yanwasa yana daga cikin abubuwan ko siffofin da wannan bincike ya yi amfani da shi domin ware fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa. Da harshe ake iya tantance al'ada mutum, don haka, wannan bincike yake ganin duk fim xin Hausa wanda aka gina shi bisa amfani da harshen Turanci ko Larabci ko Faransanci ko Indiyanci ko Yarbanci da Inyamuranci ko Nufanci ko Ggagyi a cikin sa wajen sadarwa a tsakanin 'yanwasa, to, wannan fim xin ba ya cikin sahun fina-finan Hausa. Amma dai za a iya cewa fim ne ake yi da Hausa. Amma duk fim xin da aka yi amfani da harshen Hausa, babu sirki na wani harshe daga waje har aka kammala shi za a iya cewa wannan fim xin na Hausa, domin da Hausa aka yi shi, ba a tsarma wasu baqin kalmomi waxanda ba na Hausa ba ne a cikin sa ba.

A qarshe, wannan bincike ya taqaita wannan aiki cikin wannan taswira kamar haka:



Hausa

Hausa

Yadda Ake Samar da su:

1. Asalinsu/qirqira
2. Wanki da xauraya
3. Fassara
4. Kwaskwarima
5. Baddalawa

Aiwatarwa ta

Yadda Ake Aiwatarwa

Aiwatarwa ta

Bayan Fage

Cikin Fage

1. Qirqirar labarin fim
2. Marubucin labarin fim
3. Tushen labarin fim
4. Furodusan fim
5. Darakfan fim

1. Jigon fim
2. Zubin fim
3. Harshen ‘yan fim/’yan wasa
4. Tufafin ‘yan fim/’yan wasa
5. Halayyar ‘yan wasa/ ‘yan fim

Siffofinsu/Sigoginsu

1. Neman kuxi
2. Babu kare al’adar Bahaushe
3. Soyayyar zamani/ Bukukuwan zamani/ Sharholle
4. Raye-raye da waqe-waqen zamani
5. Babu kunya, kara kawaici
6. Tasirin baqin al’adu

1. Fito da addinin Musulunci
2. Tsare al’adun Bahaushe
3. Jan hankalin al’umma da tadojinsu masu kyau (xabi’u)
4. Kixa/waqa da wasannin gargajiya
5. Ladubban magana
6. Kyautata zaman takewar Hausawa

BABI NA BIYAR

KAMMALAWA

6.0 Gabatarwa

A wannan babi ne wannan bincike mai suna “Fina-fina Hausa Na Shekarar 2000-2017: Nazarin Yanayinsu da Sigoginsu” ya kammala.An taqaita batutuwa da aka tattauna a cikin

aikin tun daga babi na farko zuwa babi na huxu. An kawo matakan tantance fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa. An ba da shawarwari ta yadda za a inganta harkar shirya fim na Hausa, musaman a kan al'amuran da suka jivanci shigo da kyawawan al'adun Hausawa a yayin shiryawa da samar da fina-finan Hausa ta yadda za a dinga cin gajiyar su a ilimance. A qarshe, an rattavo manazarta, an kawo rataye na wasu jerin sunayen fina-finan da aka yi amfani da su a cikin aikin, an kuma kawo rataye na tambayoyin bincike.

5.1 Naxewa

An kasa wannan kundi zuwa babi biyar ne. Babi na farko yana qunshe da gabatarwar aikin gaba xaya. An fitar da manyan ginshiqan tubalin ginin babi na farko, wato an gina babin ne ta hanyar kawo manufar bincike da dalilin bincike da hasashen bincike da farfajiyar bincike da muhimmacin bincike. Daga nan sai aka tsunduma cikin babi na biyu, shi ne bitar ayyukan da suka gabata masu alaqa na kusa da kuma na nesa da wannan aiki.

Babi na biyu kuwa ya tavo ra'ayin masana ne dangane da ma'anar al'adu da rabe-raben sa. Sannan an kawo fasalin matakan rayuwar al'ummar Hausawa, kamar na aure da haihuwa da bautar gargajiya da cimaka da tufafi a matsayin wasu matakan rayuwa. Har ila yau, a cikin babin an yi tsokaci a kan yadda masana suka ba da ma'anar fim da rabe-rabensa da kuma hanyoyin da ake bi wajen nazarin fim.

Babi na uku kuwa an kalle shi ne ta fuska biyu,hanyoyin tattaro bayanai ginshiqai da kuma sauran hanyoyi. An tsara tambayoyin bincike na baka da kuma tambayoyi a rubuce wxanda aka ba wa masana suka amsa, kuma aka yi tufka da warwararsu. Ababi na uku ne aka kai ziyarar wasu garuruwan qasar Hausa inda aka gana da masu ruwa da tsaki a harkar fina-finan Hausa, da ziyarar xakunan adana kayan tarihi da al'adu na garuruwan, sannan aka tattauna da masana ilimin wasan kwaikwayo na fim, aka kuma yi hira da masu shirya fina-finai da 'yan kallo. A xaya vangaren kuma an tattauna ne a bisa hanyoyin da aka bi wajen tace bayanai, an dai fara ne da kallon fina-finan Hausa, inda aka rarraba su bisa hanyoyin da aka bi wajen tace fina-fina da Hausa da kuma fina-finai cikin Hausa, a nan ne aka fito da masu taka rawa a fim a cikin fim 'yan bayan fage da 'yan cikin fage, domin in babu su babu fim, kuma rawar da suke takaa cikin fim tana tasiri dangane da al'adunsu ko kuma xabi'unsu na rayuwa a cikin fina-finai na Hausa ko kuma fina-finai da Hausa.

Babi na huxuya qunshi sakamakon da bincike ya samo a bakin Jama'a, a nan ne aka warware qunshiyar bincike inda aka yi tsokaci a kan dabarun tantance fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa. An raba babin gida biyu ne, an yi nazrin fina-finai da Hausa da kuma fina-finai cikin Hausa. An fara da nazarin fina-finai cikin Hausa, inda aka yi amfani da turakan nazarin fina-finai, wanda aka kira su da masu taka rawa a bayan fage, sun haxa da gano asalin labarin fim,sannan wane ne marubucin labarin? Waye furodusan fim xin, sannan uwa uba daraktan fim xin?Sa'annan a iya tantance fina-finan Hausa da kuma fina-finai da Hausa ta hanyar ta nazarin siffoffin fina-finan a kamar jigo da zubi da harshen 'yanwasa da halayyarsu da kuma tufafin 'yanwasan, sa'annanaka dangantasu da rayuwar Hausawa ta zahiri, wato shin ya dace ko bai da ce ba. Wannan ita ce dabarar tantance fina-finai a fagen nazari. Da

waxannan hanyoyi ne aka ci nasarar tantance fina-finai guda goma, guda biyar suna wakiltar fina-finai da Hausa, wato *Qara'i da Gwaska da Ibro Hotiho da Su Ma Mata Ne da kuma Doya da Manja,* sa'anan nan binciken ya gano fina-finai irin su *Qafar Ungulu da Juyin Sarauta Da Bori da Malam Zalimu da Na-Hauwa* suna cikin fina-finai da aka yi su cikin Hausa.

Babi na biyar kuwa nan ne aka naxe aikinkumaaka bayar da waqsu shawarwari, ga masu nazarin fina-finai da kuma masu shirya su. Haka kuma an fito da matsalolin da ake ganin suna ci ma harkar fim tuwo a qwarya tare da kawo hanyoyin da za a iya bi wajen inganta fim na Hausa. Hatta masu nazari ba a bar su a baya ba, an yi kira a garesu da su himmatu wajen samo wata kafa da za a iya nazari a wannan fage don amfanin fagen a ilmance tare da wayar da kan al'umma a bisa ci gaba da ake samu a adabin wasan kwaikwayo na fim.

5.2 Kammalawa

A wannan gavar ce za a kamala wannan bincike ta hanyar zayyano abubuwan da bincike ya gano kamar haka:

Wannan bincike ya ganofina-finan Hausa na taka muhimmiyar rawa wajen yaxa baqin al'adu Hausawa a cikin fina-finan Hausa. Matsalar ita ce ba a bin ainihin tsarin yadda rayuwar Hausawa take na dauri domin isar da saqo ga 'yan kallo. Binciken yana ganin fina-finan Hausa sun zama wata kafa ta yaxa labarai da wayar da kan al'umma.An gano cewar duk da gargaxi da faxakarwa da ke cikin fina-finan Hausa, amma nishaxi da miyagun xabi'u su ne suka fi jan hankalin Jama'a. Wataqila saboda halin qyale da ko-in-kula na baqin al'adu.

Binciken ya gano cewa abin da ya fi shige wa furodusoshi gaba yayin shirya fim shi ne, batun neman kuxi da neman suna, don haka su ne ma'anarsu na qayen fim, ba dacewa ko rashin dacewar al'adu ba. Maisali fina-finai irin su *Gwaska* da *Hotiho* da *Su ma Mata* ne da *Doya Manja*.Haka kuma wannan bincike ya gano cewa, a duk lokacin da aka dace 'yan fim suka dace da labara mai tushen gargajiyar Hausawa sukan shirya fim wanda ya bdace da tsarin rayuwar Hausawa. Misali, idan aka kalli fim xin *Juyin Sarauta da Qafar Ungulu*da *Sarki Jatau* da *Na Hauwa* da *Bori* da *Malam Zalimus*una nuni ne a kan wasutsarin rayuwar Hausawa.

Musayar fasahar 'yan fim na *Kannywood* da na *Nollywood,* ya haifar ko ya taimaka wajen kutsen baqin al'adu a cikin fina-finan Hausawa. Wanann bincike ya iya tantance cewa, fim na Hausa, shi ne, wanda yake cike da al'adu da tadojin Hausawa sannan kuma da harshen Hausa ake isar da shi, misali fim xin *Juyin Sarauta*.

Haka kuma binciken ya tantance cewa, fim da Hausa, shi ne, wanda al'adunsa da tajojinsa suka savawa Hausawa, sai kuma da harshen Hausa aka isar da shi, misali *Gwaska*.

Bugu da qari kuma,binciken ya gano cewa mafi yawa daga fina-finan da ake yi yau, musamman waxanda Furodusoshin 'yan wasansu ba tsantsar Hausawa ba ne, duk fim ne kawai da Hausa amma ban a Hausa ba ne, misali *Su ma Mata ne* da *Doya da Manja.* Misali daga cikin fina-finai guda talatin da biyu da aka nazarta guda biyar ne kawai na Hausa kuma dukkan Furodusoshin da 'yan wasansu tsatsantsar Hausawa ne. Amma daga cikin fina-finai talatin da biyu da aka nazarta guda kusan guda ashirin da takwas ban a tsantsar Hausawa ne Furodusoshin da 'yan wasan ba, don haka shi ya sa suka amsa sunan fina-finai da Hausa.

Wannan bincike ya gano cewa akwai wasu muhimman dalilai da suka yi sanadiyar shigar baqinal'adu a cikin fina-finan Hausa. Misali zamani ya sanya al'adun Hausawa, wanda kuma ya yi matuqar tasiri a cikin zamantakewar Hausawa. Don haka, a duk lokacin da aka tashi shirya fina-finan Hausa, za a so a gina su ne a bisa jigogin da za su ja hankalin jama'a a zamanance ta yadda fim zai sami karvuwa ga jama'a, ya yi suna, sannan a sami kasuwa. Don haka, ba a damu da gina fina-finai a bisa tadojin Hausawa na garagajiya ba, musamman kyawawan al'adu irin su sanya tufafin al'ada da bukukuwan gargajiya da muhallin gargajiya da shugabancin garagjiyada tarbiyya da haquri da kyautayi da amana da ladabi da kara da kawaici da girmamawa da zumunta da sauransu ba.

A wasu lokutan masu shirya fina-finan sukan juya wasu fina-finai waxanda asalinsu ba na Hausa ba ne, ana shigo da su cikin fina-finan Hausa, yin hakan bai rasa nasaba da karvuwar

wani fim da aka yina Indiyawa ko na Turawa a cikin al'umma, wanda asalinsa ba na Hausa ba ne.Don haka, sai masu shirya fim su rinqa tsarma baqin al'adun da ke cikin fim na asali.

Sannan wani abu da yake qara assasa samar dafina-finaidaHausa shi ne yawa-yawan masu shirya fina-finan Hausa ba Hausawa ba ne, don haka al'adarsu takan yi tasiri a cikin fina-finan Hausa, ko dai a cikin qullin labarin da aka yi amfani da shi wajen shirya fim ko kuma aiwatarwa, wasu lokuta da dama al'adun furodusa ko daraktan, waxanda akasarinsu ba Bahaushe ba ne yakan yi tasiri a cikin fina-finan Hausa, tamkar yadda ya bayyana a fim mai suna *"Gabas*" an nuna wata baquwar al'ada wadda ba a san Bahaushe da ita ba, Uba ne ya yi wa 'yarsa miji, amma sai ta qeqesa qasa kai tsaye ta nuna atafau ita fa ba ta son wannan miji, har ta kai tana gaya wa uban nata maganganu. Al'adar Bahaushe kuwa ya dace ne ta je ta sanar da mahaifiyarta ko kawunta ko goggonta don a san yadda za a sami maslaha, ko kuma ta gudu zuwa gidan wata innarta, amma ba ta fito ido da ido tana hayaniya da mahaifinta ba. Haka idan aka kalli fina-finan Hausa a shekarun baya na wani Mr Tunji da ya yi, ga duk mai nazari yana kallon qullin labarin za a ga vurvushin wasu al'adu Yarbawa waxanda ba a san Bahaushe da su ba.Waxannan fina-finan da Mr Tunji Bayarabe ya yi su ne "*Uwar gida*" da "*Albarka*" wato kana kallon labarin za ka san tushensa ba za ta yiwu a qasar Hausa ba. Don an nuna wasu xabi'u da al'adu waxanda ba a san Bahaushe da su ba, kuma ga shi fim yana amsa sunansa da fim xin Hausa.

Tawayar al'adu a fina-finan Hausa wuqa ce mai kaifi biyu, kodayake fina-finan farko sun qoqarta wajen gina jigoginsu a kan kyawawan tadojin Hausawa, amma waxanda ake yi yanzu

ana yin su ne domin neman kuxi “kasuwanci”. A fagen al’ada akwai kwamacala domin al’adar Huasawa ta yi wani wuri fina-finan sun yi wani fage daban. Misali sai a ga an juya baya ana magana da mutuma fina-finai da Hausa wanda kuma al’adu ne amma a al’adar Indiyawa, a al’adar Bahaushe gaba da gaba ake yi in ana magana.Haka kuma a kalli fim xin *“Yankin Imani”* a inda waimutum yana zaune wuri guda da mata da ‘ya’yansa da surukansu duka a kan kujera xaya,yaron ma sanye da baqin gilashi ana taxi. Wannan ba al’adar Bahaushe ba ce.

Bincike yana ganin lokaci ya yi da ya kamata a dinga wayarwa da al’ummomin Nijeriya kai har ma ga waxanda ba Hausawa ba ta hanyar finan-finan Hausa, da waxanda suke maqwabtan Nijeriya ta shigo da are-aren al’adu da harshe daga wasu al’ummomi zuwa cikin fina-finan Hausa domin a nuna dangantakar waccan al’ummar da ta Bahaushe: Misali, idan abokan wasa ne kamar yadda aka sani tsakanin Nufawa da Katsinawa, da Yarbawa da Gobirawa da Barebari da Fulani,wanda ta dalilin fim ne za a iya fito da wasu al’adu da aka qulla a tsakanin al’ummomin nan, kuma a qoqarin yin haka za a iya samun sakamakon are-aren al’adu da harshe a cikin fim domin za a iya samun haxakar ko nason wata al’ada a cikin fim, don labarin ba an qulla shi ne a kan Bahaushe ba ne kawai. Wataqila kuma, matsalar da ta assasa shirya fim xin ba ta samo asali daga Hausa ba ne, tana iya kasancewa daga wata al’umma ce maqwabciyar ta Hausawa, kuma ga shi ana so a shirya shi cikin harshen Hausa don a isar da wani saqo ga Bahaushe. Don haka, dole sai an shigo da tsarin baqon harshe da xabi’unsa don a samu yadda ake so, ko kuma wata shigarsu, wato tufafin na wata baquwar al’umma wacce ba ta Hausa ba, kamar irin kwalliyarsu da kixa da waqa da sauran abubuwan da zai iya jawo hankalin mai kallo. Yadda aka gani a fina-finaiirin su *Ahlil Kitabi* da *Gwaska* da *Su ma Mata ne*, fina-finai ne waxanda aka yi su da Hausa kawai, amma ba sa wakiltar tadojin Hausawa.

5.3 Shawarwari

A yanzu al'ummarmu ana cikin wani qarni, da al'adunta na gargargajiya na dakushewa musamman ga matasa, wannan ba zai rasa nasaba da yanayin sauyin rayuwa da qara dunqulewar duniya da aka samu *globalization* wanda ba ta bar al'ummar Hausa a baya ba. Kuma wannan sauyin yana yi wa al'ummar Hausawa barazana wajen dakushe al'adunta da kyawawan xabi'unmu na gargajiya. Wannan guguwar ba ta bar fina-finan Hausa a baya ba. Amma kuma duk da haka fina-finan na iya dawo da wannan kyakkywar martabar al'adun Hausawa idan aka miqe tsaye. Don haka, za a iya tallafa wa al'ummar Hausawa wajen dawo da martabar al'adun Hausawa, domin fim dai yanzu gidan kowa akwai shi, kuma ya ratsa ciki da wajen al'ummar Hausawa. Don haka, wannan bincike na kira da babbar murya ga furodusoshi da a sake duba, a ga yadda ake shirya fina-finan Hausa ta yadda za a dinga karantarwa tare da jawo hankulan al'umma ta nuna yadda tsarin suturunmu suke da cimaka da muhalli da harshe da xabi'u da yanayin zamantakewa da duk wasu jigogi da za su amsa kyawawan al'adun Hausawa a cikin fim.

Wannan bincike ya ba da wasu hanyoyi da za iya tantance fina-finan da za iya cewa ba na Hausa ba ne, amma dai suna amsa sunan fina-finan Hausa. Sannan an ba da misalai na wasu fina-finan waxanda na Hausa ne. Kamar dai yadda masu iya magana suka ce, "kowane tsuntsu kukan gidan su yake yi." Ya kamata a ce masu yin fim na Hausa su san Hausawa Musulmai suka fi kallon fim xin. Ba wai don kana shirya fim da Hausa ka xauko tsari da salo irin na

turawa, ko Indiyawa ka ce da irin shi za ka yi fim xinka ba. In ka yi haka baka yi fim na Hausa ba, ka yi fim dai da ake magana da Hausa kawai. Kuma irin haka shi ne ya sa har yanzu qasarmu da sauran qasashen Afirka ba mu ci gaba ba, saboda ba mu da tsari ko tunani namu na kanmu sai na turawa. A nan ba ana nufin kar a yi koyi da Turawa ba a wasu abubuwa ba ne gaba xaya, a'a, in mai kyau ne da zai kawo mana ci gaba da inganta rayuwarmu wanda bai ci karo da al'adummu ba addininmu ba, to in za mu yi koyi da Turawan sai mu yi shi a bisa zubi da tsari irin na addininmu da al'adunmu masu kyau. Ba yadda kawai abu ya zo mana daga turuwa mu ce da hakan za mu yi koyi kai tsaye ba, in mun yi haka ba mu waye ba, mun nuna jahilcinmu a fili da qauyanci. Ba zai tava yiwu wa a ce matsalan gidan wane a ce irin naka ne, sai dai ya yi kama.

Abin da kullum 'yan fim ba su fahimta ba shi ne, idan aka ce masu a yi fim mai nuna al'adar Bahaushe, sai su ce ai yanzu Bahaushe ba ya gidan bukka ko bunu, ba ya cin dambu, wannan yana gwada zurfin raunin jahilcin mai magana. Abin da ya kamata a duba a nan shi ne ta ya ya za a yi fina-finan Hausa su koma tushen al'adar Hausawa ta asali ne, ta yadda ko da an yi fim xin ba wanda zai kushe sai dai a yaba, duk da an san yanzu kusan rayuwar aron aro aka yi, idan aka je gidan kowanne Bahaushe zai yi wuya a ce ai ana tafiyar da tsantsan rayuwar Bahaushe kamar yadda take, ko a karkaran ma da ake ganin nan ake xan samun tsarin rayuwar al'adar Hausawa tun na dauri, nan xin ma abin da kamar wuya.

Irin raye-rayen da ake yi tsakanin mace baliga da saurayi, kowa ya san ya savawa al'adar Bahaushe balle addinin Musulunci. Wai shin dole ne fim na Hausa ba zai yi kyau ba har sai an sa

irin wannan raye-raye na fitsara da Allah-wadai? Akwai fina-finan da aka yi su da kyau sun amsa sunan su, ya amsu a wurin 'yan kallo. Misali, fina-finai kamar *Bayan Wuya*. Haka akwai waqoqi da yawa da aka yi suka yi daxi ba tare da an yi rawa ba; kamar a fim xin *Wasila*waqar," *Jamilu-Jamuluna*." *Sangaya* akwai waqar," *Ban da komai kuma ban da kowa*." Haka a fim xin *zarge* akwai waqar," qwan-qwan." duka ba rawa amma sun yi daxi sun amsu wurin jama'a. Ko a fim na *Kumbon So* ita wannan waqar an nuna al'ada sosai ba rashin kunya, ko a gaban surukanka ka iya kallo. Haka a fim xin *Kaddara* na Yakubu Lere waqar," *Ke duniya bia hankali daxinta sai an sha wuya*da *Maigidana Malmo*. Misali, ga fim xin *Garin mu da zafi*wakar," *Dawo-Dawo*." Ba rashin kunya ba fitsara, ta amsu gun 'yan kallo. Wani rawa da ake yi a fim na Hausa ko Kiristoci a Coci ba sa irin sa. Misali, a cikin fim xin *Sai Wataran*a waqar," *Ban kwana muke wa juna*," A cikin waqar ita tauraruwar ta kwanta rigingine, babban jarumin fim xin ya zo ya tsuguna gabanta yana rera mata waqa irin ta masoya. Don Allah, dole ne sai an yi haka a waqar sannan za ta yi daxi da kyau? Kawai don an ga Indiyawa suna haka, sai a aro bayan addini da al'ada ba iri xaya ba ne? Wani lokaci ana fakewa da cewa rawa da waqa al'adar Bashaushe ce, shi ya sa ake rawa. To, me ya sa 'yan Kudu a fim irin nasu ba rawa da waqa irin yadda ake yi a fina-fina Hausa? An san ko in gadon rawa ne sun gada. Za ka ya samun uwa da uba da Siriki da ‘ya da yaye suna cashewa, me ya sa ba sa jin kunyar juna domin yawancin ba Musulmai ba ne, in kuma da Musulmai ne cikin su to, ai su ba Hausawa ba ne.

Ana kira ga masu bincike a wannan fage da manazarta da malamai waxanda suke karantar wa da nazarin adabi a Jami’o’i da kwalejoji ce wa bai kamata a ce su ma suna qyamar fim ba. Tun da dai abu ne da yake da alaqa da kai, domin fim tasirinsa ya fi na likita. Wato ko an qyamace shi a gidanka, to amma dai yana nan cikin al’ummarka yana yawo, ko a maqwabta ko a

makarantarka. Don haka, a haxa qarfi da qarfe a gyara inda yake buqatar gyara a harkar. Domin fim yakan iya bin mutum har cikin uwar xaka duk da ana qyamarsa, wato akwai shi *dvd ko cd ko bidiyo* ko waya da satilat, da mata da yara za su kalla. Don haka, sai kowa ya yi hovvasa don a gyara abin ta yadda zai yi daidai da al'adunmu, don haka sai kowa yanzu ya shiga ciki ya gano shin me fim yake yi a gidana, shin yana taka rawar da ya dace a gidana ko kuwa akasin haka ne?In ko akasin ne, sai a yi gyara ta amfani da shawara da wannan bincike ya bayar. Amma bai kamata kowanne Hausawa xan boko ya dinga cewa ba ruwansa da fim. Don fim yana da tasiri sosai a ciki al'umma.

Fina-finan Hausa ba su cika fito da abubuwa na haqiqa ba, wato *realism* , wato ainihin al'amuran da suke faruwa a cikin al'ummar Hausawa, idan aka kwatanta su da fina-finan Hollywood da Yoruba da kuma na Inyamurai. Don haka, ya zama wajibi ga masu shirya fim su dinga qoqarin yin qirqirar nasu labarin, labarin na iya kasancewa abu ne da ya faru a zahirin rayuwa ko kuma akasin hakan, amma ko da yaushe a ce fim xin Hausa sai dai a dinga xauko labarin Indiyawa da Larabawa da Sinawa ana shirya fim a kan su, yin hakan zai iya hana mu bunqasa da ci gaba a harkar.

Jahilcin rashin sanin ilimi makamar fim a masana'arta fim ta Hausa yana yi wa 'yan fim illa da masu shirya shi. Ilimi haske ne, kuma an ce ko da kana da kyau ka qara da wanka, don haka ya kamata ilimi ya zo ya mamaye masana'antar fim, ta hakan za a samu cigaba a harkar. Sai ka ga mutum rana guda ya faxa harkar shirya fim, wadda a qarshe in an kammala shi, sai ka ji ana cewa, kai dai a yi sha'ani kawai, don ba za a ga armashi ba.

A wata hira da wannan bincike ya yi da AlKanawy da Shaihin Malami Abdallah Uba Adamu sun ce tun a shekarar 2012-2015 an gano Jami'o'i a qalla guda 47 a duniya sun tsunduma fagen nazarin fina-finan Hausa yanzu. Wannan ko ba ya rasa nasaba da rubuta matsaloli da ci gaba da ake tattaunawa a kan fina-finan Hausa a tarukan qarawa juna ilimi a cikin da wajen qasar nan suke yi, kuma ake jefa su a Intanat har al'ummar duniya suka gano cewar ai lallai masana'artar fim tana bunqasa. To don haka wannan bincike yana kira ga dukkan ma su hannu da shuni a cikin al'ummarmu, su zo su tallafawa wannan fage na fina-finan Hausa ta yadda za a samu ya bunqasa sosai.

Wata babbar matsala da ke ci ma fina-finan Hausa tuwo a qwarya ita ce satar kwafar ko juya fina-finai da wasu mutane sukan sake buga su domin saida wa jama'a bila addadin ba tare da izinin mai haqqin mallaka ba.Sannan babu tsari a yadda ake samar da fina-finan kowa ya sami 'yan kuxi burinsa ya samar da fim domin ya sami qwandala.

Ci gaban da fina-finan Hausa suka samu sun haxa da zuwa tarukan bita na ilimi a qasashen duniya, irin su Kanada da Amiruka da Birtaniya da Koreshiya, inda akan yi koyarwa ta haxaka *master class* yawancifina-finan haxaka takan xaga martabar fina-finan Hausa a idon duniya. Haxaka yakan xaga martabar fina-finan Hausa 'yan Arewa dalilin da ya sa akan shigo da baqi cikin fina-finan Hausa shi ne an tarbiyanci Bahaushe da son jama'a a cikin al'adarsa. Bahaushe yana ganin a matsayinsa na mutum ba ya qyamar su, sai dai in su ne suke kyamarmu qabilanci akwai ba babu ba, amma a ta dalilin fim za iya nuna wa al'umma illar sa

sannan a nuna fifikon ko alfanun zaman tare, domin a halin yanzu har ta kai waxanda ba Hausawa ba suna shiga harkar fim ana dama wa da su.

Hamisu Iyantama ya ce a yanzu Inyamurai kamar su Mr I. K. Moor da Yarbawa irin su Mr Yemi wanda aka fi sani da mai kamfanin *Y. Films* suna xaukar nauyin fina-finan Hausa da shiryawa har ma sukan ba da umurni. Amma babbar matsalar, ita ce sukan zo da labarin da yake asalinsa ba Bahaushen labari ba ne, a haka za a xaura kuma a shirya fim a kai, sai daga baya fim ya fito sai a ga ai ya yi bambarakwai. Hakan ya faru nedomin tun asalin labarin bai xauke da al'adar Bahaushe, don haka aiwatarwar ma ba za ta nuna ainihin al'adar Bahaushe ba.

Wannan bincike yana mai ba da shawarar za a iya havaka harkar fina-finan Hausa ta neman ilmin harkar fim kamar yadda takwarorinsu na Kudancin qasar nan suke yi. Wato, tun daga kan masu shirya fim wato furodusoshi da daraktoci ya kamata a koma makaranta domin a sami ilmin qwarewa a harkar shiyawa da samar da fina-finan Hausa. Misali, akwai makarantar koyar da aikin shirya fim da ke Legas da makarantar koyar da aikin talabijin, Jos. Hatta Jami'o'in qasar nan akwai sashen aikin koyar da harkar wasan kwaikwayo da na nazarin fina-finai an buxe xaya a Jami'ar Bayero, Kano, ina kira ga 'yan *Hausa Film Industry* su koma domin a samu ilmin sana'ar.

Wata gudummawar da fim yake ba da wa shi ne ta fagen zamantakewar al'umma da kuma ta fuskar addini. Ta hanyar fim a kan xauki Hadisai na Manzon Allah, Sallahu Alaihi Wasallam,

a xora bisa tafarkin koyarwar Addinin Islam. Misali fina-finai irin su "Ahalulkitabi da *'Yankin Imani*" da *"Ga Duhu ga Haske"* Hausawa Musulmai sukan qaru da karantarwar addinin Musulunci a dalilin kallon fina-finan Hausa.

MANAZARTA

Abbas, U. A. (2008). "Sassarquwar Adabi Cikin Adabi: Nazarin Adon Harshe a Waqoqin Fina- finan Hausa". Kundin Digirin Qoli.Kano:Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Abdullahi, B. (2009). "Literature and Economic Derterminism: An Analysis of Some Selected Hausa Plays". Unpblished Ph.D Thesis. Zaria:Department of Nigerian Languages and Cultures, Ahmadu Bello University.

Abdullahi, I.S.S. (2008). "Jiya ba Yau ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa". Kundin Digirin Qoli. Sokoto: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Abdulsalam, R. I. (2016). English Language And Hausa Audience: An Expression in Hausa Home Videosin Muhammed O.Betal (ed*) Nigeria Cinema: Reading Nigerian Motion Pictures.* Ibadan: Spectrum Limited.

Abubakar, I.A. (1998). "Nason Al'adu da Xabi'un Hausawa na Gargajiya Daga Wasu Littattafan Wasan Kwaikwayo". Kundin Digiri na Tsakiya. Kano:Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Adam, S. (2002). "A Study of Challenges Faced by Female Kannywood Producers." Unpublished M. A.Thesis.Kano:Department of Mass Communications,Bayero University.

Adamu, M. (1978). *TheHausa Factor in West African History*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Adamu, M. (2010). *The Major Landmarks in The Hisrory of Hausa Land*. Sokoto: Trans-Arab Publishing Limited

Adamu, M.N. (2002). "Mata a Fina-finan Hausa (1995-2002)" Kundin Digiri na Tsakiya. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jama'ar Bayero.

Adamu, M. T. (1997). *Asalin Hausawa da Harshensu*. Kano: Xan Sarkin Kura Publishers Limited.

Adamu, M. T. (1998). *Aure da Biki a Qasar Hausa*. Kano: Xan-Sarkin Kura Publishers Limited.

Adamu, U.M. (2011). *Sabon Tarihin Asalin Hausawa*. Kaduna: Espee Printing and Advertising.

Ahmad, M. (2007). "Baqin Al'adu Cikin Fina-finan Hausa". Kundin Digiri na Tsakiya. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Ahmad, U.B. (1985).*Nau'o'in Wasannin Kwaikwayon Hausawa*. Zaria: Ahmadu Bello Press.

Ahmad, M. (2016). Linguistic Versus Cultural Factors in Mass Media Translation: The Case of Hausa Film in Muhammed O.B et al (ed) *Nigeria Cinema: Reading Nigerian Motion Picture.* Ibadan: Spectrum Limited.

Ahmad, N. (2003). "The Influence of Indigenous and Foriegn Cultures in Hausa HomeVideos*"* in Adamu A.U et al (ed) *Hausa Home Videos:Technologies, Economy And Society.* Kano*:* Gidan Dabino Publishers.

Alhassan, H. Da Wasu. (1982). *Zaman Hausawa*.Zaria: Institute of Education. Ahmadu Bello University.

Ali, A.A. (2008). "Auren Bazawara a Bahaushiyar Al'ada". A Cikin *Huda-huda*. *Journal of Languages*.*Vol.1 No. 1*.Kano: Federal College Education.

Ali, M.U. (2004). Qafuwar Qungiyar Mata Masu Zuba Jarida Shirya Fina-finan Hausa. A Cikin Adamu. A.U da Wasu (Editoci). *Hausa Home Videos: Technology, Economy and Society*. Kano: Gidan Dabino Publishers.

Aliyu, A. (2001). Fagar-Jaji ko Riga-Malam Masallaci. A Cikin Adamu. A.U da Wasu (Editoci). Hausa *Home Videos: Technology, Economy and Society*. Kano: Gidan Dabino Publishers.

Aliyu, I. S. (2015). "Hanya Mai Haxa Zumuntar Dole: Zumuntar Wasan Kwaikwayon Hausa da na Fina-finai".Kaduna: Takardar da Aka Gabatar a Wajen Taron Qarawa Juna Sani, Jami'ar Jaha.

Aliyu, I.S. (2016)."Yanayin `Tir-madalla` Da Sigarsa: Tsokaci Daga Fina-finan Hausa Na Nijeriya". Kundin Digirin Qoli. Sashen Harsuna da Al'adu Afirka, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Al-Kanawy, S.A. (2004). Fina-finan Hausa: Faxakarwa ko Shagaltarwa. A Cikin Adamu. A.U da Wasu (Editoci). *Hausa Home Videos*: *Technology, Economy and Society*. Kano: Gidan Dabino Publishers.

Aminu, H. (1995). "Element of Tragedy in Hausa Literary Drama: A Case Study of *Jatau na Kyallu* and *Kulva na Varna*". Unpublished M.A Thesis.Zaria: Department of Nigerian and African Languages, Ahmadu Bello University.

Aminu, H. (2012). "Raha A Wasan Kwaikwayon Hausa: Kwatancin Wasu Wasannin *Karambana* da Wasu na *Xan Ibro*". Kundin Digiri na Qoli. Zaria:Sashen Harsuna da Al'adun Afrika, Jami'ar Ahmadu Bello.

Appadurai, A. (1996). *Modernity at Large: Cultural Dimensions and Globalization*. Minneapolis: Univ**e**rsity of Minnesota Press.

Bargery, G. P. (1934). *A Hausa English Dictionary and English Hausa Vocabulary.* London: Oxford University Press.

Barth, O. (2011). Cultural Research and Report Writing. In Obafemi and Oyo Koromi, B. et al (ed).*Perspectiveson Cultural Administration in Nigeria*, Ibadan: Craft Book Limited.

Bichi, A.Y. (1979). Cultural Reflection In Hausa Folklore: An Introducton. A Cikin *Harsunan Nijeriya*. Kano: Bayero University.

Birni Y.S. (2013). Matsayin Ajami Wajen Adana Al'adun Hausawa. *Excerpts of International Seminar. The Deterioration of Hausa Culture.* Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Buba, M. Da Gidan Dabino, A.A. (2004). Adabi Mai Tafiya: Waiwaye a Kan Fasahar Mai da Littafi Zuwa Fim. In Adamu. A.U et al (Ed). *Hausa Home Videos: Technology, Economy and Society*. Kano: Gidan Dabino Publishers.

Bunza, A.M. (2002). “Nazarin Al’adun da ke Cikin Kaset-Kaset na Hausa da Littafan Zamani (1980-2002). “Maqalar da aka Gabatar a Taron Qarawa Juna Sani. Sokoto: Jami’ar Usmanu Xanfodiyo.

Bunza, A.M. (2006). *Gadon Fexe Al’ada.* Lagos: Tawal Nigeria Limited.

Buratai, M.I.U. (2011). Cultural Industry And Development In Nigeri.In Obafemi, O. and Aya Koroma, B. et al (Ed).*Perspectives on Cultural Administration in Nigeria.*Ibadan: Craft Books Limited.

Chamo, I.Y. (2003). “Tasirin Al’adun Turawa A Cikin Fina-finan Hausa”. In Adamu A.U (Eds) *Hausa Home Videos: Technology, Economy and Society.* Kano*:* Gidan Dabino Publishers.

Chamo, I.Y. (2012). “The Changing Code of Communication in Hausa Films”. Unpublished Ph.D Thesis. Poland: Department of Oriental Studies, University of Warsaw.

Chamo, Y.I. (2004). Tasirin Al’adun Turawa a Cikin Fina-finan Hausa A Cikin Adamu. A.U da Wasu (Editoci). *Hausa Home Videos: Technology, Economy and Society*, Kano: Gidan Dabino Publishers.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, (2006). *Qamusun Hausa*. Kano: Jami’ar Bayero.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, (1981). *Rayuwar Hausawa*. Kano: Thomas Nelson Nigeria Limited.

Danjuma, A.H. (2004). “Brief History of Drama in Northern Nigeria” In Adamu A.U et al (ed) *Hausa Home Videos: Technologies, Economy and Society.* Kano: Gidan Dabino Publishers.

Dangulbi, R.A. (2013). Tasirin Baqin Al’adun ga Tarvarvarewar Tarbiyya da Zumunta A Zamantakewar Hausawa a Yau.a Cikin *Tavarvarewar Al’adun Hausawa*. Zaria:Ahmadu Bello University Press.

Dutsin-ma, L.A. (2008). “Tarbiyya a Al’adun Hausa Domin Ginin Qasa: Xauki Daga Littattafan Zube Na Hausa” A Cikin *Huda-HudaJournal of LanguagesVol. I No.1*.Kano: Federal College Education, Pmarts Press.

Xakin-Gari, A.A. (2004). “Bidiyon Kasuwar Kano: Tasirin Fina-finan Hausa A kan Al’adun Hausawa; Tsokaci a Kan Harshe, Sutura, Tarbiyya, Addini da Kuma Zaman Aure”. Sokoto: Kundin Digirin Farko, Jami’ar Usmanu Xanfodiyo.

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa.* Zaria: Amana Publishers.

Emmitt, M. and Pollock.J. (1997). *Language And Learning: An Introduction For Teaching*. Australia: Oxford University Press.

Funtua, A I. (2010). *Abincin Hausawa Da Fulani Na Gargajiya*.Kaduna: El-Abbas Printers and Media Concepts.

Furniss, G. L.(2003). “Hausa Popular Literature and Video Film: The Rapid Rise of Cultural Production in Time of Economic Decline” Germany: Department of Anthropology and African Studies, Johannesburg University.

Furnnis, G. (1996). *Poetry, Prose And Popular Culture In Hausa*. London: Edinburgh University Press Limited.

Gandu, I. M. (2006). “Tasirin Fina-finan Indiya a Kan na Hausa”. Kundin Digirin Tsakiya. Sakkwato:Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Usman Xanfodiyo.

Garba, C.Y. (1978). “Socio-Linguistic Implications of the Oral Transmission of Hausa Culture” In Yahaya I.Y et al (ed) In *Hausa Language, Literature and Culture*. Kano: Bayero University.

Garba, C.Y. (1984). *Nazarin Hausa*. Lagos: Nelson Pitman Limited.

Garba, C.Y. (1991). *Sana’o’in Gargajiya A Qasar Hausa*. Kano: Nelson Publishers.

Garba, S. (1993). “Al’adun Mutuwa A Garin Kargi”. Kundin Digiri na Farko. Zaria:Sashen Harsunan Nijeriya da Al’adun Afirka. Jami’ar Ahmadu Bello.

Giwa, T.A. (2016). Orality, Cultural Identity and Social Responsible in Africa Motion Picture in the Film Naira, *in Muhammed O.Bet al (ed) Nigeria Cinema. Reading Nigerian Motion pictures.* Ibadan: Spectrum Limited.

Gusau, G.U. (2007).“Tasirin Al’adun Hausawa a Kan Makarantun Allo a Zamfara; Nazari A Kan Wasu Al’adu da Suka Danganci Karatu da Mu’amala da Harshe”. Kundin Digiri Na Tsakiya. Sokoto: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Usmanu Xanfodiyo.

Gusau, S. M. (1999). Tarbiya A Idon Bahaushe. In *Hausa Studies.Vol.I No. I.* Sokoto: Usmanu Danfodiyo University.

Gusau, S. M. (2005).*Mawaqa da Makaxan Hausa*. Kano: Benchmark Publishers.

Gusau, S. M. (2008). “Jirwayen Cimakar Hausawa Ta Gargajiya a Cikin Waqoqin Baka”.Sakkwato:Takardar da aka Gabatar A Wajen Taron Qara wa Juna Sani a Kwalejin Ilmi ta Shehu Shagari.

Gusau, S.M. (2008). *Waqoqin Baka a Qasar Hausa: Yanaye-yanayensu Da Sigoginsu.* Kano: Benchmark Publishers.

Gusau, S. M. (2012). “Al’adun Hausawa da Wasu Hanyoyi na Bunqasa su”. Katsina: Takardar da aka Gabatar a Wajen Bikin Al’adun Hausawa da Fulani. Kwalejin Ilimi ta Tarayya.

Haralambos, M. & Holborn, M. (2013). *Sociology: Themes and Perspectives8th Edition*. London: Collins Publishers.

Hauwa, A.I. (2013).*"Bunqasar Rubutun Zube na Hausa Zuwa Faifan Bidiyo".* Paper Presented at 9th Annual Conference Organized by School of Languages. Kano: Federal College of Education.

Ibrahim, B. (2004). Hoton Mata Cikin Fina-finan Hausa: Tsokaci Tsakanin Al'ada da Zamani. A Cikin Adamu. A.U da Wasu. (Editoci). *Hausa Home Videos: Technology, Economy and Society*. Kano: Gidan Dabino Publishers.

Ibrahim, S. (2013).Bunqasar Harshen Tallar Hajojin Gargajiya a Yau. *The Deterioration of Hausa Culture*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ibrahim, M. S. (1978). Are-aren Kalmomi Cikin Hausa. in Yahaya, I.Y. and Rufa'i, A. et al (ed.). *Hausa Language, Litearature and Culture*. Kano: The First Hausa International Conference, Bayero University.

Ibrahim, M. S. (1982). "Dangantakar Al'ada da Addini; Tasirin Musulunci Kan Rayuwa

Hausawa". Kundin Digiri Na Tsakiya. Kano:Sashen Harsunan Nijeriya.Jami'ar Bayero

University.

Inuwa, U.A (2000). "Tarbiyya Cikin Fina-finan Wasannin Kwaikwayo na Hausa". Kundin Digiri na Tsakiya. Kano: Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Bayero.

Inuwa, U.A (2009). "Kutsen Baqin Al'adu a Fina-finan Hausa." Kundin Digirin Qoli.Kano: Sashen Harsunan Nijeriya,Jami'ar Bayero.

Isa, M.B. (2013). Gudunmawar Adabi ga Bunqasar Dimokuraxiyya a Nijeriya: Tsokaci a Kan Rubutattun Waqoqin Hausa. A Cikin *Studies in Hausa Language, Literature And Cultures*.Kano: Centre for the Study of Nigeria Languages, Bayero University.

Idris Y. (2013). Lalacewar Tarbiyya a Yau: Tsokaci daga "Waqar Yaki da Rashin Tarbiyya da Rashawa" Ta Alkali Alhaji Halliru Wurno. A Cikin *Tavarvarewar Al'adun Hausawa* Zaria:Ahmadu Bello University Press.

Iyan-Tama, L.H. (2011).*Majigi: Shirin Fim A Sauqaqe*. Kano: Iyantama Multimedia.

Iyan-Tama, L.H. (2004). Matsayin Fina-finan Hausa a Musulunci. A Cikin Adamu. A.U da Wasu. (Editoci). *Hausa Home Videos: Technology, Economy and Society* Kano: Gidan Dabino Publishers.

Jaja, M.B. (2008). "Hausa da Hausawa a Wajen Qasar Hausa: Tsokaci Daga Sabo Ibadan". Kundin Digiri na Tsakiya. Sashen Harsunan Najeriya, Sokoto: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Johson, D. (1997). Culture and Art In Hausa Video Films. in J. Haynes (ed) *Nigerian Video Films.* Ohio University Centre For International Studies

Junaidu, I. Da Wani. (2007). *Harshe Da Adabin Hausa A Kammale*. Ibadan: Spectrum Books Limited.

Keesing, R. M. (1976). *Cultural Anthropology A Contemporary Perspective*. London: Second Edition. Savaders College Publishing Company.

Khalid, S. (1999). Almajirci: A Hausa Cultural Phenomenon. In *Hausa Studies*. *Vol.1 No.1*Sokoto:Department of Nigerian Languages, Usman Danfodio University.

Kofoworola, E.O (1978). "A Comparative Analysis of the Development of Drama. Movies". Unpublish M.A. Thesis,Zaria: Department Of Theatre And Performing Art, Ahmadu Bello University.

Kulumbu, M.S. (2006). "Girman Asali Yana ga Al'ada: Nazarin Al'adun Hausawa Na Gargajiya". A Cikin *Gwani Academic Journal.*Misau: A Publication of A.D Rufa'i College for Legal and Islamic Studies.

Kurfi, Y.M. (2016). From Book to Film Adaptation of Story of "Bawa mai Qusumbi" in *Magana Jari Ce* To Television Serial Drama. in Muhammed O.B (Ed) *Nigeria Cinema. Reading Nigerian Motion Pictures.* Ibadan*:* Spectrum Limited.

Kwantagora, I. A. (1999). Asirin Sammu A Idon Bahaushe. In *Hausa Studies,*V*ol. I No. I.*Sokoto:Department Of Nigerian Languages,Usman Xanfodio University.

Lawal, Nuhu (2011) Wasu Al'adun Hausawa a Mahangar Waqoqin Baka na Hausa.Abuja: Century Research and Publishing Limited.

Liman, A.A. (2016). Textual Fluidity, Adaptation and Representation: The Transposition of Selected Hausa Folktales into Cinema.in Muhammed O.B. (ed) *Nigeria Cinema: Reading Nigerian Motion pictures.* Ibadan: Spectrum Limited.

Ibrahim, M. Da Wasu. (1982). *Hausa Costumes*. Zaria: Northen Nigeria Publishing Company.

Magaji, A. (1999). Kunya da Mutunta Mutane A Al'adar Bahaushe. In *Hausa Studies.*Sokoto: Department of Nigerian Languages, Usman Danfodiyo University.

Magaji, A. (2002). Dubu Da Tambarci: Wasu Bukukuwan Hausawa na Gargajiya. *Mujjalar Fasaha*. Sokoto:Jami'ar Usman Xanfodiyo.

Magaji, A. (2013). Harshe Tubalin Ginin Al'ada: Nazari A Kan Gidajen Rediyo. in The *Detarioration of Hausa Culture*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Mandawari, I. (2004). Tarihi da Turawa a Cikin Fina-finan Hausa. A Cikin Adamu. A.U da Wasu. *Hausa Home Videos: Technology, Economy and Society*. Kano: Gidan Dabino Publishers .

Mijinyawa, S. (2015). Language Preservation in Selected Songs of Ala. In *Kadaura Journal of Hausa Multi Disciplinary Studies.* Kaduna: Winners Printing Company.

Mohammed, A. (2004). Siyasar Duniya ta Harkar Fim Yaya ta Shafi Bahaushe? A Cikin Adamu. A.U da wasu. (Editoci) *Hausa Home Videos: Technology, Economy and Society*. Kano: Gidan Dabino Publishers.

Mu'azu, A. (2008). Matsayin Baqin Al'adua Qagaggun Labaran Hausa. A Cikin *Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies*.*Vol. I. No.1*.Kano: Department of Nigerian Languages. Bayero University.

Mu'azu, A. (2006). "Tasirin Baqin Al'adu a Kagaggun Labaran Soyayya Na Hausa". Kundin Digiri Na Qoli. Kano:Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Mu'azu, A. and Shehu, A. (2016). Traditional Religious and Super Situation in Some Kannywood Films. Muhammed, O.B.(Ed) *Nigeria Cinema. Reading Nigerian Motion Pictures.* Ibadan: Spectrum Limited

Muhammed, A.B. (2004). *Harshe Da Al'adun Hausawa*. Kano: Ayyub. Press.

Muhammad S.A. (2013).*Al'adar Nasaba a Waqoqin Baka Jiya da Jau: Cigaba Ko Ci Baya*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Muhammed, Y. M. (2011). *Hausa A Yau*. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Nwogu, L.I (2007). "Cultural Promotion and Image Portrayal in the Nigerian Home Vedio. M.A Dessertation. Submmited to the Department of Theater and Performing Arts. Zaria: Ahmadu Bello University.

Obidi, S.S. (2005). *Culture and Educationin Nigeria: An Historical Analysis*. Ibadan: University Press PLC.

Pawlak, N. (2002). *Hausa Outside the Mother Area Plateau Variety*. Poland: Academic Publishing House Dialog Warszawa.

Rambo, R.A. (2007). "Nazarin A Kan Wasu Kevavvun Al'adun Auren Hausawa Da Na Dakarkari". Kundin Digiri Na Tsakiya. Sakkwato: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Safana, A.B. (2000). "Wanzanci; Matsayinsa Na Al'ada Da Sana'a A Qasar Hausa". Kundin Digiri Na Tsakiya. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Sayaya S.A (2013). Gudummuwar Farauta ga Raya Al'ada da Adabin Hausawa.*The Deterioration of Hausa Culture*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Shehu, I. (2005)."Tasirin Harshe a Wasan Kwaikwayon Jami'ar Jatau Na Albarkawa". Kundin Digiri na Tsakiya,Zaria: Sashen Harsunan Nijeriya da Al'adun Afirka,Jami'ar Ahmadu Bello.

Smith, A. (1983). A Little New Light on the Collapse of the Alafinate of Yoruba. in Olusanya, G.O. (Ed) Studies In *Yoruba History and Culture*. Ibadan: University Press Limited.

Smith, A. (1987). *A Little New Light: Selected Historical Writings of Abdullahi Smith*. Ibadan: University Press Limited.

Sulaiman, A.I. (2017).“Fina-finan Hausa A Qarni Na Ashirin Da Xaya:Wani Mashigi Na Tantance Fina-finan Hausa, Da Fina-finai Da Hausa”. Kaduna: Takardar Da Aka Gabatar A Wurin Taron Qarawa Juna Ilmi.Karo na UKu,Sashen Harsunan Nijeria Da Ilimin Harshe, Jami’ar Jiha.

Sulaiman, H.A. (1990). “Tsagar Gargajiya A Qasar Kano Nazarin Ire-iren Tsaga Da Muhimmancinsu Tare Da Matsayinsu Ga Al’ummar Hausawa”. Kundin Digiri Na Tsakiya.Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Tanko, A.A. (2000). “Tasirin Harshe Da Al’adun Hausawa A Kan Gwarawa”. Kundin Digiri

Na Tsakiya. Kano:Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Uba, A.O. (2007). The Role of Hausa Culture In Intellectual Development. *Journal of School of Languages.. Vol. 3: No.1*.Ondo: Adeyemi College of Education.

Umar, H. (2004). “Tasirin Al’adun Hausawa A Kan Na Dakarkari (1800-2000)”. Kundin Digiri Na Tsakiya. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Umar, M.B. (1987). *Dangantakar Adabin Baka da Al’adun Gargajiya*. Kano: Triumph PublishingCompany.

Usman, A.K. (2016). Women Against Women: Stereo Typical Depiction of Co-wives in Xakin Amarya. In Muhammed O.B et al (ed). *Nigeria Cinema: Reading Nigerian Motion Pictures.* Ibadan: Spectrum Limited.

Waya, Z.I. (2008). Yaxuwar Hausawa Da Al’adunsu Dangane Da Aikin Hajji. In *Algaita Journal Of Current Research In Hausa Studies.Series IV. No 1*. Kano: Department of Nigerian Languages,Bayero University.

Williams, I.S. (2008). “Kwatanci Tsakanin Al’adun Hausawa Da Al’adun Tibi”. Kundin Digiri na Tsakiya. Zaria: Sashen Harsuna da Al’adun Afrika. Jami’ar Ahmadu Bello.

Yahaya I. Y. (1986). *Jagoran Nazarin Hausa*. Zariya: Gaskiya Cooporation Limited.

Yahya, A.B. (2001). Dangantakar Waqa Da Tarbiyyar ‘Ya’yan Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriyar*.Kano: Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya,Jami’ar Bayero..

Yahaya, I.Y. (1985). Tsarin Kayan Kixan Hausa Da Muhallan Kaxa Su. A Cikin *Harshe, Adabi da Al’adu*. Kano: Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Yakasai, H.M. (2002). “Masana Al’adun Hausa, Nazari da Tsokaci Kan Gudunmawar Malam Muhammed Sani Ibrahim”. A Cikin *Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies.Vol. 2 No. I.* Kano: Jami’arBayero.

Yakasai, S. A. (2013). Tasirin Fifikon Rubutu da Hanyoyin Sadarwa na Zamani Bisa na Gargajiya Cikin Adana Harshe da Al’adun Hausawa.*Excerpts of International Seminar. The Deterioration of Hausa Cultures.* Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Yakasai, S.A. (2015). Harshen Yaudara a Kafar Sadarwa ta *facebook.* A Cikin *Kadaur*a.*Vol. I No, I.*Kaduna: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Kimiyyar Harshe, Winners Printing Company.

Yakub, R.B. (2004). Gudummuwar da Mata ke Bayarwa a Shirin Fina-finan Hausa A Cikin Adamu. A.U da Wasu. *Hausa Home Videos: Technology, Economy and Society*.Kano: Gidan Dabino Publishers.

Yero, Z. S. (2017).“Hausar Yaran Mota: Nazarin Ma’ana Da Ginin Jimla”. Kundin Digirin Tsakiya. Sashen Harsunada Al’adun Afrika, Zaria: Jami’ar Ahmadu Bello.

Ziky, M. And Lateef, Y (1987). *Hausa Performing Arts and Music*. Zariya: Gaskiya Corparation Limited.

Waxanda Aka yi Hira da Su

Adamu, Abdullahi Zango, shaharren xan wasan Hausa ne, kuma yana kixa da waqa da kuma shiryawa tare ba da umarni a fina-finan Hausa. An yi hira da shi a filin baje koli da ke Kaduna a ranar 20/10/2015. Da misalin qarfe 6:00 na yamma. Xa shekara 36 da Haihuwa. Xan wasan fim na Hausa.

Ado Ahmad Gidan Dabino, xan shekara 52, marubucin qagaggun littattafan Hausa , furodusan fina-finan Hausa kuma an tattauna da shi a gidansa da ke sani mai Nagge, Kano ranar 13/1/2017.

Ahmad, AlKanawi xan shekara 56 ne, yana shirya fina-finan Hausa kuma marubucin fina-finan Hausa ne. An tattauna dashi a Ofishinsa da ke kan titin gidan namun Daji da ke Kano a ranar 30/10/2015 da qarfe 8.45 na dare.

Dr. Ayilara O. Wadda ya taimaka wajen fassara wasu harsunan 'yanwasa daga Yarbanci zuwa Ingilishi waxanda suka bayyana a cikin fina-finai irin su *Su Ma Mata Ne da Gwaska* wannan bincike ya fassara zuwa Hausa. An zauna da shi a lokuta da dama. Malami ne a Sashen Yarbanci , Kwalejin Ilimi ta Tarayya, Zariya.

Aisha, 'Yar Kano, ta shahara a masana'antar fim na Hausa, an yi hira da ita ranar 12/06/2015, a Unguwar Hotoro, Kan Titin Sabo Bakin zuwo, Kano da qarfe 3:45 na yamma tana da Shekara 48 da Haihuwa.

Aliyu, Isa Sulaiman. An tattauna da shi a lokuta mabambanta a Jami'ar Jihar Kaduna da Kwalejin Ilimi ta Tarrayya da ke Zariya a Ranar 4/2/2015 da 8/3/2015 da 12/7/2015.

Aminu, Sharif Momo, xan wasa ne kuma yana gabatar da shirye-shiryen Hausa a gidanTalabijin na Arewa. An tattauna da shi a Gidan Talabijin na Arewa, unguwar Nasarawa, Kano a ranar 13/06/2015. Da qarfe 11: 30 na safe.

Farfesa Balarabe Abdullahi na Sashen Harsunan Afirka da Al'adu. An tattauna da shi a ofishinsa ranar 7/11/2016 da da ke cikin Jami'ar Ahmadu Bello, da qarfe 4:30 na Yamma.

Falalu, Dorayi xan shekara 39, dan wasa ne, yana shirya fim yana kuma ba da umarni, an tattauna da shiranar 20/10/2015 a filin Shirya fim da ke filin baje koli, Kaduna, da qarfe 4:30 na Yamma.

Farfesa Uba Adamu Malami ne a sashen aikin jarida Jami'ar Bayero, Kano. Kuma yanzu shugaban buxaxxiyar Jami'ar Nijeriya, Abuja. An tattauna da shi aSashenaikin Jarida,Jami'ar Bayero, Kano aRanar 6/6/2015 da qarfe 1:30 na Ranar a ofishinsa.

Hamisu Lamixo Iyantama. Xan shekara 50 ne,Manajana kuma Daraktan Iyantama *Multimedia Company* da ke kan titin Sharaxa Kano. An yi hira da shi ranar 2/10/2015.

Hassan Giggs, xan shekara 48 ne, yana ba da Umarni, an tattauna da shi a ofishinsa da ke kan titin gidan Zoo, Kano. An tattauna da shi a ranar 14/10/2015.

Muktar S.S. xan shekara 38 ne, Furodusa kuma Jarumi ne, yana zaune gida mai lamba 132, Joshin gari, Zaria.

Rabi'u Rikadawa, xan shekara 50, xan wasa kuma ma'aikacin GidanRediyo Kaduna. 27/9/2015 a Kwalejin Ilimi ta Tarayya da ke Zariya da qarfe 8:16 na dare.

Shehu Hassan Kano, xan shekara 52, babban xan wasa ne a masana'antar *KennyWood*. An tattauna da shi a Unguwar Hotoro titin Sabo Bakin Zuwo, Kano. A a ranar 12/6/2015 da qarfe 5:00 na yamma.

Umar A. Umar, (Mai Jalingo) xan shekara 37, yana shirya fina-finan Hausa, an yi hira da shi a lokuta da dama, yana zaune a unguwar Zaria.

RATAYE NA XAYA 1

RATAYE NA FINA-FINAN DA AKA NAZARTA

Lamba	**Sunan Fim**	**Shekarar Fim**	**Furodusa**	**Darakta**	**Sunan Kamfani**
1.	Gwaska 1-2	2015	Falalu A. Dorayi	Adam A. Zango	Prince Zango
2.	Anisa	2015	Falalu A. Dorayi	Mu'azamu I. Yari	Yari Film Production
3.	Basarake 1-4	2011	Sani Danja	Yakubu Muhd	2 Effect Empire
4.	Yankin Imani	2013	Tijjani Ibrahim Mai Jama'a	Imran S.I Ashir	Chali Enterprise

5.	Bori	2014	Umar Mai Jalingo	Falalu Dorayi	M .J. Vedio Palace
6.	Haske	2014	Nazifi Asnanic	Aminu Saira	Saira movies
7.	Gagara Gasa	2008	Naziru Civic Centre	Aminu Saira	Malam Kato Intertainment
8.	Ashabul Kahfi	2012	Usman Mu'azu	Aminu Saira	Kabugawa Production
9.	Juyin Sarauta	2017	Rahmat Balaraba	Falalu Xorayi	Rahmat Production
10.	Hajiya Babba 1-4	2015	Naziru Dan Hajiya	Iliyasu Abdulmumin	Barumi Movies
11.	Wuta Sallau	2014	Abdull Amat	Nasiru Ali Koki	Abnur Entertaiment
12.	Maja 1-2	2013	Abba.M. Yakasai	Sadik.M. Mafia	Faidat Production and U.U.C Concept Production
13.	Alkalin Qauye	2015	Ibrahim Muhd	Mu'azamu Idi Yari	17-18-Motion Pictures
14.	Zo Ki Ji	2011	Sani Danja	Yakubu Muhd	2 Effect
15.	Kicimili 1-2	2013	Rabi Lawal Zaria	Abdulhamid Abdulkadir	Rablaj Production
16.	Qara'i	2013	Rabi'u Garga	Hassan Taye Giggs	Garga Production
17.	Doya Da Manja	2017	Umar Mai Jalingo	Falalu Xorayi	M. J. Vedio Palace
18.	Su Ma Mata Ne 1-2	2015	Uzee Concept	Umar S. K/Mazugal	U.K Entertainment
19.	Al-Ajabi	2014	Narizu Dan Hajiya	Aminu Saira	Barumi Movies
20.	Tsintsiya	2007	Hamisu Lamido	Hamisu Lamido	Iyan Tama Multimedia
21.	Qumbar Susa	2012	African Magic	Zahardeen Sani	African Magic
22.	Rumfar Shehu	2015	Ali Gumzak	Muhd MIA	MIA Production
23.	Fansa	2005	Abubakar S. Shehu	Bello Ibrahim	3SP Internation
24.	Dan Marayan Zaki	2013	Aminu Saira	Aminu Saira	Saira Movies
25.	Hindu	2015	Hassan Giggs	Garba Saleh	Flying Bird

					Pro
26.	Hotiho	2012	Umar Mai Jalingo	Falalu Xorayi	M J.Vedio Palace
27.	Malam Zalimu	2011	Kamal S.Alkali	Abdul'Aziz Dan Small	Jaga World
28.	Birnin Masoya	2011	AfricanMagic Hausa	African Magic Hausa	African Magic Hausa
29.	Ruwan Bagaja	2001	Hamisu S. Ruwa	Hamisu S. Ruwa	Multi-Purpose Concept
30.	Dutsen Fata	2005	African Magic Hausa	African Magic Hausa	African Magic Hausa
31	Qafar Ungulu	2004	Sulaiman Abubakar	Sadiq Mansur	Flyin Bird Production
32	Na-Hauwa	2016	Kabiru Ali	Aminu S. Bomo	Meena Investiment

RATAYE NA UKU: TAMBAYOYIN BINCIKE

AHAMAD BELLO UNIVERSITY, ZARIA

DEPARTMENT OF AFRICAN LANGUAGES AND CULTURES.

TAKARDAR NEMAN BAYANI

Ni xalibi ne a Jami'ar Ahmadu Bello ta Zaria, Sashen Nazarin Harsuna da Al'adun Afirka. Ina gudanar da bincike ne na Ilmi a kan fina-finan Hausa mai taken "Fina-finan Hausa NA 2000-2017:Nazarin Yanayinsu da Sigoginsu". Don haka, ina neman a taimaka a bayyana

mini gaskiyar abin da aka sani a kan waxannan tambayoyi da aka yi domin neman qarin bayani a kan wannan aiki. Amsoshin da aka bayar za a yi amfani da su ne kawai domin wannan nazari. Na gode, Allah kuma ya ba da ikon taimakawa, amin.

Ahmad S. Bello

Suna ……..……..

Shekarar Haihuwa……

Sunan Jihar Haihuwa……

Qaramar Hukuma…….....

Sunan Unguwa…….

Jinsi……...

Addini……...

Qabila……

Matsayin Ilmi/ Sana'a…….

Ka/Ki na da aure…….

SASHE NA XAYA

1. Shin fina-finan Hausa, na Hausan ne kuwa? Kawo hujja:

……

2. Lissafo fina-finan Hausa da aka sami sauye-sauyen al'adu da xabi'un Hausa a cikin su:

……

……

3. Waxanne qabilu ne aka fi samun vurvushin al’adunsu a cikin fina-finan Hausa?

……

…….

4. Shin za ka/ki iya fito da sunan Fim da aka sami wasu al’adu da Bahaushiyar al’ada ba ta yarda da su ba?

……

……

5. Me yake haifar da aron al’ada a cikin Fim xin Hausa?

……

……

7.0 Lissafo fina-finan da aka fito da kyawawan al’adun Hausawa:

……

…….

7. Wace matsala ce take addabar masana’antar Fim na Hausa? Ina mafita?

……

……

8. Ko ka yarda za a iya amfani da Fim wajen kyautata rayuwar al’ummar Hausawa?

……

……

9. Ga darajoji guda shida (6), a wace za ka iya xora Fim na Hausa dangane da tunanin Bahaushe:

Darajar A

Darajar B

Darajar C

Darajar D

Darajar E

Daraja F

10.Waxanne dalilai ne suka sa ba a iya tsara fim na Hausa bisa tubalin Bahaushiyar al'ada?

……..

11. Bayyana wasu hanyoyin da ka sani waxanda za su inganta masana'antar Fim na Hausa, su bi tsarin Bahaushiyar al'ada:

……

12. Yaya Fim na Hausa yake a jiya?

……

……

…….

13. Ya ya Fim na Hausa yake a yau?

……

……

……...

14. Wace baquwar al'ada ce ta fara shiga Fim na Hausa?

……

……

……...

15. Waxanne abubuwa ne suke dusashe Fim na Hausa?

……

…….

16. Lissafo fina-finai goma da aka yi amfani da tufafin Hausawa zalla:

……

……

17. Shin akwai wasu qabilu waxanda ba Hausawa ba waxanda sukan shiga harkar Fim na Hausa? Lissafo su da sunayensu:

……

……

…….

18.Daga cikin qabilun da suke aiwatar da fina-finan Hausa, waxanne xabi'insu ne suka fi yin tasiri a fina-finan ?

……

……

19. Waxanne xabi'u ne aka fi qyama a cikin Fim na Hausa?

……

……

……...

20. Fayyace qalubale da masana'antar Fim take fuskanta a yau, Ta yaya za ceto ta?

……

……

21. Waxanne fina-finai ne aka fi yin amfani suturun da ba a san Hausawa da su ba?

……

……

22. A bisa tsari irin ta zamantakewar Bahaushe wane irin tasiri fina-finan Hausa suke yi?

……

……

……

23. Shin tsafi na da gurbi a fina-finan Hausa?

……

……

……...

24. Idan amsar taka “e” ne, ta wuce fuska?

……

……

25. Cikin waxannan hanyoyin ba da magani na gargajiya a fina-finan Hausa, wanne aka fi amfani da shi?

- Tsubbu.
- Rufa-ido.
- Bokanci.
- Malanta

26. Ina matsayin Malaman addini a cikin fina-finan Hausa?

……

……

27. Shin yadda ake aiwatar da bukin al'adun aure a cikin fina-finan Hausa ya da ce da al'ada Bahaushiya?

……

28. Idan amsar 'ee' ce kawo hujja:

……

……

29. Ta yaya fina-finan Hausa suke gurvata al'aummar Hausawa?

……

……

30. Shin fina-finan Hausa suna taka muhimmiyar rawa wajen raya bukukuwan gargajiyar Hausawa? Idan amsarka a'a/ee ce a ba da hujja:

……

TAMBAYOYIN BINCIKE (Oral InterView)

Tsarin tambayoyin da aka yi wa mutanen da za a tattauna da su; Daraktoci da Furodusoshi da ‘Yan Fim, masu aiwatarwa.

1. Yaya sunan malamin?

2. Ina tarihin malamin/malamar?

3. Mene ne addininka?

4. Za mu iya sanin qabilarka?

5. Daga wane gari ka fito kafin ka zo mazaunin da kake a yanzu?

SASHE NA XAYA

1. Ta yaya ka sami kanka cikin wannan masana’antar?

2. Shin wannan masana’anta ta inganta tattalin arzikinka?

3. Shin wane irin ci gaba Fim ya samu dangane da yadda ake shirya shi, da kuma aiwatarwa, mussaman idan aka kwatanta da shekara goma sha-biyar a baya?

4. Shin ana samun kutsen baqin al’adun al’ummomin Nijeriya a cikin fina-finan Hausa?

5. Shin al’ummar Hausawa na amfana da fina-finan Hausa?

SASHE NA BIYU

1. Waxanne dalili ne suke jawo kutse baqin al'adu zuwa cikin fina-finan Hausa?

2. Me za ka iya cewa dangane da yadda fina-finan Hausa kan ari wasu al'adun su shigo da su cikin Fina-finan Hausa?

3. Shin za ka iya lissafa mana wasu nau'o'in fina-finan Hausa masu xauke da wasu al'adu da ba a san Hausawa da su ba?

4. Shin fina-finan Hausan ana wanzar da su ne a bisa tunani irin na Bahaushe?

5. Shin kana ganin fina-finan Hausa suna nuna tsarin zamantakewa irin ta Bahaushe.

SASHE NA BIYU

1. Waxanne dalili ne suke jawo kutse baqin al'adu zuwa cikin fina-finan Hausa?

2. Me za ka iya cewa dangane da yadda fina-finan Hausa kan ari wasu al'adun su shigo da su cikin fina-finan Hausa?

3. Shin za ka iya lissafa mana wasu nau'o'in fina-finan Hausa masu xauke da wasu al'adu da ba a san Hausawa da su ba, wanda ka sani?

4. Shin fina-finan Hausan ana wanzar da su ne a bisa tunani irin na Bahaushe?

5. Shin kana ganin fina-finan Hausa suna nuna tsarin zamantakewa irin ta Bahaushe.